[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJINE SHI□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

Page 1

Bismillahir rahmanir rahim,Ina godiya ga Allah daya bani damar fara wannan littafi ,bayan kammala  littafin soyayyata.Allah kasa yadda na fara lafiya naga bayansa lafiya ameen.

Gargadi banyarda wani ko wata ya juyamin wannnan littafi ta kowace sigar ba.

_____Wata kyakkyawar yarinya na hango sanye da kaya irin na Fulani ,wato rigar saki dakuma zaninta,duka duka rigar da kadan ta wuce cibiyar ta,saidai kuma ta daura zanin ya rufe mata cikinta ta yadda ba wanda zai ga jikinta awaje.

Farace irin mai sirkin yallow -yellow din nan,tana da doguwar fuska mai kyan tsari dauke da dogon siririn hanci har baka,bakinta dan karami kamar gidan tsutsa,tana da irin manyan idanunnan masu kamar tana jin barci,ga gashin ido zara -zara.

Girarta kuwa ,kamar wacce aka dora Mata ita dan saiti,gaban goshinta wasu yan kananan gashine kwance lub lub  kamar na jarirai.

Masha Allah yarinyar ta ko ina ta hadu ,dan doguwace marar jiki saidai fa Allah ya hore mata hips Kai kace wata babbar macece Sannan akwai alamun girma akirjinta , ma'ana dai akwai dukiyar Fulani dasuka fara tasawa akirjin nata.

Duka duka wannan yarinyar bata wuce shekara 15/16 ba ,amma kallo daya zaka yi mata kasan Allah yayi halitta agurin.

Sandace irin ta Fulani ahannunta tana dagawa sama ,da alama tana son hada kan wasu tarin sha'nun dake kiwone wani kayataccen jeji ,dan kuwa ciyawace agurin Kore sharr da ita ,sha'nun suna ta cin abarsu .

Tafiya ta farayi gurin shanun dake dan nesa da ita ,dan ita tana daga jikin wata bishiya ne tana kallon yadda suke kiwo abinsu.

Kanta ta daga ta kalli yadda garin ke hada wani irin hadari baki kirin dashi ,kuma da alama koda yaushe ruwa na iya saukowa.

"Kuzo mu tai gida abokaina kada ruwan nan ya sauko ya taba mu banin son nai mura aradu"

Cikin Yaren fulatanci take musu magana ,tana daga sandarta .aikuwa kamar wanda suke jin me take fadi suka fara yin hanyar gida .

Murmushi tayi tana mai binsu tana kara daga sandarta .

Tafiya suke cikin jajen ita kadai daga ita sai wadannan garken shanun ,sam ba alamun tsoro tattare da ita,yar wakar tama take tana daga sandar sama.

Kusan tafiyar minti biyar sukayi ,sannan na fara hango bukkokinsu  dake can gaba kadan .

AHankali naga duk wani annurin dake kan fuskar yarinyar ya dauke ,nan da nan damuwa ta maye gurbin nishadi da take ,sosai naga jikinta yayi sanyi har suka karasa wata bukka dake farkon rigar  da alama nan ne gidansu.

Garken shanun ta fara zuwa ta daure su  tsaf sannan ta nufi cikin gidan,bakinta dauke da sallama.

Lokacin har anfara yayyafi .

Ba kowa a tsakar gidan nasu ,hakan yasa ta sauke ajiyar zuciya tare da nufar wata bukka cikin sauri.

Saidai kafin ta karasa kofar bukkar aka daka mata wata uwar tsakar da saida sandar hannunta ta fadi kasa.

Afirgice ta juyi jikinta na rawa sosai kamar dan mazari.da sauri ta karaso gurin matar data daka mata tsawar,

"Gani gwagwgo"ta fada cikin rawar murya. Kallon matar nayi sai na tarar da

matar farace saidai kuma kazanta da rashin kulawa yasa tayi wani irin baki baki fari fari,sannan tana da jiki sosai sam fuskar ta ba alamun rahama a cikinta.

Tana tsaye a kofar bukkar ta tana hararar yarinyar dake durkushe gabanta.

Cikin masifa da bala'i matar ta fara magana da hausarta marar kyau.

"Da kake kokarin shigewa dakin,ubankane zai debi ruwan?

Ko kin ajiye bawanki ne a gidan?matar ta fada cikin zaro ido.

Kan yarinyar akasa jikinta na rawa ta fara magana

"Allah hukkumu hakuri gwagwgo naga ruwa na don sauka ne shiyasa ban deboba"ta fada cikin rawar murya da tsoro.

Wani wawan mari matar ta kai mata cikin rashin imani da tausayi cewar yanzu ta dawo daga kiwo kuma ko abinci bata ci  amma take kokarin sake turata rafi.

"Shegen yaro mai bakin hali wllh yanzu koke kidobo min ruwan nan dan ubanki karuwa kawai"matar ta fada tana mai hankade yarinyar .

Faduwa tayi sosai hannunta ya bugu da wani dutse dake ajiye tsakar gidan da alama na  zama ne.

Kara ta saka cikin azaba tana mai dafe hannunta dake mata wata irin azabtar zafi.

"Wayyo handi ɗin boni lalashewa gwagwgo hannu na ta ɓalle" ya rinyar ta faɗa cikin azaba.

"Shege wllh dama zai karye danafi kowa jin dadi yarinya kamar aljana,ace kinfi kowa kyau arugarnan? Na tsaneka fatto saina bata wannan shegen fuskan baki.maza ki tashi kona shakeki agurin ki mutu kowa ya huta"  cewar matar cikin bala'i da tsantsar nuna tsana ga dattin.

Cikin hanzarin ta mike ta zari wani boket din roba ta fice tana kuka sosai.

Tafiya mai nisa tayi kafin tazo rafin, har zuwa lokacin kuka take hannunta sai zogi yake mata, ruwan ta debo cike  da sauri dan kuwa ruwan da ake ya fara karfi.

Saidai me ?tana juyawa tayi arba da wani murtukeken maciji katon gaske ya fasa kai yana huci.

Wani irin mugun tsorone ya kamata nan da nan jikinta ya kama rawa har batasan lokacin da boket ɗin ya fadi kasa ya fashe ba.

Tashin hankali kenan wanda ba'a sa masa rana ,iyakar rushewa da tashin hankali yarinyar nan ta shiga.

Hannu ta ɗora aka tana mai kara ƙarfin kukanta.

"Wayyo ni fattu bukar na mutu na lalashe ya zanyi da rayuwata nashi zai karni wayyo baffana wayyo Allah ,taimaka min"

Ta faɗa tana kallon boket ɗin dake tarwatsa,dama kuma rana ta gama cin ubansa.

Shi kuwa macijin nan ganin yadda ta tsaya tana kallon sa kuma tana kallon fasashshen boket ɗin ta ,sai taga kamar neman makami take ,dan haka afusace yayi kanta

Ihu ta kwalla mai karfin gaske tare da zubewa agurin sumammiya  dan ganin yadda macijin nan yayi kanta baki bude.

Masu karatu ya kukaji?

Meye ra'ayinku akan wannan Nobel ɗin?

Ina bukatar comment dinku idan buk din nan yayi muku dadi muci gaba.

Takuce har kullum anty mammy

Msr babi□□

Comments

AndShare

Fisabilillah.

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJINE SHI□□□

Na mammy kabeer

_____Cikin tsoro take shafa dogon abun dan jin ko menene,tabbas MACIJINE dan kuwa har kansa ta taɓo.

Aikuwa da hanzari ta janye hannunta cikin kidima ta fara ja baya tare da fasa wani irin gigitaccen ƙara,

"Ahhhhhhhh wayyo Allah baffa maciji!maciji !!maciji!!!"gaba ɗaya ta kidime abinda take iya faɗi kenan jikinta na rawa kamar ɗan mazari.

Allah Sarki baffa dama ba wani barci yake yi ba ,dan yana kula da ɗakin fattu ,kasancewar ɗakin yana gaf da ƙofane,dan haka jin ihunta da yayi ,yasa shi tashi agigice ya nufi ɗakin nata.

Haskawa yayi da tocila can ya hangota jikin bangon ɗakin ta duƙunƙu ne tana ta ihu,da alama batama cikin hayyacinta.

Da sauri ya nufeta yana kiran sunanta"fadimatu !ke fadimatu menene ?ya isa haka gani akusa dake baffanki ne kinji daina ihun "baffa ya faɗa cikin ƙasa ƙasa da murya dan karya ƙara tsorata ta.

Ita kuwa gaba ɗaya ta rikice kawai kira take "baffa maciji zai sareni baffa wayyo Allah na"

Ganin halin da take ciki ne yasa baffa ya fara tofa mata addu'a ,cikin minti biyu kuwa tayi shiru sai rawa da jikinta ke famanyi,ahankali ta daga kanta ta sauƙe kyawawan idanunta akan baffan nata,kawai saita saki kuka tana mai cewa"baffa MACIJINE yake son  sarina aradu da idonsa na ganshi anan"ta faɗa tana nuna masa gurin dataga macijin.

Kallon gurin baffa yayi ,shifa ba abinda ya gani agurin ,kawai yana tunanin ko mugun mafarki tayi,dan haka cikin ƙokarin kwantar mata da hankali yace "shike nan fattu ya tafi maza koma ki kwonta kiyi addu'a ba abinda zai sameka kinji"ya faɗa cikin yanayin Hausar su ta Fulani.

Cikin kuka take girgiza masa kai "aradu baffa dawowa zaiyi tun daga rafi suke son cinyeni baffa ,bazan iya kwonshiya Ni kaɗai ba"ta ƙarasa tana mai matsowa kusa da baffan.

Shiru yayi yana tunanin mai ya kamata yayi,dan gaskiya yaga ta tsorata da yawa,dan haka cikin ƙarfin hali yace "tashi muje gurin hansai saiki kwonta shan ko"ya faɗa cikin tausaya wa.

Ai kafin ma ya rufe bakinsa ta kai ƙofa,dan ita kam babban burinta ta bar ɗakin nan,tama manta da gurin wa baffan yace taje.

Ahankali baffa cikin ɗan tsoro yake tura murfin ɗakin na hansai harya buɗe shi duka.suna kwance abinsu kan gado ita da yaranta su uku,na miji ɗaya sai mata biyu Dukansu basu kai fattu shekaruba, da alama na mijin zaiyi shekara sha uku,matan kuma basu fi sha daya ba.

Kuma dan rashin tsari irin na goggo hansai da ita da yaranta duka suke kan gadon ,har na mijin.

Ahankali baffa ya karasa yana dan bubbuga fillon da hansai ke kwance ,sai uban munshari take zabgawa,banda wari ba abinda dakin keyi.

"Hansai!hansai!!"baffa ya faɗa cikin Muryar tsoro,dan yasan idan ta farka saitayi masa bala'in ya tashe ta tana barci.

Juyi tayi tare da goge yawun barcin dake zuba abakinta taci gaba da barcinta.ahankali ya fara kiran sunanta da ɗan karfi "Hansai ! Hansai!!" Har sau biyu.

Buɗe ido tayi ahankali ta sauke su akan baffa dake tsaye ,buɗe idon tayi sosai cikin bala'in ta tace "to jarabarce ta motsa haka da cikin dare zakazo ka dameni?to wllh garama ka koma inda ka fito dan ba abinda zaka samu agurina ,wannan jaraba dame tayi kama ,ko sati biyu bakayi da saukemin jarabarka ba shine yanzu ka ƙara jajiɓo jiki kazo ka sake ko ?to wllh banda lokacinka kaficemin daga ɗaki"ta faɗa cikin masifa tana juya masa baya.

Girgiza kai yayi cikin jin kunyar fattu ,dan yasan taji abinda gwogwgo take faɗi ,kuma ai ita ba yarinya bace bare ace bata san me hakan ke nufi ba,tunda tana karatun addini.

Cikin sanyin murya yace "ashsha Hansai ba wannan ta kawoni ba ,dama ina neman alfarmar fattu ta kwana anan ne daku,dan  bazata iya kwana ita kadai ba ,atsorace take "ya faɗa cikin shakkun zata amince ko yaya.

"Kan ubannan yau kuma da wannan sabon munafurcin kuka zo ?fattu ta kwana aɗakina ,lallai in baka mutu ba zakaga ikon Allah,da can  da ubanwa take kwana? sai yau zakace ta kwana aɗakina?yarinyar mayya wato cikin dare ta lashemu ko?kai baka da asara,to ku ficemin aɗaki ,Allah yasa abinda yake tsoratatan ya cinyeta ta mutu kowa ya huta "tana gama faɗin haka ta juya taci gaba da barcinta.

Sosai maganganunta suka ɓatawa baffa rai ,saidai bashi da damar magana ,kai kawai ya girgiza yace "muje fattu"

Kuka sosai fattu keyi na tausayin su ita da baffanta ga wannan matsalar dake ƙoƙarin Kunno mata kai ,basu da gata sai Allah kawai.

Suna fita baffa yace "shiga ɗakina ki kwanta fattu,Ni bari na je ɗakin naki kinji"ya faɗa cikin sanyin murya.

Girgiza kai tayi tace "baffa Zan koma ɗakin nawa In kwanta kaima kaje ɗakinka ,idan gwagwgo tasan na kwana aɗakinka yanka Ni zata yi,dan ta hanani shiga ɗakin"ta faɗa tana mai share hawayenta tare da nufar ɗakin nata ,gabanta naci gaba da bugawa.

"Kiyi hakuri fattu komai yana da iyaka kinji,Allah zai miki sauyi Na alkairi"baffa ya faɗa yana mai mika mata tocila ya ce ki haska ki kwanta kinji ,kiyi addu'a"

Karba tayi tare da ɗaga masa kai ta koma cikin ɗakin.

Daga bakin ƙofa ta tsaya tare da haska ɗakin ko ina ,ba abinda tagani aɗakin ,hakan yasa tayi zamanta bakin ƙofar ɗakin da tocilan ɗin ta ko yaya taji motsi saita zabura ta  haska .

Sam awannan daren bata sami damar runtsawa ba ,ga sanyi da garin ya ɗauka sakamakon ruwan da aka zabga jiya.

Sai gabannin asuba sannan barci ƃarawo ya saceta.

Wani irin azababben sanyi daya ratsa ƙasusuwan tane  sakamakon ruwan sanyin da gwagwgo ta kwara mata ,shine ya sanyata zabura ta miƙe da sauri tana haki,kafin ta gama dawowa cikin hayyacinta kuma taji duka yana sauƙa ajikinta ta ko ina ,ihu ta fara tana neman taimako amma ba wanda yazo dan taimakon nata,dan baffa yana masallaci kasancewar shine limamin rugar,

"Wayyo Allah na gwogwgo kiyi haƙuri wllh bazan ƙara ba ,tsautsayine yasa na fashe miki bokati, dan Allah kiyi haƙuri gwogwgo"abinda fattu ke daɗi kenan cikin azaba dan ko ina na jikinta ciwo yake mata barin ma hannunta daya kumbura sosai ,alamun tayi targaɗe a  hannun kenan.

"Wllh yau saina kasheni Shegiyar yarinya muguwa, kafin baƙin cikinki ya kasheni ,na Tsaneki fattu bana ƙaunar ganinki arayuwata, kinsan nawa nasai bokatin nawa?kika je kika fashemin shi? Murtala huɗu da nairagoma fa na siya,wllh saina daki kuɗina kuma  kije duk inda zaki samo min kuɗin bokatina ki samomin dan bazan ɗauki asarar ba"gwogwgo ta faɗa tana haki,kuma bata daina jibgar fattu ba ,kamar ta sami jaka.

"Wayyo gwogwgo dan Allah kimin rai hannuna zai karye, wllh bada gangan na fashe miki bokati ba,macizaine suka biyo ni zasu cinyeni shine na gudu amma bada gangan nayi ba wllh"ta faɗa cikin azaba dan tuni ƙarfinta ya kare ko iya ɗaga hannunta bata yi.

"Allah ya tsine muku keda mashizan shegen yaro karuwa ,ina ruwana da macizai ? dama sun cinyeki kowa ya huta mai baƙin hali marar farin jini har yanzu kin kasa auruwa ,dama shegun macizan sun.....kasa ƙarasa magannarta tayi  sakamakon wani ƙaton abu dataji ya faɗo kanta jifff !!!kamar buhun hatsi.

"Wayyo Ni Hansai menene wannan ɗin yake zagayemin jiki?ta faɗa cikin firgici da tashin hankali tana mai jefar da iccen hannunta.aikuwa carab idanunta suka sauka akan ƙaton macijin daya nannaɗeta ko motsi bata iya yi,kuma ya fasa kai a saitin fuskarta sai huci yake yana Filato da harshe.

"Wayyo Allah na Ni hansai yau me zan gani ?na shiga ukuna malam kazo fattu ta min ture maciji zai kasheni ka taimakeni, handi ɗin bonu lalashewa ni yar nan wayyo malam"ta faɗa cin tsantsar tsoro da razani da ƙyar take magana dan ba ƙaramin shaƙar mata jiki macijin yayi ba har wuyanta.

Tsoro,fargaba da tashin hankali sune suka daɗa kashewa Fattu jiki ,dan faɗuwa tayi ƙasa warwas ko motsin kirki bata iya yi,shikenan Tata ta ƙare yana gamawa da gwogwgo tasan kanta zaiyo ,Allah Sarki innarta ,yanzu shikenan zata mutu bataga innarta ba,batasan ya fuskarta take ba ?bare tasan dangin innarta?,amma Gara ta mutumma ta huta da wannan baƙar azabar da take sha agurin gwogwgo.

Shikuwa macijin nan ƙara matse gwogwgo yake sosai ,gaba ɗaya ta fice daga hayyacinta,dan ko magana ma ta kasa ,idanunta sunyi jajur sai nishi take numfashinta na ƙoƙarin ɗauke wa.

Saida macijin nan yaga gwogwgo bata motsi alamun ta suma,kafin ya sake ta  ta hanyar janye jikinsa daga gareta.

Da gudu kuma yayi kan fattu wacce ke kwance cikin tashin hankali ganin yadda macijin nan ya kashe gwogwgo.runtse ido tayi da mugun ƙarfi tana salati da sallama da duniya,ko motsin kirki batayi ,dan  da kyar take iya jan numfashi ma.

Shikuwa macijin nan yana zuwa gareta ya tsaya saitin fuskarta ya fasa kai yana huci,sai kuma ya fara zagayeta cikin sauri da sassarfa, kafin kuma ya fara hayewa kan ruwan cikinta.....

Masu karatu mezai faru da fattu ?

Me macijin nan yake nufi da ita ne?

Anya ma macijin ne shi?

Saimun haɗe next page in Sha Allah taku har kullum anty mammy

Mrs babi□□□

Share and comment fisabilillah.

More comment

More typing.

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJINE SHI□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

Page 2

_____lhu ta kwalla mai ƙarfin gaske ,tare da zubewa agurin sumammiya,dan ganin yadda macijin nan yayo kanta baki buɗe .

Hakan ba ƙaramin tsorata ta yayi ba .

Dai dai lokacin ne kuma wani katon macijin ya nufo wannan macijin da gudun gaske ,yana zuwa ya sarkeshi  suka fara kaiwa juna sara .hakan shi ya hana wannan katon macijin ya sami damar karasawa inda fattun ke kwance asume.

Sosai macizan nan ke kaiwa junansu sara suna murdewa cikin jikin juna.ko wanne na ƙoƙarin illata dan uwansa.

Ahankali fattu ta fara bude idanunta da sukayi mata mugun nauyi tana kuma lumshesu,hannunta ta daga da nufin dafe kan nata,saidai wani azababben zafi da radadin ga wani irin zugi dataji hannun yana mata ,shine ya sanyata sanya kara tare da fashewa da kuka."washhhh hannuna wayyo kaina"ta fada cikin kukan tana mai dafe kan da dayan hannun marar ciwon.

Sai kuma ta zabura cikin azama ta zauna tana mai zare idanu da rarraba su,sakamakon tunowa da katon macijin da yayo kanta dazu.saidai kuma can ta hangi macizan biyu suna ta artabu,gaba daya sun jima kansu ciwo jini yana ta zuba akikkunansu,amma sunki daina fadan.

Tsoro ,fargaba ,tashin hankali da rudewa suka saka fattu kurma wani uban ihu tare da yunkurawa ta felle da mugun gudu tana ihu cikin rudewa dan ganin macizan sun zama biyu wato har fada suke akan waye zai cinyeta.

Duk da irin ruwan da ake zugawa mai ƙarfi ga iska ,haka tayi ta cin uban gudu ko gabanta bata gani.ikon Allah ne kawai ya kawota gidansu lafiya.

Kai tsaye ta danna cikin gidan da gudu ta shige dan dakin dayake amatsayin nata,cikin rawar jiki ta janyo wasu karare dogaye guda hudu ta kara a kofar,dan sune

Matsayin murfin kofar tata.

Dakin ba komai sai wata yar yaloluwar taburma ,wacce kallo daya zaka mata kasan cewa taga duniya,dan gaba daya ta ciccinye kuma tayi lakwam da ita.sai wani zani dake gefe daure ,da alama kayanta ne acikin.

Tana tsaye atsakar dakin ,har lokacin jikin ta rawa yake ,ga ruwa sai zuba yake ajikinta yararara!!!

Kallo daya zaka mata kasancewa afirgice take sai kif-kifta ido take tana kallon kofa,gani take kamar macizan nan zasu biyota.tayi kusan minti biyar acikin wannan halin ,kafin ta fara cire kayan jiki ta dake yararin ruwa."masha Allah nace,sakamakon ganin wani uban dogon bakin gashi mai  santsi akanta,lokacin da

take zame dan kwalin dake kanta .an raba kan biyu an daure ko wanne bangare sai kuma aka nannade ko wanne abarinsa kamar gammo.hakan da akayi shine ya hana mu ganin gashin nata tun farko.

Daurarren zanin nan ta kwance ta dauko wani zanin irin wanda ta cire da rigarsa ,saidai kayan fa sun sha jiki sosai ,sun kode sun jeme sunyi wani fari,sai wata hula baka irin ta sanyin nan ta dauko ta ajiye kusa da kayan ,sannan ta mike tsaye ta cire rigarta ta ajiye ta gefen ta barmar ahankali ta warware tsangalallen zanin shima ta ajiye gefe,ya zama daga ita sai wani kodadden pant Wanda kana gani kasan shima yaga rayuwa.kallonta nayi tun daga sama har kasa kawai nace Masha Allah.dan sura kam Allah ya halicce ta agurin fattu jikintahar wani sheki yake kamar yar masu kudi wacce ke rayuwa cikin jin dadi.

Haka ta dauki kayan ta saka ajikinta tanayi tana kuka abin kwanon ban tausayi.

Bayan ta kammala sanya kayan ne kuma saita dauki wanda ta cire ta matse sannan ta makalasu ajikin karan dake jingine akofar dakinta.

Zama tayi akan yar tabarmarta ta dukunkune jikinta tana kuka.abubuwa dayawa ke dakinta ahalin yanzu,na farko tsantsar tsoron macizan data gani dan bata taba ganin  irin wadannan macizan ba,dan dayan kam jikinsa mai matukar shekine da kyau,sai kuma hannunta dake mata azabar ciwo uwa uba kuma yunwa,rabonta da abinci tun safe data sha nono har kawo yanzu da magrib ta sanyin kai ba abinda taci.

Sosai take tausayi rayuwarta, tabbas rashin uwa babbar gibine arayuwa,yanzu da innarta na kusa da ita data rungumeta ta fada mata damuwarta,amma rashin dace ta daya shine sam batasan koda fuskar innarta ba ,bata sani Bama kotana raye koya mutu Allah shine masani.

Tana cikin wannan halin taji an ture kararan data rufe dakinta dashi.

Azabure ta mike tsaye tana shirin sanya ihu.

"Ke fattu nutsu mana nine fa ,nine baffanki"wani dattijo ne fari mai dan tsayi yake maganar,yana sanye da riga da wando na wani yadi mai arha sai takalmin sau ciki na roba,da hula irin mai malafar nan.ya shigo cikin dakin da wani kwano hannunsa.

Ajiyar zuciya ta sauke sakamakon ganin baffan nata ,da sauri ta karasa kusa dashi tace "baffan usee wollahi na tsorata ne"ta fada idonta akan kwanon dake hannunsa.

Murmushi yayi yace "hoo fattu akwai tsoro,sannu maza karbi wannan tuwon ka shinye nasan kanajin yunwa,kayi sauri kar hansai ta gani"yana fadin haka ya mika mata kwanon yayi saurin fita,dan kar matar tasa ta fito ta ganshi ya shiga uku.

Cikin sauri _sauri fattu ke cin tuwon nan kamar zata kware, tas kuwa ta cinye ta side kwanan, da sanda tafice tsakar gidan ta wanke kwanon ta ajiye akicin sannan ta sha ruwa tayi alwala ta koma daki.

Sallar la'asar tayi da magrib dan tuni an kira.

Har zuwa lokacin ruwa ake saidai bai kai ƙarfin na farko ba.tana zaune cikin zullumin matakin da gwogwgo zata dauka akanta ,na fasa mata boket har akayi ishsha tayi salla sannan ta kwanta tana mai karanta addu'a ,nan da nan barci yayi gaba da ita,har baffanta ya shigo ya duba ta yaga tayi barci addu'a yayi mata cikin tausaya wa halin kuncin da take ciki kafin yayi saurin fita.

Gwagwgo kuwa tana daki ita da yaranta suna ta hira suna cin gyada ,ba ruwansu da wane halin fattu ke ciki,shin ta dawo gidanma ko yaya taci abinci ko bata ciba?sam ba wanda ya damu ,kuma ba wanda yayi Sallah a cikinsu.

Can cikin dare fattu na barcinta damuwa da tsoro dan kuwa mafarkin macijin nan take ,saidai kuma ba na farkon bane yazo mata yanzu wannan mai kyakyakywan jikin ne,saidai gaba daya jikinsa jini yake zubarwa,ga wani irin hayaki da tururi dake fita ajikinsa, sai burkima yake yana wani irin kuka da wata murya mai amon sauti,kuma yana nufota da ƙoƙarin hawa jikinta .

Wani razanannen ihu ta kwalla tare da mikewa zaune afirgice ,tana mai waige waige,ba abinda take iya gani saboda duhun dakin ,hakan yasa tayi saurin komawa ta kwanta tare da karanta addu'a kala_kala,hannu ta mika dan janyo zaninta ta rufe jikinta dashi ,saidai kuma hannun nata taji ya sauka akan wani abu mai dan karen sanyi da santsi.

Cikin tsoro take shafa abun dan jin ko menene,tabbas MACIJINE dan  kuwa ta tabo har kansa ....

Masu karatu badai macijin ne ya biyo fattu da gaske ba?

Wane hali fattu zata shiga ?

Muje zuwa yaki ce dai anty mammy

Mrs babi□□□

Share and comment fisabilillah.

More comment

More typing.

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJINE SHI□□□

Na manya kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Hawa  macijin nan yayi kan ruwan cikin fattu ,daidai kan fuskarta ya tsaya tare da fasa kansa ,ya tsaya ƙuri yana kallon fuskar Tata, wacce tuni idanun fattu ke rufe tayi mutuwar kwance ko nunfashi ta kasa shaƙa cikin salama.

Shikuwa macijin nan ganin bata koda motsi saiya sauƙo daga ruwan cikinta ya tsaya saitin fuskar tata tare da fasa kansa yana huci ,.matsowa yayi sosai jikin fuskar tata

yana hura mata iska daga bakinsa,sannan ya ɗan ja da baya ya tsaya yana kallon ta.

Ahankali fattu ta ɗan buɗe idanunta dan ganin shin me kuma macijin nan ke shiryawa ?ta yaya yake tsara kasheta itama,saidai tana buɗe idanta suka sauka akan na macijin nan ya ƙureta da idanunsa.

Cike da tsoro da fargaba fattu ta kafe shi da nata idanun,dan tsintar kanta tayi da kasa daina kallonsa,abubuwan mamaki take gani tare da macijin,sam kwayar idanunsa ba irin ta macizai bace,sak!irin ta mutane ce saidai gurin farin yayi wani irin kala kala , blue yellow pink ,Amma asalin kwayar baƙace ƙirin.

Sai kuma taga hawaye na zubowa daga idanun macijin kamar mutum yana kuka.

"Innalillahi wa'inna ilahirin raji'un, Allahumma ajirni fi musibati waaklifni kairan minha,la'ila ha illa anta subhanaka inni kuntu minazzalimin"shine abinda fattu ta fara karantawa cikin zuciyarta jikinta na wani irin tsuma da karkarwa, tunda take bata taɓa ganin irin wannan macijin ba sai yau,ya maciji zai kasance da idanun mutane? sannan kuma jikinsa akwai banbanci sosai dana macizai,dan shi yana da wani irin jiki mai ban mamaki yadda kalar idanunsa ta kasance haka shima jikinsa yake .sannan kuma bai kai girma irin na macijin jiyan nan ba amma yana da girma shima sosai,kuma dogone na gaske.

Kallon kallo kawai ake tsakanin fattu da macijin nan,inda ahankali ya fara hucewa daga kumbura da fasa kan da yayi ,fattu na kallonsu harya koma normal jikinsa ya daidaita ,sannan ya fara ƙoƙarin barin ɗakin ta wata yar hanya dake jikin katangar karan ,wacce ita fattu sam bama tasan da ita ba sai yau,da alama dai shi yayiwa kansa hanyar.

Saida yaje gab da hanyar tasa saikuma ya juyo da kansa yana kallon fattun,shi bai tafiya ba  kuma bai dawo ciki  ba.

Sosai jikin fattu ke rawa tana zubda hawaye ,dan yau kam lamarin ya kulle mata kai ,wai wannan wane irin MACIJINE ?shin macijin ne  ma kokuma wata halittar?sannan maiyasa yaƙi yi mata komai,sai dai  ƙoƙarin ceto ta da yake atsammaninsa na ko bata numfashi?haƙiƙa akwai abin dubawa dan gane da wannan macijin.

"Fattu ! fattu!!kin tashine kinyi sallar  lokaci yana ja fa"ta tsinkayo Muryar baffa daga wajen ɗakin yana mata magana .

Jin muryar baffa da fattu tayi sai hankalinta ya ɗan kwanta  cikin ɗaga murya tace "baffa kazo ka taimaka  min gwogwgo bata motsi"ta faɗa cikin Muryar kuka tana kallon macijin.

Cikin sauri da azama baffa ya shigo ɗakin yana faɗin"subhanallah me kuma ya sami Hansai din?

Cikin kuka fattu ta kalli baffa sannan ta kalli inda macijin nan yake ,har lokacin yana tsaye yana kallon ta,

"Baffa bansani ba kawai ta shigo tana dukana sainaga ta faɗi ƙasa"abinda fattu ta tsinci kanta kenan da faɗa murya na rawa.

Ahankali macijin nan ya juyar da kansa ya bi ta yar ƙofar nan ya fice.

Sai lokacin hankali fattu da nutsuwarta suka dawo jikinta ,cikin ƙarfin hali ta yunƙura ta tashi zaune ,har lokacin akwai alamun tsoro da firgici akan fuskarta,dan jikinta sai rawa yake.

"Washhhh hannuna"ta faɗa ahankali tana mai runtse ido,dan sosai hannun ke mata mugun ciwo.

Ruwa baffa ya ɗebo mai sanyi wanda ya taru na sama,yana zuwa ya kwarawa gwogwgo ruwan cikin moɗa .aikuwa azabure ta tashi zaune tana ihu"wayyo Allah na maciji zai kasheni malam kawo ɗauki ,fattu tayiminn turen maciji,wayyo wuyana ,wayyo hannuna na shiga uku na lalace"abinda gwogwgo hansai ta farka dashi kenan,maimakon ambaton sunan Allah .

"Kayya hansai ki nutsu ba wani maciji ana fa nine bukar wannan kuma fattu ce ɗiyarki"cewar baffa kenan a ƙoƙarin sa na kwantar mata da hankali.buɗe ido gwogwgo tayi sosai ta kallesu kafin tace "kuturin bala'i Allah ya kiyaye wannan sheɗaniyar ta zama yɑata mayyace fa,wllh ture tayimin yanzun na wani maciji ya kusan hallakani,wllh sainaga bayan yarinyar nan Shegiya may.....wayyo Allah na ya dawo ya dawo"gwogwgo hansai ta faɗa sakamakon hango kan macijin nan da tayi ,ai da gudun gaske ta fice daga ɗakin tana ihu .

Girgiza kai baffa yayi yana Allah wadai da halin matar tasa ,sam baiyi dacen mata ba.kallon Fattu yayi wacce take riƙe da hannunta mai ciwon, hawaye na zuba a idanunta na azaba.

"Ashsha ashsha fattu kiyi haƙuri  kinji,komai yayi farko zaiyo ƙarshe ,Allah yana sane da halin da kike ciki in sha Allahu zakiyi dariya anan gaba"baffa ya faɗa cikin sanyin murya da ƙoƙarin kwantar mata da hankali.

Ahankali ta sanya hannu ta share hawaye idanunta ,kafin tace "baffa hannu na ciwo yake min"ta faɗa tana nuna masa hannun dayake mata ciwon.

Kallon hannun yayi yanda ya kumbura yayi suntum dashi ,cikin tausaya wa yace "ayya faɗimatu sannu. Kinji maza daure kiyi sallah saina duba miki hannu kiyi haƙuri, Allah yayi miji albarka"ya faɗa yana mai taimaka mata ta miki tsaye.

"Ameen baffa "ta faɗa tana ficewa daga ɗakin .bayi ta shiga ta kama ruwa sannan tayi alwala cikin dabara kafin ta fito ta koma ɗakin ,Sallah tayi tare da karatun alƙur'ani mai girma ,da ka take karatun dan da ahaka aka koya mata ,bayan ta idar ne baffa ya shigo ɗakin ɗauke da kwarya ahannunsa ,

" Sannu fattu karɓi wannan madarar Kisha kinji,saina duba miki hannun"baffa ya faɗa yana miƙa mata kwaryar.karɓa tayi ahankali tayi Bismillah ta kafa kanta,saida ta shanye kafin ta ajiye kwaryar .

Allah Sarki fattu tasha wahala sosai lokacin da baffa ke gyara mata hannun ,dan yayi tsami sosai ,kuka harda majina,haka baffa ya gyara mata yana mata sannu.bayan ya gama gyara mata ne yace ta kwanta ta huta kafin garin ya gama wayewa.haka ta kwanta tana ajiyar zuciya ,ba jimawa kuwa barci yayi gaba da ita ,abinka  da wanda bai sami barci ba dama.

Ficewa baffa yayi daga ɗakin ya nufi nashi cike da tausayin yar tashi dayake matuƙar ƙauna.

Ko minti talatin batayi ba tana barcin ta tsinkayo muryar gwogwgo tana kiranta "Ke gantalalliya mayya  fito dan ubanki ,ko uwarki ce zata miki aikin?Shegiyar yarinya

aljana wllh bakici bulusba yadda kika sa macijin nan ya lagartamin jiki to wllh saina rama ,fito ki ɗebomin ruwa yanzun nan .

Afirgice fattu ta tashi daga barcin ta fito da gudu tazo tana rawar jiki ,Dan bala'in tsoron gwogwgo take kamar ranta."gwogwgo dame zan ɗebo ruwan "ta faɗa kanta asunkuye.

Da ubanki zaki ɗebo ruwan  kinji ?kije ki nemomin kuɗin da zaki biyani bokatina inyaso ki ɗebomin ruwan aciki"gwogwgo ta faɗa tana daga ɗaki,dan taƙi fitowa waje kartaje macijin nan ko ajikin fattun yake.

Masu karatu har zuwa wannan lokacin fa yaran gwogwgo hansai suna kwance aɗaki suna barci.

Amma take ƙoƙarin tura fattu ɗiban ruwa da wannan safiya,alhalin bata da lafiya.dan lokacin da baffa ke gyara mata hannun tana jin ihunta.lokacin tana kwance akan gado tana hucin azabar da macijin nan ya gana mata,"Shegiyar yarinya Gara kemaki ɗandana azabar dana sha ,Allah yasa hannun ya karye ma kowa ya huta.

"Dan Allah gwogwgo kiyi haƙuri wllh bansan inda zan samo kuɗin ba kiyimin rai "fattu ta faɗa cikin kuka.

"Dan kan ubanki tashi ki ɓacemin da gani,wllh kome zakije kiyi bai dameni ba Indai zaki kawomin murtala uku da raina gomata."ta faɗa tana rarumo wani busasshen kwanon tuwo aɗakin ta cillowa fattu shi.

Allah ne ya kare fattu da tuni kwanon ya sauƙa akanta ,tayi saurin ficewa da gudu daga gidan.

"Shegiya da kin tsaya ai"cewar gwogwgo tana mai kwanciya ba ko sallar safiya.

Koda fattu ta fita daga gidan kuka take sosai ,batasan inda zata nufa ba ,ina zata samo Murtala uku da Naira goma?waye zai bata waɗannan iyayen kuɗin?  Kodai gurin jauro zataje tace ya taimaka mata da Murtala uku da Naira goman?kai a'a bazataje ba, dan  jauro ba mutumin kirki bane ,ranar nan ma hannunta yake ƙoƙarin kamawa wai yana sonta,kuma baffa yace maiyin hakan ba mutumin kirki bane.

Kusan minti biyar tana saƙa da warwara,kafin ta yanke  shawarar kawai ta tafi bakin rafin ta zauna ko Allah zai sa  ta sami abun ɗiban ruwan.

Tafiya take ahankali ,wanda kallo ɗaya zaka mata kasan batajin daɗi,hannunta mai ciwon kuwa ta rikeshi da ɗayan hannun.haka ta nufi rafin dake can bayan gari cikin jeji.

"Hai jauro wai kuwa kaga Abinda nake gani"?

Cewar  haroji kenan wanda suke zaune akan wata bishiya shida jauro can kusa da rafin da fattu ta nufa.

"Wanda aka kira da jauron ne  ya ɗago kanshi dake duƙe yana zuƙar sigari yace "me ka gano mana"?

"Wllh fattu ce kuma ita kaɗai kaganta can ta nufi rafi"ya faɗa cikin ɗoki da zumuɗi.

Da sauri jauro ya kalli gurin da harojin ke nuna masa ,aikuwa fattu ya hango ,cikin hanzari ya fito daga kan bishiyar yace "wayyeee huuhuuu ,yau kam mun fito asa'a dan wllh saimun aikata mata ,wllh saina kusan cinye fattu yau "ya faɗa cikin murna da farin ciki yana mai bin hanyar da fattu ke tafiya,harta kusan ƙarasawa rafin.

Da sauri haroji yabiyo bayansa yana faɗin"ai wllh nima saina ɗana yau ɗinnan inka gama saika birmin siɗi"

Da sauri suke tafiya dan haka cikin ƙanƙanin lokaci suka cimma ta.kawai sai gani tayi sun sata atsakiya.

Kallonsu tayi cikin tsoro da fargaba,tace"meye hakan jauro ku bani hanya in wuce"ta faɗa cikin dakiya da nuna alamun bata tsoro su.

Dariya suka kyalkyale da ita ,kafin jauro yace "wllh fattu yau saina kusan shinyeki gaba ɗayanki Allah ne ya kawo mana ke dan haka maza kwanta "ya faɗa cikin jahilci da rashin imani.

Cikin tsoro da fargaba fattu ta fara ja baya tace"jauro me na maka zaka cinyeni?dan Allah kayi haƙuri wllh bana son mutuwa yanzu ina son ganin innarta"ta faɗa lokacin harta fara zubar da hawaye.

Dariya suka saka sakawa suna tafa hannu kafin haroji yace"jauro kawai kamata da shegen ƙarfi dan bazata kwanta ba ,kuma fa kamar bata san me kake nufi ba " aikuwa jin haka sai jauro ya cakumo  fattu yana faɗin aikuwa yanzu zata san me nake nufi ,yarinya kin cika kin batse amma ba mai amfana dake" nan da nan suka fara kokawa,yana ƙoƙarin Kaita ƙasa ,ita kuma tana Turkewa da ƙoƙarin kwatar kanta. kasancewarsa namiji tuni yaci ƙarfinta dan har ya Kaita ƙasa,ga ciwon hannu.

Daram ya zauna akan ruwan cikinta yana ƙoƙarin cire mata riga.dan tuni shikan ya cire wandonsa daga shi sai wata yar Shara ajikinsa banda wari ba abinda yake yi .haroji kuwa yana tsaye ya juya baya yana gane musu koda me tahowa.

Ihu fattu take cikin tsantsar tsoro da tashin hankali ,tayi mugun razana da ganin abinda jauro ke ƙoƙarin tura mata a bakinta yana fadin"maza Kisha fattu haka ake mana lagus sha maza kiji akwai daɗi"ya faɗa yana ƙoƙarin tura mata jauronsa abakinta wacce ganinta kaɗai ya mugun tsorata fattu.dan bata taɓa ganin wannan ƙaton abun mai numfashi haka  ba sai yau.

"Wayyo Allah na shiga uku jauro menene wannan kake ƙoƙarin bani abakina ka bari bana so wayyo hannuna ,wayyo baffa zan mutu" ta faɗa tana wani irin kakkafewa jikinta na wani irin ɓari.

"Wllh yau ko zaki mutu fattu saina kusan cinyeki dan na jima da yunwarki araina, yau kuwa ba mai hanani yin.....wayyo Allah menene wannan haroji maza zoka taimakeni"jauro ya  faɗa lokacin da yaji wani gibgegen abu ya fado kansa ya duƙunƙune shi sannan yasa baki ya cafke aliyarsa.

Ihu  jauro ya kurma mai ƙarfin gaske ya daɗi can gefe guda.....

Masu karatu,menene wannan ya faɗowa jauro?

Me zai faru nan gaba?ku biyoni next page in Sha Allah,taku

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJINE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

_____Nan da nan fusatattun rugar suka nufi gidan malam bukar ,dan aiwatar da ƙudirin lamiɗo.

Allah Sarki fattu kuwa a wanann lokacin tana ɗakinta cikin jimami da tunanin abinda ta  gani yau ɗin nan,haka nan ta tsinci kanta da son sanin menene wannan abubuwan dake motsi aƙasan wuyan maciji? wanda tun daɗewa bata taɓa ganinsu ba sai yau,waya sani ma ko wani akayiwa asiri ajikin macijin ?tabbas zatayi iya ƙoƙarin ta dan ganin ta raba macijin nan da wannan abubuwan ,ta yadda koda wani aka yiwa asiri  ta hanyar macijin, to asirin zai karye .sannan tana fargabar gwogwgo ta gano cewar tana gidan kuma bata ɗebo ruwan ba.kuma ahalin da ake ciki yanzu bazata iya komawa rafin nan ba ,.dan ta tsorata dasu jauro .

Hayaniyar mutane ce ta cika gidan  nasu fattu ,wanda haka yasa gwogwgo hansai fitowa dole badan ta soba, Dan har lokacin nan ita da yaranta ba wanda yayi sallar asuba.

"Kai su waye haka suka zo suka cika mana gida da  ihu kamar ana yaƙi?"cewar gwogwgo hansai tana gyara daurin ƙirjinta dake ƙoƙarin kuncewa bayan ta fito daga ɗakin.

"Aa meye hakan ardo ?lafiya na Ganku da yawanku kun shigo?ta tambaya lokacin da idanunta ya sauka akan mutanen da suka cika gidan,kusan duk mazan garin ne.

Cikin masifa wanda aka kira da ardo yace "wllh yau saimun ɗauki mataki akan bukar da fattu ,haka kawai yarinya ta fara kashe mutane ,kuma ta rasa ta kan wa zata fara sai ɗan gidan lamiɗo ?wllh yau sai mun kashe Shegiyar yarinyar nan"ya faɗa yana wani zazzaro idanu kamar zararre.

Eh wllh afito mana da ita kawai mukaita gurin lamiɗo ya bamu izini mu kashe mayya.gaba ɗayan mutanen gurin suka faɗi haka cikin nuna fusata da ƙosawa abasu fattun .

Wani irin farin ciki da jin daɗine ya kama gwogwgo hansai ,shikenan zata rabu da alaƙaƙai cikin sauƙi Allah yasa akasheta kowa ya huta ,dama su haɗa da bukar ɗin

da yake ɗaurewa fattu gindi ,koba komai shanunsa sun zama nata.gwogwgo hansai ta faɗa cikin ranta.kafin ta kalli ardo da sauran mutanen tace "aikuwa idan aka kasheta an kyauta ,dan nima nan wllh so take ta cinyeni nida yarana, jiya da kyar mukasha data maƙuremin wuya wai saita cinyeni, ku ɗan jira kaɗan yanzu zaku ganta shegiya gantalalliya,banma san inda ta tafiba, dama haka takeyi kullum inta fice yawon iskanci bata dawowa da wuri,tana can gurin maza"gwogwgo hansai ta ƙarasa maganarta tana mai buga hannu acinya.

"Aikuwa yanzu zamuje mu nemota ko ina ta shiga,wasu sutafi bakin rafin wasu sushiga jeji, mukuma zamu jira ana "cewar ardo kenan yana kafe sandarsa akasa,sannan ya gyara tsayuwarsa.

Duk wannan abunda ke faruwa akan kunnen fattu, tana jin komai ,saidai tashin hankali,firgici tsoro da kuma ruɗewa sun hanata koda yin kwakwkwaran motsine .

Numfashinta ma da ƙyar yake fita tsabar ruɗewa.

Ta shiga uku !shikenan yanzu kasheta za'ayi?laifin me tayi da za'a kasheta?me baffanta yayi ake nemansa shima? Dama jauron mutuwa yayi ? innalillahi !!!yanzu ya zatayi.

Wani kukane ya kubce mata cikin sauri ta toshe bakinta tana kuka sosai kamar ranta zai fita,ji take dama tana da ikon ɓacewa, tabbas da ba abinda zai hanata ɓacewa ta bar duniyar ma gaba ɗaya.

Ahankali ta miƙe cikin sanɗa ta leƙo da kanta ,ba ƙaramin tsoro tajiba lokacin da taga mutanen da suka zo tafiya da ita.shikena kawai ta mutu,yanzu shikenan bazata cika burinta na ganin innarta ba?wayyo "Allah ka kawomin ɗauki "ta faɗa cikin raunananiyar muryarta mai cike da tsantsar tsoro.

Ahankali ta ƙara leƙo da kanta waje ,cikin rashin Sa'a kuwa sukayi ido huɗu da dan gidan gwogwgo hansai umaru.wanda hayaniyar mutane tasa suma suka farka.

"Laaaah aradu gwogwgo ga fattun can cikin ɗakinta tana leƙowa"ya faɗa yana nuna ɗakin da Fattu ke ciki

.cikin hanzari fattu ta koma cikin ɗakin tana mai runtse idonta ,tare da dafe ƙirjinta."shikenan sun ganni wayyo Allah na baffa,wayyo MACIJINA kana ina  kazo ka taimakeni zasu kasheni wayyo ni fattu"fattu ta faɗa tana mai leƙa hanyar nan da macijin Kebi idan zai bar ɗakin nata inya zo kamar Zariya  haka take bankada hanyar macijin da hannunta.

"Munafuka ,mayya dama kina ji ana neman ki shine kika ɓuya nan?to fito yau dubunki ta cika ,mutuwa zakiyi wllh saikin bar duniyar nan yau nima na huta da ganinki ,maza ardo zoka tafi ta ita gata nan"gwogwgo hansai ke faɗin wannan maganar tana daga bakin ƙofar dakin Fattu,dan tun lokacin nan da tasha matsa agurin  maciji bata ƙara shiga ɗakin Fattun ba.

Aikuwa kafin ta rufe baki su ardo sukayo kan Fattu suna janta.

"Wayyo Allah gwogwgo karki bari su tafi dani zasu kasheni ,wllh ban aikata komai ba wayyo Allah na gwogwgo ki taimaka min"abinda Fattu ke faɗi kenan tana miƙawa gwogwgo hannu cikin kuka mai tsanani.

"Ai wllh dana taimakeki gara hannuna ya karye Shegiyar yarinya ,kutafi da ita  can ku kashe banza" gwogwgo ta faɗa tana  kaɗa hannu irin yadda ake korar kaji ,cikin farin ciki take maganar.

Ihu Fattu keyi tana kuka,amma haka suke janta  kamar akuya aƙasa, suna cikin tafiya ne ,saiga baffa aguje yazo gabansuu ya tsaya riƙe da sanda yana ta haki,dan yana can bayan gari ya sami labarin abinda ke faruwa acikin garin da gidansa,shine ya rugo yazo .

Aikuwa Fattu na ganin baffa ta ƙara fasa ihu tana cewa" wayyo baffana ka taimakeni zasu kasheni" ta faɗa tana miƙa masa hannu,abin tausayi dukta susuce tayi buju buju da jiƙaƙkiyar ƙasa.kallonta baffa yayi

Cikin bacin rai mai tsanani ya ce.

"Sakarmin yarinya ardo,  kona rotsa maka sandar nan akanka" baffa ya faɗa cikin hargowa da ƙaraji,

Kasancewar baffa kowa  ya sanshi arugar mutumin kirki ne ,sam ba ruwansa da shiga harkar wani,sanan kuma shine ke ja musu jam'i ,hakan yasa suke ɗan ganin girma da mutuncinsa, dan haka cikin Turo baki da hura hanci  ardo yasaki hannun Fattu wanda ke mata azabar ciwo da radadi,yana mai cewa"ato lamido ne dai yace mu taho daku,dan haka ya zama dole ayiwa lamido biyayya"ya fada yana hararar gefensa, dan yaji haushin sakin wannan hannun na Fattu mai shegen laushi da dadin taɓawa da baffa yasa yayi.lol

Fattu kuwa yana sakar mata hannu ,da rarrafe ta ƙara so gurin baffa ta rirriƙe shi tana kuka da fadin"wllh baffa ba abinda na aikata,ban kashe jauro ba " ta fada cikin matsanancin kuka da tsoro, jikin ta sai rawa yake.

Riƙota baffa yayi cikin tausayawa yace "na sani Fattuna,baki kashe jauro ba ,kuma ba wanda zai kasheki, Allah na tare dake kinji"?ya fada cikin sigar rarashi,sannan ya kalli ardo yace"kai ardo ka kiyayeni ,karka ƙara ƙoƙarin  sake aikata irin wannan dabbacin akan yata, saboda baka da hankali shine zaka rinƙa janta aƙasa. Kamar wata dabba ?jahilan banza jahilin hofi,muje gurin mai garin zanji idan shiyasaka wannan ɗanyen aikin"baffa ya fada cikin mugun bacin rai yana mai riƙe Fattu suka nufi fada.

Lamido na hangosu ya fara lasar baki ya kure fattu da idanu kamar maye , yana kissima abubuwa da dama cikin ransa....

Manage please yau ina busy,Dan banyi niyar typing bama yau wllh.

Masu karatu me lamido ke nufine shima?

Hmmmmmm kubiyoni mu hade bayan sallah  danjin yadda zata kaya.

Kafin nan ina mana fatan yin salla lafiya,sannan aci Nama ahankali kar azo ana .....

Taku anty mammy

Mrs babi,□□□

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/LsrDragdsZn2UMCRLPA7uv

Banda maza Please mata kawai .

By mammy kabeer

□□□□□□□□

MACIJINE  SHI □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

_____Ihu jauro ya kurma mai ƙarfin gaske ya faɗi can gefe yana burbura tare da rikan "wayyo haroji jaurota zai cinyemin ka taimakeni  zan mutu wayyo maciji "ya ƙarasa  faɗa da kyar sakamakon wata danƙa mai ƙarfi da macijin nan yayiwa jauronsa har saida numfashinsa  ya ɗauke .

Haroji kuwa ya mugun tsorata ganin halin da jauro ke ciki,ga wannan ƙaton macijin daya kanannadeshi yana ƙoƙarin karya masa ƙasusuwa.

Cikin kiɗima ya rarumo wani ƙaton dutse yayi kan jauro da wannan macijin,yana zuwa baiyi wata wata ba ya ɗaga dutsen ya kwaɗawa macijin nan abayansa.

Aikuwa nan da nan bayan macijin ya fashe jini yayi tsartuwa har kan fuskar haroji,wani ihu haroji ya kwala ,sakamakon sauƙar jinin macijin nan akan fuskarsa ji yayi kamar an watsa masa ruwan batir,nan da nan gurin ya sale kamar wanda ya ƙone sai turiri gurin yake.

Jifa haroji yayi da dutsen hannunsa yana ihu yana faɗin"wayyo Allah idona bana gani wayyo kwayar idona ta zazzage na shiga ukuna "abinda yake daɗi kenan yana ihu da tsalle.

Shikuwa macijin nan silalewa yayi daga jikin jauro ya koma gefe guda tare da kwantar da kansa akasa ,dan kuwa sosai  haroji ya kwada masa dutsen nan,kuma da alama ya shige shi .

Gaba ɗayan abinda ke faruwa akan idanun fattu ,tana kwance tana kallon ikon Allah,tabbas zuwa yanzu ta gama yarda cewa macijin nan bashi da biyar cutar da ita ,saima taimakon ta da yake,shin wanene wanan macijin?meye alaƙarta da shi? me yake nema agurinta?anya ma MACIJINE wannan ?kodai aljanine yake zuwa mata asiffar macijin? Wadanna sune tarin tambayoyin da fattu ke yiwa kanta  tana daga kwancen wanda bata da amsarsu.

Saidai kuma gaba ɗaya hankalinta ya tashi ganin yadda macijin nan ya kwanta lamo kamar ya mutu.nan da nan tsoro ya mamaye zuciyarta ,cikin dauriya da jarumta ta yunƙura ta miƙe tsaye tana yamutse fuska,hannunta mai ciwon yana riƙe aɗaya mai lafiyar.

Gurin macijin ta nufa gabanta na ci gaba da faɗuwa,dan tsoro take kar ita kuma yayi mata wani abu.tana ƙara sawa ta durƙusa ahankali dai dai inda haroji ya buga masa wannan dutsen ,hannu ta sanya ahankali ,cikin karkarwa jiki ta  ɗan shafa gurin ciwon.ai tana ɗora hannunta agurin macijin nan yayi wata irin juyowa tare da fasa kai kamar zai sareta, cikin tsoro da fargaba ta cire hannunta tare da matsawa baya da sauri tana zare ido tana kallon macijin.

Shima yana juyowa yaga fattu ce ,sai ya tsaya yana kallon ta,tare da komawa yadda yake ,wato ya sassauta fusatar da yayi ,kawai ya tsaya yana kallon ta.

Itama kallonsa take cikin tsoro da bugawar zuciya,ahankali macijin ya fara tahowa ,har ya zo gareta ,runtse idanu tayi tana karanta addu'ar Allah ya tsareta.

Ga mamakinta kawai saitaji macijin ya hau kan cinyarta ya kanannaɗe jikinsa ya dora kansa a saman  gammon da yayi da jikinsa.

Ahankali ta buɗe idanunta tana kallonsa,shima ita yake kallo saidai idanunsa na zubar da hawaye kuma na jini .

Jikinta kawai rawa yake cike take da tsantsar tsoron abinda zai faru .juyawa tayi tana kallon haroji dake ta faman ihu yana yaɗuwa kasa.sannan ta kalli jauro wanda yake kwance ba alamun numfashi atare dashi,ga jauronsa nan tayi wani irin kumbura na ban mamaki sai jini ke zuba .

Tsorone ya ƙara kamata cikin azama ta yunƙura tare da mikewa tsaye,  ture macijin tayi daga jikinta ta kwasa da gudu tayi gida tana kuka .

Koda taje gidan, da sanɗa tayi saurin shiga ɗakinta tana kuka,zama tayi akan tabarmarta tare da kife kanta a tsakanin cinyoyinta tana kuka.damuwace fal cikin ranta,wai meke shirin faruwa ne da rayuwarta?wacece mahaifiyarta?waye wannan macijin da yake ɗaukan hukunci akan duk wanda yayi nufin cutar da ita?tanasan sanin wannan macijin waye shi,kokuma waye ya aikoshi gareta.tana cikin kukanta ne kawai taji abu yana hawa jikinta sililililili!!! Afirgice ta ɗago kanta tana kallon macijin daya gama hawa jikin nata. kansa ya ɗora akan wuyanta yana  fidda wani irin huci ,shiru tayi tana sauraron yadda macijin ke huci,sanan jikinsa yayi wani irin zafi sosai.duk yadda akayi bashi da lafiya ,kuma dukan da haroji yayi masane solar hakan.

Tausayinsane taji yayi mugun kamata,ahankali cikin tsoro ta miƙa hannunta tare da riƙo saitin wuyansa ahankali ta janyoshi, ko motsi baiyi ba bare ya hanata abinda yake yi ɗin.

Akan tabarmar ta ɗorashi tare da ci gaba da kallonsa,cikin muryar kuka tace "bawan Allah kai waye?meke tafe dakai?waya aikoka zuwa gareni?meyasa kake ƙoƙarin daukar mataki akan duk wanda ya zalumceni?dan Allah karka cutar dani, bani da kowa sai baffana,dan Allah kayi tafiyarki ,idan mutanen garin na suka farga da kai zasu kasheka ,bazan so hakan ba dan Allah na roƙeka ka tafi"ta ƙarasa maganar tana haɗa hannunta cikin kuka.

Shidai macijin nan ko motsi baiyi ba sai huci da yake yi sosai,

Ahankali ta kalli gurin da yaji ciwo dazu sai taga gurin yana turiri kuma yayi wani fari fat.shiru tayi tana kallonshi ,yanzu ya zata yi masa ne?dan da alama fa yana jin jikine, data rasa abinyi kawai saita lulluba zanin sallarta ta fara karatun Alqur'ani mai girma.cikin abinda bai wuce sakwan biyar da fara karatunta ba  kawai macijin nan ya fara wata irin murmurɗewa yana sauya kala, da farko yayi jajur dashi,sai kuma yazo yayi baƙiƙirin sosai ,wani irin hayaƙi na fita daga jikinsa .

Duk abinda yake sam fattu bata kulaba ,dan ta ɗaga  kanta sama ne tana karatun ,kuma idanunta na zubda kwalla.

Shikuwa macijin nan burburwa ya ci gaba dayi yana murɗewa jikinsa na turiri tare da sauya kala.can kuma ya fara wani irin ƙara mai kama da gurnanin  zaki.cikin tsoro fattu ta dawo da kanta ƙasa tana kallon macijin , sakamakon wannan sautin ƙara da taji yanayi.sai lokacin hankalinta ya kai kanshi taga abinda ke faruwa.

Tsorone ya kamata ƙarara "innalillahi wa'inna ilaihir raji'un"shikenan ta tabbata wannan ba maciji bane tabbas aljanine ,ko kuma aljanine  ya shiga jiki sa,na shiga uku ni fattu ya zanyi da rayuwata?meke shirin faruwa dani" ta faɗa cikin muryar tsoro da shiga ruɗu.

 Shikuwa macijin nan tana daina karatun saiya daina burburwar da wanann gurnanin,ahankali kuma jikinsa ya dawo yadda yake . Ya jima kwance lamo  kafin ya fara motsi,kansa ya ɗago tare da fasa kan  yana kallon fattu,gaba ɗaya idanunsa sun koma baƙiƙirin dasu sannan wasu irin ƙananan layoyi suka bayyana kusan guda uku aƙasan kanshi, sai wani irin motsi suke kamar ya'yan tsutsa.

Karkarwa jikin fattu keyi kamar an saka mata shokin, lamarin ya matukar bata tsoro ,meye wannan ɗin haka suka bayyana jikin macijin nan? Me yasa daga fara karatun Alqur'ani gaba daya ya sauya kama?tabbas akwai wani boyayyen al'amari game da wannan halittar dake gabanta,kuma zata ci gaba da bibiyar macijin nan sannu kan hankali har saita gano menene tattare dashi.

Tana nan maƙale jikin katangar karanta kamar ƙadangaruwa dan tsabar tsoro da shiga shock ,idanunta ƙuri akan macijin ,wanda shima ita yake kallo ,kusan minti biyar suna haka ,taga macijin ya sulale ya bar ɗakin ta wannan hanyar tashi.

Rarraba idanu ta farayi tana dafe da ƙirjinta ,yau kam tana ganin ikon Allah kala kala ,anya kuwa bata janyowa kanta masifa ba?waima meye alaƙarta da wannan halittar ne?ko dai baffanta zata sanarwa halin da ake ciki ne?kai a'a ba yanzu ba tukunna ,ya kamata ta zama jaruma tayi wanann aikin koba komai zata taimaki rayuwar macijin,dan ta fahimci akwai boyayyen al'amari atareda shi.

Su haroji kuwa gaba ɗaya ya fice daga hayyacinsa sai ihu yake yana faɗuwa ƙasa ,ahaka ya nufi gidan lamiɗon garin ,wanda shine mahaifin jauro ,yana ihu yana tumami, har yaje gaban lamiɗo ya faɗi yana "wayyo idanuna ,wayyo fuskata lamiɗo ka taimaka min.

Ruɗewa lamiɗo yayi wanda yake tsaye jikin wata sanuwa yana bata ciyawa, lamiɗo bashi da imani ,azalumine sosai ,kuma mutanen garin suna matuƙar tsoronsa, dan haka yake mulki na zalumci agarina,ganin halinda haroji yake ciki"kai haroji menene hakan ?ina jauro?me yasameka?sune tambayoyin da lamiɗo ya jerowa haroji

Cikin azabar ciwo da fitar hankali haroji yace "jauro ya mutu maciji ya cinye masa jauronsa yana bakin rafi"

Ai dajin wannan batu hankalin lamiɗo ya tashi ,nan da nan yayi kan haroji yana faɗin wane macijin ?me kake cewa ?jauro ya mutu?ƙaryane badai agarina ba ,ba wanda ya isa ya zo garina ya kashe min ɗana."lamiɗo na gama faɗin haka ya kira mazan garin ,ya sanar dasu maza aje bakin rafi ataho da jauro.

Aikuwa cikin ƙanƙanin lokaci aka ɗauko shi kamar gawa .

Nan da nan lamiɗo ya nemi haroji ya sanar dasu abinda ya faru .

Nan ya sanar dasu iya abinda idanunsa suka gani,dan shima yana cikin mugun halin mutuwa ko rayuwa dan tuni gurin da jinin nan na macijin ya taɓa ajikinsa yayi wani irin kore shar yana zubar da wani yallow ɗin ruwa .

"Lamiɗo fattu ce ta Turo mana macijin nan ,shine ya kashe jauro"abinda haroji ya faɗa kenan ya sume.

Nan da nan mutanen gurin suka fara maganganu Suna faɗin da "da hansai ta faɗa tace mayyace yarinyar ,tunda har ta fara kashe mutane ba zasu yarda ba sai an hukunta itama.

Ran lamiɗo ya ɓaci sosai ,dan dama yana jin haushi yarinyar  da ubanta,ya shirya neman aurenta amma sam taƙi yarda wai karatu take,yanzu kuwa dama tasameshi da zai hukunta su ita da tsohon nata.dan haka cikin bada umarni yace lallai lallai aje ataho da fattu da ubanta .

Nan da nan fusatattun  maza suka nufi gidan malam bukar dan aiwatar da ƙudurin lamiɗo.....

Masu karatu meke shirin faruwa ne ?

Wane hukuncin lamiɗo zai zartar akansu fattu?

Mai zai far nan gaba?

Muje zuwa yaki ce dai anty mammy

Mrs babi□□□

Share and comments fisabilillah.

More comments

More typing.

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJINE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

_____Nan da nan fusatattun rugar suka nufi gidan malam bukar ,dan aiwatar da ƙudirin lamiɗo.

Allah Sarki fattu kuwa a wanann lokacin tana ɗakinta cikin jimami da tunanin abinda ta  gani yau ɗin nan,haka nan ta tsinci kanta da son sanin menene wannan abubuwan dake motsi aƙasan wuyan maciji? wanda tun daɗewa bata taɓa ganinsu ba sai yau,waya sani ma ko wani akayiwa asiri ajikin macijin ?tabbas zatayi iya ƙoƙarin ta dan ganin ta raba macijin nan da wannan abubuwan ,ta yadda koda wani aka yiwa asiri  ta hanyar macijin, to asirin zai karye .sannan tana fargabar gwogwgo ta gano cewar tana gidan kuma bata ɗebo ruwan ba.kuma ahalin da ake ciki yanzu bazata iya komawa rafin nan ba ,.dan ta tsorata dasu jauro .

Hayaniyar mutane ce ta cika gidan  nasu fattu ,wanda haka yasa gwogwgo hansai fitowa dole badan ta soba, Dan har lokacin nan ita da yaranta ba wanda yayi sallar asuba.

"Kai su waye haka suka zo suka cika mana gida da  ihu kamar ana yaƙi?"cewar gwogwgo hansai tana gyara daurin ƙirjinta dake ƙoƙarin kuncewa bayan ta fito daga ɗakin.

"Aa meye hakan arɗo ?lafiya na Ganku da yawanku kun shigo?ta tambaya lokacin da idanunta ya sauka akan mutanen da suka cika gidan,kusan duk mazan garin ne.

Cikin masifa wanda aka kira da ardo yace "wllh yau saimun ɗauki mataki akan bukar da fattu ,haka kawai yarinya ta fara kashe mutane ,kuma ta rasa ta kan wa zata fara sai ɗan gidan lamiɗo ?wllh yau sai mun kashe Shegiyar yarinyar nan"ya faɗa yana wani zazzaro idanu kamar zararre.

Eh wllh afito mana da ita kawai mukaita gurin lamiɗo ya bamu izini mu kashe mayya.gaba ɗayan mutanen gurin suka faɗi haka cikin nuna fusata da ƙosawa abasu fattun .

Wani irin farin ciki da jin daɗine ya kama gwogwgo hansai ,shikenan zata rabu da alaƙaƙai cikin sauƙi Allah yasa akasheta kowa ya huta ,dama su haɗa da bukar ɗin da yake ɗaurewa fattu gindi ,koba komai shanunsa sun zama nata.gwogwgo hansai ta faɗa cikin ranta.kafin ta kalli ardo da sauran mutanen tace "aikuwa idan aka kasheta an kyauta ,dan nima nan wllh so take ta cinyeni nida yarana, jiya da kyar mukasha data maƙuremin wuya wai saita cinyeni, ku ɗan jira kaɗan yanzu zaku ganta shegiya gantalalliya,banma san inda ta tafiba, dama haka takeyi kullum inta fice yawon iskanci bata dawowa da wuri,tana can gurin maza"gwogwgo hansai ta ƙarasa maganarta tana mai buga hannu acinya.

"Aikuwa yanzu zamuje mu nemota ko ina ta shiga,wasu sutafi bakin rafin wasu sushiga jeji, mukuma zamu jira ana "cewar ardo kenan yana kafe sandarsa akasa,sannan ya gyara tsayuwarsa.

Duk wannan abunda ke faruwa akan kunnen fattu, tana jin komai ,saidai tashin hankali,firgici tsoro da kuma ruɗewa sun hanata koda yin kwakwkwaran motsine .

Numfashinta ma da ƙyar yake fita tsabar ruɗewa.

Ta shiga uku !shikenan yanzu kasheta za'ayi?laifin me tayi da za'a kasheta?me baffanta yayi ake nemansa shima? Dama jauron mutuwa yayi ? innalillahi !!!yanzu ya zatayi.

Wani kukane ya kubce mata cikin sauri ta toshe bakinta tana kuka sosai kamar ranta zai fita,ji take dama tana da ikon ɓacewa, tabbas da ba abinda zai hanata ɓacewa ta bar duniyar ma gaba ɗaya.

Ahankali ta miƙe cikin sanɗa ta leƙo da kanta ,ba ƙaramin tsoro tajiba lokacin da taga mutanen da suka zo tafiya da ita.shikena kawai ta mutu,yanzu shikenan bazata cika burinta na ganin innarta ba?wayyo "Allah ka kawomin ɗauki "ta faɗa cikin raunananiyar muryarta mai cike da tsantsar tsoro.

Ahankali ta ƙara leƙo da kanta waje ,cikin rashin Sa'a kuwa sukayi ido huɗu da dan gidan gwogwgo hansai umaru.wanda hayaniyar mutane tasa suma suka farka.

"Laaaah aradu gwogwgo ga fattun can cikin ɗakinta tana leƙowa"ya faɗa yana nuna ɗakin da Fattu ke ciki

.cikin hanzari fattu ta koma cikin ɗakin tana mai runtse idonta ,tare da dafe ƙirjinta."shikenan sun ganni wayyo Allah na baffa,wayyo MACIJINA kana ina kazo ka taimakeni zasu kasheni wayyo ni fattu"fattu ta faɗa tana mai leƙa hanyar nan da macijin Kebi idan zai bar ɗakin nata inya zo kamar Zariya haka take bankada hanyar macijin da hannunta.

"Munafuka ,mayya dama kina ji ana neman ki shine kika ɓuya nan?to fito yau dubunki ta cika ,mutuwa zakiyi wllh saikin bar duniyar nan yau nima na huta da ganinki ,maza arɗo zoka tafi ta ita gata nan"gwogwgo hansai ke faɗin wannan maganar tana daga bakin ƙofar dakin Fattu,dan tun lokacin nan da tasha matsa agurin maciji bata ƙara shiga ɗakin Fattun ba.

Aikuwa kafin ta rufe baki su arɗo sukayo kan Fattu suna janta.

"Wayyo Allah gwogwgo karki bari su tafi dani zasu kasheni ,wllh ban aikata komai ba wayyo Allah na gwogwgo ki taimaka min"abinda Fattu ke faɗi kenan tana miƙawa gwogwgo hannu cikin kuka mai tsanani.

"Ai wllh dana taimakeki gara hannuna ya karye Shegiyar yarinya ,kutafi da ita can ku kashe banza" gwogwgo ta faɗa tana kaɗa hannu irin yadda ake korar kaji ,cikin farin ciki take maganar.

Ihu Fattu keyi tana kuka,amma haka suke janta kamar akuya aƙasa, suna cikin tafiya ne ,saiga baffa aguje yazo gabansuu ya tsaya riƙe da sanda yana ta haki,dan

yana can bayan gari ya sami labarin abinda ke faruwa acikin garin da gidansa,shine ya rugo yazo .

Aikuwa Fattu na ganin baffa ta ƙara fasa ihu tana cewa" wayyo baffana ka taimakeni zasu kasheni" ta faɗa tana miƙa masa hannu,abin tausayi dukta susuce tayi buju buju da jiƙaƙkiyar ƙasa.kallonta baffa yayi

Cikin bacin rai mai tsanani ya ce.

"Sakarmin yarinya ardo,  kona rotsa maka sandar nan akanka" baffa ya faɗa cikin hargowa da ƙaraji,

Kasancewar baffa kowa  ya sanshi arugar mutumin kirki ne ,sam ba ruwansa da shiga harkar wani,sanan kuma shine ke ja musu jam'i ,hakan yasa suke ɗan ganin girma da mutuncinsa, dan haka cikin Turo baki da hura hanci  ardo yasaki hannun Fattu wanda ke mata azabar ciwo da raɗaɗi,yana mai cewa"ato lamiɗo ne dai yace mu taho daku,dan haka ya zama dole ayiwa lamiɗo biyayya"ya faɗa yana hararar gefensa, dan yaji haushin sakin wannan hannun na Fattu mai shegen laushi da daɗin taɓawa da baffa yasa yayi.lol

Fattu kuwa yana sakar mata hannu ,da rarrafe ta ƙara so gurin baffa ta rirriƙe shi tana kuka da faɗin"wllh baffa ba abinda na aikata,ban kashe jauro ba " ta faɗa cikin matsanancin kuka da tsoro, jikin ta sai rawa yake.

Riƙota baffa yayi cikin tausayawa yace "na sani Fattuna,baki kashe jauro ba ,kuma ba wanda zai kasheki, Allah na tare dake kinji"?ya faɗa cikin sigar rarashi,sannan ya kalli ardo yace"kai ardo ka kiyayeni ,karka ƙara ƙoƙarin  sake aikata irin wannan dabbacin akan yata, saboda baka da hankali shine zaka rinƙa janta aƙasa. Kamar wata dabba ?jahilan banza jahilin hofi,muje gurin mai garin zanji idan shiyasaka wannan ɗanyen aikin"baffa ya faɗa cikin mugun bacin rai yana mai riƙe Fattu suka nufi faɗa.

Lamiɗo na hangosu ya fara lasar baki ya kure fattu da idanu kamar maye , yana kissima abubuwa da dama cikin ransa....

Manage please yau ina busy,Dan banyi niyar typing bama yau wllh.

Masu karatu me lamiɗo ke nufine shima?

Hmmmmmm kubiyoni mu hade bayan sallah  danjin yadda zata kaya.

Kafin nan ina mana fatan yin salla lafiya,sannan aci Nama ahankali kar azo ana .....

Taku anty mammy

Mrs babi,□□□

□□□□□□□□

MACIJINE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

Ta ƙabbalallahu Minna waninkum.

Slm, yɗan uwa masoyan littafin MACIJINE, ina  miƙo gaisuwa tare da Barka da Sallah ,Allah ya maimaita mana,yasa munyi karɓaɓɓiyar

Ibada.

_____Kai tsaye su baffa suka nufi gurin lamiɗo,hannunsa riƙe da na fattu ,wacce ke tafiya ahankali cikin azabar raɗaɗin  da hannunta keyi,dakuma ciwon jiki.yayinda su arɗo ke mara musu baya burinsu kawai suga wane irin hukunci lamiɗo zai ɗauka akansu fattu ,cikin zuciyarsa arɗo yake fatan inama lamiɗo ya kori su fattu daga rugar ,inyaso su bisu hanya  suyiwa fattun fyaɗe,dan su kashe ƙishirwarta dake cin ransu.

Shikuwa mai gari tun daga nesa ya hango su fattu,gaba ɗaya nutsuwarsa ta bar jikinsa,ƙureta yayi da ido guri!!yana haɗiyar yawu da lasar leɓe kamar tsohon maye.

Kallonta yake yana ji kamar yaje ya kamota yayi ɗaka da ita.

haba malam ,yarinya bul-bul  da ita kamar nunannen tumatur,lallai yau zai sha shagali.lamiɗo ya faɗa cikin ransa yana mai kallon fattun.

Baffa kuwa suna ƙarasowa gaban mai gari ya nemi guri ya zauna tare da zaunar da fattu kusa dashi,wacce gaba ɗaya arikice take ,tsorone ƙarara shinfiɗe akan fuskarta.tayi luƙus ajikin baffanta jikinta sai rawa yake, ta kasa ɗaga kanta ta kalli kowa ,sai hawaye take sharewa.

Kowa yanemi guri ya zauna ,masu tsayuwa suka tsaya , da ƙyar lamiɗo ya iya saita kansa ya aro nutsuwa ya  yaɓa  akansa, tare da ɓata ransa ya kalli  baffa yace "malam bukar kana sane da irin abinda yɑrka take aikatawa awannan garin ?lamiɗo ya faɗa cikin kakkausar murya .

Ahankali baffa ya gyara zama kafin yace ,naji anata  wai wai  agari cewar yɑta tayiwa su jauro turen maciji ,amma sam ban yarda da wannan magana ba,dan kuwa yɑta ba mai kashe mutane bace ,sannan ba mayya bace kamar yadda ake faɗa"baffa ya faɗa cikin ɗaure fuska .

 Cike da ɓaci rai lamiɗo ya fara magana.

"To wllh malam bukar bazan ɗauki wannan abun agarina ba,yanzu ace abun nata ya wuce kan kowa sai kan ɗana  ?sannan kuma kace wai baka

yarda da zancen ba ?kana nufin nayi maka ƙarya ne?to bari kaji dole ne saina ɗauki mataki mai ƙarfi akanka da yɑr taka ,dan ka nuna rashin ɗa'a a gaban fada.bayan kuma kowa yaga abinda yɑrka tayiwa yaranmu,

Dan haka  bazan yanke hukunci yanzuba sai zuwa gobe ,idan yaranmu  sun sami lafiya,dan haka yanzu za'a shiga da ita cikin gida anan zata zauna cikin wancan bukkar da ake ajiye masu laifi .

Dan haka kowa ya watse sai zuwa gobe da la'asar adawo nan dan jin hukuncin da zan yanke"mai gari yana gama faɗin haka ya jingina da jikin kujerar da yake zaune akai.

gaba ɗayan mutanen dake  gurin sunyi na'am da wannan hukuncin nacewar fattu ta zauna a gidan mai gari ,dan karta gudu.

Kuka sosai fattu ta sanya tana riƙe hannun baffa "wayyo Allah na baffa ka taimakeni,dan Allah karka bari akulleni adakin hukunci ,wllh bani nayi musu haka ba ,kuma sunzone da nufin keta min haddi baffa ka kalli Yadda ya famamin targaɗe na wllh ba laifi na bane" fattu ta faɗa cikin matsanancin kuka kamar zata shiɗe.

Cikin tashin hankali baffa ya riƙe hannun Fattu ,ji yake kamar ya fasa ihu,aduniya ba abinda ya tsana irin  yaga Fattu cikin damuwa,"kiyi haƙuri fattu ba abinda zai sameki,in Sha Allahu Allah zai saka mana dan wannan mugunta ce ake son yi mana ,kuma Allah yana bayan mai gaskiya"yana gama faɗin haka ya juya gurin mai gari yace "lamiɗo ina neman alfarmar abarmin fattu mu tafi gida ,zamu dawo da ita zuwa goben,dan bata da lafiya kuma barinta ita kaɗai akwai matsala" ya faɗa cikin damuwa da alhinin wannan rashin adalci da ake ƙoƙarin aiwatar musu.

Cike da mugunta lamiɗo yace "kai bukar ina ganin girmanka karkasa in daina gani ka iya bakinka a faɗa kake,kasan idan na riga yanke hukunci ba mai ja dani ,dan haka ka tashi ka bani guri tun kafin raina ya gama ɓaci kuma yanzu zansa aje anemomin macijin duk inda ya shiga daga nan zuwa safiya ,"lamiɗo ya faɗa  yana mai kiran wasu matasa yace su shigar da fattu cikin bukkar.

Kuka fattu keyi tana faɗin"wayyo baffana wayyo Allah ka taimakamin zasu tafi dani wayyo Baffa na karka bari su nemo shi zasu kasheshi. "amma haka suka tura ƙeyarta suka tafi da ita ɗakin hukunci.baffa yana ji yana gani ,hawayene masu zafi suka silalo daga idon bawan Allah ,zuciyarsa kamar ta faso ƙirjinsa yakeji, ashe ma ƙoƙarin keta masa haddin yɑ akayi?amma saboda rashin imani  da adalci aka ɗora mata sharri,ba komai Allah zai saka musu.

Juyawa yayi ya nufi gida ransa amatukar jagule,yanzu idan wani abun ya sami yarinyar fa?idan wasu suka ƙara yunƙurin cutar da rayuwarta fa?"ya Allah ka karemin yarinyar nan Allah ka duba matsalolin dake kanta da wanda suke shirin samunta.ya Allah ka sauƙaƙa mata ƙalubalen dake gabanta.haka  yayi ta mata addu'a harya ƙarasa gida kwata kwata hankalinsa baya jikinsa.

Yana shiga gidan  gwogwgo hansai ta sanya dariya cike da mugunta harda riƙe ciki tana nuna baffa da hannu."wllh malam Gara ka cire wannan yarinyar daga zuciyarka,  inba haka ba kana tsaye zaka yanke jiki ka faɗi ka mutu.ba ruwa  na bani da asara, ai wllh banso lamiɗo ya kyaleta wai har sai gobe ba,daya sani yasa anyanke mata kai yau -yau ɗin nan ,da mun huta da nauyinta akanmu" ta faɗa tana turo wani baƙin ɗan kwalinta mai shegen datti zuwa gaban goshinta.

Kallon ta kawai baffa keyi ,cikin zuciyarsa yake kissima iri saɓawa gwogwgo da zaiyi dan yau zai nuna mata matsayin fattu azuciyarsa ,sai dai yana yunƙurowa da nufin maida mata martani,kawai yaji bakinsa yayi nauyi,wani irin shayinta da tsoro ya mamaye zuciyarsa.kai kawai ya girgiza ya wuce ɗakinsa ,wato itama gidan mai garin taje kenan?ba komai akwai Allah.

Fattu kuwa tunda aka turata cikin ɗakin nan banda kuka ba abinda takeyi, ita damuwarta ma yanzu bai wuce na rashin ganin macijinta ba,duk wannan abunda ke faruwa baizo ba.anya kuwa lafiya?kodai wani abu ya sameshi ne?

"Ya Allah ka kare wannan bawan naka ,ka bashi kariya daga sharrin mugayen mutane .

Shikuwa maciji adaidai wannan lokacin yana gidansu fattu yaje nemanta bai ganta ba yayi ta zagaye aɗakinta amma bata nan,tun lokacin datayi masa karatun nan daya fita yaje can jeji ya kwanta ,sam bayajin daɗin jikinsa sosai yake jin ciwo ta ko'ina ajikinsa,sai da lokaci yaja sannan ya nufi gidansu fattu ,ahankali yake tafiya cikin ciyawa da jikin katanga, harya ƙarasa gidansu fattu.

Koda yaje yaga bata nan saiya yi ta zagaye ɗakin yana nemanta ,amma bata nan. Kwanciya yayi akan ɗaurin kayanta yayi lamo kamar ya mutu.saidai hawayene ke zuba cikin idanunsa .

Can kuwa gidan mai gari ,da misalin ƙarfe bakwai na dare sosai hadari ya haɗu agarin, dan haka kowa ya shige cikin gida dan gudun zubowar ruwan,da akowane lokaci yana iya sauƙa.

Daidai wannan lokacin kuma fattu na duƙunƙune cikin ɗakin  hukunci sai kuka take zuciyarta tayi mata ƙunci ga yunwa dake addabar ta rabo ta da abinci tun madarar da baffa ya bata da safe.hannunta sai zagi yake mata.

Ahankali taji ana turo kofar ɗakin hukuncin,da alama shigowa za'ayi,ga duhu aɗakin.

Zabura tayi cikin sauri ta miƙe tsaye jikinta na karkarwa,kar dai ace su jaurone suka dawo ?wayyo  Allah na " ta faɗa tana dafe ƙirjinta ,zuciyarta kamar zata fito dan tsoro da firgici.

Cikin rawar murya tace "wa...w....ayee."

Ahankali cikin murya mai kama da raɗa,yace "ke kwantar da hankalinki,nine nan lamiɗo"

Ya faɗa yana mai haska tocilan ɗinsa  .

Cikin zubar da hawaye tace "dan Allah lamiɗo ka fitar dani daga gurin nan ,wllh ban aikata komai ba,bani na kashe jauro ba"ta faɗa cikin kuka.

"Kinga ki nutsu jauro bai mutu ba yana raye ,kuma idan kika bani haɗin kai muka yi komai  cikin sirri ,to zan kyale ki ki tafi gida abinki"lamiɗo ya faɗa yana matsowa gareta.

Ja tayi da baya cikin sauri tace "me kake so nayi maka ?dan Allah ka gyaleni na tafi gida ,an fara ruwa"ta faɗa cikin kuka,dan ta gano manufarsa ,irin tasu jauro ce ,wato fyaɗe yake son yi mata.

Matsowa lamiɗo yayi tare da ruƙo hannunta yana mai cewa"Ayya fattu yarinya mai kyau da kyan jiki ki yarda dani mana duka -duka minti nawa ne ba dayawa zanyi ba kinji ki taimaka min"ya faɗa yana mai janyota jikinsa sosai .

"Wayyo Allah na baffa kazo ka taimakeni,dan Allah lamiɗo kayi haƙuri wllh ba kyau kaji tsoron Allah ka tausaya min na roƙeka"fattu ta faɗa cikin rawar jiki da matsanancin kuka,tana mai tureshi daga jikinta,banda warin tsufa ba abinda yake yi.

"Ke dan ubanki ki tsaya ko saina miki ta ƙarfine?Shegiyar yarinya haka zamu zuba miki ido muna kallonki kin cika kinyi tunjum dake amma ba mai morarki,ki tsaya dan ubanki"lamiɗo ya faɗa yana mai ɗauke fattu da wani gigitaccen mari Wanda saida ji da ganinta suka tsaya na wucin gadi.kusan minti biyu kafin kwakwalwar ta ta dawo aiki,kuka ta sake fashewa dashi mai tsananin gaske lokacin da lamiɗon ya Kaita ƙasa yana ƙoƙarin dage yar ficiciyar rigar dake jikinta ,wacce jiƙaƙkiyar ƙasar nan ta gama bushewa .

"Innalillahi wa inna ilaihir raji'un wayyo Allah na baffa wayyo mai taimako kana ina? kazo gareni,ina buƙatar taimako ka ahhhhhhhh "fattu ta kwalla wani irin ƙara mai ƙarfi lokacin da lamiɗo yayi.....

Tofa masu karatu me lamiɗo yayiwa fattu ne ?

Muje zuwa kuci gaba  da bin alƙalamin anty mammy.

Mrs babi □□

Share and comment fisabilillah

More comment

More typing.

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJINE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

_____"Wayyo Allah na Mai taimako kana ina?kazo gareni,ina buƙatar tallafinka,ahhhhhhhhh !!!fattu ta kwalla ƙara mai tsananin ƙarfi lokacin da taji hannun maigari na ƙoƙarin taɓa mata dukiyar fulani tana mai buge hannunsa daga kan ƙirjinta.

Ɗaga hannu maigari yayi cikin fushi ya sake ɗauke fattu da wani gigitaccen mari,dan ya fuskanci tana ƙoƙarin kawo masa cikas akan ƙudurinsa,shikuwa ya rantse yau bazai bar wannan damar ta wuce shi ba.

"Dan ubanki ki tsaya nayi- nayi abinda ke gabana,wllh yau ko ubankine bukar zai zo gurin nan bai isa ya hanani aiwatar da ƙudirina akanki ba"mai gari ya faɗa yana ƙara ƙoƙarin maida hannunsa gurin dake tsole masa idanu,wato  breast ɗin fattu.

Saidai kafin hannunsa ya sauƙa ga inda yayi nufin ,yaji  wata irin shaƙa da tunda yake arayuwarsa bai taɓa tsintar kansa cikin irin makamancin wannan shaƙar a aduniya ba.

Ta ko ina yaji shi aɗaure dam-dam kamar ƙullin buhun goro.

Cikin azaba da fizgar magana mai gari yace "wayyo Allah hannuna,na shiga uku wayyo zan mutu"  ya faɗa idanunsa azazzare kamar zasu fito tsabar azaba.

Cikin hanzari fattu wacce idanunta ke rufe, ta riga ta gama fitar da rai ta sadaƙar cewa yau shikenan ta rasa budurcinta ,dan ta san ba mai zuwa ya ceceta ,koda tayi ihu ba mai jin sautin ihunta,sakamakon ruwan saman da ake tsugawa.ba zato ba tsammani tajiyo ihun maigari lokacin da maciji yayi sama dashi  ya cilla shi can gefe guda ,bayan tabbatar da cewa mai gari ya suma.ji kake ƙasss-ƙasss,hannu da ƙafar mai gari na bangaren dama sun karye.

Da sauri fattu ta kalli inda akayo jifa da mai gari dan tabbatar da cewar shiɗin ne kokuma yaya.aikuwa cikin wani irin farin ciki da murna ta yunƙura da ƙyar ta zauna tana kuka da dariya,sai kuma ta tafi gareshi cikin rarrafe tana zuwa inda macijin ke tsaye yana huci ya ƙure mai gari da ido,da alama yana son ganin maigari ko zaiyi

wani motsin ne yaje ya ƙarasashi,duba da yadda yake ta uban huci ya kafe mai garin da ido.

Fattu na zuwa ta wani kwaƙume  macijin zuwa jikinta ,ta ƙanƙameshi tana kuka kamar ran ta zai fita,kukanta na dalilai biyu ne,dalili na farko shine ganin macijinta na nan araye ba mutuwa yayi ba,kuma masu neman shi basu ganshi ba.na biyu kuma yadda yazo ya kawo mata ɗauki adaidai lokacin da ta fidda rai da  cewar zata rasa abu mafi muhimmanci arayuwarta.

"Ina ka shiga mai taimakona?na shiga damuwa na rashin ganinka, naji tsoron ko sun kamaka sun kashe ,dan Allah karka ƙara yin nesa dani na tsawon lokaci irin haka,kalli yadda suke son kawar min da budurcina, bansan me na tsare musu ba ,kowa nufinsa ya cutar dani,kai kadai ke sona,sai baffana ,bana son na rasa ɗaya daga cikinku ,kune rayuwata,farin cikina da jin daɗina,mai taimakona ina sonka har cikin zuciyata, ba ruwana da kasancewarka wata halitta ta daban,Dan kafiyemin halitta irin tawa sau dubu"duk cikin kuka fattu ke faɗin Waɗan nan maganganu,yayi da take ƙanƙame da macijinta kamar zata maida shi cikinta.yadda ta ƙanƙameshi, kai kace uwace ake ƙoƙarin rabata da ɗanta.

Ahankali macijin nan ke sauƙe wani irin numfashi kamar yana hurawa fattu iska mai sanyi ,da alama dai rarrashinta yakeyi,dan yadda yake huro iskar yana wani rufe ido da buɗewa shine zai fahimtar da kai cewar rarrashinta yake .

Zare jikinsa yayi daga ƙwaƙwumar da fattu tayi masa ya zagaye west ɗinta ,Amma Sam bai matseta ba ,sannan ya shigo da kanshi ta ƙirjinta yana kallon fuskarta yadda hawaye yayi faca -faca kan kyakkyawar fuskar tata.kallon -kallo ake tsakanin fattu da macijinta ,kallo yake mata irin na tausayawa dan abin mamaki ne sosai idan kaga yadda ya wani marairaice fuska yana ƙifta idanunsa tare da ɗan matso da kansa saitin fuskarta,sai kuma ya kwantar da kan nashi saitin da hawayenta ke tsiyaya, ta ɓangaren dama, sannan yayiwa ɓangaren hagun ma haka.

"Dariya mai haɗe da kuka fattu take yi cike da tsantsar ƙaunar wannan halitta ,hannu ta sanya ta share hawayen daya ƙara zubowa tace "na daina kukan mai taimako tunda baka so ,bazan ƙara ba ka gani ma ko "ta faɗa tana mai ƙara shafe idanunta ,saidai wasu hawayen na ƙara zubowa.

Zare jikinsa yayi yana mai hawa kan wuyanta zuwa kanta saiya leƙo da kansa ta saman kanta ,idan ta ɗago da nufin kallonsa saiya silale ya koma wuyanta ya ɓoye kansa abayanta.

Dariya fattu take cikin farin ciki da ganin cewar wai wasa yake mata dan ta sami nutsuwa ta daina kukan ,dan haka lokacin daya ɓoye abayanta sai tace "wayyo ni fattu mai taimakona ya ɓata, ya zanyi da rayuwata ,ina kake abinsona shikenan masu son cutar dani zasu sami dama akaina wayyo ga mai gari nan ya taso"ta faɗa cikin yanayi kamar tana son yin kuka .aikuwa cikin sauri macijin nan ya haye kan cinyarta yana mai fasa kai da wani kalle -kalle ya miƙa kansa can ya dawo dashi can yana huci.

Dariya fattu tayi tace "nima ramawa nayi tunda ka boyemin " ta faɗa cikin shagwaɓa kamar wacce ke gaban baffanta ko innarta.

Juyowa macijin yayi yana kallonta sai kuma ya ɗora kansa daidai saitin zuciyarta yayi lamo ,tare da rufe idanunsa.ahankali ta sanya hannu tana shafa kyakyakywan jikinsa mai matuƙar santsi da laushi.kusan minti biyar suna haka,yayinda ake tafaman zuga ruwan sama ,can gefe kuma mai garine shame shame akwance baya motsi.kallon mai gari fattu tayi ,sai taji tsoro ya cika zuciyarta,kodai shima mutuwa yayi, dan ita tama manta da batunsa aɗakin sam,idan kuma ya farka ya ƙara dawo mata fa ,gara fa su gudu daga ɗakin nan tun kafin jama'a su ankare dasu.

Cikin muryar tsoro tace "mai taimako ya kamata mu gudu gida karya farka ko wani yazo ya gammu dashi ahaka"ta faɗa tana kallon macijin dake kwance akan ƙirjinta,da alama kuma yana jin daɗin kasancewarsa ahakan.

Ahankali ya ɗago kansa tare da silalewa ƙasa yayi hanyar ƙofar fita daga bukkar,wacce mai gari ya barta abuɗe tsabar jaraba na cinsa.

Binsa fattu tayi da sauri ,harta fita saikuma ta dawo ta ɗauke tocilan nan ta mai gari ,dan taga garin yayi baƙi ƙirin kuma har lokacin ruwa ake.

Suna fita fattu ta kama sauri -sauri gudu-gudu ,tana tafe tana haska tocilan ɗin nan ,yayinda mai taimako ke biye da ita cikin salon nashi gudun ,saidai suna tafe yana zagayeta ,dan bata kariya ta kowacce kusurwa.

Suna zuwa gida kai tsaye fattu ɗakin baffa ta nufa,tana zuwa ta shiga ɗakin ahankali tana haska tocilan ɗin hannunta.Allah sarki baffa yana kan sallaya ya ɗaya hannunsa sama yana ta addu'a,juyowa yayi dan ganin hasken da ake haskowa.

"Waye anan"ya faɗa yana kunna tashi tocilan ɗin.

Ai da sauri ya miƙe tsaye yayi kan fattu,yana mai cewa"fattu kece alhmdllh fattu na ba abinda ya sameki,?ina mai garin?waye ya fito dake?baffa ya jero mata waɗannan tambayoyin alokaci guda yana mai shafa kanta cikin farin ciki .

Ahankali fattu ta kalli gefenta ta ƙasa inda macijin nan ke nannaɗe ya fasa kansa yana kallon baffa.tace "baffa wannan ne ya taimakeni, kuma shine macijin daya hukunta su jauro "ta faɗa tana haska macijin da tocilan.

Da sauri baffa yaja baya yana faɗin"subhanalla fattu wannan ai MACIJINE ,meye haɗinki dashi,matsa daga gareshi maza karya cutar dake" baffa ya faɗa cikin tsoro yana mai kamo hannun Fattu.

"Baffa ka kwantar da hankalinka ,ba abinda zai min ,domin mun jima tare dashi,zauna baffa in baka labarin haɗuwata dashi ,sannan baffa macijin nan yana cikin matsala ,dan da alama anyi amfani dashi wajen yiwa wani asiri.

Zama baffa yayi ahankali kan sallarsa ,idonsa akan macijin nan ,daya matso kusa da fattu wacce ke zaune kusa da baffanta,kallon ikon Allah baffa keyi, yadda macijin nan yayi kane-kane akan cinyar  fattunsa ya waniyi lub kamar jariri akan cinyar mahaifiyarsa.

Kallon fattu baffa yayi ,yaga ko ajikinta saima hannu data ɗora akan bayan macijin tana shafawa.

"Ina jinki fattu faɗa min komai dan hankalinta ya kwanta"

Nan fattu ta fara bashi labari tun daga farko har kawo yanzu.

Sannan ta ɗora da cewa "baffa dan Allah mu taimaki wannan macijin dan wllh yana cikin matsala ,bakaga yadda ya koma ba lokacin dana ke masa karatu,mu cire masa wannan masifar dake jikinsa"ta faɗa tana nunawa baffa waɗannan layun dake wuyan macijin.

Cike da mamaki da al'ajabi baffa ke kallon macijin ,wanda ya ƙara kafewa jikin fattu yana kallon baffa da kuma fattu.baffa yace "haƙika akwai wani ɓoyayyen al'amari dangane da wannan macijin ,kuma in sha Allah zamu taimaka masa iyakar ƙarfin

mu,tun kafin mai gari ya farfaɗo ya ɗauki matakin kashe macijin nan ,yanzu kije kiyi alwala ki dawo,dan  mu fara aiki akansa.

Cike da ɗoki fattu ta amsa da" to baffa na ina godiya agareta sosai"sannan ta ajiye macijin gefen baffa tace "mai taimako ai kasan baffana ko?to katsaya agurinsa yan zu zan dawo kaji"ta faɗa cikin murmushi tana shafa bayansa.

Kallo ta kawai yayi kafin ya kwantar da kansa ajikin gangar jikinsa dake nannaɗe.

Bayan fattu tayi alwala ta dawo dakin ne ta gabatar da sallolin dake kanta ,sannan tayi addu'ar samun nasara akan ceton macijin nan ta shafa.sanna ta juyo gurin baffa wanda ke ta tofa addu'a cikin wata ƙwarya ,zama ta gyara tana mai kallon baffa da jiran ya kammala addu'ar sa.

Shikuwa macijin nan yana ganin fattu ta zauna ya silalo ya dawo kan cinyarta ya kwanta,gaba ɗaya jikinsa asanyaye yake,kamar wanda yake tsoron faruwar wani abu.kallonsa fattu tayi tace "mai taimako ba abinda zai sameka ka kwantar da hankalinka ,in Sha Allahu zamu cire maka duk wani sihiri da akayi amfani dakai wajen yinsa"ta faɗa tana mai shafa lallausan san jikinsa mai santsi.

Miƙa mata kwaryar nan baffa yayi yace karɓi wannan fattu ki yayyafar masa ajikinsa ,kinayi kina karanta ayatul kursiyyu da falaƙi da nasi, duk abinda zaki gani karki tsorata kinji ?"baffa ya faɗa yana mika mata kwaryar,dan shikam ya gama fahimtar abubuwa da dama aka. Macijin nan.

Karɓa fattu tayi cikin nutsuwa ta fara karatun tana kuma shafa masa ruwan rubutun nan ajikinsa.

Ikon Allah,ai da fara shafa masa ruwan nan ajikinsa ya fara wani irin motsi da jijjiga ,yana murɗewa ,baffa kuma saiya ci gaba da addu'a yana tofa masa.

Ahankali hannun Fattu ya kai kan waɗaɗan na layin dake wuyan macijin nan,aikuwa damƙarsu tayi da Bismillah ta fizge da ƙarfin gaske.

Wata irin ƙara da guguwa ne suka turnike dakin gaba ɗaya baka iya ganin komai sai duhu.....

Masu karatu mutara gaba dan jin ya zata kaya.

Takuce dai Mrs babi□□

More typing.

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJINE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

_____"Wayyo Allah na Mai taimako kana ina?kazo gareni,ina buƙatar tallafinka,ahhhhhhhhh !!!fattu ta kwalla ƙara mai tsananin ƙarfi lokacin da taji hannun maigari na ƙoƙarin taɓa mata dukiyar fulani tana mai buge hannunsa daga kan ƙirjinta.

Ɗaga hannu maigari yayi cikin fushi ya sake ɗauke fattu da wani gigitaccen mari,dan ya fuskanci tana ƙoƙarin kawo masa cikas akan ƙudurinsa,shikuwa ya rantse yau bazai bar wannan damar ta wuce shi ba.

"Dan ubanki ki tsaya nayi- nayi abinda ke gabana,wllh yau ko ubankine bukar zai zo gurin nan bai isa ya hanani aiwatar da ƙudirina akanki ba"mai gari ya faɗa yana ƙara ƙoƙarin maida hannunsa gurin dake tsole masa idanu,wato  breast ɗin fattu.

Saidai kafin hannunsa ya sauƙa ga inda yayi nufin ,yaji  wata irin shaƙa da tunda yake arayuwarsa bai taɓa tsintar kansa cikin irin makamancin wannan shaƙar a aduniya ba.

Ta ko ina yaji shi aɗaure dam-dam kamar ƙullin buhun goro.

Cikin azaba da fizgar magana mai gari yace "wayyo Allah hannuna,na shiga uku wayyo zan mutu"  ya faɗa idanunsa azazzare kamar zasu fito tsabar azaba.

Cikin hanzari fattu wacce idanunta ke rufe, ta riga ta gama fitar da rai ta sadaƙar cewa yau shikenan ta rasa budurcinta ,dan ta san ba mai zuwa ya ceceta ,koda tayi ihu ba mai jin sautin ihunta,sakamakon ruwan saman da ake tsugawa.ba zato ba tsammani tajiyo ihun maigari lokacin da maciji yayi sama dashi  ya cilla shi can gefe guda ,bayan tabbatar da cewa mai gari ya suma.ji kake ƙasss-ƙasss,hannu da ƙafar mai gari na bangaren dama sun karye.

Da sauri fattu ta kalli inda akayo jifa da mai gari dan tabbatar da cewar shiɗin ne kokuma yaya.aikuwa cikin wani irin farin ciki da murna ta yunƙura da ƙyar ta zauna tana kuka da dariya,sai kuma ta tafi gareshi cikin rarrafe tana zuwa inda macijin ke tsaye yana huci ya ƙure mai gari da ido,da alama yana son ganin maigari ko zaiyi

wani motsin ne yaje ya ƙarasashi,duba da yadda yake ta uban huci ya kafe mai garin da ido.

Fattu na zuwa ta wani kwaƙume  macijin zuwa jikinta ,ta ƙanƙameshi tana kuka kamar ran ta zai fita,kukanta na dalilai biyu ne,dalili na farko shine ganin macijinta na nan araye ba mutuwa yayi ba,kuma masu neman shi basu ganshi ba.na biyu kuma yadda yazo ya kawo mata ɗauki adaidai lokacin da ta fidda rai da  cewar zata rasa abu mafi muhimmanci arayuwarta.

"Ina ka shiga mai taimakona?na shiga damuwa na rashin ganinka, naji tsoron ko sun kamaka sun kashe ,dan Allah karka ƙara yin nesa dani na tsawon lokaci irin haka,kalli yadda suke son kawar min da budurcina, bansan me na tsare musu ba ,kowa nufinsa ya cutar dani,kai kadai ke sona,sai baffana ,bana son na rasa ɗaya daga cikinku ,kune rayuwata,farin cikina da jin daɗina,mai taimakona ina sonka har cikin zuciyata, ba ruwana da kasancewarka wata halitta ta daban,Dan kafiyemin halitta irin tawa sau dubu"duk cikin kuka fattu ke faɗin Waɗan nan maganganu,yayi da take ƙanƙame da macijinta kamar zata maida shi cikinta.yadda ta ƙanƙameshi, kai kace uwace ake ƙoƙarin rabata da ɗanta.

Ahankali macijin nan ke sauƙe wani irin numfashi kamar yana hurawa fattu iska mai sanyi ,da alama dai rarrashinta yakeyi,dan yadda yake huro iskar yana wani rufe ido da buɗewa shine zai fahimtar da kai cewar rarrashinta yake .

Zare jikinsa yayi daga ƙwaƙwumar da fattu tayi masa ya zagaye west ɗinta ,Amma Sam bai matseta ba ,sannan ya shigo da kanshi ta ƙirjinta yana kallon fuskarta yadda hawaye yayi faca -faca kan kyakkyawar fuskar tata.kallon -kallo ake tsakanin fattu da macijinta ,kallo yake mata irin na tausayawa dan abin mamaki ne sosai idan kaga yadda ya wani marairaice fuska yana ƙifta idanunsa tare da ɗan matso da kansa saitin fuskarta,sai kuma ya kwantar da kan nashi saitin da hawayenta ke tsiyaya, ta ɓangaren dama, sannan yayiwa ɓangaren hagun ma haka.

"Dariya mai haɗe da kuka fattu take yi cike da tsantsar ƙaunar wannan halitta ,hannu ta sanya ta share hawayen daya ƙara zubowa tace "na daina kukan mai taimako tunda baka so ,bazan ƙara ba ka gani ma ko "ta faɗa tana mai ƙara shafe idanunta ,saidai wasu hawayen na ƙara zubowa.

Zare jikinsa yayi yana mai hawa kan wuyanta zuwa kanta saiya leƙo da kansa ta saman kanta ,idan ta ɗago da nufin kallonsa saiya silale ya koma wuyanta ya ɓoye kansa abayanta.

Dariya fattu take cikin farin ciki da ganin cewar wai wasa yake mata dan ta sami nutsuwa ta daina kukan ,dan haka lokacin daya ɓoye abayanta sai tace "wayyo ni fattu mai taimakona ya ɓata, ya zanyi da rayuwata ,ina kake abinsona shikenan masu son cutar dani zasu sami dama akaina wayyo ga mai gari nan ya taso"ta faɗa cikin yanayi kamar tana son yin kuka .aikuwa cikin sauri macijin nan ya haye kan cinyarta yana mai fasa kai da wani kalle -kalle ya miƙa kansa can ya dawo dashi can yana huci.

Dariya fattu tayi tace "nima ramawa nayi tunda ka boyemin " ta faɗa cikin shagwaɓa kamar wacce ke gaban baffanta ko innarta.

Juyowa macijin yayi yana kallonta sai kuma ya ɗora kansa daidai saitin zuciyarta yayi lamo ,tare da rufe idanunsa.ahankali ta sanya hannu tana shafa kyakyakywan jikinsa mai matuƙar santsi da laushi.kusan minti biyar suna haka,yayinda ake tafaman zuga ruwan sama ,can gefe kuma mai garine shame shame akwance baya motsi.kallon mai gari fattu tayi ,sai taji tsoro ya cika zuciyarta,kodai shima mutuwa yayi, dan ita tama manta da batunsa aɗakin sam,idan kuma ya farka ya ƙara dawo mata fa ,gara fa su gudu daga ɗakin nan tun kafin jama'a su ankare dasu.

Cikin muryar tsoro tace "mai taimako ya kamata mu gudu gida karya farka ko wani yazo ya gammu dashi ahaka"ta faɗa tana kallon macijin dake kwance akan ƙirjinta,da alama kuma yana jin daɗin kasancewarsa ahakan.

Ahankali ya ɗago kansa tare da silalewa ƙasa yayi hanyar ƙofar fita daga bukkar,wacce mai gari ya barta abuɗe tsabar jaraba na cinsa.

Binsa fattu tayi da sauri ,harta fita saikuma ta dawo ta ɗauke tocilan nan ta mai gari ,dan taga garin yayi baƙi ƙirin kuma har lokacin ruwa ake.

Suna fita fattu ta kama sauri -sauri gudu-gudu ,tana tafe tana haska tocilan ɗin nan ,yayinda mai taimako ke biye da ita cikin salon nashi gudun ,saidai suna tafe yana zagayeta ,dan bata kariya ta kowacce kusurwa.

Suna zuwa gida kai tsaye fattu ɗakin baffa ta nufa,tana zuwa ta shiga ɗakin ahankali tana haska tocilan ɗin hannunta.Allah sarki baffa yana kan sallaya ya ɗaya hannunsa sama yana ta addu'a,juyowa yayi dan ganin hasken da ake haskowa.

"Waye anan"ya faɗa yana kunna tashi tocilan ɗin.

Ai da sauri ya miƙe tsaye yayi kan fattu,yana mai cewa"fattu kece alhmdllh fattu na ba abinda ya sameki,?ina mai garin?waye ya fito dake?baffa ya jero mata waɗannan tambayoyin alokaci guda yana mai shafa kanta cikin farin ciki .

Ahankali fattu ta kalli gefenta ta ƙasa inda macijin nan ke nannaɗe ya fasa kansa yana kallon baffa.tace "baffa wannan ne ya taimakeni, kuma shine macijin daya hukunta su jauro "ta faɗa tana haska macijin da tocilan.

Da sauri baffa yaja baya yana faɗin"subhanalla fattu wannan ai MACIJINE ,meye haɗinki dashi,matsa daga gareshi maza karya cutar dake" baffa ya faɗa cikin tsoro yana mai kamo hannun Fattu.

"Baffa ka kwantar da hankalinka ,ba abinda zai min ,domin mun jima tare dashi,zauna baffa in baka labarin haɗuwata dashi ,sannan baffa macijin nan yana cikin matsala ,dan da alama anyi amfani dashi wajen yiwa wani asiri.

Zama baffa yayi ahankali kan sallarsa ,idonsa akan macijin nan ,daya matso kusa da fattu wacce ke zaune kusa da baffanta,kallon ikon Allah baffa keyi, yadda macijin nan yayi kane-kane akan cinyar  fattunsa ya waniyi lub kamar jariri akan cinyar mahaifiyarsa.

Kallon fattu baffa yayi ,yaga ko ajikinta saima hannu data ɗora akan bayan macijin tana shafawa.

"Ina jinki fattu faɗa min komai dan hankalinta ya kwanta"

Nan fattu ta fara bashi labari tun daga farko har kawo yanzu.

Sannan ta ɗora da cewa "baffa dan Allah mu taimaki wannan macijin dan wllh yana cikin matsala ,bakaga yadda ya koma ba lokacin dana ke masa karatu,mu cire masa wannan masifar dake jikinsa"ta faɗa tana nunawa baffa waɗannan layun dake wuyan macijin.

Cike da mamaki da al'ajabi baffa ke kallon macijin ,wanda ya ƙara kafewa jikin fattu yana kallon baffa da kuma fattu.baffa yace "haƙika akwai wani ɓoyayyen al'amari dangane da wannan macijin ,kuma in sha Allah zamu taimaka masa iyakar ƙarfin

mu,tun kafin mai gari ya farfaɗo ya ɗauki matakin kashe macijin nan ,yanzu kije kiyi alwala ki dawo,dan  mu fara aiki akansa.

Cike da ɗoki fattu ta amsa da" to baffa na ina godiya agareta sosai"sannan ta ajiye macijin gefen baffa tace "mai taimako ai kasan baffana ko?to katsaya agurinsa yan zu zan dawo kaji"ta faɗa cikin murmushi tana shafa bayansa.

Kallo ta kawai yayi kafin ya kwantar da kansa ajikin gangar jikinsa dake nannaɗe.

Bayan fattu tayi alwala ta dawo dakin ne ta gabatar da sallolin dake kanta ,sannan tayi addu'ar samun nasara akan ceton macijin nan ta shafa.sanna ta juyo gurin baffa wanda ke ta tofa addu'a cikin wata ƙwarya ,zama ta gyara tana mai kallon baffa da jiran ya kammala addu'ar sa.

Shikuwa macijin nan yana ganin fattu ta zauna ya silalo ya dawo kan cinyarta ya kwanta,gaba ɗaya jikinsa asanyaye yake,kamar wanda yake tsoron faruwar wani abu.kallonsa fattu tayi tace "mai taimako ba abinda zai sameka ka kwantar da hankalinka ,in Sha Allahu zamu cire maka duk wani sihiri da akayi amfani dakai wajen yinsa"ta faɗa tana mai shafa lallausan san jikinsa mai santsi.

Miƙa mata kwaryar nan baffa yayi yace karɓi wannan fattu ki yayyafar masa ajikinsa ,kinayi kina karanta ayatul kursiyyu da falaƙi da nasi, duk abinda zaki gani karki tsorata kinji ?"baffa ya faɗa yana mika mata kwaryar,dan shikam ya gama fahimtar abubuwa da dama aka. Macijin nan.

Karɓa fattu tayi cikin nutsuwa ta fara karatun tana kuma shafa masa ruwan rubutun nan ajikinsa.

Ikon Allah,ai da fara shafa masa ruwan nan ajikinsa ya fara wani irin motsi da jijjiga ,yana murɗewa ,baffa kuma saiya ci gaba da addu'a yana tofa masa.

Ahankali hannun Fattu ya kai kan waɗaɗan na layin dake wuyan macijin nan,aikuwa damƙarsu tayi da Bismillah ta fizge da ƙarfin gaske.

Wata irin ƙara da guguwa ne suka turnike dakin gaba ɗaya baka iya ganin komai sai dubhu

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Kʿara fattu ta kwalla cike da tsoro,dan ta saddaƙar kawai ta gama faɗuwa,saidai kuma maimakon tajita akan ƙasa ,saitaji ta faɗa kan wani abu mai matuƙar taushi kamar katifa.

Da sauri ta buɗe idanunta dan ganin inda ta faɗa,cikin mamaki take kallon bawan Allah nan,dan hannunsa ta faɗo, lokacin da yaga tayi baya zata faɗi ,bai ma san lokacin daya zabura yayi kanta ba ,tare da tareta ta faɗo akan hannunsa .

Kallon kallon sukewa juna basa ko ƙiftawa, yayin da bawan Allah ya zazzaro idanu waje ,irin wanda idan mutum yaga abin tsoro ɗin nan.

Ita kuma fattu mamaki take yaushe ya taso yazo gareta harya tare ta ?bata kai ga faɗuwa ƙasa ba?

Baffa ne yayi gyaran murya tare da faɗin "subhanallah,fattu sannu, Allah ya taƙaita wahala  da tuni kin faɗin ƙasa ,bawan Allah sannu kaji,kana fama da kanka amma zuciyarka mai tsafta bazata bari wani ya cituba,ina mai godiya gareka"baffa ya faɗa cike da jinjinawa bawan Allah nan,lallai akwai wani abu da Allah ya ɓoye tsakaninsa da fattunsa, haƙiƙa fattu kam,zuwa yanzu ta sami mai taimako,kuma yanzu ne ya kamata su fara neman dangin Fattu ,dan zuciyarsa na raya masa wannan bawan Allah alkairine ga rayuwar fattunsa.

Ahankali bawan Allah ya miƙar da fattu tsaye ,yana kallon ta sai dai fuskarsa sam ba walwala ,da alama dai irin mutanen  nan ne marasa yawan fara'a .

Fattu kuwa da sauri ta juya baya tana mai dafe ƙirji ,dan hango zanin da baffanta ya lulluɓawa mutumin a ƙasa,kuma da alama bai ma san zanin ya daɗi ƙasanba.

Da sauri shima ya ankare cewar ba zanin fa ajikinsa ,wato yana tsaye tsirara ne.cikin azama ya durƙusa ya ɗauki zanin yana cukuikuyewa ajikinsa, idonsa akan fattu yana fatan Allah dai yasa wannan yarinyar bata ganshi haka ba,dan ma dakin ba wani haske sosai.dan tocilolin sun kalli wani direction  ɗin ne da ban.

Zama yayi cike da jin haushin yadda zanin jikin nashi ya daɗi kasa,wai ma to ina kayansa ne?me yasa y ganshi haka ba kaya ne?

Daga kanshi yayi yana kallon baffa daya miƙa masa kwaryar da fattu ta miƙa dan abashi magani.

Karɓa yayi shikam nadan yasan menene aciki ba , kallo yabo kwaryar dashi,yana jin wani irin tashin zuciya ,dan kwaryar ta tsufa sosai ,tayi baƙi saboda ruwam rubutun da ake zubawa a cikinta.

"Maza ka shanye bawan Allah zakaji sauƙin ciwon kan"baffa ya faɗa yana nuna masa alamun ya sha da hannunsa ,dan gani yake kamar bayajin me suke faɗi.

Kafa kansa yayi yana shan maganin ,bayan ya runtse idanunsa.saida ya ɗansha da yawa kafin ya miƙawa baffa kwaryar.

Saidai ko minti ɗaya baiyi da sha ba ,ya kama yunƙirin amai.aikuwa tasss ya mayar da maganin nan,sannu kawai baffa ke masa.

Juyowa fattu tayi lokacin daya fara aman, dan tunda ta juya musu baya bata ƙara juyowa ba,saida taji yana aman.

Ahankali ta buɗe bakinta tace "sannu hamma"ta faɗa ahankali.

Kallonta yayi ,tare da kawar da kansa can gefe yana jingina da jikin katangar karan,ba tare da yayi magana ba .itama bata damu da sai yayi maganar ba,dan su tunaninsu bayajin me suke faɗi.

Cikin nutsuwa fattu ta gyara gurin da yayi aman,kanta aduke ,har zuwa lokacin gabanta yaɗuwa yake .shi kuwa bawan Allahn nan yana daga jikin bango Ya lumshe idanunsa ,kamar mai barci.saidai duk abinda fattu keyi idonsa na kanta,mamaki yake da irin kyan da yarinyar ke dashi,gata da nutsuwa komai nata gwanin burgewa.tana da hankali bata da rawar kai duk da ƙaranci irin na shekarunta.dan ya san wannan bata wuce 14/15ba amma Masha Allah,tana kyan diri irin na cikakkun mata ,kalli hips ɗinta kamar wanda aka ɗora mata shi Dass abinta. Jikin fattu ne kawai ya bata cewar kallo ta mutumin nan keyi,dan haka ahankali ta ɗago kanta ,shikuwa daidai lokacin ya ɗan ƙara buɗe idanunsa yana kallon ɗan ma dai-dai cin lips ɗin ta, masu  taushi , sai sheƙi suke.aikuwa carab ta kama shi yana mata kallon ƙurillah.

Ɗan hararar ta yayi tare da kawar da kansa ,aransa yace "wannan ta cika kallon mutane "

Kuji fa masu karatu ?ko tsakanin shi da fattun wake kallon wani?

Da sauri fattu ma ta kawar da kanta,azuciyarta tana mai cewa "kuji min mutum shi yana kallon mutane amma kuma baya son akalleshi"

"Abba waye yakawoni nan?kuma me nakeyi anan?sannan kuma ina kayan?

Baffa da fattu suka ci

tsinkayi murya mai shegen daƙi da amon sauti cikin nutsuwa.da mamaki gaba ɗaya suka bishi da kallon ,ba wanda yayi magana dan sai sukaga kamar bashi yayi maganar ba ,dan yana yadda yake bai ko buɗe idonsa ba lokacin da yayi maganar.

Jin sunyi shuri ba wanda yayi magana ne ,yasa bawan Allah buɗe idanunsa da suka ɗan yi ja kaɗan yana kallon baffa,sannan ya ƙara maimaita tambayarsa cikin Hausarsa da bata fita sosai.

"Ashsha -ashsha ikon Allah yaro ashe kana jin Yaren Hausa ?Alhmdllh.sannu kaji bari na baka kaya saika saka,inyaso zuwa wayewar gari nayi magana kaji"baffa ya faɗa yana mai buɗe wata tsohuwar bakonsa ,kaya ya daukowa bawan Allah nan ,waɗanda dasu yake zuwa sallar juma 'a .wani yaƙi ne yollow share dashi ,anyi masa ɗinkin riga da wando dogaye .miƙa masa baffa yayi yace "kasa Waɗan nan tukunna yanzu kaji"

Karɓar kayan yayi yana mai ƙare musu kallo,to ina nashi kayan da za'a bashi Waɗan nan kayan wani iri dasu haka?ɗari kansa yayi ya kalli baffa yana son yayi magana ,amma sam ya kasa,dan ba ɗabi'arsa bace yawan magana ,yana matuƙar jin wahalar yin magana ,shiyasama tun farko yaƙiyi musu magana .

Kallon fattu yayi wacce ke zaune can nesa dasu kanta aduƙe,tana wasa da yatsun hannunta ,sannan ya kalli baffa ,ya kalli kayan hannunsa kuma .

Fahimta baffa yayi cewar ,yana son saka kayan ne ,kuma yana buƙatar fattu ta bar gurin,dan haka baffa yace "fattu muɗan bashi guri ya kimtsa ko"baffa ya faɗa yana mai kama hannun fattun sukayi wajen ɗakin.

Bayan fitarsu daga ɗakin,shikuwa  kallon yabo kayan dashi yana juyasu ahannunsa, kusan minti uku kafin ya saka rigar ,dube dube yake ko zaiga boxern sa ,saidai ba alamun boxer aɗakin nan,dan haka ya saka wando yana mai turo baki da ɗan yamutse fuska.sauƙinsa ma ɗaya kayan wanke suke tas ɗasu,sai ƙamshin kilin suke.lol.

Koda ya saka kayan zamansa yayi a inda ya tashi tare da lumshe idanunsa ya faɗa duniyar tunani ,shikam a iya tunaninsa baisan meye dangantakar da da Waɗan nan mutanen ba,abinda zuciyarsa tafi yarda dashi shine,wata ƙila yayi hadarine suka ganshi suka taimakeshi.

Baffa ne yaji shiru baice musu ya kammala saka kayan ba,kuma ga fattu sai rawar ɗari take, dan zuwa wannan lokacin an jima da ɗauke ruwan saman da ake tsugawa,dare ya raba sosai.

Dan haka saiya ɗan leƙa cikin ɗakin.aikuwa azaune ya hangoshi ya jingina kansa da jikin katanga ,sannan idanunsa alumshe .

"Ayya ashe ma ya ida shiryawa fattu, shigo daga ciki kar mura ta mamaki naga kinata rawar sanyi,bana so kije ɗakinki ki kwanta saboda hansai idan ta ganki zata je ta sanar da lamiɗo kina nan"baffa ya faɗa yana mai tura ƙofar dakin nashi ya rufeta.

"Sannu bawan Allah"baffa ya faɗa cike da tausaya wa.

Jinjina kai kawai bawan Allah yayi ,ba tare da ya buɗe idonsa ba.

Zama baffa ya gyara ya ƙara cewa"ko zaka iya tuna wani abu daya danganci rayuwarka"?ya faɗa cike da fatan cewar bawan Allah nan bai manta komai na rayuwarsa ba.

"Ikon Allah ,saikace wanda yayi lossing memery zan manta da rayuwata "bawan Allahn ya faɗa cikin ransa,amma a zahiri ,ɗan buɗe idonsa yayi ya kalli baffa,sannan ya maida idonsa kan fuskar fattu wacce itama shi take kallon kamar ta sami talabijin.

"Kai wannan yarinyar ta cika kallo wllhda wani idanunta masu kama da ruwan Gwale"ya faɗa cikin zuciyarsa yana mai hararar fattun ,kafin ya ɗauke idanunsa daga kanta ya maida kan baffa .

Saida ya kai kusan minti biyu kafin ya buɗe baki ahankali kamar baya so yace "my name is  ADEEB

MUHAMMAD ASHRAF "ya faɗa yana jinjina kansa tare da kallon baffa.gani yayi baffa yana kallonsa alamun kamar bai fahimceshiba.

Lumshe idonsa yayi cike da gajiya ,sannan yace "sunana ADEEB MUHAMMAD ASHRAF"yana faɗin haka ya mayar da kansa ya jingina tare da lumshe idanunsa.

"To- to masha Allah  malam Adeeb ina ne garinku ? Baffa ya faɗa cikin gamsuwa da jin cewar shiɗin musulmine. Dan da yana ta kokwanto shin  musulmi ne shi ko arne? Amma zuwa yanzu ya sami nutsuwar jin cewa shiɗin musulmine.

Shiru yayi kamar bazai yi magana ba, kafin ya buɗe baki  yacewa baffa"nidan MISRA ne" ya faɗa yana kallon yadda baffa yayi zugum cike da tunanin ina yakejin Misra?

"Ikon Allah malam adeeb duk da dai Ni ba  sanin Misra a ina take nayi ba,amma nasan garine mai matuƙar nisa ,to zahiri gaskiya nan kana Nigeria ne ,cikin ƙauyen yaɾar ruga dake jahar Gombe"baffa ya faɗa yana kallon Adeeb wanda mamaki ya mamaye ilahirin fuskarsa , Nigeria kuma ?yaushe yazo Nigeria?bayan rabo da da Nigeria tun last year?

"Who brought me hare"?ya faɗa cikin mamaki da sanyin murya.sai kuma ya ɗan rufe idonsa tare da dage kansa kafin yace "waye ya kawoni nan?

Shiru baffa yayi ba tare da yace komai ba,na tsawon lokaci ,kafin ahankali ya nuna masa fattu yana mai cewa"haƙika wannan yarinyar itace solar haɗuwar mu dakai ,kuma anan garin ta ganka -----nan dai baffa ya bashi labarin abinda ya sani ,da kuma abinda ya faru yanzu harya koma asalin halittar da.

Tunda baffa ke magana Adeeb ya saki baki yana kallo da sauraron baffa,mamaki yake wai shine ya zama maciji?as how ? Me ya faru dashi ?waye ya maida shi hakan?ya Allah who's known how long yake cikin garin nan,ko yaya yan gidansu? Ko wane hali suke ciki yanzu?yasan yanzu haka hankalin amminsa yayi matuƙar tashi fiye dana kowa ,lallai dole ya bar garin nan ko ta halin ƙaƙa.

"Na gode sosai da taimakon rayuwata da kuka ,amma bani da wani masaniya akan abinda ya sameni, ina don barin garin nan gobe-dan akwai gagarumin abinda ke gabansa,saidai i promise you I will get you back,zan dawo gareku"ya faɗa cikin wani irin yanayi na ban tausayi,dan gaba ɗaya jikinsa asanyaye yake ,sannan damuwa ta cika fuskarsa taf! Da gani maganar ta shiga jikinsa sosai .

Cikin murmushi baffa yace ba komai malam Adeeb Allah yayi mana jagora ,saidai ina neman alfarma agareka"baffa ya faɗa cikin damuwa.

"Ba komai Abba ka faɗi duk abinda kake don faɗi and I promise zanyi maka shi"ya faɗa cikin sanyin murya mai cike da tarin damuwa.

"So nake ka tafi da ƙanwarka can garin naku ,domin ka taimaka mata wajen saduwa da asalin iyayenta baffa ya faɗa cikin tsantsar damuwa yana mai kallon fattu,wacce taji maganar baffa kamar sauƙar aradu .....

Masu karatu mu tara next page

Taku ce anty mammy Mrs babi□□

Share and comment fisabilillah.

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



Albishirinku masoya,ga dama ta samu ga mai buƙatar a tallata mata hajarta,to ashirye nake dan tallata mata cikin farashi mai sauƙi,dan haka idan kin shirya sai kiyimin magana .

_____Wata irin ƙara da guguwa ne masu  matuƙar ƙarfi da firgitarwa , suka cika dakin.ta yadda koda tafin hannunka baka iya gani tsabar duhun da ɗakin yayi,ga guguwa sai juyawa take aɗakin.

Ko kaɗan hakan bai tsorata baffa ba ,saima cigaba da yayi da karanto ayoyin shifa daga cikin alƙur'ani mai girma yana tofawa asaitin dayasan macijin nan yana gurin ,duk da duhun daya mamaye ɗakin.

Fattu kuwa wani irin tsorone da fargabar suka baibayeta , jin yadda macijin nan yake wata irin murɗewa da sakin wani sautin ƙara mai ban tsoro ,sannna kuma sai takejin yana ƙara mata nauyi sosai akan cinyarta.

Cikin tsoro da ruɗewa ta lalubo hannun baffa tace " wayyo baffa tsoro nakeji,wllh kamar yana rikiɗewa ne zuwa wata halittar ,yayimin nauyi akan cinyata baffa, baffa ina tsoron kar wani abu ya faru"Fattu ta faɗa cikin rawar murya mai cike da tsoro.

Hannunta baffa ya riƙe shima cikin yanayi na son kwantar mata da hankali yace"karki damu Fattu ba abinda zai faru sai alkairi,kici gaba da karanto addu'oi kina tofa masa  in Sha Allah komai yazo ƙarshe "baffa ya faɗi hakan tare da ci gaba da karanto zafafan addu'oi yana tofawa macijin.

Fattu ma ɗaurewa tayi taci gaba da karanto addu'ar tana tofamasa, jikinta sai rawa yake,yadda takejin alamun sauyin halittar da macijin nan keyi.idanunta arufe gam-gam.

Kusan shuɗewar mintina biyar zuwa bakwai, duhun nan ya fara yayewa ,ahankali hasken tocilolin su baffa  ya fara gauraye dakin.

Salati baffa ya farayi da ƙarfi da kiran sunayen Allah yana mai kabbara. "La'ilaha illallah muhammadur rasulullahi sallallahu alaihi wasallam,ya Allahu Ya rahmanu ,ya hayyu ,ya ƙayyum,Allahu akbar, Allahu akbar "abinda baffa keta faman faɗi kenan cike da ta'ajibi da jinjina wa ƙudurar Ubangiji,cikin hanzari ya janyo zanin rufuwarsa ya lulluɓawa maciji ,daga cikinsa zuwa ƙasansa dan ba kaya ajikinsa.

Jin yadda baffa ke tafaman kabbara da salati ne ,yasa Fattu buɗe idanunta cikin nutsuwa da kuma jarumta ,har zuwa lokacin bata fasa karanto addu'oi ba.akan

fuskar baffa ta sauƙe idanunta ,gaba ɗaya baffa ya shiga al'ajabi da mamakin abinda idanunsa suka gane masa.dan har lokacin yana kallon macijin ne ƙuri kamar ya sami talabijin.

Ahankali Fattu take sauƙe idanunta zuwa kan cinyarta,wata irin bugawa zuciyarta tayi ,lokaci ɗaya komai nata ya tsaya cak. Sai wata irin rawa da jikinta ya kama kamar zata karkarye,ta ɗauki kusan minti biyu cikin wannan halin kafin taja wani dogon numfashi tana mai buɗe baki tace"ba.....f..ff..fa ...mumm.....tttuummm....nnnee.....a..Mamman.cc.....iiii.....sai kawai ta sulale ta faɗi ƙasa daga zaunen da take.

Ba komai bane ya sanya Fattu shiga cikin wannan halin ba , face ganin wani zankaɗeɗen haɗaɗden saurayi ,fari ƙal-ƙal da tayi kwance ya kifa cikinsa akan cinyarta,maimakon macijin dake kwance akan cinyar ta ta.

Kuma wannan shine dalilin salati da baffa keta rafkawa cikin kushu'i da tsarkake baiwa da buwayar mahalicci.lallai duniya ta zama abinda tazama ,yanzu mutum ne aka mayar dashi dabba?maciji?kuma ga dukkan alamu wannan ba ɗan yankin nan bane ,dan ko kaɗan baiyi kama da mutanen mu ba.

Ahankali baffa yayi kokarin janye shi daga kan cinyar fattu ya kwantar dashi rigingine akan tabarmar.

Hannu baffa ya sanya ya gyara masa zanin daya lulluɓa masa dan rufe masa al'aurarsa.sannan ya ture gashin daya lulluɓe fuskar mutumin.

"Masha Allah ,watabarakallahu fi ahsanil kaliƙin"baffa ya faɗa adaidai lokacin da yayi arba da fuskar kyakyakywan matashin mai cike da haiba da kwarjini,ga kyan zati.

Kallonsa baffa yake ƙuri yana jinjina kai cike da mamaki da alhini,lallai duniya abin tsoroce, rayuwa bata da tabbas,Allah ka karemu,ka rabamu da sharrin maƙiya da mahassada. Baffa ya faɗa acikin zuciyarsa yana kallon bawan Allahn.

Ruwa baffa ya ɗebo ya yayyafawa fattu ,ahankali ta fara motsi tana buɗe idanunta ,tar ta buɗe idanun ta sauƙesu akan baffa, kusan minti biyu tana kallon baffa.

"Sannu Fattu kinji?tashi ki zauna kiga ikon Allah ,tashi kiga taimakon da kikayiwa rayuwar wannan bawan Allahn.

Baffa ya faɗa yana nuna mata inda macijinta yake kwance.

Zabura tayi ta tashi zaune  cikin tsoro tana kallon inda baffa ya nuna mata,da sauri ta matso kusa da baffa ta riƙe shi gamm! Jikinta sai rawa yake tace "na shiga uku baffa wllh aljani ne wannan ba mutum bane, daga maciji ya koma siffar mutum ,baffa wllh bamu san me zai koma ba nan gaba ,baffa atsorace nake"ta faɗa idanunta yana zubar da hawaye.

Ahankali baffa ya kamo hannunta yace "habaFattun baffa ,kin manta ne?macijin nan ne fa ,wanda yake taimakonki cikin hukuncin ubangiji, shine kuma kikejin tsoro yanzu?kin manta da halaccin sa gareki?meyasa bazaki tsaya tare dashiba?alokacin da yake buƙatar taimakonki kema?ki kwantar da hankalinki Fattu ina ji ajikina wannan bawan Allah shine zai zame miki bango kuma tsanin da zai haɗaki da innarki"baffa ya faɗa cikin yanayi na son kwantar mata da hankali.

Murmushi Fattu tayi cikin kwarin guiwa tace "hakane baffa ,kuma zan kula da bawan Allahn nan  in Sha Allahu ,harya sami lafiya"ta faɗa cikin kwarin guiwa,saidai har zuwa lokacin tsorone fal cikin ranta.ahankali ta matsa kusa da macijin saidai can nesa kaɗan dashi ta zauna .

Kallonsa take cike da mamakin tsantsar kyan da Allah yayiwa wannan bawan nashi, ita kam tunda take arayuwarta, bata taɓa ganin wani mutum mai kyan wannan bawan Allah ba.

Dan duk kyanta da ake faɗa ,tayi imani bata kama koda ƙafar wannan bawan Allahn ba.

Ahankali ya fara motsi yana ɗan juya kansa hagu da dama.sai kuma ya fara ɗan fizge fizge kamar yana ƙoƙarin tuna wani abunne ko kuma yana son farkawa daga wani mummunan mafarkin .

"Baffa kaga abinda yake "Fattu ta faɗa cikin zabura tana kallon baffan.

Wata yar jarka baffa ya ɗauko ya buɗe ,ahankali yafara shafa masa ruwan dake cikin jarkar. ahankali  maciji ya sauƙe wata ajiyar zuciya mai ƙarfi yana sauƙe numfashi ahankali ahankali.

Addu'oi baffa yake tayi cikin wasu magunguna kala-kala yana shafawa bawan Allah nan da yake kwance ,wanda zuwa yanzu jikinsa yayi sanyi,ba kamar dazu da yayi zafi ƙau-ƙau ba.

Tun daga ƙafafuwansa Fattu ke kallonsa har zuwa fuskarsa,masha Allah.

Wannan mutumin ya haɗu ta ko ina ,anya ma wannan ba haushene?ko bafulatanine irin mu?kai gaskiya wannan bayajin Hausa ko fulatanci,ohhh Ni Fattu yanzu wanann macijina  ne haka ?dama da mutum nake ma'amula  ashe?waye wannan bawan Allahn?su waye sukayi  masa wannan shirin haka?me yayi musu ?inane garinsu? meye sunansa?waɗan nan  sune tambayoyin da Fattu ke buƙatar amsarsu ,saidai ba mai bata amsar sai wannan bawan Allah.

Baffa ma tunani yake wannan bawan Allah daga ina yake? ,waye yayi masa wannan sihiri?koma dai menene yayi masa maganin da duk sihirin mutum bazai yi tasiri akanshi ba da yardar Allah.

Suna nan zaune jigum jigum, cike da fatan Allah yasa ya farka ba tare da wata matsalar ba,kawai suka ga ya fara motsi karo na biyu,saidai wannan karon ba fizge -fizgen yake ba ,kawai dai ya ɗan riƙe kansa yana kuma yatsina fuska.

Ido suka ƙura masa ba wanda yayi magana ,daga Fattu har baffa,kowa yayi shiru yana kallon ikon Allah.

Ahankali bawan Allahn nan ya fara bude idanunsa yana ɗan lumshesu ,kafin ya buɗe su tar kamar lantarki dan tsananin haske da sheƙin da suke yi.

Ƙur ya ƙure rufi bukkar dakin baffa da idanu,baya ko ƙiftasu,tunani yake ina ne nan?waye ya kawo shi nan?kuma yaushema suka zo nan ɗin?

Yunƙurawa yayi ya tashi zaune ahankali yana cije light pink lips ɗinsa .kallon ɗakin yake cike da mamaki ,har ya juyo zuwa inda su baffa ke zaune shida Fattu sunyi masa ƙuri suna kallonsa,baffa ya fara kalla cike da rashin sani.

"Sannu bawan Allah ka tashi ?meke maka ciwo yanzu ?me kake ji ajikinka" baffa ya faɗa lokacin da suka haɗa ido da bawan Allahn .

Ahankali bawan Allahn ya lumshe idanunsa tare da jingina da jikin bangon ɗakin.yana mai dafe kansa ,dan ciwo yake masa sosai.

"Ayya Fattu inaga fa wannan bayajin  hausa ,kuma bayajin filatanci  miƙamin wannan kwaryar In bashi magani ,da alama kanshi ke ciwo.

Cewar baffa kenan, dayaji yayi magana amma bawan Allahn bai bashi amsaba.

Ahankali Fattu ta miƙe ta ɗauki kwaryar ta miƙawa baffa ita ,tana mai cewa "baffa gashi,kuma kamar ma yana jin yunwa ko ?kaga yana shafa cikinsa"ta faɗa tana kallon yadda bawan Allah ke shafa cikinsa zuwa ƙirjinsa wanda gashi yayi kwance luf-luf akai.

Ahankali bawan Allah ya ɗago kansa yana kallon saitin dayaji sassanyar muryar Fattu na tashi.

Aikuwa karaf idanunsa suka gauraye cikin na juna ,wata irin faɗuwar gabace ta ziyarcesu alokaci guda, da sauri bawan Allahn ya kawar da kansa  yana mai dafe ƙirjinsa,dan sosai ƙirjinsa ya buga.

Bangaren Fattu ma kuwa,wata irin bugawa ƙirjinta yayi, wacce har saida taji numfashinta ya ɗauke ,wani jiri ne ya ɗebeta ,tayi baya luuuuuuu zata faɗi,ƙara ta kwalla cike da jin tsoro tana mai runtse idanunta, saidai kuma kafin ta kai ƙasan taji ta faɗa kan wani lallausan  abu mai kama da katifa tsabar laushi.

Ahankali ta buɗe idonta ta sauƙesu akan.....

Muje zuwa masu karatu yanzu muka fara.

Taku ce dai anty mammy

Mrs babi□□

Share and comment fisabilillah

More comment

More typing.

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

_____Wata leda Baffa ya ɗauko  ,ledar da ɗan nauyi ,alamun wani abune acikin ta .sannan ya ɗauki wannan rigar ta fattu ya cusa acikin ledar,safin yayi waje ,Abeed ya rufa masa baya.

Ahankali baffa ke takawa Abeed na biye dashi,saɓe da fattu akafaɗarsa,wacce ke cikin matsanancin hali na zazzaɓi,da damuwa.

Tafiya suke cikin sauri bayan sun bar gidan ,cikin ikon Allah basu haɗu da kowa ba ,har sukayi nisa da garin sosai,saida baffa ya fitar dasu kan kwalta kafin ya tsaya .

Har zuwa wannan lokacin fattu na saɓe akan kafaɗar Abeed ,duk da irin uban nisan dake tsakanin rugar da kwalta.

Ahankali Abeed ya sauƙe fattu ya ɗan jingina ta da jikinsa,dan yaga bazata iya tsayuwa ba .

"Malam Abeed karɓi wannan wasu yan kudadene da nake tarawa saboda irin wannan ranar,nasan zasu toshe muku wata kafar,dan Allah ka riƙe min alƙawari, ka kulamin da fattuna,karka bari wani ko wata ya cutar da ita,sannan kayi iyakar ƙoƙarin ka wajen sadata da  magaifanta.

Kaima zaka sami lada"baffa ya faɗa yana kallon bayansa ,hanyar da suka baro ,dan tsoro yake kar yaje ko anbiyosu,dan yasan zuwa yanzu labari ya isa kunnen lamiɗo,tunda gari yayi haske an kusan shiga sallah.

"In Sha Allahu Abba zan kula da amanar ka,na gode da taimakon da kukayimin, sannan zan dawo gareka very soon"Abeed ya faɗa cikin nutsuwarsa da rashin son magana,akwai abubuwan da yake son faɗa amma tsabar rashin son maganarsa bazai iya ba dan haka yayi shiru daga wannan maganar.

Hannun fattu baffa ya kama yariɗe gam-gam cikin nashi,kallon ta yayi yayinda itama take kallonsa cikin kuka wanda muryarta ko fita batayi sosai, shima baffa tuni zuciyarsa ta karaya ,sai hawaye sharrrr!!

"Allah ya shiga lamarin ki fattu, Allah ya karemin ke ka yasa damu da alkairi,ki kula da kanki,ki kama mutuncinsu.Allah yayi miki albarka"baffa ya faɗa cikin kuka sosai,abin tausayi.

"Baffa bana son tafiya ,dan Allah kace na zauna ,Ni nafison zama da kai akan iyayena ma asali,baffa karka tafi ka barni "Fattu ta faɗa cikin kuka harda shashsheka kamar zata shiɗe. Kafin baffa yayi magana saiga wata mota zata wuce ,da alama daga cikin Jos take .

Da sauri baffa yayi musu hannu alamun su tsaya.tambayarsu yayi ina suka nufa ,mai motar yace Kano.

Kallon Adeeb baffa yayi yace "duk da bansan inane Kanon ba amma Gara kubi wannan motar kafin tawagar mai gari su fito nemanku.

Kai kawai Abeed ya ɗada,tare da kamo hannun fattu suka nufi motar,hannunsa ɗaya riɗe da ledar da baffa ya basu.

Kuka fattu take harda ihu tana faɗin"wayyo baffana ,banason tafiya,dan Allah baffa kace na dawo wayyo baffa am wayyo Allah na ,wayyo rayuwata "

Baffa kam ko magana ya kasa tsabar kuka sai daga musu hannu kawai yake yana juya kai.

Abeed ne ya sanyata cikin motar tare da riɗe ta ,ɗan sai ƙoƙarin  fitowa take ,haka mai motar nan yaja motarsa yayi gaba,dan kaya zaije ɗaukowa.

Baffa yana tsaye har saida yaga ɓacewar motar ,sannan ya sauke wani kwauron numfashi yana mai share hawayen idanunsa,"Allah ga amanar yʼata nan  na miƙa lamarin ta ahannunka ,ya ubangiji kazama majiɓancin al'amarinta "baffa ya faɗa yana mai juya dan koma gida ayi wacce za'ayi.

Aikuwa tun kafin ya ƙarasa cikin garin ,ya hango cincirindon mutane aƙofar gidansa,jinjina kai yayi,dan dama yayi tsammanin hakan .

Suna hangoshi sukayo kan suna wllh koya fito da yʼar Shegiyar daya ɗauka matsayin yʼarsa ,da kwarton ta da suka ajiye agida,ko kuma su kashe shi yanzun nan.

Kallonsu yayi cikin kamala da dattako yace "ikon Allah me kuma mukayi dazaku kashemu?wace yarinyar kuke nema?bayan wacce mai gari ya riƙe agurinsa?baffa ya faɗa kai tsaye ba nuna alamun tsoro.

Nan wani lawwali yace masa"ai jiya yarinyar nan saida ta bari dare ya raba sannan ta sami lamiɗo tayi masa jina jina,gaba ɗaya ƙafafunsa sun ƙarye,ga hannun damanshi ma ya ɓalle baral, sannan ta gudu,kuma munsan tabbas tana gidan nan,dan kuwa hansai ta kai labari,

Kuma ta fayyace mana komai game da yarinyar ,ashe Shegiya ce ka tsinto ka kawo gidanka,sannan ka ajiye mata wani gardin suke lalata dashi,dan haka gaba ɗayanku yau sai hukunci ya hau kanku,dan lamiɗo yana nan banda ihu ba abinda yake yana kiran maciji zai kashe shi,fattu ce tayi masa ture.sannan arɗo ma yana can hannunsa guda ya shanye ya zama kamar sillan kara ,kuma duk aikin fattu ne ,dan haka yau wllh saimun kashe fattu"lawwali ya ƙare zancensa yana mai ɗaga sandarsa sama.

"Toh me yasa baku shiga kun duba fattun ba ?idan nan ta dawo,ita wacce ta kai muku rahoton saita faɗa muku inda fattun take"baffa ya faɗa yana ƙoƙarin shigewa gida.

"Kʼarya yake wllh, saidai in ya boyesu ,ko kuma sun gudu ,dama naji yana cewa su gudu dan haka karku taga masa " na tsinkayo muryar gwogwgo hansai na faɗin haka ,dan taji mugun haushi da ba'a sami su fattu cikin gidan ba.

Aikuwa baffa yana tsaye

Ba zato ba tsammani yaji sun rufeshi da duka ta ko ina.

Har saida suka kaishi ƙasa.sannan suka taitayeshi sai gurin. Mai gari.suna zuwa suka tarar ana yiwa mai gari ɗori sai ihu yake yana kuka.dan haka can ɗakin hukunci suka jefa baffa,wanda yayi kaishi sosai dan ya daku.

Allah Sarki baffa ,Allah ya saka maka.

Fattu kuwa tsabar kuka har muryarta ta dashe,can jikin ƙarshen motar ta koma tare da haɗe kai da gwuiwa tana kuka marar sauti ,jikinta sai rawa yake ,fuska ta kumbura suntum tayi jajur ,abinka da farar fata.

Abeed yana daga gefe yana kallonta ,sosai yake jin kukanta har cikin ransa,haƙiƙa yarinyar tana fuskantar ƙalubalen rayuwa and she's to Young to handle the situation.amma ya zatayi?dole ta ɗauki ƙaddara yadda yazo mata.

Kallonta yayi yadda jikinta ke ta rawa tana shashsheƙar kuka,yaso ace ya iya rarrashi, daya rarrasheta ,koba komai itaɗin yanzu amanarsace,amma Gara tayi kuka ,koba komai zata rage jin raɗaɗin da taleji cikin zuciyarta.

Tafiya suke sosai ,Dan drivern gudu yake tsulawa,kasancewar safiya ce hanyar ba motoci sosai,sai jifa-jifa suke cin karo da motocin.

Abeed yayi shiru ,tare da jingina kansa jikin kujerar da yake zaune,ba abinda ke yawo cikin zuciyarsa,sai labarin da baffa ya bashi na cewar wai shiɗin amaciji suka ganshi,to ta yaya?yaushe hakan ta faru,me yasameshi? Tabbas idan har abinda baffa ya faɗa gaskiya ne baya raba ɗayan biyu cewar sharrin Amma ne wannan ,dan ita kaɗai yake tunanin zata iya cutar dashi ,tunda afili take nuna masa ƙiyayya, amma zaibi abin ahankali harya gano mugun ƙullinta akansa kafin ya ɗauki mataki.

Ya rasa me ya tsareta Amma arayuwa sam bata ƙaunarsa ,kullum burinta ta cutar dashi,tun yana ƙarami  yake fuskantar tsangwamarta,har kawo yanzu bata fasa ba ,amma akwai lokacin da ko ance tayi masa wani abun bazata iyaba.

Juyowa yayi ya kalli inda fattu ke zaune ,har zuwa wannan lokacin kuka take ,banda rawa ba abinda jikin ta keyi.wani tausayine yaji ya kama zuciyarsa ,wannan kukan yayi yawa zai iya haifar mata da matsala.dan haka ahankali ya ɗan matsa kusa da ita ,ƙureta yayi da ido ,yana son yayi mata magana amma baisan me zaice mata ba.

Kusan minti uku yayi yana kallonta da yadda jikinta ke rawa sosai,kafin ya sanya hannunsa ahankali ya dafa kanta .

Da sauri fattu ta ɗago kanta agalabaice ,idonta ya mugun kumbura yayi jaaa!sosai lips ɗinta sai sheƙi yake .kallonsa tayi wani sabbin hawayen na kwararowa daga idanunta.

Dan yatsansa ya sanya ya share hawayen dake zuba daga idanunta,amma wasu na ƙara zubowa.

Da gyar ya buɗe bakinsa cikin hausarsa da bata fita sosai yace "menene"ya faɗa yana kallon cikin idanunta ,gabansa sai bugawa yake,ya rasa mai yasa inhar zai sanya idonsa cikin nata ,to gabansa yayi ta bugawa kenan.

Cikin dasashshiyar murya wacce  kuka ne  yasanya ta dashe fattu tace "Baffana" cikin yanayin shagwaba irin na masu kuka tayi maganar.

Wani yummmmmm!!!Adeeb yaji tun daga tsakiyar kansa har babban dan yatsan ƙafarsa.dan yanayin yadda tayi maganar sai yaji wata irin kasala ta kama shi.

Ahankali ya kumshe idanunsa yayi jimmm!kafin ya buɗe su ya ɗora akan fattu"is ok ki daina kuka"ya faɗa ahankali yana mai janyowa zuwa jikinsa ,dan shikam hakan kaɗai yake ganin zai yi mata tayi shiru.

Allah Sarki fattu kuwa tayi luƙus akan faffaɗan ƙirjinsa sai ajiyar zuciya take sauƙewa,kuma cikin ƙanƙanin lokaci ta fara jin zuciyarta nayi mata sanyi, tana nan kwance ajikinsa barcin wahala yayi gaba da ita.

Shikuwa Adeeb gaba ɗaya jinsa yake wani irin,sam ya kasa samun nutsuwa jinta da yayi cikin jikinsa ,gaba ɗaya yaji yanayinsa na  sauyawa zuwa kasala da jin wani abu mai kama da feeling ,ahankali ya jingina kansa jikin kujerar ,tare da kumshe idanunsa yana mai ƙara gyara mata kwanciyarta. Tunanin  Abie ya fara yi aƙokarinsa na kawar da abinda yake ji acikin jikinsa ,dan aganinsa wannan yarinyar tayi ƙanƙantar da har zai rinƙa jin wani abu akanta,saidai sam jikin nashi yaƙi bashi

haɗin kai,dan ji yayi lamarin na ƙara rikice masa,ganin ba sarki sai Allah yasashi cire ta daga jikinsa ya jingina ta da jikin kujerar da suke kai.

Ajiyar zuciya ya sauƙe yana mai kallon kyakyakywar fuskarta ,wacce ta ƙara wani jaaa!sosai ,ahankali ya sauƙe idanunsa zuwa lips ɗinta waɗanda ta ɗan turosu Baga cikin shagwaɓa  kamar kamar yadda yara keyi idan suna son yin kuka.

Haka kawai ya tsinci kansa da sakin wani murmushi mai ƙayatarwa, hannu yasa ya gyara mata hulɗar kanta,wacce ta ɗan zame  har gashinta na gaban goshi yasami damar fitowa .

Bai ankara ba yaji driver na cewa sun iso Kano,kallon garin yake ,yana tunanin inda zasu sami hotel ,dan su ɗan huta sannan ya sai kaya ya cire wannan na jikin nashi,dan sun matuƙar takura masa.

Tambayar drivern yayi nawane kuɗinsa ya faɗa masa ,bashi yayi cikin wanda baffa ya basu da zasu taho, sannan yace wa mai motar dan Allah hotel yake son zuwa .

Nan mai motar ya tare musu dan adaidaita yace ya kaisu hotel  mafi kusa. Ganin fattu na barci yasa Adeeb bai tashe ta ba kawai ɗauki ta yayi kamar yar tsana ya shiga adaidaita  ya zauna ,sannan itama ya zaunar da ita.kuma ko buɗe ido batayi ba ,dan barcin sosai ya kamata.

Bayan sunje ne ya kama musu ɗaki, sannan ya nufi ɗakin ,har lokacin kuma fattu na rike ahannunsa dan baya don tashi ta daga barci.

Da hannu ɗaya yayi amfani wajen bude dakin sannan ya shiga,kwantar da ita yayi akan gadon  ya lulluɓawa da ƙarin bargon dake kan gadon,sannan ya ɗan zauna shima yana mai lumshe idonsa ,gaba ɗaya agajiye yake  jinsa , dan bai saba irin wannan tafiyar haka ba.

Fita yayi ya siyo musu kaya a store ɗin cikin hotel ɗin sannan yayi musu odar abinci ya dawo,fattu nata barci taji laushin gado da katifa ga ƙaton bargo .lol

Tashi yayi ya shiga bayi yayi wanka,ya faɗa sosai kafin ya fito,agurguje ya sanya kayan daya siyo ,riga da wando ne na jins  da boxers and singlet, sai turare ,sannan yayi sallar asuba.

Masha Allah duk da bayani shiri yayi ba ,amma karkuso kuga irin kyan da  Adeeb yayi ,sosai ya ƙara zama cikakken Balarabe  mai tsananin kyau,sai ƙamshi yake zubawa.

Kwankwasa ƙofar dakin  akayi,  ahankali ya tashi yaje ya buɗe ,abincin da yayi odar ne aka kawo,kaɓar yayi ya dawo ciki.

Kallonta yayi yaga bata tashi ba ,dan haka ya zauna yana cin abincinsa.kaɗan yaci ya tashi  ,da alama bashi da yawan cin abinci sosai.

Gadon da fattu ke kwance ya nufa ,ahankali ya ɗan yaye bargon daya rufa mata,hannunsa yasanya saman goshinta,har lokacin jikinta da zafi sosai.

Filin da take kai ya ɗan bubbuga sau uku, ahankali ta buɗe idonta tana mai turo baki ,sai kuma tayi saurin tashi tana ƙarewa ɗakin kallo ,wai aljanar duniya  nan ɗin shine gidansu hamma Adeeb ?lallai yan gayune su,ji laushin gado kamar auduga.fattu ta faɗa cikin zuciyarta tana mai ƙarewa dakin kallo.

Ji  dan Allah yadda take ta wani kallon daki kamar bata taɓa ganin daki ba "Adeeb ya faɗa cikin zuciyarsa yana ɗan kallonta.

"Go and get your shower" Adeeb ya faɗa ahankali yana mai kawar da kansa .

Kallonsa take ƙuri tana rarraba ido,dan bata fahimci me yake cewa ba.

Jin bata tashiba yasa shi dan juyowa yana kallonta.

"Ɗan hararta yayi kafin yace " nace kije kiyi wanka ne"ya faɗa fuskarsa aɗaure ba walwala.

Tashi fattu tayi sumi-sumi ta nufi hanyar fita ,tana zuwa bakin ƙifar taja ta tsaya tare da juyowa yana kallonsa.

Shima kallonta yake cike da jin haushi ko ina zata kuma?nace take tayi wanka.

Ganin irin kallon da yake mata ne yasa tace "bazan iya budewa ba"ahankali tayi maganar cikin dasashshiyar muryarta kanta aƙasa.

Hararta yayi cike da jin haushin wai yaje bakin ƙofar fita, kuma tana faɗin bazata iya buɗewa,sai kace nan ne toilet ɗin.

Tashi yayi ya nufi bakin ƙofar toilet ɗin ya buɗe sannan ya juyo yana kallonta.

Shiru tayi itama tana ɗan kallon nasa,dan bata gane nufinsa ba.

Wata iska ya furzar mai zafi yana lunshe idonsa,kafin yace "zo kishiga "ya faɗa yana kallonta ,fuskarsa sam ba walwala,shi wllh ya gaji da wannan shirmen nata fa.

Kanta adurƙushe tazo  ta shige toilet ɗin , kayan daya siyo mata ya ɗauki tare da ɗan kwankwasa toilet ɗin ya buɗe kadan yace "take"

Fattu kuwa da tun shigar ta toilet ɗin ta saki baki galala tana kallon ikon Allah,anya kuwa yasan inda ya buɗe mata yace tazo tayi wanka?yo wannan ai Dakin kwanan ne,kalli da harda wani ƙaton  gado mai rami,to ma ta a ina zataga ruwan bare har tayi wankan?

Juyowa tayi tana kallon farin hannunsa daya miƙo mata leda.ƙarasawa tayi kusa dashi ta karɓi ledar sannan tayi saurin cewa "inane banɗakin?

"What " ya faɗa yana mai buɗe kofar gaba ɗaya ,sannan ya kalli fattun ko fara wankan ma batayi ba.

Cikin faɗa -faɗa  yace "do you expect me to West my time here?Ina jiranki?"ya faɗa yana zaro mata manyan fararen dara-daran idanunsa.

Nan da nan jikin fattu ya kama rawa ,tsoro ya kamata ,har kayan hannunsa saida suka faɗi  ƙasa" duk da batasan me yake cewa ba ,tabbas ta san faɗane yake mata ,cikin muryar kuka tace"dan Allah hamma kayi haƙuri bansan a inda zabga ruwan ba"ta faɗa tare da fashewa da kuka tana mai toshe bakinta.

Shiru yayi yana kallonsa,lokaci guda kuma tausayi ta ya kamashi, sai yanzu ya tuna daga inda ya taho da ita,ba abin mamaki bane idan tace bata san ya zata yi ba.dan haka cikin sanyin murya yace "is ok daina kuka "ya fadi yana mai ƙarara shigowa toilet ɗin.

Idan kina son yin  wanka nan zaki danna ruwa zai zubo, sannan idan kina biyan buƙata nan zaki zauna ,In kin gama saiki dannan nan ,wannan na wanke bakine and ga  soso da soap kin gane "ya faɗa yana kallonta .

Kai ta ɗaga masa  alamun ta gane ,

Hanyar waje ya nufa sannan ya juyo yace mata "kiyi sauri yanzu zamu wuce"yana faɗin haka yayi waje.

Zama yayi abakin gadon yana mai dafe kansa,ciwo yaji kansa nayi , sakamakon wannan doguwar maganar da yayi, gaskiya kula da yara akwai wahala ,ji yadda tasa masa ciwon kai rana ɗaya kawai.

Fattu kuwa bayan ta cire kayanta na gado ,wato rigar fulaninta yar dingila da zanin ta ,kai tsaye  gurin soso da sabulun nan ta nufa ta ɗauka sanna tazo ta tsaya saitin gurin da akace idan ta danna ruwa zai zo ,dannawa tayi tana jiran taga ta ina ruwan zai zubo,ai ba zato ba tsammani kawai taji ruwa akanta shaaaaaa!!!

Wata zabura da fattu tayi tare da watsar da  soso da sabulun nan ta kurma uban ihu iya ƙarfinta ta nufi kofar fita ba komai ajikinta "wayyo Allah na hamma wayyo kazo ka buɗe ni na shiga uku dakin yan shan jini ka kawoni ana min ruwan jini akaina wayyo hamma am" abinda fattu ke faɗa kenan cikin rikicewar da tashin hankali gaba ɗaya jikinta rawa yake kamar ɗan mazari.

Adeeb na kwance a gefen gado yayi nisa cikin tunani kawai ya biyo ihunta  ,ai baisan lokacin daya zabura da mugun sauri yayi toilet ɗin ba,yana zuwa ya buɗe kofar da da sauri ya danna kansa ciki.

Kicibis sukayi da fattu abakin ƙofar, tayo gunsa ga gudu tana kuka.

Wani irin bugawa ƙirjin  Adeeb yayi kansa ya hau juyawa ,sakamakon ganin da yayiwa fattu haka zirr ɗin ta ba kaya.tunda yake arayuwarsa yau ya taɓa ganin mace data fara girma haka ba kaya agabansa. Cikin hanzari ya juya bayansa yana mai dafe ƙirjinsa dake barazanar fashewa."innalillahi "ya faɗa cikin sassarfa  lokacin dayaji fattu ta kankameshi tana kuka.

"Sosai shima jikinsa ya hau rawa kamar ɗan mazari,cikin rawar murya yake faɗin"le..a...ve. me... Lea....ve... M....e" yana kasa nutsuwa yayi mata magana.

Fattu kuwa banda rawa ba abinda jikinta keyi,wannan wace irin masifa ce haka? wane irin gida ya kawota ,za'a cinyeta ya sama.

Runtse idanun Adeeb. Yayi da mugun ƙarfi yana ambaton sunan Allah ,ya ɗauki kusan minti biyu cikin halin ruɗewa da rawar jiki.gaba ɗaya jikinsa yayi wani iri,kafin yayi ƙarfin halin sanya hannunsa dake rawa ya fizgota daga bayansa tare da tureta can gefe guda,yana mai sauƙe numfashi cikin sauri ,kawar da kansa yayi daga gareta yana mai cewa"kisa zani ki rufe jikinki Please.

Fattu kuwa cikin rawar jiki ta ƙara matsowa gareshi sam tama manta da batun wasu kaya,"dan Allah ka fitar dani daga ,Ni gurin baffana zani "ta faɗa cikin kuka.

"Kisa zani nace miki"ya daka mata tsawar data ƙara hargitsata.tsugunnawa tayi tare da ƙanƙame jikinta tana kuka.

"Ni ka kaink gurin baffana dan Allah ka maidani gurin baffa "abinda take daɗi kenan cikin kuka da rawar jiki ,gaba ɗaya ta gama tsorata .

Zanin nata Adeeb yaje ya yayumo  cikin lalube,dan ko gani batayi sosai .yana zuwa ya lulluɓa mata sannan,ya fice daga bayin, da gyar ya iya ƙarasawa kan gadon yana zuwa ya faɗa kan gadon tare da duƙunƙune jikinsa yana rawar sanyi .....

Masu karatu mutara next oage.

Ina ganin comments ɗinku masoya ta ko ina ,ina matukar jin daɗi da ƙaunarku ga wannan novel ɗin .

Na gode sosai Allah ya bar ƙauna ,

And I love you  guys where ever  you are□□□□

Anty mammy ce

Mrs babi□□

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

_____Wata leda Baffa ya ɗauko  ,ledar da ɗan nauyi ,alamun wani abune acikin ta .sannan ya ɗauki wannan rigar ta fattu ya cusa acikin ledar,safin yayi waje ,Abeed ya rufa masa baya.

Ahankali baffa ke takawa Abeed na biye dashi,saɓe da fattu akafaɗarsa,wacce ke cikin matsanancin hali na zazzaɓi,da damuwa.

Tafiya suke cikin sauri bayan sun bar gidan ,cikin ikon Allah basu haɗu da kowa ba ,har sukayi nisa da garin sosai,saida baffa ya fitar dasu kan kwalta kafin ya tsaya .

Har zuwa wannan lokacin fattu na saɓe akan kafaɗar Abeed ,duk da irin uban nisan dake tsakanin rugar da kwalta.

Ahankali Abeed ya sauƙe fattu ya ɗan jingina ta da jikinsa,dan yaga bazata iya tsayuwa ba .

"Malam Abeed karɓi wannan wasu yan kudadene da nake tarawa saboda irin wannan ranar,nasan zasu toshe muku wata kafar,dan Allah ka riƙe min alƙawari, ka

kulamin da fattuna,karka bari wani ko wata ya cutar da ita,sannan kayi iyakar ƙoƙarin ka wajen sadata da  magaifanta.

Kaima zaka sami lada"baffa ya faɗa yana kallon bayansa ,hanyar da suka baro ,dan tsoro yake kar yaje ko anbiyosu,dan yasan zuwa yanzu labari ya isa kunnen lamiɗo,tunda gari yayi haske an kusan shiga sallah.

"In Sha Allahu Abba zan kula da amanar ka,na gode da taimakon da kukayimin, sannan zan dawo gareka very soon"Abeed ya faɗa cikin nutsuwarsa da rashin son magana,akwai abubuwan da yake son faɗa amma tsabar rashin son maganarsa bazai iya ba dan haka yayi shiru daga wannan maganar.

Hannun fattu baffa ya kama yariƙe gam-gam cikin nashi,kallon ta yayi yayinda itama take kallonsa cikin kuka wanda muryarta ko fita batayi sosai, shima baffa tuni zuciyarsa ta karaya ,sai hawaye sharrrr!!

"Allah ya shiga lamarin ki fattu, Allah ya karemin ke ka yasa damu da alkairi,ki kula da kanki,ki kama mutuncinsu.Allah yayi miki albarka"baffa ya faɗa cikin kuka sosai,abin tausayi.

"Baffa bana son tafiya ,dan Allah kace na zauna ,Ni nafison zama da kai akan iyayena ma asali,baffa karka tafi ka barni "Fattu ta faɗa cikin kuka harda shashsheka kamar zata shiɗe. Kafin baffa yayi magana saiga wata mota zata wuce ,da alama daga cikin Jos take .

Da sauri baffa yayi musu hannu alamun su tsaya.tambayarsu yayi ina suka nufa ,mai motar yace Kano.

Kallon Adeeb baffa yayi yace "duk da bansan inane Kanon ba amma Gara kubi wannan motar kafin tawagar mai gari su fito nemanku.

Kai kawai Abeed ya ɗada,tare da kamo hannun fattu suka nufi motar,hannunsa ɗaya riƙe da ledar da baffa ya basu.

Kuka fattu take harda ihu tana faɗin"wayyo baffana ,banason tafiya,dan Allah baffa kace na dawo wayyo baffa am wayyo Allah na ,wayyo rayuwata "

Baffa kam ko magana ya kasa tsabar kuka sai daga musu hannu kawai yake yana juya kai.

Abeed ne ya sanyata cikin motar tare da riƙe ta ,ɗan sai ƙoƙarin  fitowa take ,haka mai motar nan yaja motarsa yayi gaba,dan kaya zaije ɗaukowa.

Baffa yana tsaye har saida yaga ɓacewar motar ,sannan ya sauke wani kwauron numfashi yana mai share hawayen idanunsa,"Allah ga amanar yʼata nan  na miƙa lamarin ta ahannunka ,ya ubangiji kazama majiɓancin al'amarinta "baffa ya faɗa yana mai juya dan koma gida ayi wacce za'ayi.

Aikuwa tun kafin ya ƙarasa cikin garin ,ya hango cincirindon mutane aƙofar gidansa,jinjina kai yayi,dan dama yayi tsammanin hakan .

Suna hangoshi sukayo kan suna wllh koya fito da yʼar Shegiyar daya ɗauka matsayin yʼarsa ,da kwarton ta da suka ajiye agida,ko kuma su kashe shi yanzun nan.

Kallonsu yayi cikin kamala da dattako yace "ikon Allah me kuma mukayi dazaku kashemu?wace yarinyar kuke nema?bayan wacce mai gari ya riƙe agurinsa?baffa ya faɗa kai tsaye ba nuna alamun tsoro.

Nan wani lawwali yace masa"ai jiya yarinyar nan saida ta bari dare ya raba sannan ta sami lamiɗo tayi masa jina jina,gaba ɗaya ƙafafunsa sun ƙarye,ga hannun damanshi ma ya ɓalle baral, sannan ta gudu,kuma munsan tabbas tana gidan nan,dan kuwa hansai ta kai labari,

Kuma ta fayyace mana komai game da yarinyar ,ashe Shegiya ce ka tsinto ka kawo gidanka,sannan ka ajiye mata wani gardin suke lalata dashi,dan haka gaba ɗayanku yau sai hukunci ya hau kanku,dan lamiɗo yana nan banda ihu ba abinda yake yana kiran maciji zai kashe shi,fattu ce tayi masa ture.sannan arɗo ma yana can hannunsa guda ya shanye ya zama kamar sillan kara ,kuma duk aikin fattu ne ,dan haka yau wllh saimun kashe fattu"lawwali ya ƙare zancensa yana mai ɗaga sandarsa sama.

"Toh me yasa baku shiga kun duba fattun ba ?idan nan ta dawo,ita wacce ta kai muku rahoton saita faɗa muku inda fattun take"baffa ya faɗa yana ƙoƙarin shigewa gida.

"Ƙarya yake wllh, saidai in ya boyesu ,ko kuma sun gudu ,dama naji yana cewa su gudu dan haka karku taga masa " na tsinkayo muryar gwogwgo hansai na faɗin haka ,dan taji mugun haushi da ba'a sami su fattu cikin gidan ba.

Aikuwa baffa yana tsaye

Ba zato ba tsammani yaji sun rufeshi da duka ta ko ina.

Har saida suka kaishi ƙasa.sannan suka taitayeshi sai gurin. Mai gari.suna zuwa suka tarar ana yiwa mai gari ɗori sai ihu yake yana kuka.dan haka can ɗakin hukunci suka jefa baffa,wanda yayi kaishi sosai dan ya daku.

Allah Sarki baffa ,Allah ya saka maka.

Fattu kuwa tsabar kuka har muryarta ta dashe,can jikin ƙarshen motar ta koma tare da haɗe kai da gwuiwa tana kuka marar sauti ,jikinta sai rawa yake ,fuska ta kumbura suntum tayi jajur ,abinka da farar fata.

Abeed yana daga gefe yana kallonta ,sosai yake jin kukanta har cikin ransa,haƙiƙa yarinyar tana fuskantar ƙalubalen rayuwa and she's to Young to handle the situation.amma ya zatayi?dole ta ɗauki ƙaddara yadda yazo mata.

Kallonta yayi yadda jikinta ke ta rawa tana shashsheƙar kuka,yaso ace ya iya rarrashi, daya rarrasheta ,koba komai itaɗin yanzu amanarsace,amma Gara tayi kuka ,koba komai zata rage jin raɗaɗin da taleji cikin zuciyarta.

Tafiya suke sosai ,Dan drivern gudu yake tsulawa,kasancewar safiya ce hanyar ba motoci sosai,sai jifa-jifa suke cin karo da motocin.

Abeed yayi shiru ,tare da jingina kansa jikin kujerar da yake zaune,ba abinda ke yawo cikin zuciyarsa,sai labarin da baffa ya bashi na cewar wai shiɗin amaciji suka

ganshi,to ta yaya?yaushe hakan ta faru,me yasameshi? Tabbas idan har abinda baffa ya faɗa gaskiya ne baya raba ɗayan biyu cewar sharrin Amma ne wannan ,dan ita kaɗai yake tunanin zata iya cutar dashi ,tunda afili take nuna masa ƙiyayya, amma zaibi abin ahankali harya gano mugun ƙullinta akansa kafin ya ɗauki mataki.

Ya rasa me ya tsareta Amma arayuwa sam bata ƙaunarsa ,kullum burinta ta cutar dashi,tun yana ƙarami  yake fuskantar tsangwamarta,har kawo yanzu bata fasa ba ,amma akwai lokacin da ko ance tayi masa wani abun bazata iyaba.

Juyowa yayi ya kalli inda fattu ke zaune ,har zuwa wannan lokacin kuka take ,banda rawa ba abinda jikin ta keyi.wani tausayine yaji ya kama zuciyarsa ,wannan kukan yayi yawa zai iya haifar mata da matsala.dan haka ahankali ya ɗan matsa kusa da ita ,ƙureta yayi da ido ,yana son yayi mata magana amma baisan me zaice mata ba.

Kusan minti uku yayi yana kallonta da yadda jikinta ke rawa sosai,kafin ya sanya hannunsa ahankali ya dafa kanta .

Da sauri fattu ta ɗago kanta agalabaice ,idonta ya mugun kumbura yayi jaaa!sosai lips ɗinta sai sheƙi yake .kallonsa tayi wani sabbin hawayen na kwararowa daga idanunta.

Dan yatsansa ya sanya ya share hawayen dake zuba daga idanunta,amma wasu na ƙara zubowa.

Da gyar ya buɗe bakinsa cikin hausarsa da bata fita sosai yace "menene"ya faɗa yana kallon cikin idanunta ,gabansa sai bugawa yake,ya rasa mai yasa inhar zai sanya idonsa cikin nata ,to gabansa yayi ta bugawa kenan.

Cikin dasashshiyar murya wacce  kuka ne  yasanya ta dashe fattu tace "Baffana" cikin yanayin shagwaba irin na masu kuka tayi maganar.

Wani yummmmmm!!!Adeeb yaji tun daga tsakiyar kansa har babban dan yatsan ƙafarsa.dan yanayin yadda tayi maganar sai yaji wata irin kasala ta kama shi.

Ahankali ya kumshe idanunsa yayi jimmm!kafin ya buɗe su ya ɗora akan fattu"is ok ki daina kuka"ya faɗa ahankali yana mai janyowa zuwa jikinsa ,dan shikam hakan kaɗai yake ganin zai yi mata tayi shiru.

Allah Sarki fattu kuwa tayi luƙus akan faffaɗan ƙirjinsa sai ajiyar zuciya take sauƙewa,kuma cikin ƙanƙanin lokaci ta fara jin zuciyarta nayi mata sanyi, tana nan kwance ajikinsa barcin wahala yayi gaba da ita.

Shikuwa Adeeb gaba ɗaya jinsa yake wani irin,sam ya kasa samun nutsuwa jinta da yayi cikin jikinsa ,gaba ɗaya yaji yanayinsa na  sauyawa zuwa kasala da jin wani abu mai kama da feeling ,ahankali ya jingina kansa jikin kujerar ,tare da kumshe idanunsa yana mai ƙara gyara mata kwanciyarta. Tunanin  Abie ya fara yi aƙokarinsa na kawar da abinda yake ji acikin jikinsa ,dan aganinsa wannan yarinyar tayi ƙanƙantar da har zai rinƙa jin wani abu akanta,saidai sam jikin nashi yaƙi bashi haɗin kai,dan ji yayi lamarin na ƙara rikice masa,ganin ba sarki sai Allah yasashi cire ta daga jikinsa ya jingina ta da jikin kujerar da suke kai.

Ajiyar zuciya ya sauƙe yana mai kallon kyakyakywar fuskarta ,wacce ta ƙara wani jaaa!sosai ,ahankali ya sauƙe idanunsa zuwa lips ɗinta waɗanda ta ɗan turosu Baga cikin shagwaɓa  kamar kamar yadda yara keyi idan suna son yin kuka.

Haka kawai ya tsinci kansa da sakin wani murmushi mai ƙayatarwa, hannu yasa ya gyara mata hulɗar kanta,wacce ta ɗan zame  har gashinta na gaban goshi yasami damar fitowa .

Bai ankara ba yaji driver na cewa sun iso Kano,kallon garin yake ,yana tunanin inda zasu sami hotel ,dan su ɗan huta sannan ya sai kaya ya cire wannan na jikin nashi,dan sun matuƙar takura masa.

Tambayar drivern yayi nawane kuɗinsa ya faɗa masa ,bashi yayi cikin wanda baffa ya basu da zasu taho, sannan yace wa mai motar dan Allah hotel yake son zuwa .

Nan mai motar ya tare musu dan adaidaita yace ya kaisu hotel  mafi kusa. Ganin fattu na barci yasa Adeeb bai tashe ta ba kawai ɗauki ta yayi kamar yar tsana ya shiga adaidaita  ya zauna ,sannan itama ya zaunar da ita.kuma ko buɗe ido batayi ba ,dan barcin sosai ya kamata.

Bayan sunje ne ya kama musu ɗaki, sannan ya nufi ɗakin ,har lokacin kuma fattu na rike ahannunsa dan baya don tashi ta daga barci.

Da hannu ɗaya yayi amfani wajen bude dakin sannan ya shiga,kwantar da ita yayi akan gadon  ya lulluɓawa da ƙarin bargon dake kan gadon,sannan ya ɗan zauna shima yana mai lumshe idonsa ,gaba ɗaya agajiye yake  jinsa , dan bai saba irin wannan tafiyar haka ba.

Fita yayi ya siyo musu kaya a store ɗin cikin hotel ɗin sannan yayi musu odar abinci ya dawo,fattu nata barci taji laushin gado da katifa ga ƙaton bargo .lol

Tashi yayi ya shiga bayi yayi wanka,ya faɗa sosai kafin ya fito,agurguje ya sanya kayan daya siyo ,riga da wando ne na jins  da boxers and singlet, sai turare ,sannan yayi sallar asuba.

Masha Allah duk da bayani shiri yayi ba ,amma karkuso kuga irin kyan da  Adeeb yayi ,sosai ya ƙara zama cikakken Balarabe  mai tsananin kyau,sai ƙamshi yake zubawa.

Kwankwasa ƙofar dakin  akayi,  ahankali ya tashi yaje ya buɗe ,abincin da yayi odar ne aka kawo,kaɓar yayi ya dawo ciki.

Kallonta yayi yaga bata tashi ba ,dan haka ya zauna yana cin abincinsa.kaɗan yaci ya tashi  ,da alama bashi da yawan cin abinci sosai.

Gadon da fattu ke kwance ya nufa ,ahankali ya ɗan yaye bargon daya rufa mata,hannunsa yasanya saman goshinta,har lokacin jikinta da zafi sosai.

Filin da take kai ya ɗan bubbuga sau uku, ahankali ta buɗe idonta tana mai turo baki ,sai kuma tayi saurin tashi tana ƙarewa ɗakin kallo ,wai aljanar duniya  nan ɗin shine gidansu hamma Adeeb ?lallai yan gayune su,ji laushin gado kamar auduga.fattu ta faɗa cikin zuciyarta tana mai ƙarewa dakin kallo.

Ji  dan Allah yadda take ta wani kallon daki kamar bata taɓa ganin daki ba "Adeeb ya faɗa cikin zuciyarsa yana ɗan kallonta.

"Go and get your shower" Adeeb ya faɗa ahankali yana mai kawar da kansa .

Kallonsa take ƙuri tana rarraba ido,dan bata fahimci me yake cewa ba.

Jin bata tashiba yasa shi dan juyowa yana kallonta.

"Dan harararta yayi kafin yace " nace kije kiyi wanka ne"ya faɗa fuskarsa aɗaure ba walwala.

Tashi fattu tayi sumi-sumi ta nufi hanyar fita ,tana zuwa bakin ƙifar taja ta tsaya tare da juyowa yana kallonsa.

Shima kallonta yake cike da jin haushi ko ina zata kuma?nace take tayi wanka.

Ganin irin kallon da yake mata ne yasa tace "bazan iya budewa ba"ahankali tayi maganar cikin dasashshiyar muryarta kanta aƙasa.

Harararta yayi cike da jin haushin wai yaje bakin ƙofar fita, kuma tana faɗin bazata iya buɗewa,sai kace nan ne toilet ɗin.

Tashi yayi ya nufi bakin ƙofar toilet ɗin ya buɗe sannan ya juyo yana kallonta.

Shiru tayi itama tana ɗan kallon nasa,dan bata gane nufinsa ba.

Wata iska ya furzar mai zafi yana lunshe idonsa,kafin yace "zo kishiga "ya faɗa yana kallonta ,fuskarsa sam ba walwala,shi wllh ya gaji da wannan shirmen nata fa.

Kanta adurƙushe tazo  ta shige toilet ɗin , kayan daya siyo mata ya ɗauki tare da ɗan kwankwasa toilet ɗin ya buɗe kadan yace "take"

Fattu kuwa da tun shigar ta toilet ɗin ta saki baki galala tana kallon ikon Allah,anya kuwa yasan inda ya buɗe mata yace tazo tayi wanka?yo wannan ai Dakin kwanan ne,kalli da harda wani ƙaton  gado mai rami,to ma ta a ina zataga ruwan bare har tayi wankan?

Juyowa tayi tana kallon farin hannunsa daya miƙo mata leda.ƙarasawa tayi kusa dashi ta karɓi ledar sannan tayi saurin cewa "inane banɗakin?

"What " ya faɗa yana mai buɗe kofar gaba ɗaya ,sannan ya kalli fattun ko fara wankan ma batayi ba.

Cikin faɗa -faɗa  yace "do you expect me to West my time here?Ina jiranki?"ya faɗa yana zaro mata manyan fararen dara-daran idanunsa.

Nan da nan jikin fattu ya kama rawa ,tsoro ya kamata ,har kayan hannunsa saida suka faɗi  ƙasa" duk da batasan me yake cewa ba ,tabbas ta san faɗane yake mata ,cikin muryar kuka tace"dan Allah hamma kayi haƙuri bansan a inda zabga ruwan ba"ta faɗa tare da fashewa da kuka tana mai toshe bakinta.

Shiru yayi yana kallonsa,lokaci guda kuma tausayi ta ya kamashi, sai yanzu ya tuna daga inda ya taho da ita,ba abin mamaki bane idan tace bata san ya zata yi ba.dan haka cikin sanyin murya yace "is ok daina kuka "ya fadi yana mai ƙarara shigowa toilet ɗin.

Idan kina son yin  wanka nan zaki danna ruwa zai zubo, sannan idan kina biyan buƙata nan zaki zauna ,In kin gama saiki dannan nan ,wannan na wanke bakine and ga  soso da soap kin gane "ya faɗa yana kallonta .

Kai ta ɗaga masa  alamun ta gane ,

Hanyar waje ya nufa sannan ya juyo yace mata "kiyi sauri yanzu zamu wuce"yana faɗin haka yayi waje.

Zama yayi abakin gadon yana mai dafe kansa,ciwo yaji kansa nayi , sakamakon wannan doguwar maganar da yayi, gaskiya kula da yara akwai wahala ,ji yadda tasa masa ciwon kai rana ɗaya kawai.

Fattu kuwa bayan ta cire kayanta na gado ,wato rigar fulaninta yar dingila da zanin ta ,kai tsaye  gurin soso da sabulun nan ta nufa ta ɗauka sanna tazo ta tsaya saitin gurin da akace idan ta danna ruwa zai zo ,dannawa tayi tana jiran taga ta ina ruwan zai zubo,ai ba zato ba tsammani kawai taji ruwa akanta shaaaaaa!!!

Wata zabura da fattu tayi tare da watsar da  soso da sabulun nan ta kurma uban ihu iya ƙarfinta ta nufi kofar fita ba komai ajikinta "wayyo Allah na hamma wayyo kazo ka buɗe ni na shiga uku dakin yan shan jini ka kawoni ana min ruwan jini akaina

wayyo hamma am" abinda fattu ke faɗa kenan cikin rikicewar da tashin hankali gaba ɗaya jikinta rawa yake kamar ɗan mazari.

Adeeb na kwance a gefen gado yayi nisa cikin tunani kawai ya biyo ihunta ,ai baisan lokacin daya zabura da mugun sauri yayi toilet ɗin ba,yana zuwa ya buɗe kofar da da sauri ya danna kansa ciki.

Kicibis sukayi da fattu abakin ƙofar, tayo gunsa ga gudu tana kuka.

Wani irin bugawa ƙirjin Adeeb yayi kansa ya hau juyawa ,sakamakon ganin da yayiwa fattu haka zirr ɗin ta ba kaya.tunda yake arayuwarsa yau ya taɓa ganin mace data fara girma haka ba kaya agabansa. Cikin hanzari ya juya bayansa yana mai dafe ƙirjinsa dake barazanar fashewa."innalillahi "ya faɗa cikin sassarfa lokacin dayaji fattu ta kankameshi tana kuka.

"Sosai shima jikinsa ya hau rawa kamar ɗan mazari,cikin rawar murya yake faɗin"le..a...ve. me... Lea....ve... M....e" yana kasa nutsuwa yayi mata magana.

Fattu kuwa banda rawa ba abinda jikinta keyi,wannan wace irin masifa ce haka? wane irin gida ya kawota ,za'a cinyeta ya sama.

Runtse idanun Adeeb. Yayi da mugun ƙarfi yana ambaton sunan Allah ,ya ɗauki kusan minti biyu cikin halin ruɗewa da rawar jiki.gaba ɗaya jikinsa yayi wani iri,kafin yayi ƙarfin halin sanya hannunsa dake rawa ya fizgota daga bayansa tare da tureta can gefe guda,yana mai sauƙe numfashi cikin sauri ,kawar da kansa yayi daga gareta yana mai cewa"kisa zani ki rufe jikinki Please.

Fattu kuwa cikin rawar jiki ta ƙara matsowa gareshi sam tama manta da batun wasu kaya,"dan Allah ka fitar dani daga ,Ni gurin baffana zani "ta faɗa cikin kuka.

"Kisa zani nace miki"ya daka mata tsawar data ƙara hargitsata.tsugunnawa tayi tare da ƙanƙame jikinta tana kuka.

"Ni ka kaink gurin baffana dan Allah ka maidani gurin baffa "abinda take daɗi kenan cikin kuka da rawar jiki ,gaba ɗaya ta gama tsorata .

Zanin nata Adeeb yaje ya yayumo  cikin lalube,dan ko gani batayi sosai .yana zuwa ya lulluɓa mata sannan,ya fice daga bayin, da gyar ya iya ƙarasawa kan gadon yana zuwa ya faɗa kan gadon tare da duƙunƙune jikinsa yana rawar sanyi .....

Masu karatu mutara next oage.

Ina ganin comments ɗinku masoya ta ko ina ,ina matukar jin daɗi da ƙaunarku ga wannan novel ɗin .

Na gode sosai Allah ya bar ƙauna ,

And I love you  guys where ever  you are□□□□

Anty mammy ce

Mrs babi□□

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



https://www.facebook.com/groups/1627491150723081/?ref=share_group_link

Masu amfani da face book sai kuyi join wannan group ɗin .

_____"So nake ka tafi da ƙanwarka can garin naku,dan taimaka mata wajen gano iyayenta na asali"baffa ya faɗa yana kallon fattu ,wacce tunda baffa ya fara maganar take jin wani irin matsanancin faɗuwar gaba ,ji tayi maganar tasa ta sauƙa acikin tsakiyar kanta ,kamar sauƙar aradu,"wace irin magana baffa keyi ne haka" anya kuwa yasan me yake faɗi?kai a'a gaskiya bai gane me yake faɗi ba shima.

Fattu ta faɗa cikin zuciyarta,tana mai sauƙe ajiyar zuciya ,dan ta fahimci baffa yana nufin innar ta kenan,saidai kuma bata da wani dalilin bin mutumin da bata sanshi

ba,Gara tayi zamanta agurin baffanta ,inyaso innar tata inhar ta damu da ita ,zata zo gareta.

Ahankali fattu ta buɗe bakinta tace "baffa ina ganin babu buƙatar saina bishi wani garin ,dan neman innata,zan zauna anan ɗin idan da rabon zamu gana wata rana zata zo gareni baffa"fattu ta ƙare maganarta cike da mugun bugawar zuciya ,dan har lokacin kalaman baffa na mata yawo akanta.

Ajiyar zuciya baffa ya sauƙe cike da alhini abinda zai faɗa wa fattun ,kafin yace"ayya fattu amm ki saurareni, da kyau ,ki nutsu ,kuma ki sani kowane bawa da yadda ƙaddararsa ke zuwa masa.

Haƙiƙa Ni malam bukar bani ne na haife ki ba na tsincekine tun kina yarinya ƙarama "baffa ya faɗi hakan yana mai sunkuyar da kansa cike da tausayin fattu.

"Innalillahi wa'inna ilaihir raji'un baffa me kake faɗi ne haka?dan Allah baffa kayi haƙiri idan nayi maka wani laifin ne,amma karka ƙara nesanta alaƙarka dani, baffa bazan iya jura ba,bansan kowa ba sai kai ,kai kaɗai ne gata na baffa dan Allah karka rabu dani "fattu ta faɗa cikin matsanancin kuka marar sauti sosai.

Shide Adeeb kallonsu kawai yake cike da mamaki,how can that be possible ace  wai ya tafi da wata yarinya har can ƙasar su ,yace a ina ya samota ?kuma ta yaya ma zai fara neman ahalin yarinyar .shifa gaba ɗayama lamarinsu ɗaure masa kai yake ,basu sanshi ba,ba wata alaƙa atsakaninsu dashi,amma yana ƙoƙarin bashi yarinya ya tafi da ita.

Kallon baffa yayi lokacin dayaji yana magana da cewa"nasan zaki shiga ruɗu da damuwa Aduk lokacin  da kika sami wannan labarin fattu,saidai bani da yadda zanyi,yazama dole insanar dake gaskiyar abinda ke wakana,kisani fattu ina ƙaunarki fiye da yʻayʻan dana haifa na cikina dan kin fiyemin su sau dubu.amma son da nake miki bazai sa in  cutar dake ba ta hanyar ƙin faɗa miki gaskiya fattu , kisani ahalin yanzu zamanki arugar nan akwai haɗari ,idan mai gari ya farka,kinsan hukuncin da zai zartar akanki bazai mana daɗi ba .dan haka kiyi haƙuri wllh badan cutarwa yasa nace tafi dake ba,saidan ko da baya nan to nayi niyar barin garin nan dake Dan tseratar da rayuwarki"

Baffa ya faɗa hawaye na zubowa daga idanunsa.

Kuka fattu kawai take cike da wani irin baƙin ciki marar misaltuwa, wannan wace irin ƙaddara ce ?yanzu shikenan bata ga tsuntsu bata ga tsarki,baffan da take gani matsayin mahaifinta ashe shima ba mahaifinta bane?kenan ita bata da kowa?tunda ta taso take cikin bakin ciki da damuwa ,amma ta kwance zamanta cikin wannan bakin cikin akan zuwan wannan ranar.kuka take irin wanda yake fitowa kai tsaye daga zuciya ba abinda take fata ahalin yanzu kamar ace ta farka taga ashe barci take ,tayi wannan mummunan mafarkin.to suwaye iyayenta?me tayi musu suka yarda ita?shin basa son tane  ko yaya?tambayar da take tayiwa zuciyarta kenan,jikinta kuwa nan da nan ya ɗau ɓari,kan kace me tuni zazzaɓi mai zafi ya kamata.

Ahankali Adeeb ya kalli baffa na tsawon lokaci kafin ya buɗe baki cikin salonsa na rashin son magana yace "amma Abba ta yaya zaka bani yarka i tafi da ita ?bayan baka Sanni ba,bakasan koni ɗin  waye ba ,infact baka saniba ma koniɗin mugune ,Amma kake don bani yarka in tafi da ita why?Adeeb ya faɗa yana kallon baffa.

Dan murmushi baffa yayi,irin wanda yafi kuka ciwon nan,kafin yace "na yarda da kai nasan bazaka taɓa cutar min da fattu ba ,dan tun kana wata halittar wacce ta kasance muguwa kake taimakonta, bare yanzu da kake cikakken mutum.sannan na jima ina addu'a akan Allah ya kawo wanda zai zama silar farin cikin fattu ,sai haka Allah ya kawo ka,alokacin da mu bamuyi tsammani ba,kuma kallo ɗaya nayi maka zuciyata  ta aminta da kai ,nasan Allah ne ya karɓi addu'a ta.dan haka bani da wani kokwanto akanka." Baffa ta faɗa cikin nuna yanayi na gamsuwa akan hukuncin daya yanke.

Ahankali fattu ta rarrafe zuwa kusa da baffa ,hannunsa ta kama ta riƙe gamm!cikin nata ,kafin tace "baffa su waye iyayen nawa?me yasa suka yarda Ni?a ina ka tsinceni?ta faɗa cikin kuka tana mai jan majina.

Kallon ta Adeeb yayi cike da tausayawa,dan sosai yaji ta bashi tausayi, she's too young ace ta fuskanci wannan babban ƙalubalen.

Baffa ne ya fara magana da cewa"kafin na auri hansai na auri wata kanwata,yar gidan tayar babata. Inda muka kasance duka marayune daga i har ita.itace matata ta farko ,minyi aurene irin na haɗin zumunci,tana da haƙuri da kawaici ,muna zaune cikin aminci da mutunta juna,har Allah ya bata ciki.

Munyi murna sosai da samun wannan cikin ,tare da addu'ar Allah ya sauƙeta lafiya.

Wata rana kuwa naƙuda ta kamata,ganin yadda take shan wahala ,saina tafi jeji dan ɗebo mata maganin gargajiya tasha,ina cikin tafiya nayi nisa sosai da rugar nan,kwatsam saina fara jiyo kukan jariri,haka nayi ta bin sautin kukan harna cimma gurin.

Kwance na iskeki kinata kuka gaba ɗaya jikinki yayi ƙura, sannan kin kukkurje dan ga jini jini nan ma ajikin rigar dake jikinki,

Addu'a nayi tare da ɗaukoki na dawo gida .

Koda na dawo gida na iske matata tana kuka ga gawar jaririya nan gabanta.wato yar da ta haifa ta koma.

Munyi baƙin ciki sosai da rashin yarinyarmu,amma haka muka haƙura  muka mikawa Allah lamarinmu. Nan na bata labarin samoki da nayi,sai naga tana ta murna da farin ciki,batayi wata- wata ba ta karɓe ki ta fara shayar dake,koda nayi magana saitace"Allah ne ya dawo mana da farin cikinmu.dan haka zamu rikeki matsayin yarmu da muka rasa,idan kuma munji anyi cigiyarki saimu bada ke.

Nan da nan nima na yarda da shawarar ta ,dan lokaci ɗaya Allah ya samun ƙaunarki raina. Haka na gayyato mutane akayi suturar yarmu,yayinda nake faɗawa Mutane cewar yan biyu matata ta haifa ,ɗayar ta koma sai ɗayar.

Lokacin da muka tsinceki akwai wani sarƙa awuyanki,wacce da alama zata yi matukar tsada ,dan haka sai muka cire muka ajiyeta haɗe da rigar dana tsinceki da ita.

Munsha tambaya akan ya akayi baki biyo ko ɗaya daga cikinmuba,dan kin kasance kyakyakywa wacce kaf rugar nan ba wanda ya kama ƙafar kyanki,sannan gashinki ba  irin namu bane.haka dai muke samun amsar da zamu rufe bakin mutane da ita.

Shekararki biyu a duniya ,Maryama ta koma ga Allah.munyi kuka daga ni harke na rashinta, kafin daga bisani muka haƙura.

Lokacin ne na auri hansai ,wacce ta kasance ba abinda ta iya banda mugunta da baƙin hali,sam bata ƙaunar ki ,da idan tayi miki wani abun nakan yi magana ,saidai daga baya kuma sainake kasa yin maganar,koda na yunƙuro da nufin yin maganar bana iyawa.

Wannan shine taƙaitaccen tarihinki fattu na.amma na tabbata ko ba daƌe ko ba jima zaki haƌu da asalin iyayenki,jikina yana bani kun kusan haƌuwa. Wanda idan har kikaci gaba da zama cikin rugarnan, hakan bazata faru ba.zan nemeki Aduk inda kuke fattu na "baffa ya faƌa cikin kuka abin tausayi.

Fattu ma kuka take sosai kamar ranta zai fita ,"baffa ina sarƙar take "fattu ta faƌa cikin rawar murya irin ta mai zazzaɓi.

Tashi baffa yayi ya buƌe cikin jakarsa ta kaya ya ƌauko wata leda ya kunce,saiga wata sarƙa mai tsananin sheki da ƌaukar ido,sai wata ƴar riga mai kyau fara ta yara.miƙawa fattu kayan baffa yayi .

Ahankali ta karbi kayan ta rungume ajikinta tana kuka mai tsuma zuciyar mai sauraro.

Kallonsu kawai Adeeb yake ,dan zuwa yanzu ya gama ƌaukarwa kansa alƙawarin taimakawa fattu ta kowace fuska ,har saita ga iyayenta.

Baffa kansa kukan yake ,yana jimamim rabuwa da Fattun sa.

Tashi Adeeb yayi ,cikin tafiyarsa ta izza da cike jarumta ya ƙarasa kusa da fattu ,tsugunmawa yayi akusa da ita ,yana kallon fuskarta dake ta faman kuka ,gaba ƌaya tayi jajur da ita.

Hannunsa ya sanya ya ƌago habarta ya kura mata ido,buƌe idanunta tayi itama ta sauƙe cikin nashi,sun ƌauki kusan mintuna uku suna kallon juna,kafin Adeeb ya sauke wani kwauron numfashi ,sannan ya sanya babban ƌan yatsanshi ya share mata hawayen dake zuba a idonta.girgiza mata kai yayi alamun ta daina kuka.amma sam ta kasa dainawa.

Sarƙar hannunta ya karɓa yana kallo,sarkar zallar daimond ce sai sirin kwal,da gani wannan sarƙar ta doshi millions ,koma ina yarinyar nan ta fito to tabbas ƴar gidan manya ce,in Sha Allah zai haƌata da iyayenta na asali.

Sarƙar ya buƌe tare da nufar wuyanta wanda yake nan zafi ƙau da zazzaɓi,ya ƌaura mata sarƙar.nan da nan sarƙar ta ƌauki wani sheƙi da walwali.

Dawo da kallonsa yayi kan baffa wanda yake kallon duk abinda ke faruwa,zuciyarsa tana masa wani irin ƙuna da ciwo.

Saida ya ɗauki kusan minti biyar kafin yace "Abba nayi maka alƙawarin zan taimaka wajen neman asalin iyayen yarinyarka,zamuiyi amfani da wannan  sarƙa in Sha Allah everything is gonna be ok"ya faɗa cikin muryar sa mai daɗin amo .

Hannunsa baffa ya kama cikin farin ciki yace "na gode Allah yayi maka albarka,ka kulamin da fattu karka bari ta cutu "

Jinjina kai yayi shima yana mai riƙe hannun baffan, akaro na farko ya ɗanyi murmushi.masha Allah masu karatu bakuga yadda yayi wani sihirtaccen kyau ba,Dan murmushin ba ƙaramin kyau ya ƙara masaba.

Kwanciya fattu tayi akan sallaya ta juya bayanta tana ta kuka da rawar zazzaɓi,shikenan yanzu haka zata bi wannan bawan Allah da batasan koshi waye ba,meyasa iyayenta suka yarda ita?me tayi musu haka da zafi?dama baffa ya fasa ƙidurinsa na cewar saitabi wannan bawan Allah mana.

Baffa ne ya miƙe tsaye da sauri tare da leƙawa ƙofar ɗakinsa, dan tabbas yaga gilmawar mutum,aikuwa yana leƙawa ya hango zanin gwogwgo hansai tana shigewa ɗakinta. Ya Salam kenan taji duk abinda suke tattaunawa ?lallai dole su bar gidan nan kafin gari ya gama wayewa.dan yanzu kam asuba ta kawo kai,

Da sauri ya koma ɗakin yace "Adeeb akwai matsala,yanzu yanzu zaku tashi ku dau hanya,dan kuwa hansai taji duk abinda muke tattauna,kuma na tabbata ko bari bazata yi gari ya gama wayewaba zata je ta sanar da mai gari"

Baffa ya faɗa cikin tashin hankali da damuwa.

Shikuwa Adeeb ko ajikinsa ƙara gyara zama yayi ,dan bazai iya kwanciya anan gurin ba ,kafin ya kalli baffa ya ɗan taɓe baki yace "and so what idan ta faɗa masa"?

Ya faɗa cikin ko in kula.

"Bazaka  gane zalumcin lamiɗo ba Adeeb zai iya sawa kashe fattu ,dan Allah ku tashi muje In fitar daku hanya ku tafi, ka taimaka min ka ceci rayuwar yata"baffa ya faɗa cikin kuka yana durƙusa akan gwuiwoyinsa.

Da sauri Adeeb ya tashi ya kama baffa ya miƙar dashi yace "is ok Abba zamu tafi yanzu.ya faɗa yana mai kamo hannun fattu ya miƙar da ita tsaye.

Ita kuwa fattu yadda yake jin zuciyarta bayani ace mai gari yasa a kasheta Bama,koba komai zata huta da ƙuncin zuciya da damuwa.tana mikewa tayi baya zata faɗi,dan gaba ɗaya ba ƙarfi ajikinta.da sauri Adeeb ya tallafi ga zuwa jikinsa,kallon fuskarta yayi wacce ta kumbura ,sai rufe idanu take tana buɗe wa,da gani tana shan jiki sosai.

"Muje bawan Allah  ,fattu daure kinji"baffa ya faɗa cikin ruɗu ,ba abinda yake ɓukata irin yaga sun bar rugar nan.

Ganin fattu zata ɓata musu lokacine yasa  Adeeb ya ɗagata sama tsak!kamar yar tsana ya saba akafaɗarsa yacewa baffa" muke Abba"

Wata leda Baffa ya dauko,tare da rigar nan ta fattu ya cusa ciki,sannan yayi waje suka rufa masa baya.....

Masu karatu me zakuce game da rabuwar baffa da fattu?

Mrs babi ce□□

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MICIJI NE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Tafiya suke cikin motar Ba tare da kowa ya ƙara cewa komai ba,ba abinda ke tashi cikin motar dai sanyi a.c da daddaɗan kamshi, gefe guda kuma ƙira'ar sudais ke tashi cikin suratul mulk.

Gaba daya zuciyoyinsu,sun sami nutsuwa,irin wacce mai sauraron Alƙur'ani ke samun tago mashi da ita.

Adeeb yana kwance cikin kujerar, idanunsa alumshe ,ahankali yake ɗan motsa bakinsa yana bin ƙira'ar,al'adar sa kenan dama shi,inda yana cikin mota ,to karatun alƙur'ani yake sauraro. Yayin da can ƙarƙashin zuciyarsa yake jin wani irin farin ciki da annashuwa,duk da baisan tsawon lokacin daya ɗauka cikin yanayi na wata halittar ba,amma yana ji ajikinsa cewa yayi kewar ahalinsa fiye da yadda yake

tunani.ba abinda yake fata da buri irin ace yaganshi kusa da abie da ammi.ko wane yanayi zasu shiga idan suka ganshi?

Tunanin da Adeeb yayi tayi kenan cikin zuciyarsa.hakan ya hana masa fahimtar halin da fattu ke ciki.wato ta takure jikinsa sosai,sai rawar sanyi takeyi, sosai sanyin motar ke damunta, ga wani irin yanayi na kewar baffanta dake taso mata, sosai ta ƙunaci Jikin Adeeb ,aƙoƙarinta na samun gurin da dataji ɗumi.

Ahankali ta ɗan zakuɗa kadan zuwa jikinsa,ta yadda har kafaɗarta na gugar tasa.kuma har zuwa wannan lokacin tana riƙe da gefen rigarsa.

Shikuwa Adeeb jin anɗan bugeshi ,yasa shi buɗe idanunsa ahankali, ɗan juyowa yayi yana kallon fattu, wacce tayi lugus ajikinsa  tana karkarwa.

"Ke matsa daga jikina"ya faɗa cikin salon maganarsa ba tare da ya motsaba.

Da sauri fattu ta ɗan matsa ,daga jikin nashi,dan ita atunaninta dama yayi barcine.

Kallonsa tayi tare da marairaicewa tace "Hamma sanyi nake ji,kodai cikin ƙanƙara muke tafiya"ta faɗa zuciyarta ɗaya,tana ɗan gwabe fuska.

Kallonta yayi tare da hararta yace "dake baki san acikin ƙanƙara muke tafiyaba? ya faɗa cikin gatse.

Zato ido fattu tayi tare da dafe ƙirji,"na shiga ukuna Ni fattu ,dan Allah Hamma kayi min rai,mu canja wata hanyar wllh mutuwa zanyi idan naci gaba da jin sanyin nan"fattu ta faɗa cikin marairaita tana rawar sanyi,gaba ɗaya ta gama tsorata,idanunsa kuwa harya fara kawo ruwa.

Bamza Adeeb yayi da ita tare da maida idonsa ya rufe,wannan gaskiya ɓaci ƙauyencima akwai shirye atattare da ita,kamar ba tare suka shiga motar ba, ko ina taga alamun ƙanƙarama bare tace akanta suke tafiya?

Fattu kuwa ganin ya maida idanunsa ya rufe sai tsoro ya ƙara makata,da sauri ta cusa kanta tsakanin hannunsa da kujera, ta kara ƙanƙame gefen rigarsa tana kuka.

"Wayyo Hamma sanyi nakeji yana shiga cikin ƙashina ,jinina daskarewa yake" fattu ta faɗa cikin kuka,tsakaninta da Allah take kukanta.

Dafe kai Adeeb yayi tare da kallon Hisham yace "switch up that a.c" ya faɗa kamar baya so.

"Ok sir" Hisham ya amsa tare da kashe a.cn yana mamaki,yau yallaɓai ne da kansa yace akashe a.c?

Fattu kuwa ahankali taji ta daina jin sanyi da take ji,dan haka share hawayenta tayi tana mai cewa aranta."anya kuwa Hamma ba so yake ya kaini gurin yan shan jini su tsotsemin jini ba? Ahankali ta dago kanta tana kallon fuskarsa ,shagala fattu tayi da kallon kyakyakywar fuskarsa ,barin ma light pink lips ɗinsa da gashin baki yayi masa ƙawayan,ga gemunsa mai kyau sai sheƙi yake,hanci kuwa kamar wanda aka ɗora masa,gaskiya Hamma akwai kyau ,inama nike da  kyansa,aikuwa danasha gayu.

"Ke meye kika ƙuramin ido haka?karki cinyeni" Adeeb ya faɗa yana mai tsare  fattu da idanunsa masu tsananin haske.

Dan duk yadda ta ƙuresa da ido yana kallonta ,dan ba duka ya rufe idon nashi ba .

Ɗan zabura fattu tayi ta matsa baya tana soso kai,dan ba ƙaramin kunya taji ba,ashe yana kallonta ta ƙuresa da ido haka? wayyo Allah Ni fattu .ta faɗa cikin ranta tana mai kwantar da kanta jikin kujera cikin kunya.

Tun daga lokacin ba wanda ya ƙarayin magana a cikinsu.

Adeeb yana cikin tunaninsa yaji fattu ta langaɓo kansa,dan dubawa yayi saiyaga ashe ma barci tayi.kafeta yayi da idanuwansa yana kallon zallar kyau irin na fattu,duk da ƙarancin shekarunta ,amma Allah yayi mata baiwar kyau,irin kyanda sai kana kallon mutum kake ƙara ganin kyan nashi .

Gyara mata kwanciyar yayi agefen kafaɗarsa ,duk da yadda yake jinsa atakure,kasancewar kusancinsu yayi yawa ,amma haka ya daure ya barta akan kafaɗar tashi taci gaba da barcinta.

Fattu na cikin barci taji  ana dan taffing kumatunta, Ahankali ta buɗe idanunta da sukayi mata nauyi saboda barci.

"Dagani malam duk cin batani da yawun barci ko" Adeeb ya faɗa yana hararar fattu

Wacce ke kif-kifta idanunta tana mai daga masa kafaɗa,kallon kafaɗar tashi tayi,amma ita bata wani ga yawu agurin ba.

Suna fita daga Motar fattu ta gansu kusa da  wani ƙaton jet ,Aida sauri ta kamo hannun Adeeb ta rike ƙam cikin nata tana mai zaro ido.

Fizge hannunsa Adeeb yayi yana hararar fattu "stop touching please" ya faɗa yanayin gaba binsa.

Da sauri fattu ta mara masa baya,tana binsa ƙafa ƙafa.tab yaushe zata tsaya kusa da wannan abu mai kama da girman duniya?haka kawai ya fado kanta ta mutu ?

Wani farin Balarabe ne ya fito daga cikin wata ƙofa,dake ɗan nesa da inda jet ɗin ke tsaye.

Da gudu naga ya taho ya ruƙunƙume Adeeb yana sunbatarsa,kuma yana hawaye.

"Habeebi ina ka shiga ?me yasameka?kasan irin tashin hankalin da muka shiga? kowa na gida yana cikin damuwa,abie yana nan akwance ba  lafiya tunda aka rasaka"Balarabe ya faɗa cikin harshen larabci.

Murmushi kawai Adeeb yayi yana mai shafa kan wannan balaraben ,sannan  yace " where is the imam?

Cikin share hawaye mutum yace "yana ciki kai kawai muke jira.

Kallon fattu Adeeb yayi yace "jirani ana karki biyoni" ya faɗa cikin hade fuska.kafin yayi gaba.

Da sauri fattu ta kamo hannunsa cikin marairaita tace "tsoro nakeji Hamma dan Allah karka gudu ka barni"ta faɗa cikin kwabe fuska.

Zare hannunsa kawai yayi baice komai ba suka shige cikin dakin da wanann balaraben ya fito. Zama fattu tayi akan wata kujera dake gefen ta,da alama kujerar sassaƙata akayi dan zama agurin,tagumi tayi rungume da yan kayanta,tunani take yanzu idan Adeeb ya gudu ya barta anan yazatayi? Gurin wa zata?dan ita dai yadda take ganin garin nan da zungura- zunguran gidajen dake cikin garin ,zaiyo wahala idan ba shan jini akeyicikin gidajen ba.shikenan ba ita ba ƙara ganin baffanta.

Daga kanta tayi ta kalli inda aka daka motar da suka zo cikinta amma watan bataga motar ba,saidai taga wasu tarin motocin can gefe guda arufe da wani abu.

Kila duk waɗanda aka kawo su cikin motocin can an shanye musu jininsu.yanzu itama haka za'a shanye nata jinin idan Hamma ya gudu?"wayyo ni fattu naga rayuwa "ta faɗa tana mai leave fuska da waige waige .

Shikuwa Adeeb koda suka shiga ƙofar nan,

Kusan minti talatin suka ɗauka cikin dakin kafin suka fito,  ,lokacin fattu hatta fara kuka, tana ganinsa taji wani sanyi cikin ranta,da hanzarin ta ta miƙa tare da nufarsa tana kuka,tana zuwa ta kama hannunsa cikin kuka take cewa"Hamma harba fara kuka ,nayi tunanin gudawa kayi ka barni, anan ado a shanye min jinina, dan Allah Hamma karka ƙara tafiya ka barni" fattu ta faɗa tana mai ɗora kanta akan damtsen hannunsa. Wani irin yanayi na tausayinsa Adeeb yaji yana ratsa zuciyarsa,Allah Sarki,yasan ahalin yanzu bata da wani gata saina Allah saikuma shi,shi kaɗai ta sani,zaiyo iyakar ƙoƙarin sa ,wajen kula da ita har su cimma burin su. hannunta kawai Adeeb ya kama ,  tare da  nufar cikin jirgin nan.

Noƙewa fattu ta farayi cikin rawar jiki tace"Hamma na tuba Dan Allah karka sani cikin wannan abun mai kama da kifi" fattu ta faɗa tana mai ƙoƙarin zare hannunta daga cikin nashi.

Tsayawa yayi tare da kallon wannan balaraben yace tareeƙ ka shiga ciki "ya faɗa cikin harshen larabci.

Jinjina kai tareeƙ yayi tare da kama ɗayan hannun Adeeb ya sunbata kafin ya shige cikin jet ɗin.

Kallonta Adeeb yayi yaga yadda gaba ɗaya ta firgice,sai ƙoƙarin zame hannunta take cikin nashi.

Ahankali ya sanya hannunsa ya kawota jikinsa,yayi mata side hug,kana yace " ki nutsu kinji,ba abinda zai miki zamu tafi gidane acikinsa" ya faɗa yana mai shafa kanta.

Jinjina kai fattu tayi tare da cewa"Ni bazan bikaba Hamma kamaida Ni gurin baffa ,bazan shiga wannan abunba tsoro nakeji,kifine da,muna shiga haɗiyemu zaiyi Hamma"ta kai ƙarshen maganarta cikin kuka.

Murmushin Adeeb yayi akaro na farko tun tasowarsu daga Kano,wai haɗiyesu zaiyi ,kifine.kai wannan yarinyar akwai ƙauyanci.

Ganin dai da gaske fattu atsorace take, sai kawai ya juyo da ita zuwa gabansa ,bai jira komai ba ya haɗar da jikinsa ya rungumeta cikin faffaɗan ƙirjinsa,ahankali yake shafa kanta zuwa kafadunta .

Shiru fattu tayi sakamakon wani irin nutsuwa mai cike da sa annashuwa dataji tana ratsa dukkan sassan jikinta,luɓ tayi cikin jikinsa ta daina wannan rawar jikin,idanunta kawai ta kumshe tana shaƙar daddaɗan kamshi da Adeeb keyi.

Kusan minti uku Adeeb ya bata ajikinsa,yayinda shima yake jinsa cikin wani irin yanayi na samun nutsuwa da peace of mine ,ji yake kamar suyi ta zama ahakan, amma tunowa da yayi da abinda ke gabansa yasashi saurin ɗagota daga jikin nashi,ƙara komawa fattu tayi ta kwantar da kanta akan ƙirjinsa,ba tare da tasan tayi hakan ba,.cibiya ya karatu kafin yace "to dagamin jiki karki karyani"ya faɗa daidai saitin kunne ta. Wani yuuuuuuu fattu taji ,jiri na  neman dibanta, lokacin da iskar bakin Adeeb ta bugi kunnenta,da sauri ta rike damtsensa tana mai runtse idanunta,saida suka sake ɗiban minti kusan biyu,kafin Adeeb ya ɗagota,wanna karon bayi musu ba,saidai kanta na ƙasa cikin jin kunya.

"Ya isheki haka ko kina don daɗi?"Adeeb ya faɗa yana kallon fuskarta.

Shiru tayi kanta a ƙasa ba tace komai ba.

Hannunta Adeeb ya kama suka fara taka matakalar. Taku ɗaya biyu kawai fattu tayi luuuuuu zata daɗi ƙasa ,da sauri cikin azama Adeeb ya ruƙota ,yana mai zato idanu waje.

Fattu kuwa ji tayi kanta yana juyawa sosai,tace "Hamma ka rikeni zan faɗi "ta faɗa tana mai kumshe idanunta.

"Ina tare dake ba abinda zai sameki"Adeeb ya faɗa ,yana mai ɗaya fattu kamar ya ɗauki jaririya ya shige cikin jet din.

Wow wato shi kansa cikin jet ɗin abin kallo e ,tsayawa fasalta yadda ya tsaru kuma bata lokacine,na barku kawai ku ƙiyasta tsaruwar jet ɗin.

Sin yanufa ya zauna tare da rungume fattu cikin jikinsa,yana shafa kanta ahankali.

Belt ya ɗaura musu kafin ya ɗanan wani ɗan guri saiga kujerar ta mike ,yadda mutum zai iya kwanciya akai.

Wata har danja ya latsa ,nan danan mai tuƙin wato tareeƙ ya tada jirgin sukayi kula sukayi sama.

Ƙara gyarawa fattu kwanciya Adeeb yayi ajikinsa yana mai kallon fuskarta dake cike da tsoro,idanunta arufe gam, da hannunta shima ta rukunkume Adeeb dasu, idanunta kuma na tsiyayar da ruwan hawaye .

Ahankali Adeeb ya sanya hannunsa yana mai share mata hawayen bakinsa ya kai daidai goshinta kamar zaiyi mata kiss saikuma yayi saurin dauke kansa .

Ajiyar zuciya Adeeb yayi yana mai kallon sararin samaniya cike da jin wani irin shauƙi cikin zuciyarsa

Manage please my people,

Banda caji wllh nefa ya sami matsala.

Mrs babi ce□□□

Share and comment fisabilillah

More comment

More typing.

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Kwanci Adeeb yayi akan gadon ,tare da duƙunƙunewa guri ɗaya ,jikinsa kuwa banda rawa ba abinda yake ,idanunsa arufe ruf!

Ba abinda yake gani cikin idanunsa face hoton surar fattu.

"Ya Salam ! Ya Allah save"Adeeb ya faɗa ahankali yana mai riƙe matarsa ɗata ke masa wani ciwo na lokaci guda.

Fattu kuwa tana jin fitarsa da sauri itama ta fito tana kuka.jikin madubi taje ta tsaya tana kallon yadda ya faɗa kan gadon tare da dunƙulewa yana rawar sanyi,cikin ranta take rayawa kodai baida lafiya ne ?ko shima zazzaɓin yake ?

Ganin idan ta tsaya zancen zuci saita shekarar agurin,gashi batayi sallaba.

Dan haka cikin tsoro da fargaba ta fara takawa zuwa jikin gadon ,tana zuwa taka ta tsaya ,tare da sanya bayan hannunta ta share hawayen daya silalo daga cikin idanunta.

Cikin sanyin murya tace "hamma zanyi sallah" ta faɗa kanta a ƙasa.

Yana jinta yayi shiru abinsa, yana ci gaba da jin yadda matarsa ke masa ciwo tana ƙullewa,ahankali yake karanta addu'oi cikin ransa ,fatansa kawai ya daina jin wannan azabar da kuma yanayin dake bibiyar ilahirin jikinsa.

Kusan minti biyar fattu na tsaye kanta aƙasa ,jifa jifa tana share hawayen dake zubowa daga idanunta.aranta kuwa cewa take "wannan hamma wllh baida kirki ,san ba bakinsu ɗaya da macijina ba,dubi yadda nayi masa magana ya wani shareni.

Shikuwa Adeeb yana kwancene yana ci gaba da ambaton sunan Allah,harya samu marar ta kafa masa ,sai wani uban gini dake karo masa agishinsa ,duk da sanyin a.c dake ɗakin hotel ɗin.

Ahankali yake sauƙe ajiyar zuciya yana ɗan kumshe idanunsa.kafin ya tashi zaune yana mai dafe da kansa.

Ganin ya tashi zaune yasa Fattu ɗan ja da baya,dan ita tsoronsa ma takeji yanzu ,dan wllh da gani masifaffene.

Kallon gefen ta yayi ba tare da ya lalle ta kai tsaye ba,sannan ya ɗan ja tsaki yana mai yamutsa fuska da turo baki,kamar wani mace ,sannan ya miƙe ya shiga bayin ,ruwan wanka ya haɗa mata cikin boket dan yasan ba iya shiga kwamin wannan zata yi ba, sannan ya ɗauki sisi da sabulu ta ajiye mata .ya ratsa makilin acikin sabon burush sannan ya ɗan leƙa cikin ɗakin .tana tsaye kamar gunki ,har lokacin share hawaye take ,kumshe ido yayi yana mai cewa, wannan ta cika kuka ,cikin ransa.

Kafin ya buɗe baki ahankali yace "zo" ya faɗa kamar baya so.badan Allah yasa Fattu mai saurin ji bace da bazata ji me yace ba.

Ahankali take takowa cikin yanayi na tsoro,dan dai tana tsoron masifarsa ne da ba abinda zai sa ta koma wannan ɗakin da ake ruwan jini.

Shiga tayi tare da tsayawa tana kallonsa.jikin sink ya matsa tare da miƙa mata burush ɗin yana mai cewa "oya wash your mouth"

Shiru fattu tayi tana kallonsa tare da kallon burush ɗin data karɓa daga hannunsa.

Kallon ta yayi shima fuska aɗaure yace "wanke baki" ya faɗa cikin ƙosawa ,yana jinjina ƙauyanci irin na fattu wai ko burush bata sani ba.

Ita kuwa fattu kallonsa tayi tare da kallon burush ɗin ,cikin ranta tace ikon Allah ,su nan da wannan abun suke wanke baki,mutuwa saidai hawaye da gishiri.ƙara kallonsa tayi suka haɗa ido,da sauri kowa ya kawar da kansa ,cikin shagwabar da fattu batasan tana da ita ba tace "hamma Ni ban iya wanke baki da wannan ba"ta faɗa tana miƙa masa burush ɗin.

Wani yarrrrr yaji ajikinsa, saboda  salon yadda tayi maganar ,saiyaga kamar da gangan take wani abun.harara ya salla mata kafin ya karɓi burush ɗin yace "open your mouth"

Gurun fattu tayi tana kallonsa  ba tare da ta buɗe bakin ba.

Runtse ido yayi cikin ciwon rai yace da ɗan ƙarfi"haaaaaa"ya faɗa yana bude dan madaidaicin bakinsa.

Buɗe nata bakin tayi kamar yadda taga yayi, wanda yake nan ɗan mitsitsi kamar gidan tsutsa ,haƙora ta farare tass dasu,ajere reras.

"Masha Allah "Adeeb ya faɗa cikin rashin sanin ya furta hakan.

Saida ya faɗa kafin ya ankare.kallon fattu yayi suka haɗa ido,harara ya watsa mata yana mai cewa"kaki cinyeni da wannan lulu eyes ɗin naki"Adeeb ya faɗa yana mai sanya burush ɗin cikin bakin fattu.

Ahankali yake wanke mata haƙoran nata masu kyau da ɗaukar hankali,yana wanke wa yana kallon fuskarta,ita kuwa ta rufe idanunta ƙam!wani irin takeji bakin nata,gashi abun da shegen zaƙi, anya kuwa ba abin sha bane ya manta yace na wanke baki ne?

Aikuwa wllh saita ɗan sha taji ya faɗinsa yake.Adeeb bai sankara ba kawai yaga ta tattara kumar bakinta ta haɗeye ƙut!

Zaro ido yayi tare da buɗe baki cike da mamaki yace "what!!" Kin shanye kunfar?oh my God" ya faɗa yana zare burush ɗin daga bakinta.

Yace "oya fito dashi"ya faɗa yana zare mata idanu.

Shagwabar fuska fattu tayi kafin tace "ai na shanye zaƙi gareshi" ta faɗa tana mai sunkuyar da kanta.

Girgiza kai kawai Adeeb yayi,baice komai ba ya kunna fanfo yace ta tara ta kuskure bakin,

Hannu ta saka ta tari ruwan sannan ta kuskure bakinta.wani fayau taji bakin nata yayi ,sosai taji yayi mata daɗi ga kamshin strowberry da bakin keyi.

Nuna mata ruwan wanka yayi yace tayi wanka ,yanzu ta fito yana jiranta.

Kai ta daga masa,tana nufar gurin da boket ɗin yake ajiye.

Harya kama handle ɗin kofar sai kuma ya juyo yace "kiyi alwala anan"ya faɗa yana nuna mata jikin sink din tare da ficewa.

Zama yayi abakin gado  bayan fito daga toilet ɗin ,haka kawai yaji yana cikin farin ciki,sai murmushin yake,abinda ba al'adar shi bace yawan fara'a.

Fattu kuwa ko minti biyar batayi ba ,sai gata ta fito sanye da Kayan ta data cire .

Kallon ta Adeeb yayi yace " ina kayan dana baki?"

Miƙa masa al'adar tayi  tana mai cewa"bazan iya sawa ba harɗe Ni zasu yi"

Kallon ledar yayi sannan ya lalle ta, karba yayi tare da budewa ya zazzage,doguwar rigar baƙa mai dan faɗi sai ɗan kwalin rigar shima baki,kuma yana da girma.wai amma sune bazata iya sawa ba '

"Take it ,ya faɗa cikin hade fuska.

Kallonsa tayi, tare da karɓar ledar,bawai dan ta ji me yace ba ,saidan taga yana miƙa  mata  ledar .

"Wuce kije kisa"ya faɗa ba alamun wasa afuskarsa.

Juyawa tayi sumi"sumi ta koma toilet ɗin ,amma bata rufe ƙofarba ,ta yadda dataji burum,zata arce.

Haka ta cire kayanta ta sanya wanna doguwar rigar ,masha Allah rigar tayi mata kyau sosai ,saita fito ras da ita.maimaiko ta lulluɓa dan kwalin ,sai kawai ta daura akanta.,sannan ta sanya kayanta wanda ta cire  cikin ledar sabon kayan.

Fitowa tayi tana tattare rigar ,dan harga Allah jinta take aharharde,tafi don tsangalallen ,zaninta.

Tana fitowa Adeeb yabi ta da kallon,aransa yana mai yaba irin Khan da tayi ,amma jibi yadda yake wani dage rigar.

"Hamma a ina zanyi sallar?ta faɗa tana kallon gefensa.

Shiru yayi yana kallon ta kafin yace "zo nan"

Cikin tsoro take takowa har zuwa kusa dashi,tana fatan kar yayi mata faɗa irin na ɗazu.

Mikewa yayi tare da zare ɗan kwalin kanta,ya warware shi tare da yi mata rolling irin yadda yaga amminsa da ƙannansa nayi.

Masha Allah ai nan danna fattu ta fito abalarabiya sak, tayi kyau sosai da sosai,kamar ba fattu yar fillo ba.

"Kije can kiyi sallah"ya faɗa yana nuna mata kan dardumar da yayi Sallah shima.

Bayan ta idar da sallar Adeeb yana kallon ta,masha Allah ba wani kuskure cikin sallar Tata,dan fattu tana da ilimin addini sosai.

Abinci ya nuna mata yace tayi sauri taci zasu tafi.bata wani ciabincin kirki ba,dan ji tayi sam abincin baiyi mata daɗi ba,tafi son tuwo ko madarar shanu.

Shima bai wani damu ba ,dan yaga bataci abinci ba sosai.tashi yayi yace mata suje .

Yayi gaba tana binsa abaya. Riƙe da rigarta, hannun dayan kuma tana riƙe da ledar kayanta.

Suna fita daga hotel ɗin kai tsaye gurin masu saida waya ya nufa , wata ƙaramar waya ya siya da layi,ba tare da ya tambayi kuɗi su ba ,naga ya bada duka kuɗin nan dake cikin leda,dan dama suna hannunsa,wanan rigar kawai ya cire daga ledar,sosai naga mai saida wayoyin yana ta murna da godiya har kasa ya durƙusa yana godiya.

Haɗa wayar Adeeb yayi tare da sanya layin ,kati ya karɓa gurin mai saida wayar ,aikuwa da sauri ya ɗauki mata na dari biyar ya mika masa.

Wata number naga ya daddana cikin wayar,bayan ya gama sanya katin acikin wayar.

Magana ya farayi cikin harshen larabci,bayan anɗaga wayar daya kira.ni dai ba dan me yake cewa a,saidai naga kamar yana kwatancen inda yake ne.

Bayan ya kammala wayar ne yana ƙoƙarin sanyata cikin Aljihu,kawai yaji mutum yana ƙwaƙwumarsa kamar za'a shige cikin jikinsa.

Da sauri ya kalli gefen hagunsa ,inda  tanan yake jin alamun mutum ɗin,aikuwa fattu ya gani tsaye ta kama gefen rigarsa,jikinsa har rawa yake tana ɓoye fuskarta ajikinsa.

Hannunsa ya sanya tare da kamo hannunta ya dawo da ita zuwa gabansa.

Saida ya ɗan harareta kafin yace "menene kuma"ya faɗa cikin salon maganarsa kamar baya so.

Ahankali fattu ta nuna masa  wasu matasa kusan su goma da suka tsaya suna kallonsu.tace "waɗan can ne ke kallona "kallon gurin matasan yayi,yaga yadda suka kafesu da idanu,kuma ba akowa suke kallo ba face fattu,nan da nan yaji wani irin ɓaci rai da ciwon zuciya ya turnuƙeshi,

Cikin hanzari ya maida fattu bayansa yana mai hararar matasan nan,zuciyarsa kamar zata fito dan tsabar ɓaci rai.gaba ɗaya yaji gurin yayi masa baƙi kirin,Bama yason tsayuwa agurin, dan haka cikin zafin nama ya fizgi hannun fattu suka fara tafiya daga gurin,mai saida wayoyin yana ta masa godiya da Allah ya kiyaye amma ko sauraransa baiyi ba.

Can wani guri ya koma tare da tsayawa ,shi kaɗai dai huci yake,dan me zasu tsaya suna kallon ta ,shifa saiyaga kamar ma ɗaya ƙirjin fattu yake kallo. Cikin sauri ya juyo tare da kallon fattu tun daga sama har ƙasa.ba wani abu daya bayyana ajikinta ,wanda za'ace shigarta batayi daidai ba ,saidai fa idan ka ƙura mata ido zaka iya gane ba bra ajikinta.

Lallai ke nan bata sanya bra ajikinta?

"Ke meyasa baki saka wannan abun ba kafin kisa rigarnan"

Ya faɗa cikin fushi da bakin rai.

Kallonsa fattu tayi cikin rashin fahimta dan bata gane me yake nufi ba,kawai saita sunkuyar da kanta ƙasa tace "kayi haƙuri Ni banga komaiba inda rigar ba"ta faɗa Muryar har ta fara rawa,alamun zata yi kuka.

Harya buɗe baki zaiyi magana yaji wayarsa  na ringing,tsaki yayi kafin ya ɗaya call ɗin.

Shiru yayi na tsawon lokaci kafin yace "Yes  i sawa them"ya kashe wayar .

Dan fitowa yayi daga gurin dasuke tsayen naga ya ɗaga hannunsa .

Wata tsuleliyar mota naga ta taho gareshi,suuuuuu,baka ko jin ƙagarta,kallon ɗaya zakayiwa motar kasan anɓadda Naira agurin,farking motar tayi agabansa,kafin mai riƙon ya fito cikin sauri yana mai faɗin "your highly well come back sir"mutumin ya faɗa yana mai durƙusawa har kasa gaban Abeed.

Kafadar mutumin Abeed ya dafa tare da miƙar dashi tsaye,sannan ya ɗan rungumeshi yana mai bubbuga bayansa.

"Let go hisham"Abeed ya faɗa yana mai nufar motar ,da sauri wanda aka kira da Hisham  ya budewa Adeeb motar ,shikuma ya shiga gidan baya ya zauna.

"Hamma " fattu ta faɗa cikin sauri tana mai ƙarasowa jikin motar ganin ya shige cikin motar yana ƙoƙarin barcinta.

Adeeb kuwa da gangan yayi banza da ita ,intaga dama ta ƙara so ta shiga motar,dan haushinta ya keji sosai ,ai da gangan ta wani tsaya har wasu ba zaune ke ƙare mata kallo.

Hisham ne ya kalli fattu yace "yan mata lafiya kuwa?

Shagwabe fuska fattu tayi tana kallon Adeeb tace "gurin hamma zani gashinan acikin nan"ta faɗa tana nuna mai Adeeb ,wanda ya wani ɗauke kai .

"Yallaɓai this ...

"Let her in"Adeeb ya faɗa cikin katse Hisham .

"Yes sir"Hisham ya faɗa cikin bin umarni,ya kauce daga bakin ƙofar motar yana mai cewa fattu"shiga"

Da saurinta kuwa  ta shige kusa da Adeeb ta zauna ,harda sauƙe ajiyar zuciya.

Ahankali ta sanya hannunta tare da riƙe gefen rigar Adeeb ta kalle- kallen motar.banda faɗuwa ba abinda gabanta keyi.

"Yallaɓai where are we going now"

Hisham ya tambaya cikin girmamawa.

"Abuja" Adeeb ya faɗa tare da kwantar da kansa jikin kujera ,ac na ratsa shi ta ko ina.

Nan Hisham ya kunna mota suka cilla sai Abuja.

Ko daga Abuja kuma sai ina ?

Ga dai Hajiya fattu cikin mota mai a.c ana baza idanu.

Muje zuwa ku biyoni sannu kan hankali.

Anty mammy ce

Mrs babi□□□

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy

Elegant online writers□□

Free book

_____Tafiya suke cikin sararin samani,yayin da Fattu ke ruƙunkume da Adeeb jikinta naci gaba da rawa,kuma har lokacin idanunta akulle suke.

Ɗan juyowa Adeeb yayi yana mai kallonta ,shi mamakin tsoro irin na fattu yake,sam baiga abun tsoro ahawa jirgi ba,dubi yadda ta wani uzzurawa kanta,ko idanu ta kasa buɗe wa.

Ni kuwa nace malam Adeeb fattu fa ko ganin jirgi baya taɓa yi ba ,bare ta hau,ai dole ta shiga cikin cakwakiya,akaranta na farko.

Kallon fuskarta Adeeb keyi kamar bai taɓa ganin taba,haka kawai yake jin wani bakon al'amari tare dashi, jin yadda fattu ta ruƙunƙumeshin nan ,sai yake jin hakan yayi masa daɗi sosai,saidai yana tsoron abinda zuciya da gangar jikin sa ke ɓuƙatar aikatawa,idanu ya kirawo lips ɗinta ƙuri,cikin wani irin mugun son ya sunbacesu,gabansa sai bugawa yake,har wani lasar lips ɗin da yake ,yana hasko yadda zai sunbaci lips ɗin fattun.iyakar ƙokari Adeeb yayi dan hana kansa aikata abinda zuciyarsa ke tsananin muradi, amma ya kasa,dan jinsa yayi gaba ɗaya yanayinsa ya sauya ,ahankali cikin mugun son isar da saƙon zuciyarsa  ya nufi ɗan bakin  na fattu, har wani rawa bakinsa keyi,

Yana gan da kai bakin nasa cikin nata ne ,fattu tayi waral!da idanunta,ma'ana ta buɗe idanun nata ba zato ba tsammani,karaf kuwa idanunsa ya sarƙe dana juna,da sauri Adeeb ya runtse idanunsa tare da kawar da kansa can gefe,saidai bai daga daga rankwafowar da yayi ba,jikinsa gaba daya yana manne dana fattun,wani irin abu yakeji mai kama da mayen karfe ,yana fusgarsa zuwa ga aiwatar da burinsa, kiss fa only kiss Adeeb you can do it ,dan ka samawa kanka  mafita daga yanayin da kake ciki.

Zuciyar Adeeb ke bashi wannan shawarar,ahankali ya ƙara bude idanunsa wanda suka fara sauya yanayi daga fari tas zuwa wani irin sirkin jaaa da wani ratsin pink.

Kallon fattu yayi wacce itama shi take kallo tana wani rarraba idanu,Ita dai batasan me yake nufi ba,taga ya kwanto jikinta ne ,ƙila ahaka ake tafiyar ,amma kuma me yasami idanunsa haka,idan bata mantaba ,yanayin da idanunsa ya shiga yanzu,kusan kalar da idanunsa yake ne lokacin da yake macijinsa, kodai macijin zai ƙara zama ne?na shiga uku na idan yazama maciji yanzu yazanyi?ina zamuje cikin wannan halittar mai kama da kifi?nan da nan tsoro ya kama fattu ƙara rikoshi tayi sosai cikin muryar tsoro tace "Hamma menene?dan Allah karka ƙara zama maciji

kai kadai nake dashi,idan ka koma maciji ya zanyi,waye zai fitar dani daga wannan cikin kifin da muka shi?ta faɗa cikin salon shagwaɓa taba mai zubda hawaye.

Da ƙarfin gaske Adeeb ya runtse idanunsa, yana mai furta "ya Salam wannan yarinyar zata kashe ni fa"dan yanayin yadda tayi maganar ba ƙaramin tasiri yayi akan Adeeb ba,hakan saiya ƙara masa jin wani iri ajikinsa,gani yake kamar da gangan tayi hakan ma.

Kansa banda juyawa ba abinda yake,yayinda zuciyarsa ke ta bashi shawarar kawai ya sunbaci fattun .cikin rashin sanin abinyi Adeeb ya ɗora bakinsa kan na fattu,ba tare da ɓata lokaciba ya fara kissing ɗinta kamar ya sami lolli pop,zaro idanu fattu tayi cike da tsantsar tsoro da mamaki,meye hakan kuma Hamma keyi?me yasa yake shan bakina?kodai shima yana cinye mutane ne?shikenan Ni fattu naga ta kaina ,wayyo Allah na,daga cikin fiki saikuma shanye baki?nan da nan fattu ta fara rawar jiki fiye da da,cikin zuciyarta tana take ta faman haure haure da ƙoƙarin ture Adeeb,amma kuma azahiri ta kasa koda ɗaga dan yatsanta ne bare tayi yunƙurin kwacewa.

Shikuwa Adeeb ɗora bakinsa kan bakin fattu keda wuya ,gaba ɗaya haddarsa ta zube,tuni ya nemi inda kansa yake ya rasa,kissing ɗin bakin fattu kawai yake kamar Mayunwacin zaki.

Kusan minti shida zuwa bakwai Adeeb na abu ɗaya,cikin kwancewar kai da rasa tunani,fattu kuwa tun tana jin abinda yakeyi kamar waiwayi yake mata har ta fara jin wani azababben zafi da raɗaɗi ,dan ji tayi kamar zai tsinke mata lips,tuni ta fara kuka tana ɗan bubbuga damtsen hannunsa.

Hankali da tunanin Adeeb ne suka dawo jikinsa lokaci ɗaya,kuma ya fahimci abinda yake aikatawa da Fattun, cikin wata irin azama da hanzari ya  dago kansa tare da cire bakinsa daga cikin na fattun.

Da sauri ya zareta daga jikinsa yana mai mikewa cikin hanzari ya nufi wani daki,yana layi kamar ɗan maye.

Yana shiga ɗakin ya kulle ƙofar tare da zamewa ajikin ƙofar ya zauna dabas. Dafe kansa yayi yana mai runtse idanunsa."meye hakan ?me na aikata kenan?wane irin kallo yarinyar zata rinƙa min yanzu?ohh my God ,why Adeeb !why am I losing my

control over her?"Adeeb ya faɗa Afili yana  mai tsakumo sukar kansa wacce ke kwance lub-lub.

"Me ka aikata ba dai-dai ba Adeeb bakayi laifin komai ba ,kuma ba abin ƙi kayi ba just colm down"wani sashe na zuciyar Adeeb ne ke sanar dashi wannan maganar cikin yanayin rarrashi.

Ahankali ya sauƙe wata ƙaƙkarfar ajiyar zuciya yana mai rarrafawa ya kwanta akan wani ƙayataccen gado dake cikin ɗakin.kwanciyar rigingine yayi tare da kumshe idanunsa.ba abinda ke masa gizo sai moment ɗin daya kasance cikinsa yanzu nan.tabbas bai taɓa jinsa cikin wata ni'imtacciyar rayuwa makaman iyar wadda ya fito daga cikinta ba yanzu,wannan yarinyar da yake mata kallon baby he can't imagine ace wai just kissing ɗin ta zai sanya shi cikin wannan yanayin ba.

Kusan minti goma Adeeb ya ɗauka a kwance yana ta saƙa da warwara,gaba ɗaya ya kawowa kansa matsala,yana zaman zamansa ,yanzu inbanda amsawa ba abinda mararsa keyi.

Tsaki yayi akaro na barkatai kafin ya mike cikin ƙarfin hali ya buɗe wata ƙofa ya shiga, wanka yayi ya tsarkake jikinsa kafin ya fito sanye da wata jallabiya, danaga ya buɗe wani guri ya zarota.

Zama yayi abakin gadon daya kwanta dazu,yana tunani,me Yakamata yayi yanzu? Gara kawai ya fuske ya fita,idan ba haka ba yarinyar zata rinka masa wani iri. Kallo ne.dan haka mikewa yayi tare da ɗaure fuskarsa sosai kafin ya fito  daga ɗakin.

Fattu kuwa lokacin da Adeeb ya zareta daga jikinsa ,zama tayi atsorace kan kujerar jirgin tare da ƙanƙame jikinta,wani irin abu yakeji ajikin nata wanda bata san menene ba,gefe guda kuma lips ɗin ta dataji yana mata zugi,hannu ta kai tare da taɓa lips ɗin ta ,aikuwa jinsa tayi yayi tauri gurin,alamun ya kumbura kenan.

Hannu ta sanya tare da share hawaye ta ,sannan ta kira kanta akan cinyarta tana kuka. Ita sam batasan meye hakan da Hamma yayi mata ke nufi ba,kuma gaba ɗaya jikinta yayi wani irin ,sam bata jin ƙarfi ajikinta,gashi har lokaci ji take kamar bakin Hamma nata yana cikin nata bakin.tana cikin wannan halin ne taji buɗe kofarsa .

Firgigit tayi tare da zabura tana kallon inda taji ƙarar.haɗa ido sukayi da Hamma nata kallonsa take ƙuri ,ganin har kaya ma ya canja ,ko a ina ya sami kayan oho"

Shikuwa Adeeb ganin sun haɗa idanu ya wani galla mata harara yana nufar kujerar dake dayan bangaren.

Binsa da kallo fattu tayi tana mai son zuwa inda yake , amma tana tsoron yadda taga ya haɗe fuska.

Ɗan juyowa Adeeb yayi jin cewar idanun fattu na kansa.

Harara ya ƙara zabga mata cikin basarwa yace " karki cinyeni da ido fa,bayan kin gama cinyemin baki"ya faɗa yana saurin kawar da kansa,dan shi kansa saida yaji kunyar abinda ya faɗa.tunda yasan shine marar gaskiya .

Fattu kuwa shiru tayi tana tunani,yaushe ta cinye masa bakin?kodai hankalin mutum yana gushewane idan yana cikin wannan abun,har yayi abu bai sani ba.dago kai tayi tana mai kallon Adeeb kafin cikin muryar mamaki tace "Hamma to meyasa na cinye maka bakin?kuma amma ai naga ga bakinka anan ajikinka, saidai ma ni nawa bakin dake min zafi " fattu ta faɗa cike da mamaki.

Dariya ce taso kama Adeeb amma ya manne sannan ya kalleta yace" inaga kina da aljanu ko?haka kawai ki ka kama shamin baki kamar kin Sami sweet , shine zakice min  bakinki na miki ciwo?

"Na shiga ukuna Ni fattu Wllh Hamma bansan nayi ba ,nima kawai ganinki nayi kana shamin bakina kagani nan gurin ma ya kumbura ciwo yakemin"fattu ta faɗa tana ɗan turo kanta tare da nuna masa lips ɗinta na ƙasa wanda ya tasa.

Kallon lips ɗin Adeeb yayi cike da  jinjinawa wauta irinta fattu,sam bata da wayo ko kaɗan,kafin yace "maganinki ai garin don banzarki kika kuwa kanki ciwo ,Ni ba ruwana, kuma saikin faɗamin inda kika koyi wannan abunda kikayimin"Adeeb ya faɗa yana hararar fattu.

Allah Sarki fattu kuwa tuni idanunta sun kawo ruwa,marairaicewa tayi tana mai juya kai,"Ayya Hamma  nisa ba mayya ba ina zanyi wannan aikin mayyun,wllh bansan nayi maka ba dan Allah kayi haƙuri,nima bansan menene hakan yake nufi ba,amma idan kaji haushi ka rama kawai"fattu ta faɗa tana mai shashsheƙar kuka tare da

goge wahaye,tsakani da Allah ita ina tasan ma tayi masa wannan abun,ita ba mayyaba ba komai ba ina ita ina shan bakin wani,ai ƙazantane ma wannan.

Lallai ma yarinyar nan wato shine maye kenan ?hmmmm zakiyi bayanin maye.Adeeb ya faɗa cikin ransa yana mai jingina kansa da jikin kujera,dan sosai yaji kansa na ciwo wanan doguwar maganar da yayi.

Bai ƙara cewa komai ba sai kumshe idanunsa da yayi ya jingina jikin kujerar,ba abinda yake gani sai lips ɗinsa cikin bakin fattu,ahankali yake sakin murmushi, ta gefen bakinsa,haƙiƙa al'amarin yayi masa daɗi sosai .

Fattu kuwa ganin ya lunshe idanunsa yasa ta ɗan juya ta kalli window.

Kan bala'i me zata fani,?gani tayi kamar ta saka hannunta ta kamo gajimare ,kuma saitaga kamar asama suke.

Ɗan Dada leƙa kanta tayi sosai,yadda zata hango da gaske a sama suke ko a ƙasa,aikuwa wllh asaman suke,hana wani wawan ihu da fattu ta kurma tare da buga tsalle ta fito daga kan kujerar nan tayi kan Adeeb,ba  Adeeb  kadai ba ,hatta tareeƙ saida ya jiyo ihun fattu.

Arazane Adeeb daya lula duniyar sa ta nishaɗi ya buɗe ido tare da mikewa tsaye cikin tsoro,kawai saijin fattu yayi ta fado kansa tana ihu"wayyo Allah na Ni fattu na shiga ukuna ,Hamma ka taimakeni,wllh duniyar sama suke tafiya ,dama saida nace bazan shiga cikin wannan  kifin ba  amma saboda mugunta ka shigo dani gashinan sai sama akeyi damu, wayyo Allah Hamma ka fitar dani daga nan wayyo baffa an,e....a.yyy.y..oooo ga....ji...immarr,sai kawai ta tafi luuuu tayi baya zata faɗi.alamun ta suma.

Da sauri Adeeb ya dariya zuwa jikinsa,kumatunta yake ɗan bugawa yana faɗin"hey! hey!! wake up  HULWA wake up please,Adeeb ya faɗa cikin mugun damuwa ,komawa yayi ya zauna tare da riƙe ta ahannunsa, dan bubbuga kumatunta yake yana kiran HULWA !HULWA,amma ina HULWA kam tayi kisan zango.

Gefensa ya danna wata yar jar danja ,saiga wata ƙaramar ƙora ta buɗe ,ruwane da lemuka kala kala aciki da alamu dai fridge me,robar ruwan ya ɗauko tare da

budewa,Ahankali yake tattara mata ruwan yana shafawa akan fuskarta amma ko motsi batayi ba.

Hankalinsa yayi mugun tashi,sosai hannunsa ya kai saitin zuciyarta ya taɓa,da sauri kuma ya zare hannun nashi,sakamakon karo da yaci da tudun ƙirjin fattu.

Ɗagota yayi tare da ɗora bakinsa kan nata ,sannan ya toshe hancinta,ya fara hura mata iska ,amma nan ma shiru,bayi motsiba,

Cikin mugun tashin hankali Adeeb ya ƙanƙame fattu ajikinsa yana faɗin "AM sorry HULWA Please wake up  " ya faɗa yana mai kara ƙankameta ajikinsa.nan da nan idanunsa suka fara rikiɗewa zuwa kaloli daban daban ,wani irin huci yake yana zazzage idanu jikinsa ya kama bari.idan kaga Adeeb a wanna lokacin tabbas zaka shiga cikin kuɗu da tsantsar tsoro ,dan gaba ɗaya kamaninsa sun sauya. Shiba mutum ba Shiba aljan ba.

Cikin wanan halin suka sami isowa Misra,kai tsaye wani guest haose ɗin Adeeb na sirri Tareeƙ ya nufa ,suna sauka kuwa ,Adeeb ya kinkimo fattu da gudu yake sauka akan jirgin,kai tsaye yana zuwa jikin ƙofar ya fara daddanna wasu nonbobi jikin wata yar na'ura,cikin second kofar ta fara budewa tana faɗin well come back prince Adeeb Muhammad Ashraf , long time no see" kota kanta baibiba yayi cikin gidan da gudu,kai tsaye wani daki ya shiga ,yana zuwa bai jira wata wata ba daddanna wani guri tare da shigewa cikin wani ɗan banzan haɗaɗden  jacuzy  mai matuƙar girma da kyau,ruwane ya fara zubowa daga samansu, mai sanyi sosai,wanda idan haka kawai aka zubawa mutum ruwan  nan tabbas sai yayi jinya.

Bubbuga kumatun fattu yaci gaba dayi yana kiran sunanta"HULWA ! HULWA!! HULWA!!! Har sau uku,Ahankali fattu ta fara bude idanunta tana lumshewa, kafin ta buɗe su duka, da sauri kuma ta ƙankame Adeeb tana mai cewa"dan Allah Hamma kafitar dani dana cikin kifin na wllh tsoro nakeji,Hamma, fattu ta faɗa tana mai rawar jiki.

Janyota Adeeb yayi zuwa jikinsa yana mai sakin wata kakkarfar ajiyar zuciya,"AM sorry HULWA ba abinda zai sameki ina tare da ke ,Please karki ƙara suma irin haka,saura kaɗan zuciyata ta buga" ya faɗa cikin rashin sanin abinda yake faɗi.

" Hamma mufita dan Allah" fattu ta sake faɗa.

Ahankali Adeeb ya riƙe kumatun fattu yana kallonta kafin yace "ki nutsu HULWA ba acikin jirgin muke ba yanzu,mun fita kalli kigani we are in toilet now ,bazan taɓa barin wani abu ya samekiba ,domin kuɗin mallakina ce kuma amanata, sannan ma....saikuma yayi shiru ,tare da cire hannunsa daga kan fuskar ta,fitowa yayi daga cikin ruwan ,sannan ya kamo hannunta ya fito da ita ,sai rawar sanyi yake,wani ɗaki ya kaita tare da zaunar da ita akan wani makeken gado,a baidamu da yadda jikinta ke jiƙe ba,wani ƙaton bargo ya dauko ya lulluɓa mata,sannan ya nufi jikin wani bango,nidai naga ya danna wani guri,kawai naga bango Ya dare,kaya sun bayyana.ehe mana bango Ya dare zance,tunda idan ka kalli gurin bazaka taba tsammanin akwai wata ƙofa dazata bude ajikinsa ba.

Wasu kaya naga ya dauko masu kama dana sanyi riga da wando sannan. Ya dawo kusa da fattu da ke binsa da kallo yace "kisa wannan kayan ,kinji,zanje in shirya nima yanzu zan dawo " ya faɗa yana mika mata kayan.

Karba tayi cikin rawar hannu tana mai binsa da  kallo harya fice daga ɗakin.

Bin dakin fattu tayi da kallo,ikon Allah wai nan ɗin ɗakin mutum ne ,saikace wanda aka tattaro duk kayan jin daɗin duniya aka ajiye aciki.

Ahankali ta mike ta cire kayan jikinta sannan ta sanya riga da wando da Adeeb ya bata,kayan sunyi mata kyau sosai,saidai wando yayi mata tsayi rigar ma haka,kasancewar Adeeb dogone sosai,hakan yasa rigar ta sauƙo ta rufe mata manyan mazaunanta.sanna kuma rigar tana da hula,hmmmmm nan da nan fattu ta koma wata irin yanar balarabiyar nan tayi mugun kyau cikin kayan .

Kayan data cire ɗin ta dauka tare da rikews ahannunta tana tsaye ,tana waige waige kallo ɗaya zaka mata kasan afirgice take.

Bude ɗakin Adeeb yayi bayan yayi noking yaji shiru,

"Masha Allah " shine abinda Adeeb ya iya faɗi lokacin da yayi arba da fattu cikin kayan nan.

Shima yana sanye da wata farar jallabiya ajikinsa da hirami akansa.yayi kyau sosai cikin shigar tasu ta larabawa.

Cikin ɗakin ya nufa yana mai jure fattu da idanu,ita kuwa kanta na ƙasa,riƙe da jiƙaƙkun kayanta.

Cikin wata irin murya mai kama da mutum na jin barci Adeeb yace "Hulwa"

Ahankali fattu ta daga kanta tana kallon bayan Adeeb ɗin dan gani ta ina hulwar zata fito.....

Muje zuwa masu karatu,

Mrs babi ce□□□

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

_____Cikin wani irin salo da murya mai maka da yana jin barci,Adeeb yace "Hulwa"

Ahankali fattu ta dago kanta tana mai kallon bayan Adeeb ɗan ganin ta ina hulwar zata fito.

Rarraba idanu take ,amma bataga kowa ba,ikon Allah ko ina hulwar take ?bisani Banga kowa abayansa ba ,kuma ba kowa cikin ɗakin nan, fattu ta faɗa tana mai waige bayanta ,dan ita dai bataga hulwa anan ba.

Duk abinda take Adeeb na kallonta,kuma ya gane me take nufi,wato suna daya faɗa shine bata ganeba,take neman mai sunan.

Juyowa fattu tayi ta kalli Adeeb ɗin cikin rashin fahimta tace "Hamma Ina hulwar take ?naga ba kowa cikin ɗakin nan ?

Kallonta yayi tare da ɗan zafi ido yace "yanzu ke bakuga hulwar tawa ba anan?" Ya faɗa yana mata kallon tuhuma.

Waigawa fattu ta sakeyi bayanta,amma wllh ita kam bataga kowa ba,juyowa tayi tace "alƙur'ani banga kowa ba" ta faɗa tana ɗan buɗe hannayenta dan tabbatar masa da cewar ba kowa aɗakin.

Yaɓe baki yayi yace "matata ce hulwa kuma gata nan akusa dani idan ke bakya ganinta toni ina ganin abata,ya faɗa yana ɗan kallon kusa da gadon da fattu ke tsaye.

Ai fattu najin haka wani irin tsoro ya kamata,da gudu ta watsar da kayan hannunta ta taho gareshi ,tana zuwa ta biye abayansa tana tsuma, ahankali take masa faɗa cikin kunnensa,"aradu Hamma aljanna kake gani ba matar ka ba,dan ba kowa acikin ɗakin nan,Ni dama tun dazu nakewa dakin kallon na aljanu,dan wannan ɗakin baiyi kama dana mutane ba ,kyanshi yayi yawa aradun Allah" fattu ta ƙare magannarta cikin kunne Adeeb da sunan tana masa raɗa dan kar Hulwa tajisu.

Tunda ta fara masa magana akunne ya wani lumshe idanunsa,har cikin ƙwaƙwalwar sa yake jin sautin maganarta, yayi da yake jin tana zaga dukkan ilahirin jikinsa, wani yuuuuum yakeji ajikinsa har kamar zai faɗi.ahankali ya buɗe idanunsa,jin ta kai aya akan maganar tata. Wacce shidai yaji farkon,amma sam bai fahimci me take fadi ba daga ƙarshen.

Yana shirin yin magana ne yajiyo ƙarar na'urar sanarda mutum yayi bako tana faɗin tareek na jikansa afalo.

Dan haka ya fasa yin maganar ,kawai saiya juyo yana kallon fattun da tunanin idanunsa,ahankali ya buɗe baki da gyara yace "wait for me here I will be back" ya faɗa yana ƙoƙarin buɗe kofar,ai carab fattu ta kama hannunsa ta riƙe cikin nata gam!tana kallonsa.

Kallonta yayi shima da nuna alamun menene?

Turo baki tayi tace " Ni ma zan bila Hamma,dan naji ka kira sunan wasu mutanen da yawa,bayan waccan hulwar Ni wllh tsoro nake ji" fattu ta faɗa tana mai kallon fuskarsa.

Hannunsa data rike cikin nashi,yabi da kallon,kafin ya ɗago yana kallonta,waima shi yaushe ya kira sunan wasu mutane kuma?ahankali ya sanya hannu ya zare nata hannun daga nashi kafin yace"bazaki bini ba, kuma Ni nace ne ki Kijirani kawai"ya faɗa yana hararta tare da bude ƙofar,yana sanya ƙafarsa waje fattu ma ta fito jikinta sai rawa yake,juyowa yayi yana kallonta fuska ba walwala yace " koma"

Marairaicewa fattu tayi kafin tace " wllh tsoro nakeji,dan Allah kaje dani,wannan hulwar fa tana ciki" harara ya Banka mata kafin yace "get in I said ,hulwar ta cinyeki" ya faɗa yana turata ciki dakin yana ƙofar ya kulle.

Hauka yake yaje da ita gurin tareek cikin wannan shigar?ai wllh idan tareek ya ganta ahana,inaga saina kusan mutuwa dan baƙin ciki.cewar Adeeb kenan yana nufar madaidaicin falon daya gaji da hadewa,zama yayi yana kallon tareek ɗin cikin yanayinsa ya haɗe fuska.

"Yallaɓai me yake faruwa ne ?naga ka shigo cikin tashin hankali?"tareek ya faɗa cikin harshen larabci yana kallon Adeeb ɗin.

Ajiyar zuciya Adeeb yayi kafin ya jingina kansa jikin kujera ,kusan minti biyu kafin ya buɗe baki dagyar yace " ta tsoratane ,shine ta suma" shima cikin harshen larabci yayi maganar.

"Ya Salam, yallaɓai koka sanar da ita wanann maganar ne?"

"No ban faɗa mata ba" cewar Adeeb .

Shiru suka ɗanyi na wani lokaci, kafin tareek yace "yallaɓai abie baisan da dawowarsa,bansanar da kowa ba kamar yadda ka buƙata"

Ɗagowa Adeeb yayi daga kwanciyar da yayi jikin kujera,kafin yace " Yes,bana son ya sani yanzu,sai dare yayi zamuje gurinsa, ka shirya komai da komai,yanzu zanje na rage suman nan ne" Adeeb ya faɗa yana mai shafa dogon lallausan gashin kansa zuwa gefen fuskarsa da gemunsa.

"Ok me kake ɓukata yanzu yallaɓai " tareek ya faɗa cikin ladabi.

"Kaje ka kawo mata kayan buƙata duka, sannan ka tahomin da wayoyi ayi duk abinda ya kamata" yana faɗin haka bai jira me Tareek zaiceba ya miƙe tare da nufar wani ɗakin da ban.

Fattu kuwa Adeeb yana kulle ƙofar taji wani mugun tsoro da fargaba, wayyo Allah,yanzu ya zanyi idan hulwar nan mai shan jini ce ? Kuma gashi bana ganinta ?

Zama tayi agurin tare da ƙanƙame jikinta tana kuka sosai harda shashsheka,Allah Sarki baffanta ,ko wane hali yake ciki yanzu?ko wane hukunci mai gari ya ɗauka akansa? Allah dai ya kare mata baffanta Aduk yanayin daya tsinci kansa.

Tana nan zaune sai waige waige take ,ta gaji sosai ga yunwa ,ga barci,gashi tana sonyin salla dan rabonta da abinci tun wanann jakwalkwalon da Hamma ya bata

awanann gidan.tana zaune shiru kawai taga wasu labulaye masu  suna saukowa ahankali daga kowane bango na ɗakin.wata zabura da tayi cikin tsoro ta kwallah ihu tana mai komawa tsakiyar dakin ,banda rawa ba abinda jikinta keyi"wayyo Allah ma hulwa dan Allah kiyi haƙuri,karki cinyeni ,wllh ba abinda nayi miki,Hamma ne ya kawoni gidanki"abinda fattu ke fadi kenan tana rawar jiki da karkarwa,tana juye juye atsakiyar dakin,ta kalli wannan bangon ta kalli wancan..

Sukuwa labulaye ,sai sauka suke kasa,kuma basu tsayaba ,saida suka dire har aƙasa.

Sai kuma taga hasken ɗakin ya sauya kala ,daga farin haske zuwa dim light,kuma daga can gefe wata bishi sai walwali take .

Kuka sosai fattu keyi cikin tsoro da rashin sanin abinyi,yaukan yasan kwananta kawai ya kare kamar wacce akace kalli can ,tana juyowa wajen da sif ɗin nan take ,kawai taga abubuwa kamar malam bude mana littafi, suna ta yawonsu ajikin sif ɗin.

Wata irin numfashi fattu ta jaa da ƙarfi,kafin kuma tayi ƙasa sululu ta faɗa kan gadon asume.

Shikuwa Adeeb yana shiga wannan dakin kwanciya ya ɗanyi akan lafiyayyen gadon dake ɗakin,so yake ya ɗan huta,dan gaba ɗaya yarinyar nan ta gama gajiyar dashi ,yana kwanciya sai yayi tunanin ai baiyi Sallah ba,dan haka tashi yayi tare da sake wanka sannan yayi Sallah,ya koma toilet ɗin ya gabata fuskarsa,sosai naga kyansa ya ƙara fitowa ,ashema kyanshi ya wuce yadda nake tunani,dan kallo daya idan kayi masa ,kuma kuka haɗa idanu ,bazaka iya ƙara yarda ku haɗa ido ba,dan yana da wani irin kwarjini da haiba.

Wannan karon ƙananan kaya ya sanya,riga da wando ne na jins, rigar light blue ce ,yayinda wando kuma ya kasance blue ne sosai.kansa ya taje, sannan ya fashe jikinsa da tauraruwa masu masifar ƙamshi, danaga ya buɗe wata loka guda ,duka turarukane acikin lokar tunda ga sama har ƙasanta.

Wata lokar ya buɗe naga agoguna ,masu azabar kyau da tsada,wani agogon kwal ya dauko ya daura ahanannunsa, sannan ,sannan ya buɗe bangaren takalma,nidai gefe na koma na zama yar kallo.dan abun yafi karfina, daki guda duka na kayan Amfanin mutum ɗaya?wani aikin sai amasar.

Yana gama shiryawa ,dakin ya dauki wani ƙamshi mai rikitarwa da sanya nutsuwa,kanshi ya taje sannan ya shafa mayuka kusan kala biyar akan nashi,tuni kan ya dauki walwali da sheƙi,

Fitowa yayi daga ɗakin ya nufi kitchen,masu karatu kuzo kuga kitchen ,aini kodaga nam aka barni ,tabbas na more,dan iya tsaruwa kitchen ɗin nan ya tsaru.

Wani irin tea naga ya haɗa ,sannan ya siya kwai tare da imdomie,shikam arayuwarsa baida wani abinci daga tea  sai imdomie  saiko nama,

Yana gama  haɗawa ya tsaya yana kallon abincin daya haɗa ɗin cikin wani kayataccen faranti, mamakin kansa yake ,wai yau shine da haɗawa wata abinci,kuma shi zai kai mata da kansa.koda yake ai itaɗin amanar sa ce,kuma dole ya kula da ita.

Ɗaukar tiren yayi ya nufi dakin da Fattun ke ciki,

Kwankwasawa yayi kafin ya dannan wani guri sai ga kofar tana komawa gefe guda,harya buɗe gaba ɗaya ɗaya .

Kansa ya kunna cikin dakin yana mai kallon yadda komai ya canza,wannan alamun e na lokacin barcinsa yayi ,dama haka dakunan aka shiryasu suke sauya komai da kansu,idan lokacin barcin rana ne kona dare ,kokuma safiya .

Ajiye tiren yayi yana mai kallon ta ina zai hangi fattu,can ya hangota kwance akan gado ,saidai da'alama kwanciyar bata daɗi bace, dan haka da sauri ya nufeta, kamar yadda yayi tsammani kuwa suma tayi,cike da fargaba ya ɗagota yana mai kiran sunanta ,"Hulwa !hulwa!!amma bata ko motsaba,ajiye ta yayi tare da bude fridge ya dauko ruwa mai sanyi yana yayyafa mata.amma bata ko motsaba ,wai wannan suman na menene haka?duka duka yaushema ta dawo hayyacinta ne ? gashi yanzu ta ƙara suka.

Huci kawai yake yana kallon fuskarta,zuciyarsa kamar zata fasa ƙirjinsa ta fito,sam baya ƙaunar ganin fattu cikin wani mugun yanayi,waima menene yayi silar wannan suman nata ne?kallon dakin yayi yana mai jinjina kai ,ba shakka tayi arba da yadda dakin nan ke sauyawa ne,wani irin runtse idanunsa yayi tare da dafe kansa,duk laifinane dana fita da ita da duk haka bata faru ba.bude idanunsa yayi wanda suka juye zuwa na macizai sak, ahankali jikinsa ya kama wata irin girgiza yana hayaƙi,kan kace me saiga ɗakin ya turnuƙe da hayaƙi, kusan minti biyar dakin yana

wanann yanayi hayaƙi da wata irin ƙara,kafin hayaƙi ya  baje, saiga wani murtukeken maciji mai girman gaske ya fasa kai yana huci.

Cikin tafiyar macizai macijin nan ya fara sauƙa daga kan gadon ,bangon dakin ya kama tare da fara lauye jikin wanan haɗaɗdun labulayen yana nannadesu tare da fesa musu wani irin ruwa daga bakinsa,da zaran ya fesa ruwan sai kaga labulen yana hayaƙi tare da murmushewa, haka yayi tayi saida  ya bata gaba dayan labulayenan sannan ya fara bugun kwayayen dakin dake bada hasken nan mai ban sha'awa  da jelarsa.tas saida ya gama fashesu, sannan ya nufi kan gadon,yana zuwa ya hau kan cikin fattu dake kwance ,cikin halin suma,zagayeta ya farayi tare da shigewa ciki rigarta  sosai,yana goga  mata sanyin dake jikinsa.

Aikuwa sanyin yana fara ratsa fattu ,ta fara bude idanunta ahankali,tana mai dafe kanta tare da yamutse fuska.

Abu taji yana fitowa sululu daga cikin rigarta,da sauri ta tashi zaune tana mai daga rigarta sama,daidai lokacin shikuwa macijin ya gama fitowa daga jikin nata.

Saƙare fattu tayi tana kallon macijin cike da tsantsar mamaki,shima macijin kallonta yake ido cikin ido.

Masu karatu meke faruwa ne?

Wannan macijin kuma waye?

Shin Adeeb dama bai daina zama macijin ba?

Muje zuwa takuce anty mammy

Mrs babi□□□

Share and comment

Fisabilillah.

More comments

More typing.

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Saƙare,fattu tayi tana kallon macijin cike da tsantsar mamaki, kamar yadda macijin ke kallon fattu shima ido cikin ido.

Ahankali fattu ta lumshe idonta,tana mai ambaton sunan Allah,abin da ya bata mamaki shine,sam bataji tsoroba, saima bin jikin macijin da tayi da kallo,tabbas wannan macijin ta ne na yar ruga, kenan hakan na nufin Hammanta ne ya ƙara zama maciji? innalillahi ,yanzu yazatayi kenan?awane matsayin take idan bai dawo mutum ba?

Ahankali ta furta "Hammana" hawaye na zubowa daga cikin idanunta.

Shikuwa macijin yana ganin hawayen nan nata,ya taho zuwa gareta,yana zuwa ya hau kan cinyarta tare da nannaɗe jikinsa ya ɗora kansa akan kafaɗunta.

Lumshe ido fattu tayi cikin kuka tace " dan Allah HAMMA karka zauna cikin wannan yanayin,bazan iya rayuwa Ni kadai cikin wannan gidan mai aljanu ba, dazuma saida Hulwarka tazo ta tsoratani, gaba daya ta sanja duniyar wannan dakin ,ya koma wata kala,kalli kagani yanzu yadda ya koma,Hamma inajin tsoro"fattu ta faɗa tare da ɗora hannunta akan macijin tana shafawa.

Dagowa macijin yayi tare da zuba mata idanu,itama kallonsa take hawaye na zubowa daga idanunta. Jikinta ya fara zagayewa yana yana nannaɗeta,kafin kuma yayi baya da ita akan gadon,kwanciya fattu tayi tare da runtse idanunta .

Ita kam tariga ta gama sallama wa rayuwa, tasan idan har macijinta bai dawo mutum ba to mutuwa zatayi, ahalin da ake ciki yanzu tana jinsa ne har cikin ranta,kome takeyi shi take gani,ba abinda take bukata akullum kamar tajita kusa dashi,ta san duk ransa wani ya ganshi matsayin maciji ,to za'ayi ƙoƙarin kashe mata shine,wanda tayi imanin duk randa aka kashe Hamma, to tabbas da gawarsa za'a binnesu.

Shikuwa maciji bayan ya kwantar da fattu saiya zare jikinsa daga nannaɗetan da yayi,sannan ya kamo bargon dake kan gadon ya lullaba ajikin fattu,duk abinda yake kallonsa fattu keyi cike da tausayawa,ace mutum yana komawa wata da bar daban? kuma mai haɗari wacce kowa ke gudunta.saukowa yayi daga kan gadon tare da tsayawa daga can gefenta yana kallonta, itama kallonsa take ,kusan minti uku suna kallon juna,yayin da fattu ke zubda hawaye,juyawa yayi tare da nufar ƙofar dakin.

"Dan Allah Hamma ka dawo mutum,kada ka tafi ka barni,ina don kasancewa tare da kai,bani da kowa awannan sabuwar duniyar saikai"abinda fattu ta faɗa kenan lokacin da taga yana ƙoƙarin ficewa daga ɗakin.

Aikuwa tsayawa yayi kamar wanda yake sauraron me take faɗi .saida ta kai aya azancenta,kafin ya kalleta da idanunsa masu naunuka daban daban,sannan ya fice daga ɗakin.

Kuka sosai fattu ta fashe dashi,tana daga kwancen nan,shikenan komai yazo mata ƙarshe,idan  Hamma ya tafi ya barta,ita ahalin yanzu ma, ta fara tunanin kodai duniyar aljanu ya kawo ta?

Haka tayi ta kukanta tana daga kwance har barcine wahala yayi gaba da ita.

Shikuwa Adeeb yana fita kai tsaye dakin daya baro ya nufa ,ahankali yake jan jikinsa , harya kai kan gadon ,hawa yayi tare da kwantawa lamo kamar baya nunfashi,rufe idanunsa yayi yana nishi da gyar, kafin kuma jikinsa ya kama girgiza sosai yana hayaƙi,  sosai dakin ya turnuƙe da hayaƙi kafin ya washe.

Ikon Allah Adeeb na hanga kwance akan gadon nan,ya duƙunƙune jikinsa,sai rawa yake kamar mai jin sanyi,ahankali ya ɗaya hannunsa dake ta faman rawa ya dage kansa,yana mai yamutse fuska ,da alama kan ke masa ciwo,kusan minti goma ya ɗauka cikin wanan halin kafin naga ya miƙe jiki ba kwari,ya nufi toilet ,wanka yayi tare da sake kaya,ya fito cikin fara tass ɗin jallabiyya.

Zama yayi akan wata kujera dake gaban gadon,kujerar tsabar kyanta ,kai kace da zallar kwal akayita.sai ƙamshi  yake bugawa, kallon ɗakin yake yana mai mamakin shidai yasan ya fita zuwa kitchen kuma har yayi girki,bayan nan kuma ya nufi dakin Hulwa, kuma...

Da sauri ya mike yana mai zafi ido,tabbas asume ya ganta aɗakin ,amma kuma me yasa shi yaganshi ana ?me ya dawo dashi ɗakinsa.

Da sauri ya nufi ƙofa yana ficewa daga dakin,saidai yana fita kafin ya kai dakin nata,yaji sanarwar zuwan tareeƙ,kallon kofar Tata yayi sannan ya nufi bakin ƙofar shigowa falon, yana ƀudewa ya ga tareeƙ da kaya riƙi-riƙi ahannunsa.

Kallonsa tareeƙ yayi yace "yallaƀai lafiya kuwa?

Ahankali Adeeb ya lumshe idanunsa kafin ya jinjinawa tareek din kai,alamu lafiya ba komai.

Shigowa tareeƙ yayi da kayan ya ajiye yana mai cewa"yallaɓai idan an duba sai afadamin abinda babu aciki." Nan ma dai kai kawai Adeeb ya daga sannan ya kalli kayan ,ledojine kusan guda goma manya-manya.

Kallon Tareeƙ yayi na dan wani lokaci kafin yace "an shirya komai na zuwan gurin mai Abie"?

" Eh yallaɓai komai ya kammala ,lokaci kawai muke jira" cewar tareeƙ kenan cikin girmamawa .

Jinjina kai Adeeb yayi kafin yace " U can go"

"Ok yallabai"

Tareeƙ ya faɗa yana mai barin falon .

Kayan da tareeƙ ya ajiye Adeeb yayi da kallo kafin ya ɗauki leda ɗaya yana ɗan leƙawa, idanunsa ne suka sauka kan inner wear masu bala'in kyau da tsada,da sauri ya rufe ledar yana ɗan kallon ƙofa, dan sosa kansa yayi kafin ya dauko bra guda ɗaya da hannunsa yana mai kallonta,shiru yayi yana tunanin lallai zatayiwa fattu daidai,dan ahalin yanzu yana kallon abubuwan ta daya taɓa gani a toilet,murmushin yay tare da dan sosa kansa kafin ya ɗauki ledojin duka ahannunsa yayi dakin fattun.

Yana tura ƙofar kuwa ya jiyo ƙinkishin kukanta,tana zaune a tsakiyar gadon ta haɗa kai da gwuiwa tana kuka.dan bata wani jima tana barcin ba ta farka kuma ita tsoro takeji taje ta taɓa kofar wannan hulwar ta kuma tsoratata.

Da sauri ya ƙarasa cikin dakin yana kallonta,tsayawa yayi akanta bayan ya ajiye ledojin dake hannunsa,sosai yake jin tausayin fattu cikin zuciyarsa,sam baya kyaunar ganinta cikin damuwa,yanzu zaiji zuciyarsa tayi masa zafi sosai.

"Hulwa " Adeeb ya furta cikin muryarsa mai sanyi da nutsuwa.

Da sauri fattu ta ɗago kanta ,sakamakon jin Muryar Adeeb da tayi,

Ai bata san lokacin data diro daga kan gadon nan ba ta wani ƙanƙame Adeeb da iya ƙarfinta tana kuka,

"Hammana dama nasan bazaka gudu ka barni ba, Hamma na shiga damuwa sosai lokacin danaga ka koma macijin nan,nayi tunanin guduwa zakayi ka barni

Hammana dan Allah karka rabu dani"fattu ta faɗa cikin matsanancin kuka,wanda zamu iya cewa na farin cikine.

ahankali Adeeb ya lumshe idanunsa,tare da sakin ajiyar zuciya"har abada bazan taba rabuwa dake ba,ina tare dake komai rintsi komai wuya hulwatee" abinda Adeeb ya faɗa kenan , cikin zuciyarsa,amma azahiri kawai rungume fattu yayi shima ,yana mai shafa bayanta ahankali.

Kuka sosai fattu keyi tana kara rungume Adeeb,bazata iya faɗin irin farin cikin da take cikiba,

" Ya isa haka kukan " Adeeb ya faɗa yana mai ɗago kanta.komar da kan nata tayi tare da kara kwanciya akan faffaɗan ƙirjinsa.

Murmushi kawai Adeeb ya tsinci kansa dayi,yana mai shafa bayan fattu,sosai yake jin wani nishadi idan fattu ta ruƙunkume shi nan ,ji yake kamar su tabbata ahaka.

Bangaren Fattuna dai hakan ne ,ji tayi bata don rabuwa da jikin Adeeb ɗin,dan ba ƙaramin nutsuwa take samu akan wannan ƙirjin nashiba.

Kusan minti goma suna rungume da juna ,kafin Adeeb yayi karfin halin cire ta daga jikinsa yana mai cewa" waike bazai sakeni ba saikin karyani?kin fiye son jiki fa" ya faɗa  yana ɗan hararta .

Kai ta duniyar ƙasa kafin tace "Hamma yunwa nakeji" kallon inda ya ajiye abincin dazu yayi kafin ya janyo table ɗin zuwa gaban gadon,

"  Zauna "yace mata.

Zama tayi abakin gadon tana kallonsa,farin ciki fal cikin ranta.

Tea ya haɗa mata sannan ya mika mata flate ɗin kwan da bread zuwa gabanta.wani bowl ya mika mata ta wanke hannunta,kafin ta fara cin abincin,lallai fattu na jin yunwa ,dan kuwa tass ta kawar da abincin nan,shidai kallonta kawai yake,azuciyarsa yace "wannan badai ciba" tana gamawa tayi hamdala tana mai lashe lips ɗinta,ɗago kai tayi suka haɗa ido da Adeeb ,saikuma kunya ta kamata,ganin yadda ta kawar da uban abincin nan.

Shikuwa Adeeb cewa yayi " kin koshi ko zaki ƙara dan naga kedin akwai ci kamar Gara"

Dan shagwabe fuska tayi kafin tace "Allah Hamma abincinne ke wuce silik -silik,ba dan ma na cinyeba.ta faɗa tana kallon farantin.

Kureta kawai yayi da ido yana kallonta baice komaiba,dagowa tayi suka haɗa ido ,hararta yayi yace "zaki fara kallonsa ko" girgiza kai tayi tare da maida kanta ƙasa."zanyi sallah Hamma"ta faɗa kanta a ƙasa.

Nuna mata toilet yayi da hannunsa ,ba tare da yace komai ba.

Mikewa tayi yake bakin ƙofar ta tsaya tare da juyowa.

Yana kallonta baice komai ba,dan yasan me take nufi,ita komai bata iyaba

Saida yayi jimmm!kafin ya mike ya ƙarasa jinkin ƙofar, ya murda handle ɗin yace "kin gani haka ake yi"jinjina kai tayi tare da mamakin wai ƙifama sai anwani murɗata kamar kan fanfo"

Maida ƙurar yayi ya kulle sanan yace "buɗe"kallonsa tayi kafin ta kalli ƙofar, hannunta ta sanya tayi kamar yadda yayi aikuwa saiga ƙofa ta bude.wata dariya ce ta kwacewa fattu ganin tayi nasarar buɗe kofar tace " hahhahhh laaaah Hamma dan Allah kaga abin sauƙi wllh kuma budewa daɗi"ta faɗa tana kara sanya dariya cikin farin ciki.

Shikansa Adeeb dariyar tayi har saida fararen haƙoransa suka bayyana.jijjiga kai yayi kafin ya wuce ciki yana faɗin"Allah ya shiryeki"

Komai saida ya nuna mata ,sanan yasa ta kunna da kanta,aikuwa fattu gaba ɗaya yau ta zama kamar wata shasha ,data kunna abu yayi zata kama dariya,wataran harda ɗan tsallenta takeyi.

Shidai fitowa yayi ya barta dan tayi wanka da alwala.

Bude kayan da tareeƙ ya kawo yayi ,wata doguwar pink ɗin riga ya dauko da mahaifinta ya ajiye mata,sannan ya dauko wani fant da bra ya ajiye akan gadon,sannan fice.

Bayan fattu tayi sallah ne taga kaya akan gado,ɗauka tayi tana kallon kayan,sunyi mata kyau a ido sosai ,amma saita ajiye da sauri tace "ƙilama na hulwar tasane ,Ni wllh na tsani wannan hulwar" ta faɗa tana hararar kayan.

Adeeb me ya shigo cikin dakin da sallama can ƙasan maƙoshinsa.

Tsayawa yayi yana kallon fattu ganin bata sake kayan daya ajiye mata ba.

" Baki Ga kaya bane kika maida wannan. Dan ƙazanta" Adeeb ya faɗa tana hararar fattu.

"Kayi hakuri Hamma nayi tunanin  a hulwar taka ne ai" fattu ta faɗa tana daga kayan,

"Hamma wannan fa " ta faɗa tana daga bra ɗin nan.

" Baki san me ake yi da itaba  maza ki shirya ina jiranki" ya faɗa hararta tare da ficewa daga ɗakin.

Fattu kuwa data rasa ya zatayi da bra ɗin na sai kawai ta sanya kayanta haka tayi waje .

Tana fitowa Adeeb ya biya da kallo ganin bata sanya bra dinba ,yace ……..

Mu hade next page

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Kallon- kallo naga matan nan nayi atsakaninsu, ko wacce tana jifar yar uwarta da mugun kallo, yayi  da zuciyoyinsu ke buga cike da mamaki .

" Habeebee ina kashiga? Me yasami rayuwarka? Na shiga damu matuƙa lokacin da muka wayi gari an nemeka anrasa ba ƙasashen da bamu zagaye ba wajen nemanka, na sanya ƙudede, kadarori,dama  kanfanunuwa na ga duk wanda ya kawo min koda labarin in da kake ne,amma bamu sami komai da ya shafeka ba,meke faruwa habeebee?"dattijon nan ya faɗa yana mai shafa fuskar Adeeb hawaye na zuba daga idanunsa.

Ahankali Adeeb ya kamo hannun mahaifin nashi ,tare da sumbatar hannunsa ,sannan yace " abie wasu abubuwan basu buƙatar afadesu,saidai kawai mubarsu cikin zuciyarmu, sannan muyi ta kallon azzaluman dake neman ganin bayanmu da bakin halinsu." Adeeb ya faɗa yana mai kallon daya daga cikin matan dake tsaye aɗakin.

Kallone irin na duk abinda kike aikatawa akaina, na sani kuma ki kiyaye ranar haduwarmu.

Ahankali naga matar cikin ruɗewa da irin kallon da Adeeb ke mata,ta sanya gefen mayafin dake kanta tana goge zufa daga goshinta ,kanta a ƙasa.

Ita kuwa ɗayar mata cikin sassarfa ta karaso gaban Adeeb ,hannu tasa akan kumatunsa tana shafawa, hawaye ya gama wanke mata fuska.

"Hayatee nayi kewarka fiye da yadda zan fadamaka, naji daɗi da Allah ya kuɓutar dakai daga sharrin mahassada" matar ta faɗa cikin kuka tana mai rungume Adeeb.

" Ammina" Adeeb ya faɗa cikin wata irin murya mai cike da kewa ,yana mai rungume matar daya kira da amminsa.

Matashinnan kuwa gaba daya ya haɗe fuska ,ba alamun fara'a ko murnar dawowar Adeeb gida atare dashi.zamu iya cewa ma bakin ciki yake da ganin Adeeb ɗin.

Zama sukayi abakin gadon ,shida mahaifin nashi,fuskokinsu dauke da mafificin farin ciki da ɗauki ganin juna.

" Habeebee ka bani labarin abinda ya faru" mahaifinsa ya faɗa yana mai kwantar da kan Adeeb ɗin akan cinyarsa.

Kwanciya Adeeb yayi tare da kamo hannun mahaifin nashi kafin yace " abie ,zan baka labarin komai daya sameni ,amma yanzu baka da lafiya ka huta kayi barci abie na" Adeeb ya faɗa yana sumbatar hannun mahaifin nashi.

Dariyar farin ciki abie yayi tare da shafa kan Adeeb yace " ai naji sauki yanzu kam ,wanda yayi silar kamuwa da cutar yazo ya bani magani,bana jin ciwon komai habeebee likita ,zaka iya tafiya" abie ya faɗa yana mai kallon likitan cikin fara'a .

Godiya likitan yayi cikin garmamawa ,yana mai taya sarki murnar dawowar Adeeb ɗin gida,dan kowa yasan da batun bacewar Adeeb ɗin.

Dubawa nayi cikin dakin naga ya rage daga sarki sai Adeeb da ammi,amma ɗayar matar da saurayin nan tuni sun bar ɗakin.

Fattu kuwa tana nan zaune afalon wannan matar ta sauko daga saman sarki cikin wani irin yanayi ,dan ko lura da fattu batayi ba, sai ƙoƙarin kiran waya take .

Ba jimawa kuma,saiga wannan kyakyakywan saurayin shima ya fito cikin fushi da bacin rai,kallonsa fattu keyi taba dan hango yanayin kama da sukayi da Adeeb,saidai ko kama ƙafar kyan Adeeb baiyi ba.

Harya gota inda fattu ke zaune ,sai kuma ya dawo da sauri ya tsaya akanta.

Fattu kuwa da sauri ta mike tsaye tana kallonsa.ganin irin yadda ya tsaya mata akai ƙerere.

Shikuwa saurayin nan mai suna,Rashad ,wani irin. Shegen kallo yake bin fattu dashi,tunda ga sama har kasa,wow wannan kayan fa ?daga ina haka?ya faɗa cikin zuciyarsa yana mai kashewa fattu idanu.

Haɗe fuska fattu tayi tana mai turo baki tare da kawar da kanta gefe.

"Hi babe !" Rashad ya faɗa yana mai ƙoƙarin kamo hannun fattu.

Da sauri fattu tayi baya tana mai turo baki tare da biye hannunta abayanta.

Murmushin gefen baki yayi tare da shafa gefen fuskar fattu yace " yanzu ina cikin hanzari amma zan nemeki,dan kin kwanta araina kuma yawuna ya tsinke" ya faɗa yana mai wucewa bayan ya sunbaci hannun daya taɓa fuskar fattu dashi.

Duk zancen da yake da larabci yake yinsa,dan haka ba abinda fattu ta fahimta cikin zancen nasa.taɓe baki tayi tare da binsa da harara , tana faɗin" Allah ya isa taɓa min fuska da kayi" ta faɗa afili tana mai murguda baki,sannan ta koma ta zauna.

Tana nan zaune shiru -shiru agurin nan ,tunanin take ko ina Hamma ya shiga ya barta anan?karfa taje tana zaune kawai taji anfara yankan naman jikinta,ga shegen sanyin falon duk ya isheta.

Wani irin ƙamshine ya doki hancin fattu,cikin sauri ta lumshe idanunta tare da budewa tana mai kallon ta inda tajiyo ƙamshin,

Masha Allah,wata kyakyakywar budurwace mai tsananin kyau da gayu,taci ado da wata doguwar riga baƙa ,mai tsayin  gaske ,dan saida wasu yammata kusa su shida dake Binta abaya suka riƙe kasan rigar,gaba daya wuyanta da hannunta hatta gashin kanta anyi masa ado ne da kwal,tayi kyau matukar gaske,kallo daya zakayi mata kasan tana cikin farin ciki,dan kuwa sai murmushi take,tana tafiya ɗas-ɗas cikin salo da yanga.

Kallonta kawai fattu keyi cike da tunanin wannan ɗin ko wacece?amma gaskiya yar gayuce ta gaske,nima nan gaba irin wannan kwalliyar zan riƙayi inji ta yanga abina.fattu ta faɗa cike da murmushi tana kallon budurwar.

Ita kuwa budurwa tana karasowa tsakiyar falon ,idonta ya sauƙa akan fattu,dammmm !taji  gabanta ya faɗi, wannan ɗin kuma wacece?daga ina haka?me takeyi acikin babban falo?budurwar ta faɗa cikin zuciyarta ,tana mai jin wani irin tsabar fattu cikin zuciyarta,dan saitaga duk yadda take taƙama da kyau wannan yarinyar tafita,saidai kawai tafi wannan wayewa da sanin duniya.

Kallon -kallo aka fara tsakanin fattu da wannan budurwa,ba abinda ya ƙara batawa budurwar nan rai irin yadda fattu ta tsareta da ido,wato ko shakkar ta ma batayi.

Cikin takunta na isa da rangwada ta ƙarasa gurin da Fattun ke zaune,

Kallon wulaƙanci take yiwa fattu tana wani yamutse fuska.

" Wacece ke?

Budurwar ta faɗa cikin harshen larabci.

Kallonta fattu tayi ba tare da tace komai ba,dan bata san me take cewa ba.

Ran budurwar ne ya ɓaci sosai,hannu tasa tare da fizgo fattu ta kama kwalar rigarta, cikin isa da gadara take faɗin" ke kinsan komi wacece ina miki magana kika shareni?ke yar uban waye marar kunya?"budurwar ta sake faɗa cikin fushi,

Fattu kuwa cikin jin zafin abinda budurwar tayi mata ta ballawa budurwar harara tare da ture hannun budurwar  daga wuyanta,tana mai murguda baki.

Gaba daya hadiman da suka taki budurwar nan zato ido sukayi,cikin tsoro da tausaya wa fattu ,dan ta tabka babban kuskure.

Zato ido budurwar tayi itama tana mai kallon fattu ," kee!!! Ni kika turewa hannu? lallai minti babban kuskure.budurwar ta faɗa tana mai ɗauke fattu da wani lafiyayyen mari, kafin fattu da gama dawowa cikin hayyacinta ta sake jin wani zazzafan marin a dayan kumatunta.

Wani irin azabar raɗaɗine ya ziyarci fuskar fattu,cikin hanzari ta dafe duka kumatunta tana kallon  budurwar nan,nan da nan zuciyar yayan Fulani ta motsowa fattu, ai batasan lokacin data ɗaga hannu itama ta shararawa budurwar nan matuka har biyu ba.....

Manage please my fans,

Wllh am seek.

Mrs babi ce□□□

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Fattu kuwa data rasa inda zata maƙala wannan abun ,sai kawai ta sanya kayanta haka ta yi waje gurin Adeeb, kafin ta fita daga ƙofar saida ta buɗe ta rufe kusan sau biyar,idan buɗe saitayi dariya ta ƙara rifewa, sannan ta buɗe,murna take sosai itama yanzu ta iya buɗe kofar yan wata duniyat.

Tana fitowa kuwa Adeeb ya bita da kallo, so yake yaga ko tasaka wannan abun,saidai kamar yadda ya tsammata ,bata saka ɗin ba kuwa,dan haka  kallonta yayi tare da dalla mata harara yace " kingama shiryawa kenan?" Kai fattu ta daga

masa tana gyara lullubin da tayiwa matakin kamar wata amarya,ta rufe kusan rabin fuskarta ,sannan ta kama wuyan ta rike ƙam da hannunta.

Shiru yayi yana ɗan wani tunani,shi baisan ta yaya zai faɗa mata cewar tasaka bra ɗin ba,dan haka sai yace" ina wannan abun da kika tambayeni na menene?"ya faɗa yana kallonta.

Itama kallonsa tayi kafin tace " na barshi agurin ne ,dan bansan a ina ake sakawa ba" ta faɗa tana ƙara riƙe wuyanta, dan kar mayafin ya faɗi.

Kallonta yayi  har  zaiyo magana sai kuma ya fasa ,wayoyin  da tareeƙ ya taho masa da su ya ɗauki daya daga ciki , ya daga tare da kiran tareeƙ .

Yana dagawa yace "ka tahomin da make up artist yanzu ta shirya yarinyar nan"

"Ok sir " tareeƙ ya faɗa yana mai kiran wata number.

"Koma daki" Adeeb ya faɗa yana mai mikewa shima ya bar gurin.juyawa tayi ta koma tana mai tunanin kodai tayi masa wani abunne ? Taji yace ta koma ɗauki? zama tayi bakin gado tana mai cire mayafin nan ,dama duk ya isheta.gashin kanta ta shafa,tun wannan daurin dake kanta ,shine har yanzu,kuma kan nata ƙaiƙayi yake mata amma Indai ta  zata ƙaramin wanka saita nemi omo ta wanke kan dashi .

Ba komawa saiga tarin ya shigo gidan,waya ya kira Adeeb yake sanar dashi sun karaso.

Cewa Adeeb yayi ya nuna mata ɗakin farko  shikuma yashigo ɗakin hutu.

Kasancewar ba inda tareeƙ bai sani ba acikin gidan,dan haka ya nunawa matar wacce take balarabiya ce dakin yace tayiwa yarinyar ciki duk abinda ya dace .

Shikuma ya shiga dakin da Adeeb ke ciki.

Da sallama ya shiga dakin,Adeeb na kwance akan gado, ba barci yake ba ,amma idanunsa alumshe suke .zama tareeƙ yayi yana mai cewa" yallaɓai fatan dai kana cikin ƙoshin lafiya"

Ahankali Adeeb ya yunƙura ya tashi zaune,kallon tareeƙ yayi kafin ya sauke ajiyar zuciya yace " tareeƙ ina tunanin  abinda nayi ne ,kada yarinyar nan taga kamar na cutar da itane"Adeeb ya faɗa yana kallon tareeƙ da yanayin damuwa akan fuskarsa.

"Ko kaɗan yallaɓai,idan har tayi tunani zata gane baka cutar da itaba, kuma Allah yaga niyyarka, kayi hakan ne dan kare martabarta da kiyaye hakkin Allah, amma yallaɓai mai zai hana kasanar da ita abinda ke faruwa ,dan gudun samun matsala nan gaba"tareeƙ ya faɗa yana mai kallon ogan nashi .

Shiru Adeeb yayi na kusan minti biyu kafin yace" no tareeƙ ,she's too young ace munyi wannan maganar da ita,is better mubar maganar atsaninmu har zuwa lokacin da Allah zai bayyana iyayenta,inyaso saina basu ita ahannunsa,sannan kaga tayi free .

"Shikenan yallaɓai amma yanzu kana ganin ,zaka kaita can gidane,ko kuma zata zauna anan?"tareeƙ ya faɗa yana kallon Adeeb da jiran jin me zaice.

Kusan minti biyu Adeeb ya ɗauka kafin yace" ko zamanta anan tare dani akwai matsala tareeƙ bana so wataran zuciya ta Kani ga aikata wani abun da zai zamo na cutar da ita,zan kaita can gida gurin ammi  ne tunda nima mafi zama can din" ya faɗa yana mai lumshe idanunsa.

" Hakan yayi yallaɓai, Allah ya baka nasara akan kudirinka na alkairi" tareeƙ ya faɗa cike da ƙaunar ogannasa.

"Ameen "Adeeb ya amsa ahankali tare da kwanciya.

Ita kuwa wannan matar mai make up,kasancewar tareeƙ yayi mata bayanin komai tun kafin su zo gidan,dan haka da sallama tashi ga cikin dakin,juyowa fattu tayi da sauri tana kallon matar.

Murmushi matar tayi tare da kama hannun fattu ta miƙar da ita tsaye tana murmushi,

Kallonta kawai fattu keyi cikin tsoro da rashin sanin ko itaɗin wacece?

Cikin harshen larabci matar ke cewa" kai masha Allah yarinya mai kyau da daukar hankali,gaskiya kina da sihirtaccen kyau,yɣata, zanyi Mali kwalliya mai kyau kamar ke" ta kai karshen magannarta tana murmushi. ita dai fattu kallon matar take tana tunanin wannan ɗin kuma daga ina ?wacece?kodai itace hulwar?

Ahankali matar ta kama fattu ta zaunar da ita bakin gadon,gashin fattu ta fara warwarewa, " kai masha Allah,kina da gashi mai tsananin kyau,samun irin gashinki ba kowacce mace ba,larabawan ma" matar ta faɗa cikin harshen labarci,

Ita dai fattu tayi gurum cike da tsoron matar,gashi kuma ta kasa koda yunƙurin gudawa ne bare ta tsere.haka matar ta kama fattu sukaje toilet ta wanke mata kanta tass,sanann suka fito.

Gaban madubi ta kai fattu tare da ɗauki handryer ta busar da kan na fattu,mayuka kala-kala ta shafawa fattu akanta,kan kame tuni kan fattu ya ɗauki wani sheki da ƙamshi, ita kanta fattu wani sawai takejin kan nata.

Gyara mata kan tayi sosai sannan ta ɗaure mata shi da wani ƙaton ribom mai kyau.

Kwalliya tayiwa fattu cikin nutsuwa ba mai yawa ba,daga powder sai lips da kwalli ta sawa fattu a idonta,irin sakun nan da larabawa keyi,kusan rabin ido.

Kai fattu fa tayi mugun kyau fuskar nan Tata kamar farin wata dan haske,kwalliyar ta karbi fuskarta sosai,kodan ba tabayin kwalliyar tayi ba oho?

Ledojin nan mata ta buɗe tare da ɗauko wata bakar doguwar riga,dama kuma kayan duk dogayen riguna ne masu kyau da sutura jiki.

Har zata dauko su bra,sai taga wata akan gadon ,dan haka sai bata daukoba.

Wani ƙaton towel ta ɗauko ,dake gefen kofar bandakin asaƙale ,mikawa fattu tayi tare da cewa ta cire kayan jikinta ,saita sanya bra ɗin sannan tasa kayan nan.cikin harshen larabci matar ke magana.dan bata san cewa fattu bata jin larabci ba,dan kuwa ita tayi tunanin fattun yɣar Misran  ce itama.

Kallon fattu tayi gurum! Kamar kurma,dan bata san me matar ke faɗi ba.ganin fattu bata karɓi towel ɗin ba tana zaune kawai yasa matar tunanin kodai kurmace?

Kwatance ta farayiwa fattu da hannu,cikin ikon Allah kuwa fattu ta gane wai rigar zata cire ta ɗaura towel din .karɓa fattu tayi tare da daura towel din asaman ƙirjinta.murmushi matar tayi tare da ɗaukar bra ɗin ta mikawa fattu.kallon brar fattu tayi tare da kallon matar" tab Ni nasan me zanyi da wannan abun da kina wani mikomin" fattu ta faɗa cikin ranta tana mai turo baki tare da kauda kanta.

Murmushin matar tayi tana mai rayawa aranta ,kodai fattun kunyar saka bra ɗin take?dan ga dukkan alamu wannan ne karonta na farko asaka bra ɗin.

Cikin hikima da dabara matar ta sakawa fattu bra bayan sun sha artabu,dan fattu sam ƙin yarda tayi da farko, aganinta wannan hulwar so take ta gane mata abubuwa,amma cikin hikima matar tayiwa fattu munin ba ganin jikinta zatayi ba tana son rufe mata jikinta ne,sannan ta dagawa fattu rigar jikinta tare da nuna mata itama ta saka irinta.sai lokacin fattu ta fahimci inda ake saka bra ɗin.ikon Allah wato suma waɗannan abubuwan harda jakar da ake boyewa?lallai zakaga abu da yawa idan baka mutuba.

Aikuwa tsif bra din tayiwa fattu ajikinta,Dan dama koda tareeƙ yaje karbowa cewa yayi budurwa yar kimanin 16 za'a haɗawa kayan,

Saidai fanties ɗin duk sun mata kaɗan sosai,da gyar matar ta samo mata wani mai kama da gajeren wando sannan tasaka.

Da kanta ta sanya rigar ajikinta,masha Allah masu karatu duk wanda yaga fattu awannan lokacin zaiyi tunani wata fattun aka sake,dan tayi kyau har ta gaji da yin kyan.

Tauraruwa matar ta fadawa fattu ajikinta masu daɗin ƙamshi,sannan tayi mata rolling ta ɓame da wani kyakykyawan abinda ake riƙe mayafi dashi dan gudun zamewa.

Sosai matar ke yaba kyan da Fattun tayi , ga sarƙarta sai walwala take,matar sai kallon sakar take cike da jinjina irin kuɗin da aka batar wajen siyanta,kafin ta kama hannun fattun ta juya da ita gaban madubi.saida gaban fattu ya faɗilokacin datayi arba da kyakyakywar fuskarta jikin madubi,hannu tasa tare da shafa fuskartata,dan tabbatarwa itaɗince kuwa.

Kuri!! Fattu ta kure kanta da kallo ta jikin madubi,wai dama haka take  ko kuma dai ba ita bace wannan ɗin?anya matar nan ba sake mata fuska tayi ba ?dan dan ita bataga tsohuwar fuskarta ta da ajikin madubin ba.

Murmushin tayi lokacin data ɗan mintsini hannunta kadan,kuma  taji zafi.

Wllh nice ,nice fattun baffa, gaba daya na zama yar gayu aradu zan tsula tsiya, wayyo Allah na ,ina Hamma yazo ya ganni ,yaga yadda na koma fattu yar gayu.

Juyowa fattu tayi tana kallon matar nan, fuskarta dauke da murmushi, itama matar murmushin tayi tana yaba kyau da Allah ya ba faytu.

Wayar matar ce tayi ƙara hakan yasa ta dauka ba tare da tace komai ba ta kara akunnenta,

"To yallaɓai ganin nan"

Shine abinda matar ta faɗa tana mai haɗa jakarta ,sallama tayi fattu bayan ta rungume fattun.

Koda matar ta fita tsayawa fattu tayi jikin madubin nan tana ƙara kallon kanta,tajita nan ta juya can tana dariya ƙasa -ƙasa.

Adeeb ne ya shigo ɗakin sanye da farar jallabiya mai tsananin kyau da ɗaukar ido,kansa kuma hiramine sai wannan baƙin abun da suke ɗorawa asaman hiramin, ba ƙaramin kyau yayi ba sai sheƙi fuskarsa keyi.

Tsak !ya tsaya abakin ƙofar yana mai faɗin "masha Allah,watabarakallahu fi ahsanil kaliƙin" lokacin da yayi arba da yar gayu fattu,wacce Bama tasan yana gurin ba,kallon kanta kawai take ,ta taɓa nan ta taɓa can.

Saida yayi gama ƙureta da kallo,yaga dai idan ya biye ta kallonta to zasu kwana anan ba tare da ya gaji da kallon nata ba,dan haka sai yayi ɗan gyaran murya  kafin yace " idan kin gama kalle madubin zo mutafi.

Sai lokacin fattu ta an kare da Hammana nata na gurin" cikin jin daɗi ta nufeshi tana murmushi," Hamma kalli yadda matar nan ta sauya min fuska? Wllh gani nake kamar bani ba "fattu ta faɗa tana dariyarta mai burge wa da ban sha'awa.

Kallonta kawai Adeeb yake ,dan shikam ya rasa bakin magana ma,gaba ɗaya fattu ta sanya shi cikin wani yanayi na ruɗewa da zallar kyanta.

Ita kuwa tana tsaye gabansa sai rangaji take ,jinta take kamar sarauniya yau ɗin nan.

Ahankali Adeeb ya kai kallonsa kan waɗan nan abubuwan na fattu, ajiyar zuciya ya sauke ganin yanzu kam ta saka wannan abar.dan haka hannunta kawai ya kamo sukayi waje.

Sai lokacin fattu ta sami damar kallon tsarin falon,sama gidan baki ɗaya .

Suna tafe amma fattu na waige waige,ikon Allah Allah garin daɗi na nesa,ashe su amaƙabarta suke,anya kuwa wannan gidan ba aljannar duniya bane.ahankali tace " kaikuwa Hamma dan Allah wannan gidan na waye?"ta faɗa tana kallon yadda yake danna nonbibin bude ƙofar.

Kallonta yayi bayan sun fito farfajiyar gidan,kafin ahankali yace "nawa ne"

Baki fattu ta buɗe cike da mamaki kafin tace " ikon Allah, to Hamma a ina ka sami kudin gina wannan gidan, dan nasan aradu zai kai kusan dubu saba'in ko tamanin " ta faɗa tana irin jinjina kan nan  na ta kwaso kudi da yawa.

Dariya ce ma ta kama Adeeb ,saidai kasancewarsa ba mai yawan dariya ba yasa yayi murmushi kawai ,kafin yace " ki tara kuɗin da kika faɗa kibani na baki gidan" ya faɗa cikin nishadi,haka kawai yake jinsa cikin wani irin nishaɗi dajin daɗi

Kama baki fattu tayi cikin zato ido tace"woooooh Ni ɗiyar baffa,ina zanga wannan uban kuɗaɗen? saidai idan  kaina san siyar insamu, Ni wllh bazan gina gida irin wannan ba ma,haba saikace wanda zan zauna da aljanun duniya acikin" ta faɗa tana wani dan taɓe baki irinna rufamin ashirin nan.

Kallonta Adeeb ya ɗanyi, yadda take ta zuba masa surutu,ashe dama tana da surutu haka?yanzu ta sake dashi sosai,kuma ya fuskanci idan suna tare sam bata fiye lura da wasu abubuwan da zata gani taji tsoroba.

Dai dai nan suka kawo wajen ajiye motoci,kafin su karasa saiga tareeƙ ya fito daga cikin wata rantsatstsiyar mota Black,mai baƙin gilasai,motace yar ubansu wacce kana gani kasan anyi barin kuɗin agurinta.

Bude musu motar yayi yana ɗan satar kallon fattu,wai zuƙi haka yarinyar take dama,gaskiya yana fatan Allah yasa wanan alherin da suka ƙalla karya kunce .

Hararta Adeeb yayi cikin jin haushi yadda ya kafawa fattu idanu yace " to yi da gaske ka cinyeta" ya faɗa cikin harshen larabci yana hararar tareeƙ .

Dan sosa kai tareeƙ yayi yana murmushi,azuciyarsa yana faɗin lallai yallaɓai irin wannan kishi haka kiri-ƙiri?hmmmmm .

Shiga motar sukayi fattu na ta kallon yadda motar take wani sukuf da ita ,kamar siffar wani kwaron,

Kallon Adeeb tayi wanda ya jingina kansa da jikin kujera as usual idanunsa alumshe.

"Hamma  wai a wannan duniyar da mukazo, acikin kwarya ake yawo ne?"ta faɗa tana mai riƙe haɓa.

Idonsa daya ya buɗe tare da kallon ta ,yana rasa mai zai ce mata dan takaice wai motace ƙwaro,kai fattu sai gyaran Allah.

Ganin yayi shiru ta kuma cewa "Hamma yanzu kuma wace duniyar zamu?"

Kai Adeeb ya dafe cike da gajiya surutu yace " duniyar cinye mutane masu surutu" ya faɗa yana hararta.

Allah Sarki fattu dagalo!!tayi tana kallonsa cikin mutuwar jiki ,kafin ahankali ta ɗan matsa kusa dashi tare da kamo hannun rigarsa ta rike tayi kalar tausayi sosai ,ashe duk murnar da take dama duniyar cinye mutane zasu koma,?shikenan bazata ƙara ganin baffanta ba?

Ahankali tace "Hamma baffa....

"Hihhhhhhhh" Adeeb ya fada yana mai ɗora danyatsarsa  akan  bakin fattu,sannan ya kwanto da kanta zuwa kafaɗarsa.

Kwanciya tayi lamo cike da tunani kala kala aranta .

Tafiya sukayi mai ɗan nisa kafin naga sunzo gaban wani irin makeken  gida mai matukar girma da ƙasa,girman gidan yayi haɗa anguwanni manya guda uku,get suka nufa ,suna idan akaga tareeƙ sai abude masa cikin girmamawa,ba wanda ya kula da Adeeb dake bayan motar,dan glass ɗin bakinsa sosai.

Saida suka wuce manyan get bakwai ,kafin suka nufi wani get mai matukar kyau da girma,wani irin walwali get ɗin keyi kai kace da zallar kwal akayishi.

Daga samansa kuma wasu danjojine masu ruwan kwal ke rubuta,

 Well come to the King palace cikin manyan baki.

Ahankali get din ya buɗe bayan wata doguwar na'ura ta danno kai ta haske ko ina cikin motar .

"Yallaɓai mun karaso" tareeƙ ya faɗa yana ɗan juyowa kadan.

Shiru Adeeb yayi yana mai jin wani irin kewa da damuwa azuciyarsa." Tareeƙ how long na dauka ba'asan inda nake ba?Adeeb ya tambaya cikin sanyin murya.

"Yallaɓai  5 months 3days" tareeƙ ya faɗa cikin jimami.

Runtse idanu Adeeb yayi tare da budewa ,da sauri kuma ya yunƙura  tare da dauke kan fattu daga kafaɗunsa,wacce tayi lamo kamar mai barci tsoro duk ya gama cika mata ciki.

Fitowa yayi daga motar kafin ya fara takawa cikin nutsuwa da jin  kewar iyayensa.

Da sauri fattu ta fito daga mota ita ta riga da gudu tabi bayan Adeeb,Allah yasa flat shoe ne akafarta.saurin kamo gefen hiraminsa tayi ta riƙe gan cikin hannunta.yana jinta baice mata komai ba ,har suka kai bakin ƙofar.

Ahankali ya nuna fuskarsa jikin wani dan madubi,wani dogon layine naga yana zagaye fuskar tashi,kafin kofar ta buɗe da kanta,yana sanya kafa  cikin wani tafkeken falo ,naji wata murya ta dauki

Magana," Well come home prince Adeeb Muhammad Ashraf ,your hinest you have a big surprise to see "

Masu karatu fattu fa gaba ɗaya ta tsure da  ganin irin duniyar da suka shigo,wani irin mahaukacin falone ,wanda ta ko ina matsalar benece acikinsa, ga wani dan banzan sanyi da ƙamshi dake dukan hancin ta.nan da nan jikinta ya kama rawa.

Ta rike hannun Adeeb gam-gam cikin nata.

Kamo hannun nata yayi tare da kanta zuwa cikin tsakiyar falon,wanda da gyar fattu ke taka ƙafarta dan wani irin kaishi da taji a ƙasa dakin.

Zaunar da ita yayi yana mai kallonta,

"Ki zauna anan, za'a shigo dake yanzu."

Adeeb ya faɗa yana mai kallon yadda jikinta ke tsuma.

Hannunsa ta kara damkewa kafin tace "Hamma tsoro nakeji sosai" ta faɗa cikin rawar murya.

Hannun nata ya kama ahankali ya kai bakinsa ya sunbata, kafin ya shafa gefen fuskarta ,yace kijirani kinji " yana faɗin haka yabi matakalar dake  tsakiyar falon yayi sama.

Kallo fattu tabishi dashi cike da tsantsar tsoron wannan guri.hawayene ya zubo mata sharrrrr!! Daga idanunta,ahankali ta sanya hannu ta share wahayen .

Shikuwa Adeeb wani haɗaɗden part ɗin naga ya nufa asaman,hadimaine birjik farfajiyar gurin kowa da abinda yake ,tafiya yake cikin sauri da sassafar,ba abinda yake so da buri illa yayi ido hudu da abinsa.wata baiwa ce ta ankare da Adeeb,cikin hanzari ta zube ƙasa tana faɗin

Takawarka lafiya ,dan sarki jikan sarki,yarima mai jiran gado,alherin Allah ya kai maka.

Da sauri duka suka ankare da abinda baiwar nanke fadi,cikin azama da tsantsar farin ciki sauran ma suka zube ƙasa suna kwasar gaisu da murnar ganin Adeeb,ba wanda Adeeb ya kula kai tsaye dakin mahaifinsa ya nufa.

Ahankali ya buɗe kofar  cikin sanyin murya yayi sallama.

Wani farin Balarabe dattijone kwance akan wani lafiyayyen gado irin na sarakuna masu ji da kansu,gefensa kuma wani likita ne ke ƙoƙarin daura masa ruwa ahannunsa,

Sai wani mata guda biyu dattijai, sunsha ado da gwala-gwalai na alfarma ,ko wacce tana inbakiyi bani guri,

Sai wani farin matashi zaune kusa da dattijon nan,ya riƙe hannunsa.

Cikin azama dattijon ya wani zabura tare da sauƙowa daga kan gadon yana mai goge idanunsa,kafin cikin rawar murya yace " habeebee Adeeb "

Ya faɗa tana nuna gofar dakin ,inda Adeeb ke tsaye ,cikin shaukin ganin mahaifin nashi.

Gaba dayan yan dakin ne suka biyo suna kallon ƙofar dakin,aikuwa Adeeb ne ya dawo,prince Adeeb ya dawo gida.

Da gudu Adeeb ya karaso cikin dakin tare da rungume dattijon nan ajikinsa tsantsan yana mai faɗin," habeebe rurh cikin kuka"

Shima kuka kawai dattijon nan yasa tare da ƙanƙame Adeeb ajikinsa.

Matan nan kuwa kallon kallo naga sun fara cikin rudewa da shiga kokwanto.

Masu karatu  muje zuwa yau dai ga fattu cikin gidan sarautar Masar,koya zata kasance?

Ga kuma Adeeb jikin mahaifinsa .

Sai mun hade next page.

Anty mammynku ce

Mrs babi□□□

Share and comment fisabilillah

More comment

More typing.

[7/25, 5:59 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

_____Kallon- kallo naga matan nan nayi atsakaninsu, ko wacce tana jifar yɗar uwarta da mugun kallo, yayi  da zuciyoyinsu ke buga cike da mamaki .

" Habeebee ina kashiga? Me yasami rayuwarka? Na shiga damu matuƙa lokacin da muka wayi gari an nemeka anrasa ba ƙasashen da bamu zagaye ba wajen nemanka, na sanya ƙudede, kadarori,dama  kanfanunuwa na ga duk wanda ya kawo min koda labarin in da kake ne,amma bamu sami komai da ya shafeka ba,meke faruwa habeebee?"dattijon nan ya faɗa yana mai shafa fuskar Adeeb hawaye na zuba daga idanunsa.

Ahankali Adeeb ya kamo hannun mahaifin nashi ,tare da sumbatar hannunsa ,sannan yace " abie wasu abubuwan basu buƙatar afadesu,saidai kawai mubarsu cikin zuciyarmu, sannan muyi ta kallon azzaluman dake  neman ganin bayanmu  da bakin halinsu." Adeeb ya faɗa yana mai kallon daya daga cikin matan dake tsaye aɗakin.

Kallone irin na duk abinda kike aikatawa akaina, na  sani kuma ki kiyaye ranar haduwarmu.

Ahankali naga matar cikin ruɗewa da irin kallon da Adeeb ke mata,ta sanya gefen mayafin dake kanta tana goge zufa daga goshinta ,kanta a ƙasa.

Ita kuwa ɗayar mata cikin sassarfa ta karaso gaban Adeeb ,hannu tasa akan kumatunsa tana shafawa, hawaye ya gama wanke mata fuska.

"Hayatee nayi kewarka  fiye da yadda zan fadamaka, naji daɗi da Allah ya kuɓutar dakai daga sharrin mahassada" matar ta faɗa cikin kuka tana mai rungume Adeeb.

" Ammina" Adeeb ya faɗa cikin wata irin murya mai cike da kewa ,yana mai rungume matar daya kira da amminsa.

Matashinnan kuwa gaba daya ya haɗe fuska ,ba alamun fara'a ko murnar dawowar Adeeb gida atare dashi.zamu iya cewa ma bakin ciki yake da ganin Adeeb ɗin.

Zama sukayi abakin gadon ,shida mahaifin nashi,fuskokinsu dauke da mafificin farin ciki da ɗauki ganin juna.

" Habeebee ka bani labarin abinda ya faru" mahaifinsa ya faɗa yana mai kwantar da kan Adeeb ɗin akan cinyarsa.

Kwanciya Adeeb yayi tare da kamo hannun mahaifin nashi kafin yace " abie ,zan baka labarin komai daya sameni ,amma yanzu baka da lafiya ka huta kayi barci abie na" Adeeb ya faɗa yana sumbatar hannun mahaifin nashi.

Dariyar farin ciki abie yayi tare da shafa kan Adeeb yace " ai naji sauki yanzu kam ,wanda yayi silar kamuwa da cutar yazo ya bani magani,bana jin ciwon komai habeebee likita ,zaka iya tafiya" abie ya faɗa yana mai kallon likitan cikin fara'a .

Godiya likitan yayi cikin garmamawa ,yana mai taya sarki murnar dawowar Adeeb ɗin gida,dan kowa yasan da batun bacewar Adeeb ɗin.

Dubawa nayi cikin dakin naga ya rage daga sarki sai Adeeb da ammi,amma ɗayar matar da saurayin nan tuni sun bar ɗakin.

Fattu kuwa tana nan zaune afalon wannan matar ta sauko daga saman sarki cikin wani irin yanayi ,dan ko lura da fattu batayi ba, sai ƙoƙarin kiran waya take .

Ba jimawa kuma,saiga wannan kyakyakywan saurayin shima ya fito cikin fushi da bacin rai,kallonsa fattu keyi taba dan hango yanayin kama da sukayi da Adeeb,saidai ko kama ƙafar kyan Adeeb baiyi ba.

Harya gota inda fattu ke zaune ,sai kuma ya dawo da sauri ya tsaya akanta.

Fattu kuwa da sauri ta mike tsaye tana kallonsa.ganin irin yadda ya tsaya mata akai ƙerere.

Shikuwa saurayin nan mai suna,Rashad ,wani irin. Shegen kallo yake bin fattu dashi,tunda ga sama har kasa,wow wannan kayan fa ?daga ina haka?ya faɗa cikin zuciyarsa yana mai kashewa fattu idanu.

Haɗe fuska fattu tayi tana mai turo baki tare da kawar da kanta gefe.

"Hi babe !" Rashad ya faɗa yana mai ƙoƙarin kamo hannun fattu.

Da sauri fattu tayi baya tana mai turo baki tare da biye hannunta abayanta.

Murmushin gefen baki yayi tare da shafa gefen  fuskar fattu yace " yanzu ina cikin hanzari amma zan nemeki,dan kin kwanta araina kuma yawuna ya tsinke" ya faɗa yana mai wucewa bayan ya sunbaci hannun daya taɓa fuskar fattu dashi.

Duk zancen da yake da larabci yake yinsa,dan haka ba abinda fattu ta fahimta cikin zancen nasa.taɓe baki tayi tare da binsa da harara , tana faɗin" Allah ya isa taɓa min fuska da kayi" ta faɗa afili tana mai murguda baki,sannan ta koma ta zauna.

Tana nan zaune shiru -shiru agurin nan ,tunanin take ko ina Hamma ya shiga ya barta anan?karfa taje tana zaune kawai taji anfara yankan naman jikinta,ga shegen sanyin falon duk ya isheta.

Wani irin ƙamshine ya doki hancin fattu,cikin sauri ta lumshe idanunta tare da budewa tana mai kallon ta inda tajiyo ƙamshin,

Masha Allah,wata kyakyakywar budurwace mai tsananin kyau da gayu,taci ado da wata doguwar riga baƙa ,mai tsayin  gaske ,dan saida wasu yammata kusa su shida dake Binta abaya suka riƙe kasan rigar,gaba daya wuyanta da hannunta hatta gashin kanta anyi masa ado ne da kwal,tayi kyau matukar gaske,kallo daya zakayi mata kasan tana cikin farin ciki,dan kuwa sai murmushi take,tana tafiya ɗas-ɗas cikin salo da yanga.

Kallonta kawai fattu keyi cike da tunanin wannan ɗin ko wacece?amma gaskiya yar gayuce ta gaske,nima nan gaba irin wannan kwalliyar zan riƙayi inji ta yanga abina.fattu ta faɗa cike da murmushi tana kallon budurwar.

Ita kuwa budurwa tana karasowa tsakiyar falon ,idonta ya sauƙa akan fattu,dammmm !taji  gabanta ya faɗi, wannan ɗin kuma wacece?daga ina haka?me takeyi acikin babban falo?budurwar ta faɗa cikin zuciyarta ,tana mai jin wani irin tsabar fattu cikin zuciyarta,dan saitaga duk yadda take taƙama da kyau wannan yarinyar tafita,saidai kawai tafi wannan wayewa da sanin duniya.

Kallon -kallo aka fara tsakanin fattu da wannan budurwa,ba abinda ya ƙara batawa budurwar nan rai irin yadda fattu ta tsareta da ido,wato ko shakkar ta ma batayi.

Cikin takunta na isa da rangwada ta ƙarasa gurin da Fattun ke zaune,

Kallon wulaƙanci take yiwa fattu tana wani yamutse fuska.

" Wacece ke?

Budurwar ta faɗa cikin harshen larabci.

Kallonta fattu tayi ba tare da tace komai ba,dan bata san me take cewa ba.

Ran budurwar ne ya ɓaci sosai,hannu tasa tare da fizgo fattu ta kama kwalar rigarta, cikin isa da gadara take faɗin" ke kinsan komi wacece ina miki magana kika shareni?ke yaɗar uban waye marar kunya?"budurwar ta sake faɗa cikin fushi,

Fattu kuwa cikin jin zafin abinda budurwar tayi mata ta ballawa budurwar harara tare da ture hannun budurwar  daga wuyanta,tana mai murguda baki.

Gaba daya hadiman da suka taki budurwar nan zato ido sukayi,cikin tsoro da tausaya wa fattu ,dan ta tabka babban kuskure.

Zato ido budurwar tayi itama tana mai kallon fattu ," kee!!! Ni kika turewa hannu? lallai minti babban kuskure.budurwar ta faɗa tana mai ɗauke fattu da wani lafiyayyen mari, kafin fattu da gama dawowa cikin hayyacinta ta sake jin wani zazzafan marin a dayan kumatunta.

Wani irin azabar raɗaɗine ya ziyarci fuskar fattu,cikin hanzari ta dafe duka kumatunta tana kallon  budurwar nan,nan da nan zuciyar yaƴan Fulani ta motsowa fattu, ai batasan lokacin data ɗaga hannu itama ta shararawa budurwar nan matuka har biyu ba.....

Manage please my fans,

Wllh am seek.

Mrs babi ce□□□

[7/25, 8:16 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer (anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



https://facebook.com/groups/943534712916776/

Masu amfani da Facebook sai kuyi join wan nan link din

_____cike da zallar madarar mamaki budurwar nan ke kallon fattu,tunda take arayuwarta ba wani mahaluƙin daya taɓa daga hannu  da sunann ya faɗa mata koda baƙar magana ne, amma wai yau itace tsaye gaban wata kucakar yarinya,sannan agaban bayinta ,dafe da kunci,wai da sunan an sharara mata maruka har biyu?

Lallai wannan yau ko yar gidan uban waye saita gane kurenta, zata san cewa ni Zulaihat nafi ƙarfin awulaƙantani ,kuma azauna lafiya.

Gaba ɗaya barorin gimbiya Zulaihat atsorace suke ,kuma kawunansu sunkuye a ƙasa, yayin da zuciyoyinsu ke bugawa cikin tsoro da fargabar abinda zai biyo baya.

Fattu kuwa tana tsaye riƙe da ƙugu,ta ƙurawa gimbiya Zulaihat idanu,kamar yadda itama ke kallon fattun,lokaci ɗaya fattu taji mugun tsabar Zulaihat cikin

zuciyarta,haka kawai zata wani daga hannu ta dallamin uban mari?ai wllh saidai acinyeni agidan nan,amma idan wannan banzar tayi min abu saina rama dan ba tsoronta nakeji ba ehe.fattu ke wannan zancen ,cikin zuciyarta tare da murguda baki bayan ta kammala zancen zucinta.

H

Ahargitse gimbiya Zulaihat ta fara juye-juye ,can ta hango wani ƙarin flower vase na tangaran,da hanzari tayi gurin da tare da rarumoshi tayi kan fattu tana huci.

Tsorone ya gama kama fattu,yanzu idan ta jibga mata wannan ƙaton abun akai ,ai wllh sai kanta yayi raga-raga,tab yaseen bazata tsaya ba.baya fattu ta farayi cikin tsoro tana mai kallon gimbiya Zulaihat,

Ita kuwa gimbiya zulaihat ganin fattu na ƙoƙarin gudawa yasa ta dakawa hadimanta tsawa akan su riƙe mata fattu,wani irin zafi takeji cikin zuciyarta,wllh zata iya kashe fattu yadda takejin tsanar fattun cikin ranta,dan haka tayi rantsuwa yau saita illata fattu,ta yadda  ko hannunta bazai ƙara moruwa ba,bare ta sake gigin marin wani.

Cikin azama kuwa suka tsakumi fattu suka riƙe ta,ihu fattu ta fara cike da tsoron abinda matar nan zata mata," wayyo Allah na Hamma kazo, zasu cinyeni danya da raina ,wayyo hammana!wayyo Hamma kana ina!! Fattu ta faɗa cikin ihu,lokacin da tajita ahannun waɗannan manyan yan matan masu shegen ƙarfi.

Zulaihat kuwa cikin rashin imani da tsana take faɗin,"wllh yau saikin komi wacece ,kin siya babban kuskuren taɓa Zulaihat,kuma yau zaki girbi abinda kika shuka" Zulaihat ta faɗa cikin fushi tana daga wannan flower vase ɗin da iya ƙarfi ta zata sakarwa fattu.

"Zulaihaaaatttttt!!!!" Aka kwalla kiran sunan gimbiya Zulaihat din ,cikin wani irin sauti mai ƙarfin gaske ,wanda saida dukansu suka tsorata .

Afirgice Zulaihat ta saki flower vase ɗin nan daga hannunta ya fadi ƙasa.

Ba kowa bane yayi mata wannan bahagon kiran face Adeeb ,wanda ya fito ne dan shigowa da fattu gurin mai martaba,lokacin ya gama basu labarin irin taimakon da fattu da baffanta sukayi masa ,da kuma dalilin tahowa da ita nan ɗin .shine mai martaba yace ya shigo da ita ciki.

Dama kuma yana zaune ne ,amma zuciyarsa tana can gurin fattu,dan yasan ta da shegen tsoro,abu kaɗan ne zai firgitata.

Dan haka cikin sauri yake tafi lokacin daya fito daga part ɗin sarki,

Yana doso babban farko kuwa ya fara jin ihuj fattu tana kiran sunansa.dan haka da gudunsa ya ƙaraso cikin falon,yana zuwa idanunsa sukayi masa mummunan gani,Zulaihat na ƙoƙarin illata masa Hulwa.

Cike da tsoro bayin nan suka saki fattu tare da zubewa kasa suna gaida Adeeb.

Wani shegen kallo da Adeeb ya watsa musune yasasu ficewa daga falon da gudu cike da tsantsar tsoro .

Fattu kuwa da gudu ta nufi Adeeb tana kuka,cikin sauri shima yake saukowa daga matakalar benen, uku -uku,hurhuɗu yake tsallake step din, atsakiya falon suka hade da fattu,tana zuwa ta faɗa ƙirjinsa tare da ƙanƙame shi tana kuka."Hamma mutafi daga gidan nan,tsoro nakeji,wannan matar muguwace daga zuwa ta ta mareni har sau biyu,kuma tasa wadancan doyoyin suka rikeni wai zata baremin kai" fattu ke faɗin haka cikin kuka tana kwance akan ƙirjin Adeeb.

Wani irin tausayin fattu ne yake mamaye ilahirin jikin Adeeb,tare da tsantsar jin haushin Zulaihat cikin ransa.

Ahankali yake shafa bayan fattu yana shiiiiiiiii da bakinsa alamun rarrashi.

Idanunsa sun kada sunyi mugun jaaaa ya kafesu akan fuskar Zulaihat,wacce tayi mutuwar tsaye tana kallon wannan yarinyar kwance akan ƙirjin Adeeb,wanda ita bata taɓa samun wannan damar ba.banda bugawa ba abinda zuciyarta keyi,lallai akwai gagarumar matsala,wacece wannan yarinyar?meye alaƙarta da Adeeb?

Cikin daukewar tunani da tsananin kishi daya rufewazulaihat idanu,kunsan matan larabawa da bakin kishi,Zulaihat ta nufi kansu Adeeb gadan -gadan.tana zuwa ta sanya hannu tare da ƙoƙarin fizge fattu daga jikin Adeeb.

Wasu zafafan marukane guda biyu suka sami gurbin zama akan fuskar Zulaihat ɗin,wanda sun fitowa daga hannun Adeeb.

Kusan minti biyu Zulaihat ta dauka kafin ji da ganinta sudawo daidai.

Ihu ta kurma cikin azaba tana mai dafe kumatunta" habeebee nika mara?akan wannan jakar?wacece ita?meye alaƙarka da ita ?  Da har zata kwanta akan ƙirjinsa,kaikuwa kana rarrashinta?Zulaihat ta faɗa cikin kuka da rikicewa.

Wani matsiyacin kallo Adeeb yayi mata, yana mai gyarawa fattu kwanciyarta akan ƙirjinsa kafin yace " ita ɗin mutumce mai matukar muhimmanci arayuwata,mafi kusanci da zuciyata wacce zan iya aikata komai akanta,ki kiyaye nan gaba,hukuncin da zan miki bazaiyiwa kowa daɗi ba " Adeeb ya faɗa cikin wata iriyar murya mai kama da ta basasa,yana mai nuna Zulaihat da hannunsa.

Cikin karawa kukanta ƙarfi Zulaihat tace" kana nufin harni,tafini muhimmanci agareka?" Ta faɗa cikin ruɗu.

Wani banzan kallo Adeeb ya wurgawa Zulaihat kafin yace " ke wacece?wane matsayi kike dashi agareni,karki ƙara haɗa kanki da  Hulwa banza shashasha marar zuciya da kamun kai " Adeeb ya fada yana mai juyawa da fattu suka fara tafiya zuwa sama.

Cikin kuka kamar zata shiɗe Zulaihat tace " wacece ita"

Saida sukayi taku kusan uku ,kafin Adeeb ya juyo cikin murtukakkiyar fuskarsa yace " MATA TACE ita" ya faɗa yana mai tsare Zulaihat da idanu.

Wani wasan ihu Zulaihat ta kwalla tare da ficewa da gudu ta nufi waje.

Harara Adeeb ya bita dashi kafin ya juya suka ci gaba da tafiya ,duk abinda suka faɗa fattu batasani ba, dan da Yaren larabci sukayi maganarsu.

Saida sukaje bakin ƙofar part ɗin sarki sannan Adeeb ya tsaya tare da gogewa fattu hawayenta.yace "kinga duk kin bata kwalliyarki da hawaye, kiyi shiru zamuje gurin abie ne yanzu kinji?karki damu bazata ƙara yi miki komai ba"ya faɗa yana mai riƙe kumatunta.

Kallonsa fattu keyi tare da shagwabe fuska tace " Hamma Ni tsoro nakeji"

"Ba abinda zai sameki ,bagani ba?" Ya faɗa yana kama hannunta suka shiga dakin abie.

Zulaihat kuwa tana ficewa daga falon,kai tsaye mota taje ta shiga tana kuka kamar ranta zai fice,da mugun gudu take tafiya hatta bar cikin masarautar ,kai tsaye wani hotel ta nufa tana zuwa dama akwai dakin dake amazaunin nata cikin hotel ɗin.

Fridge ta buɗe tare da ɗauko wata kwalba ta buɗe cikin sauri tare da kafa kai ,saida ta shanye abinda ke ciki tass kafin ta jefar da kwalbar. Waya ta dauka tare da kiran wata number tace tana jira.

Ko minti biyar ba'ayin saiga wani saurayi kyakyakywa ya shigo ɗakin ,yana zuwa lokacin harta fara fita daga hayyacinta ,tana surutai," saina kasheta ,saina ranta da yarimana ,nawa ne Ni kadai.

Rungume saurayin tayi suka fara aikata alfasharsu,subhanallah,Zulaihat Allah ya shirya.

Adeeb kuwa suna shiga dakin abie ,fattu ta kama gefen rigarsa ta rike gan! Cikin hannunta .ammi ce ta ƙaraso tare da kamo hannun fattu tana murmushi tace "yʏata yar albarka sannu kinji" ammi ta faɗa tana mai rungume fattu.

Abie ma murmushi taye yana mai kallon fattu ,lokaci ɗaya yaji yarinyar ta kwanta masa arai tana da hankali da nutsuwa.

Nan ammi tace agurinta fattu zata zauna ,ita zata kula da ita ,sannan zata taya Adeeb cigiyar mahaifan fattun.

Bayan sati guda Sarki ya hada wani gagarumin taro na farin cikin dawowar babban dansa magajin faɗa,wanda aka gayyato sarakuna daga kasashe daban -daban.

Kuma nan da kwana biyu taron zai gudana,dan haka gyara ake yiwa masarautar sosai.ko ina ka kalla an gyara shi yayi mugun kyau,

Adeeb kuwa shima yanzu ya shiga busy,yana ɗan bin kamfanoninsa na kasashe daban -daban yana duba yadda harkokin ke tafiya,dan haka yau kwana hudu baya gida .kuma basu hadu da  fattu ba .

Gaba ɗaya fattu ta shiga damuwa,kullum tana cikin dakinta da aka bata mai shehun kyau,saidai akawo mata abinci taci ,tayi wanka ta kwanta.

Ko falo baya fita.itama ammi gaba ɗaya bata zama tana ta uzuri.

Gashi bata ita tare su ba,Gara ammi wataran  takan dan yi mata Hausa kadan kadan.

Yau dai fattu tana zaune shiru ,tace bari ta fito falo dan yasan huta kuma ta duba Hammana.

Tana sanye da doguwar riga milk mai fadi kanta yanke da mayafin rigar,ba kwalliya akan fuskarta amma tayi kyau sosai.

Falon ta fito tana binsa da kallo,ya hadu iyakar hafuwa, sai ƙamshi ke tashi ta ko ina.

Tana ɗan zagayenta afalon ,taji anbude kofa.

Juyawa tayi ɗan ganin waye ya shigo,

Rashad ne ya shigo ɗakin shida zulaihat.suna tafe suna dan magana ,da alama kuma rarraba jin Zulaihat ɗin yake.

Turus suka tsaya suna kallon -kallo atsakaninsu su ukun.

Ita dai fattu kallonsu take tana tunanin,dama wannan matar agidan nan take ?tun ranar bata sake ganinta ba,sannan

Kuma ta gane wannan. Saurayin,shine wanda ya taba mata kumatu awancan ɗakin,dan haka da sauri fattu ta kawar da kanta gefe tare da hade fuska, nemar guri tayi ta zauna akan lumtsuma luntsuman kujerun da suka yiwa falon ƙawanya.

"Kai !!Rashad me wannan fitsararriyar keyi anan?aikuwa wllh saina koya mata hankali"Zulaihat ta faɗa tana ƙoƙarin ƙarasawa kusa da fattu.

Da sauri Rashad ya riko hannunta yana mai faɗin "haba -haba ke matsala ta dake gaggawa ,ba yanzu muka gama magana dake ba,zaki taimakeni,nima zan taimakeki, cikin sauƙin kowa ya sami abinda yake so.

Idan kika yi wani abu yanzu ,to shirin mu ga zai wargaje,kuma kinsan wancan horon bashi da sauƙi ko kaɗan.ba dai jini ne za'ayi taron nan ba? Rashad ya faɗa yana mai sakin wani shegen murmushi.

Jinjina kai Zulaihat tayi tana mai hararar fattu.

Cigaba Rashad yayi da maganarsa"to ki kwantar da hankalinki, ranar zamu aiwatar da ƙudirinmu akanta ,zamu tarwatsa koma menene ke tsakaninsu,Ni sam na kasa gane inda ammi ta dosa ,bata bamu goyon baya kamar yadda ya kamata,amma zamuiyi komai da kanmu.

Kedai kawai ki danne zuciyarki akan komai har zuwa jibin"

Rashad ya faɗa cike da ƙarfafawa Zulaihat gwuiwa.

Jinjina kai tayi cikin murmushi tace " nasanka nasan halinka,kuma zaka iya Allah ya nuna mana lokaci, amma wllh na tsani yarinyar nan sosai acikin raina" Zulaihat ta faɗa tana hararar fattu.

Fattu kuwa murguda mata baki tayi itama tana mai cewa cikin ranta" oho dai saidai kiyi ta hararata amma wllh baki isa ki doke  in gyaleki ba ,ba ruwana da wani kin girmeni ehe" fattu ta faɗa tana mai dan dukan cinyarta har saida ƙaran ya fito sukaji.

Kallonta sukayi gaba dayansu ,Zulaihat tace ka "gani ko dukda batasan me muke cewa ba,amma kalli abinda take ?wllh daka barni na tattara yarinyar nan,ai Prince baya gida bare yace wani abu"Zulaihat ta faɗa cikin muryar bacin rai.

"No karki fara,ko baya gida yanzu ai kinsan zai dawo ko?kuma ma gaskiya bazan bari ki taba min kayana ba,dan gaskiya ina hango hutu agurin man sosai " Rashad ya faɗa yana wani kashe ido tare da kallon fattu.

" Wllh Ni haushi ma kake bani ,akan wannan kucakar zaka wani tsaya bata lokacinka,me zaka samu jikin wannan banzar?"cewar Zulaihat cikin haushi.

" Ke wllh ƙarya kike kinsan wannan yarinyar tafiki komai na mata ,kalleta mana da kyau ki gani ,aikinsa  ba karya ,malam komai yaji yadda ake bukata" cewar Rashad cikin wani irin shegen voice .

Tsabar haushi daya kama Zulaihat tashi tayi afusace ta bar falon tana ƙunƙuni.

Adeeb yana can ƙasar farin yana gudanar da binciken kasuwanci sa ,gefe guda kuma ya dage sosai wajen neman iyayen fattu,yasa hoton sarkar nan Tata da rigarta tare da nuna yana neman wanda yasan waɗan nan kayan,saidai bai yarda ya nuna wata alama da zata nuna shike neman wanda yasan wani abu game da kayan  ba,dan nunawa yayi shidin talaka ne sosai .

Kullum suna waya da ammi yana tambayarta fattu ,sannan yace ta rinƙa koya mata Yaren larabci ,kuma ammi tana kokarin koyawa fattun ,dan yau take son kawo tsohuwa salima ,ta zauna tare da Fattun dan ta koya mata Yaren sosai,tunda ita ta iya hausa sosai.kuma kusan ahannunta Adeeb ya girma ,ita tayi renonshi.

Wai ina batun baffa ne?

Allah Sarki baffa lokacin da aka kaishi dakin hukunci ,saida yayi kwana biyu basu wai-waiceshiba,yana can yana fama da zazzabi sakamakon dukan da sukayi masa.sau daya ake kawo masa abinci.

Ranar kwana na biyun ne da yamma aka fito dashi dan zartar da hukunci,lokacin mai gari ya danji dama -dama an gyara masa karayar daya samu har uku .jauro kuma yana nan cikin halin bakin ciki,dan kuwa jauronsa ta lalace ,bazata ƙara amfanuwa ba,ta motse ta zama yar ririya kamar sillen kara.

Shiruwa abokin ta'asar tashi,yanan ido daya ya tsiyaye ,rabin fuska ya zagwanye ,ya zama kamar horo,arɗo ma hannu ya shanye ya zama kamar lauje.

Cikin fushi da bacin rai tare da bakin ciki mai gari yace , sakamakon ta'adda cin da baffa da yar shegen daya kawo musu cikin gari sukayi,an karbe duk wasu shanayensa da tumakai harda gidansa ,matsayin diyyar abinda mayyar daya kawo gidansa tayi,sannan ankoreshi daga garin ,saboda ƙarya da cin amanar yan garin da yayi ,na cewa fattu yarsace.

Baffa yayi kuka sosai,akan wannan rashin adalcin da akayi masa.amma haka ya haƙura ya miƙawa Allah lamarinsa.

Koda ya dawo gida tuni labari ya isa kunne gwogwgo hansai,dan haka yana shigo taci kwalarsa tace ya bata takardar ta bazata iya zama da faƙiri ba.

Nan take kuwa baffa yayi mata saki daya .kuma sam ta hana yayan ta subi baffa. Shi kadai ya bar garin cikin mawuyacin hali.

Allah Sarki baffa ,Allah ya saka maka wannan zalumcin da akayi maka.

Acan misra kuwa ,amma na hango zaune akan wata ƙayatacciyar kujera , da waya ahanunta ,magana take cike da nuna yanayi na jimami, masu mata hidima na can gefenta azaune.

" Zanyi duk iya ƙoƙarin na,ɗan ganin naja yarinyar ajikina, in Sha Allah muke da nasara" amma ta faɗa tana mai ajiye wayar.

Murmushi tayi kafin tace" Maryam zaki san koni wacece ,zanyi abinda saiya girgizaki,saina rabaki da dan da kike takama dashi" amma ta faɗa tana mai gutsirar apple.

Amma dai itace kishiyar mahaifiyar Adeeb,wacce lokacin da Adeeb yazo ta bar ɗakin mahaifin Adeeb cikin ruɗani.

Washe gari da safe fattu ta tashi da wani irin matsanancin ciwon mara,sai kuka take tana riƙe da cikinta.

Tsohuwa salima nata rarrashinta tare da bata haƙuri,dan tana tunanin period me zai yiwa fattun.

Sosai fattu ke jin mugun ciwon mara,sai murƙususu take cike da azaba tana kiran " Wayyo Hammana zan mutu "

Wani irin amai ne ya yunkuro mata,da gudu ta mike ,da nufin zuwa toilet ,saidai taku daya biyu, jiri  ya kwasheta ta tafi luuuuuuuu tayi kasa.....

Masu karatu  masoya,ina godiya da addu'ar ku gareni ,kuma jiki alhamdulillah naji sauƙin sosai ,

Na gode sosai da kulawa,

Much luv sosai da sosai.

Mrs babi ce □□□

Share and comments

Fisabilillah.

More comments

More typing.

[7/26, 11:08 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

_____Wani irin amaine ya tasowa fattu,dan haka da gudu ta mike tana mai riƙe baki,sannan ta nufi toilet.saidai taku ɗaya -biyu tayi kiri ya kwasheta,baya tayi luuuuu!!!zata faɗi.da sauri ta runtse idonta tana mai saki wani ɗan siririn ihu,gaba daya ta gama saddaƙarda cewa ta fadi ,jira kawai take taji ta ina zata fara jin raɗaɗin.saidai maimakon tajita aƙasa,sai taji ta faɗa jikin mutum,wani irin ƙamshine ya ziyarci hancinta mai daɗin gaske,da sauri ta buɗe idanunta dan ganin jikinwa ta faɗa.

ido hudu sukayi da Hammanta, dan shigowarsa kenan dakin ya hangota zata faɗi ,shine yayi saurin tarota, dama yana sauka afadar ko gurin mai martaba baijeba yayi sashin ammi,duk kuwa da cewar maimartaban yana ta kiransa awaya akan ya dawo gida .

Dan kumshe ido fattu tayi cikin azabar  ciwon da mararta keyi ,sannan ta buɗe idonta ,tare da saukesu akan Hammanta,so take ta gasgata shiɗin ne ko gizo idonta keyi.

Aikuwa shine wllh Hammanta ne ya dawo,cikin azama kuwa fattu ta rungume Adeeb tare da sakin kuka,dama kuma kukan take.

" Hamma ina katafi ka barni?inata nemanka amma banganka ba?dan Allah Hamma karka ƙara tafiya ka barni,kaga bani da lafiya cikinsu ciwo yake min sosai" fattu ta faɗa tana mai cusa kanta aƙirjin Adeeb .

Ahankali Adeeb ya lumshe idanunsa tare da rungume fattu shima tsan-tsam ajikinsa,dan kuwa tabbas ba karya yayi kewar fattu sosai ,kullum da ita yake kwana yake tashi,kwana uku da yayi baya ganinta ,jinsa yake kamar mara lafiya.

" Is ok stop crying hulwa,ai gani na dawo ko?"ya faɗa yana mai ɗago kanta .

Buɗe baki tayi da nufin yin magana ,amma gaba daya aman nan ya taho mata ,aiku ba ɓata lokaci  ta wanke Adeeb tass!! Da aman nan ajikinsa.

Shikuwa Adeeb ko ajikinsa ,bai damu da aman da tayi masa ba ,ya riƙe ta sosai ajikinsa yana mai shafa bayanta,tausayinta yake ji har cikin ransa,bata da lafiya sosai dole ya kira likita adubata.

Tsohuwa salima ce ta karaso garesu tare da faɗin"ayya sannu fateema  kinji,maza kawota kaje ka wanke jikinka, wllh tun jiya take fama da ciwon cikin nan,nace yaro kodai girma ne zaizo mata?tsohuwa ta faɗa tana mai kallon Adeeb,

Dan sunkuyar da kansa yayi ƙasa yana mai sosa kai,dan ya gani abinda tsohuwa ke nufi,ita haka take dama ba ruwanta idan zata faɗi magana,kai tsaye take faɗi.

" Ammm nanny bari na kira likita ya dubata. Ya faɗa yana nufar toilet riƙe da fattu,wanke mata jiki yayi tare da bakinta, shima ya wanke inda ta batashi,sannan ya dawo da ita cikin ɗakin, kwantar da ita yayi akan gado tare da shafa gefen fuskarta yace"sannu yanzu za'a baki magani kinji?"ya faɗa cike da tausayawa,ji yake kamar ya maida ciwon jikinsa.

Lumshe ido fattu tayi tare da kamo hannunsa ta rike gam cikin nata tace"Hamma karka tafi dan Allah" fattu ta faɗa tana mai lumshe idanunta .

Hannun nata ya riƙe da ɗayan hannunsa kafin yace "ba inda zani zan sake kaya in dawo yanzu" ya faɗa yana mai mikewa tare da ficewa daga dakin.

Tare suka dawo shida likita,wadda ta kasance likitar gidan ce , mai duba mata.

Sosai ta duba fattu ,kuma ta gane period ke don zuwa mata ,kuma farkon yine shiyasa take jin ciwo.

Dan haka bayani tayiwa Adeeb tare da bashi magungunan da Fattun zata sha.sannan ta lika always Jikin pant taba nanny akan idan jinin yazo saita bata tasanya.

" Yawwa Ni dama nayi tunanin ko girma ne  zatayi ,dan ciwon yayi yawa,Allah Sarki ashe kuwa shine ,bari na haɗa mata tea mai zafi ta sha"nanny ta faɗa cikin tausayawa tana mai nufar kitchen.

Shidai Adeeb yana zaune bakin gado,tunda yaji abinda ke damun fattu,baice komai ba ,kawai yana kallonta dan ta ɗan sami barci .

Cikin girmamawa likitar tayiwa Adeeb sallama ta fita akan zata dawo anjima .

Kai kawai ya ɗaga mata ba tare da ya kalletaba.

Kusan minti biyar saiga nanny ta dawo riƙe da wani kyakykyawan kofi sai turiri yake ,mikawa Adeeb kofin tayi tana mai cewa" ungo magajin faɗa tashe ta maza ta sha zatayi daɗi,kuma jinin zai sauko da wuri" ta faɗa tana mai nufar ƙofa again tana cewa " bari i ke in kula da farfesun can dana ɗora mata,kasan shima yana taimakawa mace idan tana jini"ta faɗa tana ficewa.

Kallo Adeeb ya bita dashi,yana mai girgiza kai,yana son tsohuwar nan ,saidai tacika surutu da sanya mutum jin kunya.

Ahankali ya ɗan shafe fuskar fattu da tayi wani fayau da ita ,sai kyalli take,ahankali ta buɗe idanunta tare da saukewa akan kyakykyawar fuskar hammata.

"Hamma" ta furta ahankali tana kallonsa.

" Tashi Kisha tea maza" ya faɗa yana mai taimaka mata ta zauna bayan ta sanya mata fillo abayanta.

Da kansa yake bata tea ɗin abaki,saida tasha kusan rabi sannan tace ya isheta, ajiye sauran yayi yana mai kallonta kafin yace" ya kike jin jikin naki?"

"  Da sauki Hamma saidai jikina ba kwari ,kuma har yanzu inajin ciwo anan dina"fattu ta faɗa tana mai nuna masa saitin marar ta.

Kawar da kai yayi da sauri yana mai cewa" is ok zai daina "

" Hamma zanyi fitsari" fattu ta faɗa ahankali.

Dan kallonta yayi kafin yace " zaki iya zuwa toilet ɗin?"

Kai ta daga masa tana mai yunkurawa ,tashi tayi tsaye tana ɗan yamutse fuska. Sai taji kamar lema ajikinta,juyawa tayi tare da kallon inda ta tashi,zato idanu tayi lokacin data jini agurin,da sauri ta kai hannunta ta shafo bayanta ,tana mai kallon hannun,aikuwa jini ne kuma daga jikinta ya fito,ƙara zato idanu tayi cikin tsoro tana mai faɗin" na shiga ukuna Hamma jini ,jine yana zuba ajikina,wayyo Allah Hamma jini"fattu ta faɗa tana mai nuna masa hannunta ,jikinta na rawa sosai kamar ana kada mata gangi,

Kallonta Adeeb yayi da sauri ,yana mai kallon hannun nata ,lumshe idanu tayi yana mai jin wani iri ajikinsa,tausayi fattu ke bashi,ita bata san komai ba ,yanzu meye abin damuwa akan wannan ga yadda jikinta ke rawa kamar ana yankata.?

Ahankali ya mike tsaye tare da dafa kafadun fattun yace " ki nutsu mana ,wannan ba wani abun damuwa bane kinji dama hakan na faruwa ga ko wace mace data kai shekaru irin naki" yayi shiru yana ɗan sauke nunfashi ahankali.

Fattu kuwa kuka take tana cikin tashin hankali,sam Bama tajin me Adeeb ke faɗi,sai cewa take " Hamma jini ajikina, dan Allah kace ya daina zuba ,na shiga uku jinina zai kare wayyo baffana" abinda take fadi kenan jikinta na rawa .

Gaba daya Adeeb yana rasa me zaicewa fattu,dan haka kallonta kawai yake cikin damuwa,suna cikin haka saiga nanny ta shigo, ajiyar zuciya Adeeb yayi tare da kallon nanny amarairaice.

" Aa meke faruwa ne haka magajin faɗa?(da yake haka take kiransa) taci gaba ,naga fateema na kuka ,kaikuma ka tasata gaba  da kallo kaima kamar salati kukan?nanny ta fada tana mai karasowa cikin dakin.

Ahankali Adeeb yace "nanny kiyi mata bayani kuka take, wai bata so" ya faɗa kamar zaiyi kuka.

"Yau naga ikon Allah fateema meye baki so?ko maganin ne baki don sha?kiyi haƙuri ai lafiya ake nema miki kinji ?kuma da kinsha jinin zai....sai kuma tayi shiru tare da bin gadon da fattu ta tashi da kallo,to kace jinin ne yazo ,wato shi tagani take cewa bata so,Allah Sarki ai zaki saba dayake wannan ɗin  na farko ne ,zo muje In gyara miki jiki yi shiru" nanny ta faɗa tana mai kamo hannun fattun suka nufi toilet.

Kallonsu Adeeb yayi tare da sauke ajiyar zuciya ,sannan ya fice daga ɗakin,bayan ya janye zanin gadon daga kan gadon,ya ajiye gefe guda,tare da shimfida wani.

Kai tsaye gurin mai martaba ya nufa,yana shiga ya tadda mai martaba tare da amma, zama yayi kusa da mahaifin nashi,bayan ya jefa wa amma wani kallon na tsana .

Kawar da kai amma tayi tare da sakin murmushin gefen baki tace yaro yarone ,cikin zuciyarta.

" Habeebee Barka da dawo ,yanzu nake ƙoƙarin sake kiranka,ai najika shiru,kasan yanzu bana son koda da minti ɗaya ka ƙara nisa dani"abie ya faɗa yana mai shafa kan Adeeb.

Murmushi Adeeb yayi tare da sumbatar hannun mahaifinsa kafin yace " abie wancan karon ma ,kaddarace ta sameni,har Allah ya ba maƙiya nasara akaina,saidai ahalin yanzu kar nake kallon,kowa sannan ba abinda mutum ya isa yayimin  na cutarwa in Sha Allah" Adeeb ya faɗa yana mai kallon ammi cike da tsana .

Itama ammi kallon Adeeb take ,tana mai suna maganganunsa ,kafin ta sauke ajiyar zuciya tayi sallama da mai martaba tare da ficewa daga ɗakin.

Waya ta dauko tana mai kiran wata number tace " mu hadu yanzu-yanzun nan" sannan ta kashe wayar.

Adeeb yana fitowa daga ɗakin abie ya nufi bangaren da amminsa ke hutawa,

Wayace akunnenta kuma da alama wayar da take mai muhimmanci ce ,saidai tana hango Adeeb ya tunkarota tayi saurin katse wayar tana mai cewa " zan kira -zan kira" bata jira amsar dayan vangaren ba ta kashe wayar.

Zama yayi kusa da ita tare da kamo hannunta ya sumbata, kanshi ta shafa taba faɗin Allah yayi maka albarka.

Ya jima suna dan hira ,kuma duk akan kunyar fattun ne ,kafin ya mike yace zaije  ya huta.

Kʻura mata ido naga ammi tayi ta baya ,kuma fuskarta amugun hade ,kafin kuma tayi wani murmushi tana mai jinjina kanta....

Masu karatu manage ,

Yau naje gidan suna ne.

Saida na dawo nayi wanna typing ɗin.

Much luv.

Mrs babi ce□□

Share and comment fisabilillah.

[7/27, 7:53 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

_____Adeeb yana barin gurin saiga rashy ya ƙaraso,zama yayi kusa da mahaifiyar tasa tare da sumbatar hannunta,

Kansa ta shafa tana faɗin ",magajin faɗa prince Rashad Muhammad ashraf"ta faɗa cike da jin dadin sunan.

Turo baki Rashad yayi tare da kallon ammi yace " ammi ta yaya zan zamo magajin fadar?bayan kinƙi yin wani abu akan wannan al'amari,ki dubafa,Adeeb ya dawo gida,kuma cikin ƙoshin lafiya yake,kina tunanin abie zai bar Adeeb ne,sannan Ni ya ɗorani akan karagar?

Shiru ammi tayi tana kallon Rashad har ya kai ƙarshe azancensa,kafin tayi wani murmushi kana tace " Rashad kenan,kasan dai Adeeb yana jin maganata,sannan baya tsallake umarnina, yanzu akwai Abinda nake tunani akan yarinyar can ,daya zo da ita. Ina son tabbatar da wani abu ne game yarinyar ,wannan sarƙa ta wuyanta tabbas nasan iyalan dake da irin sarƙa,kuma sun rasa yarinyar su tsawon shekaru,

Amma idan har na tabbatar da zargina akanta,to zanyi iyakar ƙoƙarina na ganin bata haɗu da ahalin nata ba,dan haduwarsu da ahalin babban koma bayane agareni. Masanin ido kawai ,zakaga abinda zanyi akan wannan al'amarin.

Murmushi Rashad yayi tare da jin wani sanyi cikin ransa,dan yasan tabbas mahaifiyar tasu zatayi ƙoƙarin akan wannan al'amarin.

"Amma ammi Zulaihat fa?kinsan yadda take ƙaunar Adeeb ,kada ta bamu matsala"cewar Rashad kenan yana gutsirar dabino .

"Barni da zulaihat,bana jinta ko kaɗan ,yarinyar da ba wani hankali ta cika ba,itama bazan bari ta auri Adeeb ɗin ba ,lokaci kawai nake jira in maidata can gida"ammi ta faɗa cike da murmushi akan fuskarta.

Sun jima suna tattauna ita da Rashad agurin ,kafin suka koma cikin gida.

Fattu kuwa suna shiga toilet nanny ta hada mata ruwan wanka mai zafi,tace tayi wanka maza.

Bayan tayi wankan ne ,nanny ta bata wannan pant din tasa ajikinta ,sannan suka fito,har zuwa lokacin kuka fattu keyi,har yanzu jinin bai daina zubowa ba,yanzu idan jinta ya kare ya zatayi?mutuwa fa zatayi kenan.

Nanny sai rarrashinta take akan taci farfesun nan tasaha magani amma taki,kuma har lokacin marar ta ciwo take mata.

Suna cikin haka saiga Adeeb ya shigo ɗakin,tana ganinsa jikinta ya ƙaru.tun kafin ya zauna ta fara magana.

" Hamma na shiga uku har yanzu jini na zuba yake ,tsoro nake karya kare In mutu,dan Allah Hamma ka taimaka min" fattu ta faɗa tana mai miƙa masa hannu cikin kuka sosai.

Da ɗan sauri Adeeb ya ƙaraso kusa da ita ya zauna,kallonta yake cike da tausayi,kafin ya riƙe hannunta wanda take miƙa masa yana ɗan murzawa kana yace" kina so ya daina zubowa " ya faɗa cikin sanyin muryarsa.

Da sauri fattu ta jinjina kai tana hawaye.

" To kiyi shiru,ki daina kuka, sannan ki nutsu kici abinci Kisha magani,zakiga ya daina zubowa" Adeeb ya faɗa yana mai share mata hawaye wasu na zubowa.

"Hamma da gaske idan na daina kukan zai daina zubowa Ni tsoro nakeji kar jinina ya ƙare" ta faɗa cikin muryar kuka tana mai shagwabe fuska.

Jinjina mata kai yayi yace " sosai ma kuwa,kuma jininki bazai ƙare a idan kika daina kuka"

Ahankali fattu ta sanya bayan hannunta ta share hawayen,tana mai kallon Hammana nata.

Farfesun ya karba ahannun nanny ya fara ɗiba da cokali yana bata abakin,haka take cin farfesun kamar magani,kusan lokaci shida tayi tace ta koshi.

Bai takura mata ba,ya ajiye flate ɗin ,magungunan ya bare tare da miƙa mata.yamutse fuska tayi tana mai turo baki,alamun bata so.

Kallonta Adeeb yayi kafin yace " ok baki son abun ya tsaya kenan?"

" Ina so Hamma amma Ni bana son wannan abun aradu" ta fada cike da shagwaba, kafeta yayi  da idanunsa masu matuƙar haske da ɗaukar hankali,wani irin yakeji idan tana masa shagwabar nan,nan take zaiji jikinsa yayi week, kasala ta lullubeshi ,gara yayi ya bata maganin nan kar ayi abin kunya gaban nanny.

Hannunsa yaji fattu ta kama cikin nata tattausan hannu ,wani yuummmmm!! Yaji gaba ɗaya jikinsa ya ɗauka ,ahankali ya lumshe idanunsa yana mai sauke ajiyar zuciya.

" Hamma zansha to  kabani"fattu ta faɗa tana mai ƙara damke hannun Adeeb cikin nata.

Ƙara damke idanunsa yayi tamau yana mai fidda wani sauti da ɗan sauri,kusan minti biyu idanunsa na runtse ,kafin ya budesu,har sun sauya kala daga fari tas zuwa ɗan jaa kadan.

Ahankali ya zare hannunsa daga cikin nata,jikinsa sam ba kwari,maganin ya mika mata ,buɗe baki tayi ya saka mata maganin sannan ya bata ruwa.da gyar ta hadiye maganin tana ƙoƙarin yin amai.

Janyota yayi zuwa jikinsa ya rungume ta tsam-tsam ,yana ɗan shafa bayanta slowly.

Lumshe idanu fattu tayi tana mai  shaƙar daddaɗan kamshi jikin Adeeb,lokaci guda kuma taji ciwon marar ta na raguwa sosai.

Shima Adeeb idanu arufe yake shafa bayan fattu,yana mai jin wani yanayi atattare dashi ,dadinsa ma nanny ta bar ɗakin tuni.dan haka gyara zama yayi ,tare da jingina bayansa jikin gado.sosai yake jin dadin yanayin da suke ciki ahalin yanzu,gaba daya yanayinsa ya sauya.sosai yake jin kansa cikin hali na buƙatuwa,wanda har wani hucin iska yake fesarwa daga bakinsa.

Ahankali ya dago kan fattu tare da ƙura mata idanu,itama kallonsa take ,dan wani iri takeji ajikinta,bata san me takeji ba,amma kawai tana so hammanta yayi ta shafa mata bayanta.

Ahankali Adeeb ya kira sunanta" Hulwa"can cikin makoshinsa,kallonsa take jin ya kira sunan Hulwa kuma yana kallonta.

Bai damu da kallon da take masa ba yaci gaba da magana " me kike buƙata yanzu? ina ne yake miki ciwo" ya faɗa kamar mai yi mata  rada asaitin kunnen ta.

Da sauri ta ƙanƙame dantsen hannusa tana mai lumshe idanunta,dan wani irin abu dataji yana mata yawo cikin jikinta,lokacin da sautin muryarsa tare da iskar bakinsa suka doki kunne ta.

"Hammmma" ta furta ahankali cikin jan sunan.

Kallonta yake tare da karantar yanayin da take ciki,ko shakka babu yasan tana jin makamancin abinda yake ji ajikinsa,saidai shikam baida niyyar cutar da fattu,ko kaɗan dole yake nesanta kanshi daga gareta ,dan gudun faruwar wani abu.

Ahankali ya ƙara maimaita mata tambayar ,saidai wannan karon bai kai bakinsa saitin kunnenta ba.

"Hannunsa fattu ta kamo tare da ɗorawa asaitin mararta" marar Tata kuwa tayi zafi sosai ,kallon fuskarta Adeeb yayi wacce har yanzu idanunta ke rufe,

"Nan ke miki ciwo" Adeeb ya faɗa ahankali muryarsa na dan rawa.

Jinjina kai fattu tayi ba tare da ta buɗe idanunta ba.

Ahankali ya kwantar da ita akan gadon,sannan ya ɗan daga doguwar rigar dake jikinta,nan take santala -santalan farare cinyoyinta suka bayyana,kallo Adeeb yabo cinyar Tata dashi,yana mai ambaton sunan Allah cikin ransa.

Ahankali yake ɗan shafa marar Tata tare da dan dannawa kadan kadan ,kamar yana mata tausa , shiru fattu tayi tana jin wani irin sanyi da daɗi na ratsa dukkan sassan jikinta,sosai take jin dadin abinda Hamma ka mata,dan kuwa tuni ta nemi ciwon mararta ta rasa,sai wani nishi take ahankali tana mai riƙe zanin gadon .kwantowa Adeeb yayi tare da ƙurawa lips ɗin ta idanu,buɗe ido fattu tayi tana mai kallon fuskarsa,

Kusan minti biyu suna kallon juna,kafin Adeeb yaji bazai iya ɗaurewa ba kawai ya hada bakinsu guri ɗaya ya fara kissing ɗin fattu.

Kusan mintina biyar zuwa bakwai suka ɗauka cikin wannan halin,gaba daya Adeeb ya fice daga hayyacinsa ,Banda nishinsa ba abinda kake juyowa aɗakin,yayinda fattu kuwa tayi lakwas tana amsar sakonsa, da alama dai itama tana karbar sakon yadda ya kamata.

Kamar wanda aka tsikara,Adeeb yayi saurin zare bakinsa tare da mikewa yayi hanyar fita daga dakin yana tangadi kamar ɗan giya.

Fattu ma saurin juya bayanta tayi tare da runtse idanunta,wani irin abu takeji yana yawo ajikinta ,kuma bataso hamma ya daina mata wannan abun ba sam.

Adeeb yana fitowa daga dakin fattu sukayi kiciɓis da Rashad shikuma yana shigowa babban falon,

Baki sake tashar ke kallon Adeeb ,ganin yanayin da yake ciki,kar dai ace Adeeb zagayawa yake gurin yarinyar nan fa? Dan kallo daya Zakayiwa Adeeb kasan yana cikin hali na buƙatuwa.

Kodai dama kafuwarta ce bamu sani ba ?yace taimakonsa tayi shima yake son taimakonta?(Dan ba Wanda yasan meye alaƙar dake tsakanin fattu da Adeeb ,hatta mai martaba ,sam Adeeb bai fada masa ba.

Shikuwa Adeeb ko kallon inda Rashad take baiyiba ,yayi ficewarsa daga ɗakin,Dan shikadai yasan meke damunsa.

Kai tsaye Rashad ya nufi dakin da fattu ke ciki,tana kwance  har lokacin bata ko motsaba, kallonta yake cike da tsantsar sha'awar ta ,abun tayi ta ko ina kalli hips ɗin ta kamar zai fasa rigar nan,ahankali ya Rashad ya ƙarasa bakin gadon yana mai karewa fattu kallo ,wani irin kashe ido yake yana mai jin kamar ya ruƙunkumeta ajikinsa,hmmmmm Allah ya kamu gobe ,ko kaɗan bazan saurarawa babyn nan ba,Rashad ya faɗa yana mai miƙa hannu da nufin taba abinda ke taimake masa idanu ajikinta.

" Kai- kai ɗan nan menene haka?me zakayi mata ajikin nata ?zo maza ka fice" nanny ta faɗa tana nuna masa hanyar waje.

Dan sosa kai Rashad yayi yana mai hararar nanny kafin ya fice daga dakin yana faɗin "wllh tsohuwar nan ta fiye samun guri,duk wannan banzan ne ya bata dama ,amma zanyi maganinta  ne.ya faɗa yana mai ficewa daga ɗakin.

Ammi kuwa waya ta dauka tare da kiran wata number,bugu biyu aka daga ,murmushi ammi tayi tana faɗin " ƙawatafatan dai kina hanya ,zakizo gurin taron namu ?"

Ta can daya bangaren bansan me akacewa ammi ba ,na dai ji tace "hmmmmm ke dai ki bari kawai saikinzo dan akwai gagarumar matsala sosai"

Shiru ta ɗanyi kaɗan kafin tace " shikenan Allah ya kawoki lafiya  dole mu san abinyi" ta faɗa cike da daure fuska.

Ajiye wayar tayi tare da yin shiru ,da'alama tayi zurfi cikin tunanin mafita.

Adeeb kuwa yana shiga part dinsa ya zube akan kujera,ko takalmin bai iya cire wa ba ,kwanciya yayi rub da ciki akan kujerar ,idanunsa alumshe ya dafe mararsa da hannun damarsa ,fuskarsa ayamutse. Sai huci yake sauƙewa.

Wayarsa ce take ta faman ringing ,Amma ya kasa ɗagawa,haka tayi ta ƙara harta tsinke.

Dole ya ɗauki mataki ,dan gaskiya yana cikin matsala ,idan haka taci gaba da kasancewa to zai shiga damuwa matuka.

Ajiyar zuciya sauke arako na ba adadi,yana mai kara damke mararsa,ba abinda yake ji dagani sai fattu kwance kan ƙirjinsa,yayinda yanayinsa ke kara yin nisa.

"Washhhh " ya furta ahankali yana mai dantse lips ɗinsa na ƙasa.

Nan da nan jikinsa ya kama rawa zazzaɓi mai zafi ya rufeshi ruff..

Muje zuwa masu karatu.

Anty mammy  ce

Mrs babi□□

Share and comment

Fisabilillah.

[7/29, 8:58 AM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

_____"Washhhhhh "Adeeb ya furta ahankali yana mai dantse lips ɗinsa na ƙasa, cikin azaba da radaɗin ciwo,juyi kawai yake akan kujerar,banda bari ba abinda jikinsa keyi,ko yaya ya runtse idanunsa Hulwa yake hangowa,gaba daya ya kasa cire moment ɗinsu,na dazu cikin zuciyarsa,kuma duk lokacin daya hasko moment ɗin ,ji yake tamkar anƙara masa zafin ciwon ne.

Nan da nan cikin lokaci ƙanƙani zazzaɓi mai zafin gaske ya lulluɓeshi.duƙunƙunewa yayi akan kujerar yana mai rawar ɗari da fidda wani irin nishi na azaba.

Wayarsa ce ta ɗauki ƙara akaro na biyu,amma ko inda take bai kallaba hatta tsinke.

Shikuwa tareeƙ da yaji wayar nata shiga kuma ba'a ɗagaba,sai kawai ya shigo part ɗin Adeeb ɗin ta baya.dama shike kiransa tun dazu ,yana don zasu tattauna akan wata magana.

Shigowa yayi cikin falon da sallamarsa,bayan yayi ta nokking yaji shiru.

Kallo yabo falon dashi aƙoƙarinsa na gano inda Adeeb ɗin yake ,dan yafi tunanin ma yana ɗaki.

Saidai kuma akan kujera ya hango Adeeb ɗin cikin mawuyacin hali,da sauri ya ƙarasa gareshi yana mai durƙusa akasan kurar da Adeeb ke kwance.cikin rikicewa yake faɗin" yallaɓai lafiya kuwa?meke faruwa?baka da lafiya ne?tareeƙ ya faɗa cikin ruɗu yana mai taɓa jikin Adeeb ɗin.aikuwa jikinsa yayi zafi ƙau kamar wuta.

Ahankali Adeeb ya buɗe idanunsa tare da ɗan juyowa ,dan  da ya tura kansa ne jikin kurar ya bada baya.kallon tareeƙ yayi cikin mayen ciwo kafin yace " tareeƙ bani magani Please my seek" ya faɗa yana mai jihar da kansa yaci gaba da kwanciya.

Da sauri tareeƙ ya mike tare da shiga uwar ɗakan Adeeb dan dauko maganin.

Wow masu karatu wato yadda Adeeb yake na daban ,haka komai nashi yake na daban,Dan karkuso kufa haduwa adakin  Adeeb,komai na cikin uwar dakan,pich ne da  milk ,hatta silafas  ɗin toilet pich ne jikinsa da milk.banda ƙamari ba abinda dakin keyi.

Maganin tareeƙ ya dauko,dan yasan meke damun yallaɓai ɗin nasa,lokaci zuwa lokaci yakanyi wannan irin ciwon marar.

Ruwa ya dauko cikin fridge ,sannna ya ƙaraso kusa da Adeeb ,maganin ya ɓallo tare da miƙa wa Adeeb ɗin yana mai cewa" yallaɓai ga maganin"

Saida Adeeb yayi kusan minti biyu kafin ya yi ƙura da gyar ya tashi zaune hannunsa riƙe da mararsa, wacce take mugun mirɗa masa,har wani ƙara take.

Karɓar yayi tare da kaiwa bakinsa ,sannan ya kora da ruwa yana sauke numfashi da sauri da sauri.idanunsa sunyi mugun jama'a,sun ƙanƙance.ahankali ya furta " na gode tareeƙ" ya faɗa idanunsa alumshe ya jingina da jikin kujerar.

" Yallaɓi aikinna ne kula da lafiyarka, dan bani da wani ɗan uwa daya wuceka, daga mahaifiyata saikai nake kallo inji daɗi,amma yallaɓai inaga lokaci yayi da yakamata akawo karshen wannan ciwon,abin yana matukar damuna"tareeƙ ya faɗa kamar zaiyi kuka,dan harga Allah baya ƙaunar ganin Adeeb cikin damuwa ko ƙanƙani.

Adeeb ya ɗauke tamkar ƙaninsa da suke ciki ɗaya,tun suna yara suka taso tare,dan tareeƙ ɗan gidan nanny ne,mahaifinsa ya rasu tun yana yaro,agidansu Adeeb ya rayu da mahaifiyarsa,cikin kulawa da nuna kauna .

Ajiyar zuciya mai ƙarfi Adeeb ya sauke dan marar tasa ta fara lafawa,kafin yace " karka damu tareeƙ komai zaizo karshe in sha Allah " ya faɗa yana mai kwanciya akan kujerar.

Jinjina kai tareeƙ yayi tare da kallon Adeeb cikin tausaya wa yace " yallaɓai ko zakayi wanka?

Jinjina akai kawai Adeeb yayi alamun ehh zaiyi" tareeƙ da kansa ya haɗawa Adeeb ruwan wanka kafin yazo ya sanar da shi.

Mikewa Adeeb yayi lokacin jikinsa ya haɗa zufa sosai ,kan tareeƙ ya shafa cikin murmushin ƙarfin hali kafin ya shige cikin dakin.

Binsa da kallo tareeƙ yayi cike da mugun ƙaunarsa aransa, akwai abubuwa da yawa da yake son sanar da uban gidan nasa,saidai yana tsoron ta yadda zai karɓi maganar ,dan kuwa hankali bazai taba daukar abinda yake son sanar dashi ba,amma zaiyi iyakar ƙokarinsa wajen bawa Adeeb kariya ga duk masu don kawo masa hari arayuwarsa.

Amma ce zaune cikin ɗakinta,yayin da Rashad ke zaune shima kusa da ita ,fuskarsa sam ba walwala, da alama dai suna tattauna wata magana ne mai muhimmanci,

"Rashad bana son irin rayuwar da kakeyi ko kaɗan,sam baka jin maganata,ka maida ammi itace uwarka itace ta isa dakai,kasani ba'a yarda da kishiyar uwa dan wasu ba alkairine azuciyarsu ba,Ni dai nina haifeka ,kuma kasan bazan taɓa cutar da kaiba,amma ka haɗa kai da  maƙiyiyata sai abinda tace kakeyi ,to wllh ka kiyayeni,idan na juyo kanka bazakaji daɗi ba,yau kusan kwana uku baka ko leƙo dakin  nan ba  da sunan ka ganni ,sai yau da kazo min da wani zancen banza,to ina mai gargaɗinka akan yarinyar nan ba ruwanka da ita,kasan halin Adeeb sarai ,kome yayi maka kaika sani" amma ta kai ƙarshen batunta tana mai huci da jin ciwo cikin zuciyarta,sam Rashad bai ɗauke ta matsayin uwa ba,ya mika al'amarinsa kaf ga ammi ,hakan na matukar yiwa amma ciwo,yazo su hada kai susan me suke ciki amma yaƙi.

Rashad kuwa banda hura hanci ba abinda yake,yana zatace wani wai baruwansa da babyn na?wannan ma ai shirmene,wllh saidai kome zai faru ya faru ,amma ya gani ya gyasa kuma saiya ɗana.ya faɗa cikin zuciyarsa,kafin ya mike cikin rashin biyayya ga mahaifiyar tasa yake magana" nufa ba wanda ya isa ya hanani yin abinda naga dama,ke dayake hanaki naki uzurin, ko kina tunanin duk irin mugun abinda kike ƙullawa Adeeb ɗin ban sani ba?wllh idan aka takuramin zan fasa kwai ba ruwana,kinji kinsawa mata ido,baiwar Allah ita kuma tana ta nunawa danki so da kulawa" Rashad ya faɗa cikin rashin kunya yana ficewa daga ɗakin.

Kallonsa kawai amma keyi,idan da sabo yaci ace ta saba da rashin kunyar rashad,sam baya ganin girmanta, amma zatayi maganinsa.

Ta faɗa cikin ranta tana mai tunanin yadda zata wulaƙanta ammi cikin ruwan sanyi.

Fattu kuwa barcine yayi nasarar ɗauke ta ,har cikin barcinta mafarkin Hammana tayi tayi,yana mata wasanninsa masu nutsar da jiki da zuciya .sai kusan la'asar kafin ta farka daga barci,ba laifi marar ta daina ciwo,dan likatar nan ta dawo  dan ta dubata lokacin tana barci .

Wanka nanny ta sata tayi tare da bata wata always ɗin ta saka bayan ta lika mata jikin pant.abinci taci tasha magani sannan ta zauna akan gado tana kallon Film ɗin da nanny ta kunna mata jikin kayan kallo.

Ta maida hankalinta sosai tana kallon Film ɗin ,indian yayinda take ganin kamar itace da Hammana suke lobayya.lol

Nanny ce ta shigo ɗakin ta zauna kusa da fattu tana mai faɗin" sannu yar nan ya jikin naki? Nanny ta faɗa tana ajiye wani bolw duke da kayan marmari a cikinsa.

Kallonta fattu tayi tare da sakin murmushi,dan tana ƙaunar matar har cikin zuciyarta,tana da kirki ga kulawa da mutum,dan zaman da sukayi sosai fattu ke cintar wasu kalmomin na larabci,saidai baya iya maidawa ba.

Jinjina kai tayi alamun da sauƙi, kafin ta fara cin apple.sosai take jin dadin wannan abun mai kama da dankali aradu idan tanacinsa har wani lumshe ido take.

Ammi ce ta shigo ɗakin cikin shigar ta ta  koda yaushe wato doguwar riga mai shegen kyau da ɗaukar ido,gaba daya jikinsa sarkokin gwal ne ,sai ƙamshi take bugawa,cikin murmushi take shafa fuskar fattu tare da mata ya jiki,sunkuyar da kai fattu tayi cikin kunya,bata e komai ba.

Kallon wuyan fattu  ammi tayi, tare da kafe sarƙar wuyan nata da ido,tabbas tasan wannan sarƙar da masu alaƙa da ita,amma ta yaya sarƙar zata kasance a wuyan wannan yarinyar,lallai dole ta raba ta da sarƙar nan dan kawar da zargi.zama tayi abakin gadon,cikin murmushi tana shafa lalausan bakin gashin fattu,kafin ta kalli nanny cikin murmushi tace " nanny yar taki fa akwai kunya sosai,ban sani ba kodai sirikata ce ita?da alama ko suna soyayya da dana ne " ta faɗa tana mai shafa sarƙar da hannunta.

Murmushi nanny tayi wacce ke tsaye can gefe tun shigowar ammi dakin,kafin tace " ranki ya dade gimbiyar uwar magajin faɗa,ba wannan alamun atare dasu,yana mata kallon ƙanwa itama tana masa kallon yaya ne,wannan shine abinda na fuskanta atsakaninsu" nanny ta faɗa cikin murmushi tana kallon fattu.

Murmushi itama ammin tayi,tana mai jin wani sanyi cikin ranta,yanzu ta sami nutsuwa ,akan ba wata alaƙa atsakaninsu,saura biye duk wata alama da zata sa agane iyayen fattu.

" Nanny kawo mata lemo mana ,naga ba wani drinks agabanta " ammi ta faɗa dan son fitar da nanny ɗaga ɗakin.

Da sauri nanny ta fice tana faɗin " angama ranki ya dade" tana fita ammi ta kalli fattu tare da sakar mata wata uwar harara,ta gefe ,kafin ahankali cikin dabara ,ta yadda fattu bazata taɓa tsammanin ancire sarƙar wuyanta ba ,ammi ta zare sarƙar tare da damkewa cikin hannunta.

Lokacin da take zare sarƙar ,da sauri fattu ta kai hannunta dan jin abu yana ɗan yawo awuyanta. Cikin sauri ammi tace " ayya yʼata bari incire miki  wani ɗan zarene awuyan naki" ta faɗa tana mai karasa cire sarƙar.

Nanny na shigowa ita kuma ammi ta mike tare da ficewa daga ɗakin cikin tsantsar farin ciki.da alama komai zaizo mata cikin sauƙi.

Adeeb kuwa bayan yayi wanka ya huta,sannan yaci abinci kaɗan ,kafin ya janyo computer yana ɗan wasu ayyukan da ita,har lokacin yana jin ciwon marar kaɗan,saidai ba zazzaɓin.yana aikin ne kawai amma zuciya da tunaninsa suna kan fattu,dan so yake yaga Wane hali take ciki.kasa ɗaurewa tayi ya dauko wayarsa ya kira nanny, Tana dagawa ta ce " magajin fada ɗana ɗan albarka,me kake buƙata.

Murmushi yayi yana mai ɗan kumshe idanunsa,bayan amminsa nanny itace uwar riƙonsa da bazai taba daina ƙaunarta ba.cikin sanyin murya irin ta masu jinya yace "nanny ya jikin nata" ?

"Jiki kam da sauƙi ka gantama tana kallo bari na bata wayar."

Cewar nanny Tana mai karawa fattu wayar akunne.

"Hmmmmm Indai wanna ce Allah yasa tasan me ake yi da wayar ma"Adeeb ya faɗa cikin zuciyarsa.

Fattu kuwa kallon nanny tayi jin ta ƙara mata waya akunne,meye kuma wannan haka ?nanny ta doramin akunne na?

Fahimtar kamar fattu bata gane me zatayi da wayar bane yasa nanny tace " yayanki ne Adeeb ya ke magana,riƙe bari naje kitchen" nanny ta faɗa tana damkewa fattu wayar ahannunta.

Kallon haɗaɗdiyar wayar fattu tayi tana mai cewa acikin" Hamma kuma anan,to ta yaya yashiga cikin wannan ɗan karamin abun har yake magana?wayyo Allah na ta yaya Hamma zai fito ?na shiga ukuna Hamma kana ina ?kana jina ?dan Allah ka fito" fattu ta faɗa cikin muryar kuka,nan da nan hawaye ya fara wanke mata fuska.

Lumshe idanu Adeeb yayi ta can bangaren dan yana jin duk abinda yake fadi,kuma yasan za'ayi hakan .ya rasa wane irin shirme ke samun fattu,yanzu inda zuwa yayi ta ganshiba shikenan zatayi ta kukane gashi bata da lafiya.

Mikewa yayi da sauri ya nufi ƙofa.

Rashad ne tare da ammi suna tsaye jikin wata ɣar ƙaramar runfa mai kama da bukka ,magana suke mai muhimmanci,dan kuwa sai murmushi Rashad keyi yana kallon ammi.

" Aikuwa ammi yanzu zanje na ɗan ganta dan wllh ko barci bana iyayi,gaba daya babyn ta rikitani " rashad ya faɗa yana mai dage gira daya.

Dariya ammi tayi kafin tace " maza ɗan jeka abinka ,ba mai hanaka abinda ranka ke so,amma karka sake kayi mata komai,kajira lokaci,kawai kaje ka ganta kasami nutsuwa ranka" ta faɗa tana mai shafa kan Rashad din.

Murmushin jin dadi yayi tare da sumbatar hannun ammi,yace " shiyasa nake sonki fiye da mahaifiyata ammina"ya faɗa yana barin gurin.

Wani shegen murmushi ammi tayi tana mai binsa da kallo kafin tace " dani kike magana hafsat, nayi alƙawarin saina kawo karshenki afadar nan, keda ɗanki.koba dani zakiyi gasa ba?muje zuwa" ammi ta faɗa cike da gadara tana kaɗan kai.

rashad na shiga dakin da fattu take ya ganta zaune tana kuka,ga apple ɗin ta ahannu wani abaki,cike da shaukin babyn ya ƙarasa inda take ya zauna kusa da ita sosai ,da sauri fattu ta matsa can gefen gadon tana kukanta.

"Ohhh baby menene kike kuka?masu kyau ga basa kuka kiyi shiru,fadamin  abinda ke saki kuka ?ko zakuɗa chocolate?ko ice cream kike so,Rashad ya faɗa yana mai ƙara matsawa kusa da fattu sosai .

Yunƙurin mikewa fattu tayi daga gurin da take ,dan ya kunaceta sosai,rashad yayi saurin janyota jikinsa ya rungume ta, ta gefe" haba babu kiyi shiru mana bana son ganin ki cikin damuwa,zo in baki chocolate kinji" ya faɗa yana ƙoƙarin hade bakinsu guri daya bayan ya riƙe fuskarta.

Cikin kuka fattu ta hankaɗe shi tare da fitowa daga kan gadon tayi kofa da gudu tana kuka.biyota yayi shima,saidai kafin ya ƙaraso ta buɗe kofar ,tana buɗewa kuwa taji ta faɗa jikin mutum,da sauri cikin tsoron ko rashad ne fattu ta dago kanta tana kallonsa. Ai tana ganin Adeeb ne tayi sauri ƙanƙameshi tana kuka.

Riketa yayi da sauri shima yana mai shafa bayanta ahankali,idanunsa alumshe" ya isa haka ba gani ba ?ki daina kukan " Adeeb ya faɗa yana mai dago kanta.

Cikin kuka fattu take nuna masa rashad" Hamma kace ya fita bana son ganinsa tsoro yake bani"ta faɗa tana mai ƙara kwantar da kanta aƙirjin Adeeb.

Da sauri Adeeb ya dawo kansa ,aikuwa carab idanunsa ya sauka akan na rashad,wanda yayi tsilli -tsilli dashi yana kallonsa.

Cikin wata irin zuciya da ɓaci rai Adeeb yace "what? rashad ?ubanme kakeyi anan? me yakawoka dakin Hulwa?me kayi mata" Adeeb ya faɗa cikin karaji yana ture fattu gefe guda tare da tunkarar rashad gadan-gadan kamar wani zaki.

Rashad kuwa cikin rashin kunyarsa ,duk da yana jin tsoron Adeeb ɗin,yace" kamar ya me ya kawoni ɗalibta?nazone in dubata kamar yadda ammi tace ,kuma kaima ai...bai karasaba sakamakon wani bahagon mari da Adeeb ya ɗauke shi dashi,kafin ya dawo hayyacinsa ya ƙara ma  wani marin,nan da nan hancin rashad ya fara zubar da jini,kuma Adeeb ya shaƙe masa wuya tare da haɗa shi da bango.

Jikinsa banda karkarwa ba abinda yake" idan ka sake ka ƙara kallon koda inda Hulwa take ,wllh,billahi,saina illataka .wawa jaki dan iska "Adeeb ya faɗa cikin zafin rai da jin kamar ya karkarya rashad ɗin.

Rashad kuwa tsoro ya gama kamashi, gashi Adeeb ya shaƙe masa wuya yana neman kashe shi.sai dukan hannun Adeeb yake akan ya sake mai wuya,yana kakari

Kuka kawai fattu keyi tana daga tsaye jikinta na rawa ganin abinda ke faruwa,nan da nan jini ya ƙara balle mata sai zuba yake bul-bul yana bin ƙafarta.

Da gudu nanny ta shigo ɗakin tana salati" magajin fada zaka kashe shi ,maza sake mai wuya " ta faɗa tana mai kama hannun Adeeb ɗin.

Gaba daya hankalin Adeeb baya jikinsa.tsantsar kishi da tsanar rashad ke dukan zuciyarsa.sam yaki sake mai wuya.

Rashad sai kakarin mutuwa yake.

Ammi ce ta shigo ɗakin arude tana zuwa ta kama fuskar Adeeb tana faɗin"my prince meye hakan?zaka kashe shine sakeshi mana ,nice fa na aikoshi"ammi ta faɗa cike da tsoron kar Adeeb ya kashe rashad.

Amma ko gezau Adeeb baiyi ba ,ba kuma alamun zai sake rashad ɗin.

Rashad kuwa gaba daya jikinsa yayi kaishi dan ko hannunsa ma ya kasa dagawa bare ya kwaci kansa.

Da jan kafa fattu ta ƙaraso garesu,tare da rungume Adeeb ta baya cikin kuka take faɗin"Hamma ka sakeshi,zai mutu dan Allah Hamma ka bari,jinina yana zuba zan mutu Hammana " ta faɗa tana mai ƙanƙame Adeeb sosai ta baya tana kuka.

Sakin rashad Adeeb yayi yana mai runtse idanunsa da mugun ƙarfi,kafin ya dunƙule hannunsa ya daki bango da karfin gaske.

Juyo da fattu yayi zuwa gabansa tare da ƙanƙame ta ajikinsa yana sauke wata zazzafar ajiyar zuciya.

Ba tare da yayi magana ba ya kama hannunta suka fice daga ɗakin.

Da gudu su ammi sukayi kan rashad daya fadi ƙasa yana ta tari,ruwa nanny ta kawo masa mai sanyi,ɗan kwalla Uba daya kafa kai saida ya shanye ruwan tass.yana sauke ajiyar zuciya da shafa wuyansa cikin azaba.

Sannu suke ta masa ,kafin ammi ta kamashi suka bar ɗakin tare da nufar nata ɗakin.

"Wllh ammi tunda yayi min wannan ƙamshin mutuwar akan wannan yarinyar,nayi alƙawarin gobe saina yi mata fyade mafi muni agidan nan,saina  yi mata abinda ko likitoci bazasu iya ɗin keta ba Adeeb ya yawo bala'in da bazai kare ba agareshi da ma yarinyar" rashad

Ya faɗa cikin azaba yana lumshe idanun.

Kai ammi ta jijjiga cikin bashi kwarin gwuiwa tace "ina bayanta ɗana kayi mata hukunci wanda ya dace da ita"

Ammi ta faɗa tana mai goge masa hancinsa.

Azuciyarta kusa ,dariya take cike da jin daɗi tana mai cewa"haka nake son ku kasance kullum cikin masifa da tashin hankali,kaida uwaraka yanzu ma kuka fara gani,Allah ya kamu goben...

To masu karatu nima dai haka nace ,Allah ya kamu goben ɗan ganin ya zata kaya.

Hausawa gareku, masoya,jiya ƙunƙuni shiru ,wllh ina uzurine amma kuna raina.One luv□□

Anty mammy ce

Mrs babi□□□

Share and comment fisabilillah.

More comment

More typing.

[8/1, 1:30 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

_____kai tsaye Adeeb  part ɗin sa  ya wuce da fattu ,wacce ke kuka kamar ba gobe ,gaba ɗaya atsorace take da ganin yanayin na adeeb.ita tsoronta ma kada wani abu yasameshi, ko ya sanja halitta .

Suna shiga Adeeb ya zaunar da fattu akan kujera ,sam baidamu da yadda jikinta ya ɓaci ba,wani irin tuƙuƙin baƙin ciki yake ji cikin zuciyarsa ,lallai Rashad ya taɓowa kansa ,inhar ya ce zai nuna halin ɗan akuyancinsa akan fattu,to zai iya aikata masa komai ma,dan bazai taɓa iya daukar kowane irin abu akan fattu ba,duk ƙanƙantarsa kuwa.

Kaiwa yake da kawowa atsakiyar ƙarin falon kashi,banda dukan hannunsa ba abinda yake ,idanunsa sunyi bala'in sauyawa ,wannan karon gaba ɗaya idon nashi sun koma blue sosai ,sai wani irin huci yake kamar zaki.

Fattu kuwa ta takure guri ɗaya ,atsorace take sosai,ta kasa koda kallon Adeeb ne ,dan gaba ɗaya kamanninsa sun sauya,har wani bari jikinsa keyi.

Kuka take ƙasa ƙasa ,yayi da take jin yadda jini ke zuba ajikinta,dan har zuwa lokacin akiɗime take.

Juyowa Adeeb yayi yana kallon fattu ,tausayi ta yake ji sosai cikin ransa,yana tuna cewa itaɗin amanace agurinsa,dole ya kula da rayuwarta,bayan haka yana jin tamkar ita ɗin rayuwarsa ce ,bazai bari wani abu ya cutar da ita ba.

Gurin ta ya nufa cikin takunsa mai cike da izza,tsugunnawa yayi agabanta tare da tsura mata ido,dagowa tayi da sauri itama tana kallonsa.da sauri ta sunkuyar da kanta tana kuka ." Dan Allah Hamma kayi haƙuri,kada wani abu ya sameka " ta faɗa tana mai dagowa tare da kallon cikin idanunsa.

Shima kallonta yake cike da tausayawa,hannunsa ya ɗora akan fuskar fattu yana mai share mata hawaye,idanunsa akan fuskarta,

Ɗayan hannun nashi yasa tare da riƙe duka  kumatunta,yana kallonta,tsawon mintuna yayi yana kallonta ,kafin ya sauƙe ajiyar zuciya  da ƙarfi  kafin ya fara magana ,cikin ƙunar zuciya .

" Hulwa " ya faɗa ahankali yana mai kallon fuskarta.

Kallonsa take tana mai tunanin sunan daya kiranta dashi.

Jinjina kai yayi tare da ci gaba " daga yau idan kikaji na kira sunan Hulwa ,to dake nake wannan shine sunan dana zaɓa dan kira ki dashi,saboda ke ɗin ta musamman ce agareni,kina da matsayi mai girma acikin  nan ɗina.ya faɗa yana mai nuna saidin zuciyarsa.kafin yaci gaba" ki faɗa min me Rashad yayi miki?yaushe ya fara kulaki? " Adeeb ya faɗa trying to colmn his mine,Dan kar fattu ta ƙara tsorata .

Girgiza kai fattu tayi tare da share hawayen idanunta ,kafin cikin sanyin murya tace " Hamma Ni bansanshi ba, amma na taɓa ganinsa lokacin da mukazo gidan nan,yayimin magana amma ban kulashi ba,sai dazu ina kwance shine yazo zai taɓani" fattu ta ƙarasa cikin muryar kuka.

Runtse idanu Adeeb yayi da ƙarfi,yana mai jin zuciyarsa kamar zata ƙone,cikin wata irin murya Adeeb yace " ya taɓaki ne ?kuma ina ya taɓa miki?Adeeb ya faɗa jikinsa na wani irin bari.

Girgiza kai fattu tayi tana mai cewa " bai taɓani ba shine na gudu zan fita kai kuma kazo"

Ƙara riɓe fuskarta yayi cike da haɗe fuska sosai yace " ki faɗa min gaskiya Hulwa ya taɓa ki ne ko a'a" Adeeb ya faɗa cikin dan tsawa,har saida fattu ta ɗan zabura.

Kuka fattu ta ƙara sanyawa tana mai faɗawa jikin Adeeb " Hamma ka daina kana bani tsoro " ta faɗa cikin kuka tana kanƙameshi.

Shima ƙanƙameta yayi ajikinsa kamar zai maidata cikinsa.ahankali yake shafa bayanta alamun rarrashi,ita kuwa sai kuka take ahankali tana mai ƙanƙame dashi.

"Ya isa haka Hulwa ,ki daina kuka ,bana so zuciyata tana zafi idan na ganki cikin damuwa,Please stop crying" Adeeb ya faɗa yana mai shafa baƙin gashin fattu ,wanda ba ko ɗan kwali akanta.

Ahankali fattu ta rage sautin kukan ta,har tayi shiru gaba ɗaya,sai ajiyar zuciya take sauƙewa.

Kusan minti biyar suna rungume da juna,kafin fattu ta ɗan motsa tare da kiran sunansa"Hamma"

Ahankali ya buɗe idanunsa dake lumshe yana sauraran bugun zuciyar fattu ,tare nashi bugun zuciyar,ji yayi suba bugawa akusan tare.

Dagota yayi daga jikinsa yana kallonta da sauraron abinda zata faɗa masa.

Kallonsa tayi itama tana mai dan gwaɓe fuska kafin ta kalli ƙafafunta ,sannan ta ƙara dagowa tana kallonsa" jini Hamma"ta  faɗa tana ɗan yarfe hannu.

Da sauri ya kalli ƙafafun nata,aikuwa jini har kan lallausan kafet ɗin dake tsakar ɗakin.miƙewa yayi da sauri tare da miƙa mata hannu,alamun ta mike tsaye.

Kama hannun nashi tayi tare da mikewa tsaye,gaba ɗaya gurin da take zaune ya ɓaci da jini .dan dafe kai Adeeb yayi tare da kallonta yana mai faɗin" sannu ba inkijin ciwo ?kai ta daga masa alamun ehh.hannunta ya kama ya nufi toilet da ita.ruwa ya haɗa mata mai zafi da kansa,sannan yace tayi wanka .

Kallonsa tayi bayan ta gama ƙarewa toilet ɗin kallo,kafin tace " Hamma nifa ban iya shiga kogi ba" ta faɗa cikin muryar ta mai daɗin sauraro .

Kallonta yayi tare da dan hararar ta sannan ya ce " aikuwa yau sai kin shiga kogin nan ,ko kuma nayi miki wankan da kaina" ya faɗa yana hararta ,wai kogi ji shiririta ko ina taga kogin?

Juyawa yayi da nufin fita daga toilet ɗin dan tayi wankan ,da sauri fattu ta riƙo hannunsa ,juyowa yayi ya na mai kallonta da alamun tambayar menene.

Marairaicewa tayi kafin tace " Hamma dan Allah ka zubamin ruwan acikin bokiti, Ni banason wannan abun , kalli fa kagani idan na shiga nutsuwa zanyi" fattu ta faɗa tana mai nuna masa wai ya kalli girman kwamin wankan.

Dafe kai kawai Adeeb yayi yana mai kallon fattu,shikam baisan yaushe fattu zata waye ba,komai ita saita juyar dashi zuwa abin tsoro.

Hannunta ya kama  zuwa bakin kwamin wankan ,cikin ɗaure fuska ya kama rigarta yana ƙoƙarin cire mata ,da sauri ta riƙe hannunsa dan harya kawo rigar wajen cinyarta." Hamma zanyi da kaina kayi haƙuri" fattu ta faɗa tana mai zaro ido ,ganin da gaske yake ƙoƙarin cire mata rigar.

Sakin rigar yayi tare da juya mata baya yace " kiyi wankan yanzun nan  zan dawo " ya faɗa yana ja mata ƙofar.

Koda Adeeb ya fito daga toilet ɗin Safa da marwa yake tayi cikin dakin,ba abinda yake masa yawo acikin zuciyarsa ,sai abinda rashad yayi ƙoƙarin yiwa fattu,wato taɓa jikinta.

Hannunsa ya sanya tare da dukan bangon dakin da ƙarfin gaske ,yana huci cikin wata irin zazzafar murya yake faɗin" Rashad kayi kuskure na farko ,idan har ka sake yunƙurin taba min matata ,yayi shiru yana huci kamar wani zaki,kafin ya mike tsaye tare da barin ɗakin, shida kansa ya gyara gurin da fattu ta ɓata ,dan bazai sa wani ya gyara gurin da fattu ta ɓata ba.yana gamawa kuwa

Kai tsaye bangaren ammi ya nufa yana shiga ya tarar da ita zaune ana taje mata gashi.

Zama yayi akusa da ita ba tare da yace komai ba.

Cikin girmamawa gaba ɗaya haɗiman suka gaida Adeeb tare da ficewa daga ɗakin.

Cike da kulawa ammi ta kamo hannun Adeeb tare da shafa kansa " mu Prince kayi haƙuri da abinda ya faru tsakanin ka da Rashad , ba yadda banyi dashi akan ya gyale yarinyar nan, domin kuwa kai kazo da ita ,kuma a ƙarƙashin kulawar ka  take bana son tashib hankali,amma sai cewa yayi ai ba matar ka bace dan kazo da ita ,wai shi sonta yake kuma ba wanda ya isa yashi tsakaninsu da ita.

Amma my prince kai menene alakarka da yarinyar nan ?dan musan yadda zamu bullowa lamarin ,tun kafin asami matsala"ammi ta faɗa tana mai kallon Adeeb da son jin abinda zaice akan alaƙarsa da yarinyar.

Adeeb kuwa wanda ransa ya ƙara ɓaci sosai da abinda ammi ta faɗa masa cewa rashad ɗin ya faɗa ,cikin furzar da wata zazzafar iska  Adeeb ya kalli ammi kafin yace " amma dole na ɗauki mataki akan rashad ,bazan taba bari ya cutar da yarinyar nan ba ,dan ita ɗin amanata ce " yana faɗin haka ya mike tare da barin dakin.

Murmushi ammi tayi tare da lumshe ido ,lallai burinta yana gab da cika akan waɗan nan yan uwan.

Bangaren nanny ya nufa yace ta bashi kayan fattu ,cike da kulawa nanny tace " ayya ɗan nan ,daka dawo da ita nan ta shirya ,dan kuwa zamanta acan gurinka akwai matsala ,kasan akwai yan sa ido " nanny ta faɗa cike da kulawa.

Kallonta kawai Adeeb yayi, tare da karbar kayan data ciro masa harda pant ɗin data sakawa always ," zata dawo " kawai ya faɗa tare da barin dakin.

Fattu kuwa lokacin data kammala wankan ta sosai taji jikinta yayi mata daɗi ,saidai kumasam ƙin shiga cikin kwamin tayi ta kunna shaya tayi wankanta,saidai damuwarta ɗaya yadda taga jinin nan yaƙi daina zuba. Hawaye ta share daga idanunta kafin ta janyo wani ƙaton bargo ta daura ƙirji dashi.

Ɓudewa tayi tare da fitowa falon ta tsaya jikin bango ,bata son ta zauna jinin ya ƙara batata.abin mamaki tsaf taga an gyara gurin data bata ɗin nan.

Ko waye ya gyara oho!fattu ta faɗa cikin ranta .

Adeeb ne ya shigo ɗakin riɕe da kayan fattu dake ta zuba ƙamari,kallonta yayi tare da kawar da kansa ,ajiye kayan yayi akan gado yace " kisa  kayan ki sameni afalo" sannan ya bar ɗakin.

Bayan fattu ta sanya kayan harda pant din Dan ta gane yadda ake sakawa tunda nanny ta faɗa mata .kanta ta yane da mayafin kayan,sannan ta nufi gaban madubi,turare ta gani dan haka ta ɗauka tare da bude murfin kwalbar gaba ɗaya

tana masa shafawa irin ta mai. Sannan tana yaba ƙamshin wannan man shafawa azuciyarta.

Saida ta gama sannan ta fito falon.

Tun kafin ta gama buɗe ƙofar ƙamshin turaren ya bugi hancin Adeeb ,da sauri ya dago kansa,lokacin data ƙaraso kusa dashi gaba ɗaya falon ya kiɗime da ƙamshin wannan mayen turaren na Adeeb, turarene irin mai shegen kyau da tsada r nan, kwalbar yar karama ce ,wacce kuɗi ta yakai kusan dubu dari biyar ,ɗan kaɗan ake shafawa amma sai yayi sati bai bar jikin mutum ba.shine malam fattu ta shafa matsayin mai.

Kallonta yake hatta ƙara so kusa dashi ta tsaya .

Wasa take da yan yatsunta,yayin da kanta ke ƙasa.

Lumshe ido Adeeb yayi sakamakon yadda ƙamshin turaren nan ke ratsa dukkan wani sannan na jikinsa.

Buɗe ido yayi yana kallonta kafin ya kamo hannunta ya zaunar da ita ,hancinsa ya kai daidai wuyansa yana ɗan shaƙar ƙamshin jikinta.

Lumshe ido fattu tayi lokacin da hucin numfashin Adeeb ya sauka akan dokin wuyanta.

Kallonta Adeeb yayi idanunta alumshe ta damƙe gefen kujerar da take kai,

Kalli yarinyar nan mafa A ce kalli daga ɗan matsawa kusa da ita yadda take cakumo kujera ,hmmm. Adeeb ya faɗa cikin zuciyarsa yana mai ci gaba da kallon fattu.

" Ki buɗe ido ki,saiki saki kujerar karki Yahaya ko" Adeeb ya faɗa yana mai matso da fuskarsa saitin ta fattu,duk da yadda ƙamshin turaren nan ke ƙoƙarin hawa masa kai.

Da sauri fattu ta buɗe idonta tana mai kallon Adeeb ,tare da sakin kujerar ,kunya kamar ta kasheta .

Turo baki tayi tana mai ƙif-ƙif ta ido.

" Me yasa kika samin turare?" Adeeb ya faɗa yana mai  kawar da kansa .

Kallonsa fattu tayi kafin tace " Hamma bansa turare ba ,kawai na shafa mai ne" fattu ta faɗa kanta a ƙasa.

Ajiyar zuciya Adeeb yayi kafin yace" haka ake turare agarinku?

" Dan murmushi fattu tayi kafin tace "Hamma to mu ina zamuga wani turarema ,mufa ko mai ma bamu cika shafawa ba" fattu ta faɗa tana ɗan watsa hannu,kamar ba ita ta gama kukan tsoro ba ɗazu.

" Shiyasa kikayi min  ɓarnar turare ko? Bakisan yana da tsada ba ?Adeeb ya faɗa yana ɗan kallon gefenta.

" Ayya Hamma bansan turare bane ,kawai ƙamshin ne yayi min daɗi,shine na shafa amma kayi haƙuri Hamma zan siya maka wani" fattu ta faɗa tana ɗan dafa kafaɗar Adeeb.

Kallonta yayi kafin ya kalli hannunta data ɗora akan kafadunsa.

Zare hannun tayi da sauri tana mai sunkuyar da kanta.

"Ina zaki sami kuɗin da zaki siyamin wani? Kinsan kuɗin da ne" Cewar adeeb yana ɗan murmushi.dan yasan yanzu fattu zatayiwa turaren kuɗi.

" Karka damu Hamma zan tara kudi mai yawan da kai kusan dubu uku ,saina siya maka turaren da yawa.

Dariya ce ta kama Adeeb ,wai dubu uku !sai kace kudin sadaka .

" Shikenan ki tara dubu ukun saina kaiki kisiyamin" cewar Adeeb kenan yana mai kallon wuyanta.

Hannu yakai kan wuyan nata ya ɗan shafa cike da mamaki kafin yace " Hulwa" dagowa tayi tana kallonsa,yace "ina sarkar nan?"

Hannu fattu ta kai tare da shafa wuyanta ,taji wayam, shiru tayi tana ɗan tunani ,ina ta ajiye sarkar nan kuwa?amma ta kasa tunowa," Hamma bansan inda sarkar take ba" ta faɗa cikin damuwa tana shafa wuyanta.

Shiru Adeeb yayi yana nazari,lallai sace sarkar akayi,kuma akwai wanda yake zargi ,dan haka kallonta yayi yace " waye yazo dakinki " shiru tayi na ɗan lokaci kafin tace Hamma Ni bansani ba dan nayi barci "

"Shikenan tashi muje" Adeeb ya faɗa yana mai haɗe fuska sosai,yasan ba kowa bane ya ɗauke wannan sarkar face Rashad ,kuma amma ita zata sashi ya ɗauke,shi yasan dama saita bashi matsala sosai,amma zai ɗau mataki .

Amma kuwa hankalinta ba ƙaramin tashi yayi ba da ganin halin da Rashad ke ciki,yanzu akan wannan yarinyar Adeeb yayiwa Rashad wannan dukan.

Lallai ya taɓowa kansa.

Kuma dole mai martaba yasan da wannan batun ,

Rashad kuwa ba abinda yake sai tunanin zuwan gobe ,lallai ya shiryawa goben nan Allah ya nuna mata dan kuwa zai bar wa Adeeb babban darasi akan fattu.

Sorry kwana biyu ina biki shiyasa kuka jini shiru.

Muje zuwa masu karatu

Mrs babi ce □□□

[8/4, 11:56 AM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Kai tsaye part ɗin nanny Adeeb ya nufa da fattu,suna zuwa kuwa nanny ta gyara ko ina sai ƙamshi ke tashi,dakin fattu suka shiga ,ya zaunar da ita abakin gado.kallonta yayi na ɗan wani lokaci yana tunanin wannan ƙamshin na jikinta yayi yawa ,kuma zai iya sanyata mura ma,dan shi kansa ƙamshin ya buwaye shi.

Ahankali ya buɗe bakinsa yana  mai faɗin " nanny ahaɗa mata ruwa tayi wanka saita sake wannan kayan" ya faɗa yana kallon nanny dake kusa da fattu tana faɗin" ke yar nan !wannan ƙamshin fa?tunda kuka dosa part ɗin nan nake jin ƙamshin,turaren magajin faɗa,ashe ajikinki yake"cewar nanny Tana mai kallon fattu,kafin ta dawo da kallonta kan Adeeb tana mai cewa" ai dole ma tayi wanka dan wannan turaren yayi yawa ajikinta,kasan shi kuma turare shu'umin abune,yanzu zai saka cikin wani hali,barin ma wannan turare naka mai sanyi ƙamshi, ga yara irin su Rashad birjik afada" nanny ta faɗa tana mai kama hannun fattu suka nufi toilet.

Shiru Adeeb yayi yana kallon ƙofar da suka shiga,lallai dole ma ya hana fattu sanya turare dan maganar nanny gaskiya ce,shi kansa cikin wani irin shauƙi yake jinsa,hakanan tunda ya shaƙi ƙamshin ajikin fattu.

Tashi yayi cikin nutsuwa ya fice daga ɗakin.

Dakin ammi ya nufa lokacin tana zaune gaban wani ƙaton akwati mai ruwan gwal ,sai sheƙi yake da ɗaukar ido,ba komai bane cikin akwatin sai sarƙoƙinta na gwal kala -kala.

Wata yar ƙaramar akwatin ce ahannunta tana mai kallon sarkar fattu data adana aciki.

Murmushi tayi tare da faɗin"nayi alƙawarin keda haɗuwa da  ahalinki saidai alahira,zanyi ƙoƙarin toshe duk wata hanya da zata sadaki dasu,domin cike burina" ammi ta faɗa cikin zuciyarta tana mai murmushi da ƙarewa kyakyakywar sarƙar kallo.

Kamar daga sama ta tsinkayo sallar Adeeb .dan haka cikin azama ta maida sarƙar cikin dan akwatin tare da rufe babban ta maida shi ajiyarsa.

Zama Adeeb yayi kusa da ita ,ba tare da yaga abinda tayi ba.cikin zafin zuciya yake magana da harshen larabci" ammi zan ɗauki mataki mai tsanani akan Rashad da mahaifiyarsa ,Dan kuwa sun ƙetare iyakarsu" Adeeb ya faɗa yana huci cikin ɓaci rai.

Wani daɗine ya mamaye zuciyar ammi ,amma a zahiri da sauri ta kamo hannun Adeeb tana mai marairaice fuska tace " haba habeebee ,me yayi zafi ?me sukayi maka?Indai akan wannan maganar ce ,to kabar komai ahannuna zanyi wa tubkar hanci,bazai kara zuwa gurin ta ba"Ammi ta faɗa tana mai shafa bayan hannun Adeeb ɗin.

Girgiza kai yayi cike da jin tsanar Rashad da Amma,kafin yace " ba wannan maganar bace,ammi Rashad ya ɗauke sarƙar da zata zama makamin da zai sada yarinyar da mahifanta,kuma nasan wannan tabbas shirin Amma ne, Ammi na rasa me kika tsarewa matar nan ta Tsaneki da ahalinki baki ɗaya,kullum burinta ta ganmu cikin tashin hankali ,why Ammi ?" Adeeb ya faɗa cikin mugun damuwa da tausayin Ammin nashi.

Sosai Ammi ta marairaice fuska kamar zatayi kuka ,kafin ta fara magana" habeebee nima bansani ba ,duk yadda nake ƙaunarta da iyalinta,amma sam bata gani tun kana yaro take ƙoƙarin saita ga bayanka ,amma Allah bai bata Sa'a ba, kai dai karvi gaba da haƙuri, sannan kabi komai cikin lumana.kuma awannan karon na goyi bayan ka ɗauki mataki akansu har sai sun bayyana sarƙar nan" Ammi ta faɗa cikin ƙarfafa gwuiwa ga Adeeb . Jinjina kai yayi cike da gamsu da shawarar ammin nashi.sun jima suna tattaunawa akan al'amarin ,ba abinda ammi ke yi sai tunzura Adeeb cikin cikima da basira.

Amma kuwa tana zaune abakin dagon Rashad,yayin da take shafa masa maganin zafi aciwonsa bayan yayi wanka da ruwan dumi.sosai take jin zafin abinda Adeeb

yayiwa Rashad,kalli yadda yaji masa ciwo kamar wani marar gata?lallai saita ɗauki mataki,dan bazata yarda da wannan cin mutuncin ba.

Kallon Rashad tayi wanda yake ɗan runtse ido idan ta shafa masa maganin

zafin.

"Haƙiƙa Adeeb yana wuri gona da iri masarautar nan,kaima fa ɗane ba bawa ba,dan me zaiyi maka irin wannan dukan?saikace ya sami yaronsa, haƙiƙa bazan amince ba ,dole mai martaba ya shiga maganar nan,kuma wllh nayi alƙawarin sainaga bayan Ammi ,dan kuwa ita ke daure masa....yake abinda yaga dama.haka kawai an maidamu kamar wasu matasa iko agida,bazai yiwuba ,sam bazan laminci wannan abun ba" Amma ta kai ƙarshen zancen ta cikin fushi sosai da bacin rai.

Kallonta Rashad yayi shima cikin ɓaci rai,yana mai faɗin "amma kibar wannan maganar atsakanin mu ,kar ki bari mai martaba yaji,dan kuwa da kaina zan ɗauki mataki,wllh saina yi masa abinda sai yayi dana sanin aikata min wannan abun akan wata bare,ke dai kawai ki zubamin ido" Rashad ya faɗa yana mai kitsa abubuwa cikin ransa.

Wannan kenan.

Baƙi sun fara zuwa ta ko ina ,manyan sarakai da yan siyasa na ƙasar Misra, ko ina acikin gidan jama'ane keta kaiwa da kawowa,dan kuwa yau ne za'a gudanar da ƙayatacciyar walimar murnar dawowar prince Adeeb gida,daga ɓangaren Amma baƙi sunzo sosai,matan sarakuna na ƙasashe da dama,da matan manyan masu kudi da yan siyasa.dan haka hadimai sai kaiwa da kawowa suke dan kula da  baki.

Yayin da bangaren Ammi kuwa ,ba magana ,dan kuwa itace uwar taro ,mai gayya mai aiki kenan,sosai ta tara manyan matan sarakuna dana yan siyasa ,da matan manyan attajiran larabawa,kai harda na ƙasashen Afrika .

Ammi taci uwar kwalliya cikin kaya na alfarma ,tayi ado da gwala-gwalai sai ƙamari take bugawa tana cikin matan data gayyata suna ta hira kafin a fara gudanar da taro.

Busar sarewace ta karfe fadar ,alamun da ke nuna wasu baƙin sarakan sun sami hallara,murmushi Ammi tayi dan kuwa ta gane busar ko ta wace ƙasace, ba kowa bace bace yar uwarta gimbiya Zulaihat ,wacce ke auren Sarkin gana.dan haka cikin farin ciki ta mike tare da cewa matan tana zuwa.kafin ta fice zuwa farfajiyar da aka ware musamman dan tarbar baƙin ta ,gurine ƙayatacce wanda yasha ado ,aka wadatashi da komai na jin dadi.

Tana tafe haɗimanta na biye da ita ,murmushine ɗauke akan fuskarta wanda ya ƙara ƙasa ta fuskar tata.

Wata farar mace ce kyakyakywar gaske ta fito daga cikin lafiyayyar motar da aka bude,masha Allah matar ta ko ina ta hadu ,fuskarta ɗauke da murmushi mai ƙayatarwa,idanunta na kan Ammi rungume juna sukayi cikin farin ciki,ammi keyiwa matar Barka da zuwa.

Wasu kyawawan yara ne su biyu suka fito daga ɗaya gefen,da ala'ma yaran tagwayene duba da yadda suke tsananin kama da juna.yaran zasu kai shekara goma ,saidai yanayin jin dadi da hutu,yasa zaka yi tunanin sun wuce hakan,suna sanye da kaya iri ɗaya ,cikin shiga ta ya'yan sarakai.

Gurinsu ammi suna nufo cike da murna suka rungume Ammi,ita cikin jin daɗi ta rungumesu tare da sunbatar  gishinsu,tana mai faɗin," yazeed and zayyad  my children" ammi ta faɗa tana shafa kansu.

Part ɗin ammi suka nufa gaba ɗayansu,cike da murna.

Adeeb ne zaune bakin gado yayin da tareeƙ ke gefensa ,yana tashi shiryawa,shi dama Adeeb baida aboki ,tareeƙ kaɗai ne abokinsa kuma yaronsa,dashi yake ko wace irin shawara ,dan haka ya zuma suna zaune suna shiryawa,dan Adeeb baya barin kowa ya shigo masa part ɗinsa, shi fa akan dole yake abubuwan masarauta, dan sam sarauta bata burgeshi, yafi son kasuwancinsa.

Kallon tareeƙ yayi yana mai faɗin,"tareeƙ nufa na gaji da wannan shirin Please ya isa haka" ya faɗa yana ɗan kwaɓe fuska cikin salon shagwaba.

Murmushi tareeƙ yayi yana mai ɗaurawa Adeeb wani agogon azurfa ahannunsa kafin yace " yallaɓai yaufa dole kayi haƙuri ,dan kuwa saikayi shiga irin ta yarima sosai " tareeƙ ya faɗa yana ɗan danne dariyarsa ganin yadda Adeeb ya wani marairaice kamar zaiyi kuka.hararsa Adeeb yayi yana mai faɗin" dariya ma zakayimin ko?ai kaima mugune nasani ,shiyasa kake ta lodamin kaya haka kamar wani dan dako"

Dariya sosai tareeƙ ya sanya yana mai faɗin" yallabai kasan fa yau sauka gaji da ganin yan mata ,dan zasu yi ta kawo maka hari ne,Suda iyayensu,dan haka dole kayi adon da zaka rikitasu" tare ya faɗa yana kallon yanayin Adeeb ɗin.

Haɗe rai Adeeb yayi yana mai gwabe baki yace " aikuwa zasu wahalar da kansu ne kawai,dan duk ba wacce zata burgeni acikinsu" ya faɗa yana mai mikewa tare da gyara kwalar rigarsa.

Murmushi tareeƙ yayi kafin yace "amma yallaɓai yau idan Madam ta ganka zaiyi wahala ta gane ka ,dan kuwa kayi matuƙar kyau Masha Allah,yau lafiya ayarimanka sai" tareeƙ ya faɗa yana mikawa Adeeb wani takobi ,wanda ke matukar gyalli da ɗaukar ido.

Murmushi ne yakub cewa adeeb,jin tareeƙ ya ambaci Madam,kallon kansa ya karayi cikin madubi,masha Allah,ko aljanu ya kalli Adeeb to tabbas dole saiya yaba kyau da Allah yayiwa adeeb.

" Kasan bata da lafiya ma,kuma bazata je gurin taron nan ba,zata zauna tare da nanny ,acikin gida,dan haka muyi sauri muje In dubawa sai mu wuce " Adeeb ya faɗa yana mai rataya takobin.

Murmushi tareeƙ yayi yana mai jin dadi cikin zuciyarsa,tabbas hasashensa yana neman zama gaskiya,dan kuwa ya kula Adeeb ya faɗa kogin SOYAYYA ,wanda hakan yayi masa daɗi,fattu itace daidai da Adeeb." Yallaɓai kayi kama da mai son zuwa ganin budurwarsa fa" tareeƙ ya faɗa yana ɗan sosa kansa.

Ƙeyarsa adeeb ya ɗan buga kafin yace " ka manta dai ba budurwa ba ,mata zakace ,kuma kasan hakkin ta ne induba lafiyarta ,kafin na sawwaƙe mata,iya muje" Adeeb ya faɗa yana mai kamo hannun tareeƙ.

Murmushi tareeƙ yayi yana mai cewa " zaka dawo hanya ma yallaɓai" ya faɗa cikin zuciyarsa.

Suna fitowa kuwa hadiman da suke ƙofar part ɗin suka ɗauka kirari da bushe bushe irin na larabawa,runtse ido Adeeb yayi cike da damuwa,dan shikam wannan bushe bushe baya so ,dan dai ba yadda zaiyine.

Cikin takun izza da isa yake takawa ,tareeƙ yan gefensa sai hadiman dake binsa baya suna busa.

Kai tsaye ya wuce part ɗin ammi,da gudu su zayyad suka taho suka rungume ,Adeeb cike da murna ,dan kuwa sun saba dashi sosai.dagsu yayi daya bayan ɗaya yana dariya ,

Gimbiya suhaimat ma cike da murmushi take kallon Adeeb,yaron yana burgeni sosai,yana da nutsuwa ga don yara,har ƙasa ya durƙusa ya gaida gimbiya suhaimat,da amminsa, sosai ammi ke yaba kyan da Adeeb ɗin yayi,wani lambu ta ɗauko na na zinare ta sanya masa hannunsa ,tare da wani turare mai kanshi daɗi.

Murmushi yayi tare da mata godiya sosai,kafin ya ɗan juyo yana kallon gimbiya suhaimat,haka kawai yaji gabansa ya fadi sosai ,wani tunanine ya ɗarsu cikin zuciyarsa ,saidai da sauri ya kawar da batun daga ransa,ya yayi waje .yana gab da ficewa saiga gimbiya Zulaihat ta shigo part ɗin ,taci uban ado kamar wacce zata gasar sarautar kyau.

Kallo daya Adeeb yayi mata ya kauda kansa tare da haɗe fuska.

Ita kuwa neman gigicewa tayi da yadda taga Adeeb yayi kyau,cikin hanzari ta tari gabansa tare da kamo hannunsa tana mai jin kamar ta rungume shi.

Wani shegen kallo da Adeeb ya watsa mata ,bata san lokacin datayi saurin sakin hannunsa ba ," kayi kyau my prince"ta faɗa tana wani narkar da fuska cike da tsantsar ƙaunar Adeeb ɗin.

Harara ya watsa mata tare da tsaki kafin ya bar gurin cikin sauri.

Kai tsaye part ɗin nanny suka shige ,tana zaune afalo ,gefen ta kuma ,wani ɗan karamin akwatine mai kyau da ɗaukar ido.

Zama sukayi shida tareeƙ suka sata atsakiya, gaida ta sukayi,ta amsa cikin farin ciki tana mai shafa kan Adeeb,akwatin nan ta buɗe tare da ɗauko wani zobe mai kyau sosai ta zira masa ayatsansa na dama.

Murmushi yayi tare da sumbatar zoben kafin yace " tana ina " ya faɗa cikin salonsa yana ɗan yamutse fuska.

"Tana ciki magajin faɗa " nanny ta faɗa .

Tashi yayi cikin nutsuwa ya nufi dakin da fattu ke zaune.....

Masu karatu ina barar addu'ar ku,iftila'in rusau ne ya faru agarinmu,wllh gidaje sai rushewa suke,,dan Allah ku samu cikin addu'a bayin Allah suna cikin damuwa sosai ,shiyasa kukajini shiru kwana biyu,abin ya taɓa har anguwar da mahaifiyata take

Muna buƙatar addu'ar ku.

Na gode

Mrs babi ce□□

[8/6, 9:01 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

_____Tashi Adeeb yayi cikin nutsuwa, da takunsa irin na jaruman maza ,ya nufi ɗakin da fattu ke ciki.

Fattu na zaune abakin gado, tayi shiru kamar mai tunanin wani abu,Adeeb ya turo ƙofar da sallama ɗauke abakinsa,saidai idan ba ka kasa kunne ba ,to bazakaji me yake faɗi ba.

Dago Kai fattu tayi jin muryar Adeeb  datayi,baki buɗe take kallon Adeeb ,tunda take arayuwarta,zata iya cewa bata taɓa ganin mutum mai kyau irin na Adeeb ba ."masha Allah"fattu ta faɗa tana mai mikewa tsaye fuskarta ɗauke da murmushi,ta ƙure Adeeb da ido kamar yau ta taɓa ganinsa.

Ƙarasowa Adeeb yayi cikin ɗakin,shima idonsa na kanta ,dan haka kawai yaga tayi masa kyau shima .

Ɗan hararta yayi kafin yace " Please karki cinyeni da kallo mana"ya faɗa yana ɗan wani gwabe fuska cikin shagwabar da baisan yayi ba.

Da sauri fattu ta sanya hannu tare da rufe fuskarta tana ɗan dariya ,dan kunya taji da yadda yayi salon maganar tasa.

"Hamma kayi kyau sosai ,kai mai kyaune" fattu ta faɗa kanta a ƙasa tana ɗan mirza hannunta.

Wani irin sanyi ne yake ratsa zuciyar Adeeb, sosai yaji daɗin maganar fattu ,dan haka cikin wani irin shauƙi ya mika hannunsa tare da dago habarta .kallon juna suke ido cikin ido,murmushi Adeeb yayi kafin yace "kin tabbata nayi kyau a idonki? wankana yayi miki kyau?" Ya faɗa yana mai kallon lips ɗin fattu ,wanda yake ji kamar ya cinyesu.

Lumshe ido fattu tayi tare da jinjina kai tace " Hamma bantaɓa ganin mutum mai kyan ka ba,kuma Ni kullum ma kyau kakemin" ta faɗa tana ɗan riƙe lips ɗin ta na ƙasa da haƙoranta.

Wani irin abu Adeeb yaji yana masa yawo ajikinsa,sosai yake jin yana son rungumar fattu ajikinsa ,duk lokacin da yake tare da ita yakan tsinci kansa cikin wani irin shauƙin son kasancewa da ita .

Murmushi yayi tare da shafa gefen fuskarta yace " to me zaki bani matsayin kyautar dazan fita gurin taro da ita?" Ya faɗa idanunsa akan lips ɗin ta.

Shiru fattu tayi tana ɗan rarraba ido,to ita me take dashi ma ?dazata ba Hamma?

"Hamma Ni bani da komai fa ,bansan me zan baka ba.

Kallonta yake baya ko ƙiftawa ,ajiyar zuciya ya sauke yana faɗin " shikenan tunda ba abinda zaki bani,zan tafi,amma karki fito ko ina kinji?ki kwanta kiyi barci da zaran mun tashi daga gurin taro zanzo in ganki "Adeeb ya faɗa yana mai kallon fuskarta.

Jinjina kai fattu tayi tana mai kallon Adeeb ɗin,sai taji bataji daɗi ba ,ace ya tambaye ta wani abu ita kuma bata bashi ba,kuma duk abinda take dashi ma ai shine ya siya mata,to mezata bashi?fattu ta faɗa cikin zuciyarta ,fuskarta ɗauke da yanayin damuwa.

Ahankali Adeeb ya fara takawa zuwa bakin ƙofar fita daga ɗakin haka kawai yake jinsa wani iri, sam baya don rabuwa da fattu yau ɗin nan.ganin yana neman fita yasa Fattu ta tako da sauri tare da rungumeshi ta baya.

Dammm!dammmmm!!dammmm!!!gaban Adeeb ya bada wani sauti na bugawa.

Cikin hanzari ya runtse idanunsa,dan yadda yaji fattun ajikinsa ,abin yazo masa cikin bazata.

"Hamma kayi haƙuri wllh bani da abinda zan baka ,amma indai na tara kuɗina zan siya maka cin-cin burodi,nima baffa ke siyomin idan yaje gari, ka fadi abinda kake

so nayi maka yanzun" ta faɗa tana mai gyara kanta dake kwance tsakiyar bayan Adeeb.

Cikin dauriya da jarumta Adeeb ya sanya hannunsa ya jawo fattu zuwa gabansa.bude idanunsa yayi dasuka fara rinewa sai wani lumshewa da budewa yake .

Ido ya ƙura mata na wani lokaci,kafin ya matso da fuskarsa zuwa gareta,ta yadda numfashinsa ke sauka akan Tata fuskar.

"Kin amince Ni na ɗauki Abinda nake ganin yayi amatsayin kyauta ta " Adeeb ya faɗa cikin  voice ɗinsa mai kama da yana mata raɗa.

Da sauri fattu ta gyada kanta ,dan yadda yayi maganar saiya sata jin wani iri atare da ita.

Lips ɗinta Adeeb ya kalla cike da tsantsar son jinsu cikin bakinsa.bai jira komai ba ya ɗora nasa lips ɗin nata.

Gaba ɗayansu sun shiga wani irin yanayi mai wuyar fassaruwa ,cikin salo da narkar da zuciyar mace Adeeb ke kissing fattu ,yayi da ita kuma take jin abin da yake mata har cikin ranta.idonsu alumshe yake sun lula wata duniyar ,dan tuni Adeeb ya mance da batun taro ,ya sami  lips ɗin fattu kamar ya sami lollipop.

Bugun da akeyiwa ƙofar ne yasa Adeeb saurin dawowa cikin hayyacinsa,ahankali ya zare lips ɗin sa daga bakin fattu yana kallonta .har lokacin idanunta alumshe suke ,sai sauke numfashi take cikin sauri,jikinta yana bari.

Bakin gado Adeeb ya zaunar da ita,tare da shafa gefen fuskarta yace " wannan ma ya isheni nishaɗi har agama taron ,antee sururi Hulwa" Adeeb ya faɗa yana mai juyawa ya bar ɗakin.

Saƙare fattu ta zauna abakin gadon kamar wata butumbutumi,haƙiƙa tana jin Hamma har cikin ranta,wani irin shauƙi takeji game dashi,sannan ko kaɗan bata jin damuwa idan tana tare dashi,lallai Hammanta shine farin cikinta,ga shi aduk lokacin

da Hamman nata ke sha mata baki tanajin wani irin nishaɗi sosai,ko me yasa ma yake sha mata bakin oho?

Murmushi tayi tare da shafa lips ɗin ta ,tanaji kamar har yanzu hamman na shan lips ɗin nata.

Taro yayi taro ta ko ina ka ƙalla jama'ane Malik a haɗaɗden ɗakin taron dake cikin masarautar,abie na zaune kan wata kyakykyawar kujera ta zinare, yayinda Adeeb ke gefensa shima zaune kan wata kujera mai shegen kyau da ɗaukar hankali.

Gaba ɗaya yan gidansu Adeeb suna zaune kan kujeru masu kyau,sai baki sarakuna da matayensu,kowa kagani yayi ado na kece raini,

Yan mata sai kaiwa Adeeb hari suke da idanuwansu da jikinsu, amma ba wacce ta ishe shi kallo acikinsu.

Anata jawabai da taya abie murnar dawowar ɗansa bayan tsawon lokaci da aka dauka ana nemansa.

Ammi na zaune ita da tawagarta,yayinda  gimbiya suhaimat ke kusa da ita ,sai sauran baƙinta, hakama amma na zaune tare da Tata tawagar cikin ado mai kyau.wata matace zaune agefenta tana ɗan kallon ammi,kafin ta juyo da kallonta ga amma tace " Dole saikinyi da gaske kafin ki gama da matar can,makircin ta yayi yawa,ina tsoron kaidinta"

Kallon ammi itama amma keyi kafin ta sauke ajiyar zuciya tace " karki damu Maryam,ninasan ta inda zan bullowa al'amarin nan,akwai Abinda ke ɗauremin kai sosai,game da gimbiya suhaimat,

ina don gano asalin gaskiyar abin kafin nayiwa ammi kwaf ɗaya,amma zanyi bincike sosai akan lamarin.

"Shikenan zan ci gaba da baki goyon baya ,Abdul lokacin da kike buƙatar taimakona ƙofa abude take" cewar matar.

Godiya amma tayi mata cikin murmushi,

Nan dai suka ci gaba da tattauna akan yadda zasu ga bayan ammi.

Rashad na hango zaune cikin wani kaya masu kyau irin na sarauta,fuskarsa ɗauke da murmushi,ya kafe Adeeb da ido baya ko kiftawa.wayarsace tayi ƙara dan haka ya ɗauka tare da karawa akunnensa, har lokacin idonsa na kan Adeeb,wanda shima

hankalinsa yayo kan Rashad ɗin,kallonsa yake cike da tsana, tun lokacin da ya zaune yake kallon Rashad ɗin yana kula da duk wani motsinsa.

Dan kwata-kwata zuciyarsa bata yarda da Rashad ɗin ba,gani yake kamar akwai wani makircin da yake ƙullawa.

Dan haka ya sa tareeƙ ya kula da Rashad sosai.

"Ya kamata fa kaje ka aiwatar da abinda zakayi, kafin lokaci ya ƙure " ammi ta faɗa tana ɗan kallon gefen da Rashad ke zaune,waya kange akunnenta,da alam ita ta kira Rashad ɗin.

Wata dariya Rashad yayi kafin yace " ammina ta kaina ,ina sane da lokaci,yanzu zan tashi domin cike burina, yau saina hana Adeeb barci da irin aika -aikar da zanyi masa" Rashad ya faɗa idanunsa ƙur akan Adeeb, wanda ya  Dan rangwafo kusa da mai martaba ,da alama suna magana ne.

Kashe wayar ammi tayi tare da sauke wata ajiyar zuciya mai ƙarfi,kafin ta kalli gimbiya suhaimat tace " Ni kuwa suhaimat  ina wannan sarƙar taku ta ahali, bana gajiya da kallonta ko kaɗan ,naga banganta atare da ke ba" ammi ta faɗa tana mai kallon gimbiya suhaimat.

Murmushi matar tayi kafin tace " har abada bazan taɓa rabuwa da wannan sarƙar ba,dan kuwa itace shaidar dazata sadani da yʻata, Aduk inda take,ina ji ajikina mun kusa haduwa da juna kuma nayi alƙawarin saina ɗauki fansar rabani da ita da akayi na tsawon shekaru,akan koma waye keda hannu cikin al'amarin " ta faɗa idanunta cike da kwallah.kafin ta ɗan daga mayafin jikinta ,saiga sarƙar ta bayyana ,ƙurawa sarƙar idanu ammi tayi,tabbas wannan irin sarƙar wuyan yarinyar can ce ,hakan na nufin fattu itace ɗiyar suhaimat da suka rasa shekarun baya?innalillahi wa'inna ilaihir raji'un.banga ta zama ba. Cewar ammi cikin zuciyarta.

Da sauri ta miƙe tana mai faɗin "suhaimat ina zuwa "bata jira amsar taba tayi gaba.

Rashad ma ganin ammi ta mike yayi saurin bin bayanta dan zuwa ga fattu,yau kam za'ayi ta ta ƙare.

Zulaihat dake zaune cikin ƙawayenta tana ta zuba izza da iyawa ,ganin su duka biyun sunyi waje hakan yasa itama ta mike cikin sauri ta rufa musu baya, dan kuwa

tare zasu aikata mugun nufin nasu akan fattu,  tana son ganin komai ya wakana akan idonta ,

Ko ina zasu kuma oho?

Muje zuwa masu karatu,

Manage please har yanzu muna cike da alhini.

Na gode sosai da addu'ar ku garemu,waɗanda suka kirani,da waɗanda sukayi min ta waya.

□□

Anty mammy ce

Mrs babi□□

Share and comment fisabilillah.

[8/7, 7:26 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

_____Abakin ƙofar hall ɗin Zulaihat ta tarar da Rashad ,yana tsaye da waya ahannunsa ,da alama kira yake ƙoƙarin yi,saidai yana ganinta ya maida wayar cikin aljihunsa yana mai faɗin,"yawwa dama ke nake ƙoƙarin kira,sai gaki kin fito.

Ƙarasowa Zulaihat tayi kusa dashi ta tsaya" ya ake ciki ne ?" Ta faɗa tana ɗan waigen bayanta.

"Yau burina zai cika ,zan sami abinda ke hanani barci,kuma zanyiwa Adeeb illah,saina rama dukan da yayi min akan yarinyar da yake iƙirarin yar amanar da ce,bayan kuma Ni nasan dadironsa ce ,kawai kishine da mugunta sukayi masa yawa,shine ya hanani Nima in ɗana"cewar Rashad yana mai kallon Zulaihat.

"Kaga Rashad karka ƙara cewa dadiron my Prince ce,karkayi masa sharri,dan kuwa nasan halinsa nasan koshi waye,wllh bazai taba ajiye yarinyar nan dan biyan buƙatarsa ba,mutumin da har maganin sha'awa nake saka masa alemo,dan kawai yayi tarayya dani,amma duk yadda ya galabaita bazai koda rungumeni ba.

Dama dai kaine akace ka ajiye ta dan biyan buƙatarka,to wannan kam na yarda dan nasan kai din namamajo ne " Zulaihat ta faɗa tana mai galla masa harara,dan taji haushin sharrin da yayiwa adeeb,ita da take burin ace itace zata fara bude Adeeb aledarsa ina zataso jin wannan batu.

Wani shegen kallo Rashad ya watsa mata kafin yace " banza  yar tasha ,ke har Ni zaki cewa na mamajo? Ai duk iskancina ban kaki ba,kefa yar maye ce sannan jarababbiya, Ni kaina sau nawa ina taimaka miki ?ina ce wataran har guduwa nake saboda jarabarki ?zaki raina min hankali wawiya kawai" Rashad ya faɗa cikin faɗa.

Haushi sosai ya kama Zulaihat ,ranta ya ɓaci da kalaman Rashad gareta ,wato har gori zaiyi mata ,dan ta neme shi kusan sau uku ?ba komai zai gane kurensa wllh.

"Ni kakeyiwa gori Rashad ?to wllh kasani bazan taimaka maka akan ƙudirinka na yauba ,saidai kayi kai kadai ,banza marar mutunci" Zulaihat ta faɗa cikin ɓaci rai tana mai barin gurin cikin sauri.

Tsaki Rashad yayi yana mai faɗin"aikin banza ,da me zaki iyamin agurin banda kema kice kina so intaimaka miki ,Ni kuwa ranata ta yau duka ta fine baby ce,yar ƙwaya kawai " ya faɗa yana mai nufar part ɗin ammi.

Ammi kuwa tana zuwa part ɗinta cikin ɗakinta ta nufa ,ƙullewa tayi tare da zama bakin gado,tana tunani iri iri cikin ranta, wata akwati ta ɗauko  dake can ƙasan gadon ta tare da budewa,

Tana buɗewa wani hayaƙi yayo sama baƙiƙirin dashi,banda wari ba abinda ke tashi cikin hayaƙin nan,da sauri ammi ta toshe hancinta, tana mai zaro ido waje,abayyane ta furta " na shiga ukuna ba dai kwalbar nan ta fashe ba? Shikenan ta faru ta ƙare ,dama nasan hakan zata faru wayyo Allah na" ammi ta faɗa tana mai bin wata kwalba yar gajeriya da ta tarwatseda ido,wani farin abu mai kauri yana ta motsi kamar tsutsa.

Bugun ƙofar da ammi tajine yasata saurin rufe akwatin ta tura can kasan gado,saita kanta tayi cikin ɗauriya ta nufi ƙofar .

Rashad ta gani tsaye abakin ƙofar ,"ammi ya ake ciki ne ?ta yaya zan ɗauki yarinyar ne ?kinsan ba aɗakin ta zan aiwatar da ƙudirina ba,dan wancan mayen zai iya zuwa ya cin mini" ya faɗa yana kallon fuskar ammi .

"Ka tafi can ɗayan part ɗina ka jira zan kawo maka ita da kaina ,ina son kayi mata abinda nan da wata guda ma bazata san inda kanta yake ba,bana son ka tausaya mata ko kaɗan"ammi ta fada fuskarta ahaɗe.

"Kada ku damu ammi bazan taɓa baki kunya ba,nayi alƙawarin saina yi mata abinda Bama ki tsammata ba"Rashad ya faɗa yana wani irin killer smile.

Ficewa ammi tayi tare da nufar part ɗin su fattu.ba kowa afalon,dan kuwa nanny ta ɗan leƙe gurin taron ,ganin fattu kwance tana barci.

Cikin ɗakin ammi ta shiga ,tsaye tayi agaban gadon da fattu ke kwance ,idanunta arufe kamar mai barci,amma idanunta biyu,hammanta kawai  take tunani.

Kusan minti uku ammi tayi tana kallon fattu dake kwance ,tabbas ko tantama batayi ,wannan yarinyar gimbiya suhaimat ce ,dan kuwa sai yanzu take ganin tsantsar kamannin dake tsakaninsu,amma ta yaya suka haɗu da Adeeb?har ya taho da ita nan?wannan shine abinda take son sani.

Ganin fattu ta ɗan motsa ne yasa ammi ta ɗan kira sunanta " fateema tashi"

Ammi ta faɗa tana ɗan shafa kan fattu.

Ahankali cikin nutsuwa fattu ta tashi zaune tana ɗan mika ,dan ta jima akwance.

Murmushi tayiwa ammi tare da sunkuyar da kanta ƙasa cikin kunya .

"Fateema Sarkin kunya,ke kadaice aɗakin ne"ammi ta faɗa cikin Hausa ,dan kuwa ta iya Hausa sosai itama.

Jinjina kai fattu tayi tana wasa da yan yatsunta.

Murmushi ammi tayi tana shafa kan fattu kafin tace " to ya jikin naki,?"

" Da sauƙi inna"fattu ta faɗa cikin yar karamar muryarsa mai dadi.

"Kinga bai kamata ki zauna ke kaɗai anan ba kowa ba,dan haka maza ki tashi ki koma can ɗaya part ɗin sauki kwanta kiyi barcinki kinji?kafin tashi daga taron" ammi ta faɗa tana mai kamo hannun fattu cikin nata ,suka fice daga ɗakin.

Binta fattu tayi ba tare da ta musaba, dan tana tsananin jin kunyar ammi,saidai haka kawai taji gabanta na faɗuwa,gashi hammanta yace karta fita ko ina ,karya dawo bai ganta ba ransa ya ɓaci.

Haka dai tabi ammi har zuwa wancan part ɗin da Rashad take ciki.

Wani ɗaki ammi ta kaita tare da zaunar da ita akan kado,tace cikin murmushi"ki zamanki anan kinji,idan kina jin barci saiki kwanta,akwai abubuwan ci ,acikin fridge idan kinji bukatar ci" ammi ta faɗa tana mai kallon fattu ,fuskarta ɗauke da murmushi.

Jinjina kai fattu tayi kafin tace "inna !Hamma yace karbaje ko ina ,karya dawo kuma bai ganni ba"ta faɗa kanta aƙasa.

Wata uwar harara ammi ta bankawa fattu,kuji yar iyayi shegiya mai kama da aljanu,zaki gane kurenki, ne yau zaki yabawa aya zaƙinta,dagake har Adeeb ɗin.

Da sauri ta saki fuska tana murmushi,ganin fattu ta ɗago kai tana kallonta,"karki damu habeebtee zan sanar da Adeeb nina kawoki nan kinji?"ammi ta faɗa tana sumbatar goshin fattu .kafin ta fice daga ɗakin.

Rashad ta ci karo dashi abakin ƙofar ,daga shi sai wando iya gwuiwa da singlet,kallonsa ammi tayi cike da murmushi,tana mai faɗin"Rashad kenan,wannan zumuɗin haka?,nidai ka kula da maganata banson asami matsala" ammi ta faɗa tana mai kamo kunnensa.

Murmushi yayi yace "baki da matsala ammina,ke dai kawai kijira sakamako"ya faɗa yana mai murmushin mugunta.

"Amma ka jira sai an jima kadan,zan kulle ƙofar ta baya,inka gama sauka fice ta ɗayan ƙofar" jinjina kai Rashad yayi cikin zaƙuwa da son ammi tayi ta fice daga ɗakin.

Adeeb yana zaune kusa da abie ,saidai haka kawai yakejin gabansa na faɗuwa ,sosai yake jin faduwar gaban.fattu kawai yake tunani yana ji cikin ransa yana buƙatar ganinta ahalin yanzu.

Kallonsa ya kai inda Rashad ke zaune,saidai ba alamunsa agurin.gabansa ne ya ƙara mugun faɗuwa,ina Rashad ya nufa?yaushe ya bar gurin?

Da sauri ya yunƙura zai mike,dan zuwa ya duba fattu,saidai  gurin taron ne ya kara de da kiran sunansa Adeeb,ana buƙatar yayi jawabin godiya ga baki .

Kallon abie yayi cikin yanayi na marairaita ,amma abin ya jinjina masa kai alamun yaje yayi jawabin.

Haka Adeeb ya karbi lasifikar nan badan ransa yaso ba,burinsa kawai yaje gurin fattu.

Adaidai wannan lokacin kuma Rashad ya kulle ƙofofin ɗakin daga falon har zuwa toilet duka,ɗakin da fattu ke ciki kawai ya bari abuɗe .kai tsaye ya kunna kansa cikin ɗakin.

Fattu na zaune abakin gadon inda ammi ta zaunar da ita,zuciyarta sam bata aminta da zaman ɗakin nan ba, sai kalle kalle take,

Da sauri ta juyo atsorace jin kamar mutum atsaye akanta.

Ido huɗu sukayi da Rashad tsaye abakin ƙofa yana kallonta ,fuskarsa ɗauke da murmushi irin na yan duniya,

Da sauri fattu ta miƙe tsaye jikinta na rawa,me wannan mutum yake yi anan kuma? ba innar Hamma tace nan ma ɗalibta bane?innalillahi,wayyo hammana kana ina? fattu ta faɗa cikin ranta jikinta na rawa matuƙa.

Murmushi Rashad keta famanyi,yana takowa cikin ɗakin bayan ya kulle ƙofar,cikin harshen larabci yake faɗin"yan mata meye na tsorata haka?nimafa nazone nayi miki abinda wancan wawan yayan nawa ke miki,ki nutsu yarinya musha daɗinmu tare ,dan kuwa yau wllh ko mutuwa zakiyi saina kwashi daɗi" ya faɗa yana mai karasowa bakin gadon.

Kuka fattu ta fara tana mai yarfe  hannu, dan kuwa sosai take fahimtar yaren yanzu,dan haka ta fahimci da dama abubuwan daya faɗa,

"Wayyo Allah na kayi hakuri dan Allah ,wllh niba yar iska bace ,kuma Hamma baya min komai,kayi min rai dan Allah"fattu ta faɗa cikin kuka sosai tana ja da baya.

Zagaye suka fara ita da Rashad,yana ƙoƙarin kamota,ita kuma tana zillewa cikin kuka tana masa magiya,akan ya barta karya mata komai.

Ganin zata ɓata masa lokaci ne kawai yayi wani tsalle tare da damko gashin kanta cikin fushi ya wanka mata mari tare da hankaɗata kan gadon.

"Dan ubanki ki nutsu wllh idan kika ɓatamin lokaci,saina yi miki fata-fata anan gurin,kina abu kamar baki san me nake sanyi ba ,ko irin baki taba yi ɗin nan ba,shi wancan wawan idan yazo haka kike masa?Rashad ya faɗa cikin tsawa yana mai haurowa kan gadon.

Cikin azama fattu ta mirgina can karshen gadon tana kuka,tare da kiran "wayyo hammana kazo ,Hamma kazo ka taimakeni"

Ran Rashad ne ya ƙara ɓaci ganin zata ɓata masa lokaci,da sauri shima ya bita ya damko gashin kanta,ya ƙara wanke ta da mari, nan da nan gefen bakinta ya fashe jini ya fara zuba.

Ihu fattu ta kwalla cikin azaba tana kuka tare da riƙe hannunsa daya damko gashin kanta .

Ƙoƙarin Rashad yake ya haɗe bakinsa dana fattu ,amma sai kauda kai take tana kuka tare da juya kai.

Bakinta Rashad ta matse da karfin gaske ,gaba ɗaya kamaninsa sun sauya ,ba abinda yake so da buri illa yabiya buƙatarsa da fattu.gashi sai neman bashi matsala take.

Hannunsa ɗayan ya ɗora akan ƙirjin fattu ,zaro ido fattu tayi cikin tsantsar razana da jin hannunsa inda ba wanda ya taba ɗorawa,da karfi ta dunkule hannunta tare da buga masa aciki.

Ihu Rashad ya kwalla Dan kuwa ta bugeshi sosai acikinsa.

Hankaɗata yayi jikin bango ,aikuwa ta buga kanta ajikin bangon ,ji kake gummm!!ta gwara kanta.

Ihu ta kwalla cikin azaba tana mai dafe goshinta da jini ya wanke ,tsabar azaba numfashinta har ɗauke wa yake.

Ko tashi ta kasayi,da rarrafe ta nufi bakin ƙofa jini na zuba agoshinta.

Cikin mugun bacin rai Rashad ya nufota, rigarta ya kamo ta baya ya fizgota baya.

Mari yayi ta sauƙe mata har guda hudu,sannan ya cilla ta kan gadon,

Gaba ɗaya fattu ta fita daga hayyacinta ,ko hannunta bata iya dagawa,numfashinta sai kaiwa da kawowa yake,

Rashad kuwa cikin rashin imani ya zare wando sa tare da singlet yayi kan fattu gadan -gadan ,yana zuwa ya janye gadon tare da kama rigar fattu ya yagatadaga sama har ƙasa ,sannan ya.....

Wayyo fattu ,Hamma kana ina kazo ka ceci fattunka,shikenan Rashad zai cutar da fattunka .

Da gudu na fice dan nemo inda Adeeb yake .saiki biyoni muje nemansa tare.

Taku ce anty mammy Mrs babi□□

Share and comment fisabilillah

More comment

More typing.d

[8/9, 9:13 AM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Gaba ɗaya Rashad ya zama kamar wani mahaukaci,ba abinda ke gabansa face biyan buƙatarsa.

Gaban rigar  fattu ya kama da karfin tsiya ya tsargeta ,tun daga sama har ƙasa.

Nan da nan farar best ɗin fattu da baƙin skin tite ɗin ta suka bayya, Allah ma yasa wandon har ƙasa yake.

" Wllh yau ko da zaki mutu ,saina ida nufina akanki,banga wanda zai iya karbarki daga hannuna ba" Rashad ya faɗa cikin wata irin murya ta azzalumai,waɗanda suka manta da cewar Allah yana kallonsu duk abinda suke aikatawa.

Da gyar fattu ta iya buɗe rinannun idanunta ,wanda tsabar mari da kuka suka sanya idanun kumbura sosai.

Ahankali take daga lips ɗin ta magana take amma saiƙa kura mata ido zaka fahimci me take cewa."wallahu galibun ala amrina" shine abinda take ta maimaitawa abakinta.

Ƙoƙarin zare skin tite ɗin Rashad keyi amma sam ya kasa,jikinsa sai rawa yake,yana jin kamar wanda ake jona masa  shocking,Amma tsabar masifa da jaraba ,yaki fasa abinda yakeyi,

Cikin haushi,ya ƙara kaiwa kumatun fattu mari mai zafi da shiga jiki."Dan ubanki me kikasa ajikinki?idan na taɓaki nakejin kamar ana zuƙemin  jini?"Rashad ya faɗa yana mai kai fuskarsa saitin Tata,bakinsa ya ɗora akan na fattu,aikuwa ba wata wata fattu ta gartsa masa cizo alips ɗinsa.kara ya kwalla yana mai komawa gefe dafe da lips ɗin sa na ƙasa "kai -kai -kai Ni kika ciza Dan uwarki?zaki gane kurenki ,wllh yau saina kusan kasheki Shegiyar yarinya mai taurin kai"Rashad ya faɗa yana mai danƙo gashin fattu ,wanda yayi buju-buju.

Fattu fa ko motsin kirki bata iyayi,gaba ɗaya jikinta ya saki,tunda take a rayuwarta,bata taɓa shiga tashin hankali da azaba irin na yauba.

Sunan Allah kawai take ambata cikin ranta.

Adeeb kuwa cikin gaggawa yayi jawabinsa tare da godiya ga baƙin da suka zo dan tayashi murnar dawowa gida cikin ƙoshin lafiya.sosai ƙirjinsa ke mugun bugawa zuciyarsa  kamar zata fito waje,idanunsa sunyi jajur dasu,wani irin ɗaci yakeji cikin zuciyarsa,sannan ko dana second ɗaya ne fattu taƙi barin tunaninsa.

Gefen da Rashad ke zaune Adeeb ya ƙara kai dubansa, baya gurin har zuwa yanzu,kai gaskiya akwai Abinda ke faruwa ,dole yaje ya duba Hulwa.

Dan haka cikin hanzari ya mike tsaye ,kallonsa abie yayi tare da tambayar ina zashi haka ?ya mike cikin hanzari,sanar da abie yayi cewar kansa ke ciwo yana son yaje ya kwanta.

Sanin da abie yayi cewar ,sam Adeeb yana son hayaniyane,yasa shi cewa yaje ya kwanta sannan yasha magani,akwai maganar da zasu yi zuwa dare.

Cikin sauri da sassarfa Adeeb ya nufi ƙofar barin hall ɗin,yana ɗan kallon gefen da tareeƙ ke zaune,saidai baiga tareeƙ agurin ba.dan haka ficewa yayi daga hall ɗin yana mai  takawa da sauri sosai.

Bangaren nanny ya nufa kai tsaye,yana shiga ya tarar da tareeƙ da nanny atsaye cirko -cirko,gabansa ne ya ƙara faɗuwa ,da sauri ya karasa gurin nanny yana kallonta,"nanny Ina Hulwa?"ya faɗa cikin muryar damuwa.

Kallonsa nanny tayi itama da alamun  damuwa akan fuskarta tace " to magajin fada,nan da ka ganmu wllh ita muke nema,naje gurin taron can kenan,na barta tana barci,kuma ina dawowa naga bata ɗakin,na duba ko ina cikin bangaren nan banganta ba,saiga tareeƙ kuma yana tambayar ko Rashad ya shigo nan"

Da sauri Adeeb ya nufi ɗakin da fattu ke zaune gabansa naci gaba da bugawa da ƙarfi.

Ko ina ya duba amma bata nan,to ina taje?yasan dai ba yawo takeyi ba ,ba inda ta sani cikin fadar nan,ko part ɗin sa ma sau ɗaya ya kaita,da sauri ya juyo yana kallon tareeƙ," Ina Rashad yayi?"ya tambayi tareeƙ cikin wata irin murya mai kama da ta basawa.

"Yallaɓai ina zaune naga lokacin da Rashad  ke waya,kuma saiya fito waje,hankalina bai kwanta da fitowar sa ba,dan haka saina biyoshi,ina fitowa na hangesu shida Zulaihat,dan haka na buya ina sauraron me zasuce,yallaɓai amma banji me suke tattaunawa ba,saidai ga dukkan alamu akwai abunda suka ƙulla tare, sai dai kuma basu sami jituwa ba,dan kuwa cikin fushi suka rabu.

Nayi ƙoƙarin bin Rashad Dan ganin inda ya nufa amma ban ganshi ba" tareeƙ ya faɗa yana kallon Adeeb cikin damuwa.

Dafe kai Adeeb yayi zuciyarsa na masa zafi,lallai idan har wani abu Rashad ke ƙoƙarin aikatawa akan Hulwa ,to zai gane kurensa wllh azeem,saiya ɗanɗani kudarsa.

Cikin sauri Adeeb ya nufi ƙofar fita daga part ɗin,tareeƙ ya na biye dashi,ganin zasu fice yasa nanny tayi saurin bin bayansu dan bazata iya zama ba.

Suna fita daga part din,  kai tsaye Adeeb part din ammi ya nufa,ko fattu can ta tafi,saidai suna gab da shiga ya tsinkayi Muryar ammi na kiran sa,tsayawa yayi harta ƙaraso,"lafiya na ganku haka afujajan?gashi ka bar gurin taro ba'atashi ba?"ammi ta faɗa tana karantar yanayin Adeeb.

Ahankali Adeeb ya sauke wata ajiyar zuciya mai zafi,tare da lumshe idanu kana yace "ammi mun rasa inda yarinyar nan tayi ne ,shine zamu duba ko tana party ɗinki" Adeeb ya faɗa cikin yamutsar fuska kamar zaiyi kuka.

"Hmmmmm ji dan Allah wai akan wannan Shegiyar yarinyar suka tada hankalinsu haka,dan kawai basu ganta ba.

Tukunnama wllh sai kunga yadda rayuwarta ta koma yanzu,dan nasan Rashad ya kammala aikinsa"ammi ta faɗa cikin zuciyarta,amma azahiri,

Cikin hanzari ta riƙo hannun Adeeb tana mai zaro ido." Ikon Allah ina kuma ta nufa? dan gaskiya  bata part ɗina, sai dai kuma ɗazu naga Rashad yana shawagi tsakanin part ɗina Dana nanny,Allah yasa bashine yayi mata wani abu ba" cewar ammi tana mai dafe kai cikin nuna tsantsar tashin hankali.

Gaban Adeeb ne ya fadi ,shikenan dama yasan hakan zata  iya kasancewa, dan kuwa sam yau bai yarda da Rashad ba dama ,"innalillahi "Adeeb ya faɗa cikin ruɗu da tashin hankali.

Da sauri ya kunna kansa cikin part ɗin na ammi,suka rufa masa baya.

Saidai nan ma sunyi iya bincike su amma bata nan,wasa -wasa fa sune har part ɗin Rashad Amma bashi ba Hulwa,zuwa wannan lokacin Adeeb ya shiga tsantsar tashin hankalin da bazai misaltuba,gaba ɗaya fuskarsa tayi jaaa kamar manja, idanunsa sun koma kala kalan nan,idan ya buɗe baki har wani turiri zakaga yana fitowa daga bakin nasa.

Hankali kowa ya tashi,tsakanin ammi ,tareeƙ ,nanny dakuma amma ,wacce ta tsincesu abangaren Rashad,Dan itama  nemansa tayi ta rasa agurin taron,shine tazo dubawa ko part ɗin sa ya dawo.

Sai kuma ta riskesu suna dubansa.sosai tashiga tashin hankali,karfa Rashad ya janyo mata wata sabuwar matsalar,amma tasan ma bai zama lallai abinda suke zargi ya kasance ba.

Cikin wani irin voice Adeeb ya juyo yana kallon amma tare da fara magana " wllh ! wllh!!wllh!!! idan wani abu ya sami hulwa ta silar ɗank,i nayi alƙawarin saina illatashi,ta yadda ke kanki bazaki so ganinsa ba" Adeeb ya faɗa yana mai nuna amma da ɗan yatsanshi, tsabar masifa da bala'i kumatunsa har rawa suke.

Cikin tsoro amma ta ja baya tana mai dafe ƙirjinta ,dan kuwa ta tsorata da yanayin na Adeeb,tana kuma fatan Allah yasa ba hannun Rashad aɓatan fattu.

Can kuwa wajen taro ,anyi addu'oi,kuma anci  ansha taro ya tashi lafita,abie yana ta tunanin ina iyalin nashi suka nufa ,dan baiga kowa agurin taron ba,zuciyarsa na raya masa akwai Abinda ke faruwa ,dan haka kai tsaye bayan ya sallami baƙinsa ya nufi bangaren sa ,jakadiyarsa ya tura cikin gida dan ta gano masa ko lafiya.

Adeeb yana gama korawa ammi warning yayi waje cikin zazzafar zuciya da jin jikinsa yana masa wani irin rawa,idanunsa gaba ɗaya ya rine zuwa kalar na macizai.tsoro sosai ya kama su ammi da nanny,hatta tareeƙ atsorace yake,dan bai taba ganin yallaɓan nashi cikin wannan yanayin ba.

Part ɗin sa ya nufa kai tsaye,saidai yana zuwa saitin ɗaya part ɗin  na ,ammi yaji zuciyarsa ta tsananta da  bugawa ,cak yaja ya tsaya tare da ƙure ƙofar part ɗin da idanunsa.zuciyarsa na raya masa ya shiga ya duba,saidai yana tunanin ammi bata fiye amfani da bangaren nan ba ,kuma me zai kawo Rashad nan ma ?

Idan kuma yazo nan ɗin da Hulwa dan kawar da tunaninka fa ?ɗayar zuciyar ta bashi amsa.dan haka ba bata lokaci ya kama handle ɗin kofar ya murza da zummar shiga,saidai kuma akulle yaji ƙofar ,hakan ya matukar bashi mamaki,dan kuwa kullum part din nan abuɗe yake ,koda ammi bata ciki akwai hadimai acikinsa.amma how comes yau zai kasance akulle haka.nan take zuciyarsa ta bashi lallai Hulwa na cikin part ɗin nan.daidai lokacin su ammi suka ƙara so gurin.kallon tareeƙ yayi cikin wata irin murya yace " na tabbata Hulwa na cikin nan,saidai ina mamakin yadda part ɗin ya kasance akulle karon farko" ya faɗa yana kallon ammi,wacce tayi wiƙi - wiƙi tsoro ya ɗan bayyana akan fuskarta.

Dan kuwa Adeeb ya kafeta da mayun idanunsa.sam ba zargin ta yake ba,kawai yana tunanin yadda aka yaudareta ne itama har akayi amfani da part ɗinta.dan baya raba ɗaya biyu cewar Rashad na cikin part ɗin.

Cikin in-ina ammi tace "habeebe a.a.a...k.wai spy ..kk...eyy " ta faɗa cikin jan numfashi.

Kallonta tareeƙ yayi cike da zargi,dan shikam harga Allah tun farko ita ya zarga dan yasan bakin nufin ta akan  abun daya shafi Adeeb sarai.

Amma ma kallon ammi take cike da tuhuma,karfa tuggu ta haɗawa Rashad Dan kawai tana son ganin bayanta?

" Wai wannan wane irin wandone kika sa ?kusan minti nawa ina ƙoƙarin cirewa amma na kasa?wllh idan ma wani siddabarun kikayiwa wandon nan yaƙi fita,to zanyi abuna ahaka, dan ubanki yau ɗin nan nayi alƙawarin ,sai Adeeb yayi kwanan baƙin ciki "Rashad ya faɗa yana hankaɗa fattu kan wani ƙaton tebur dake ajiye gefen gado ,da alama an ajiyeshine ɗan ɗora kofuna ko abinci idan bukatar hakan ta taso.

Aikuwa tana fadawa ta fada kan wani glass cup, nan da nan  ya tarwatse gaba ɗaya ya sossoketa aƙirjinta da wuyanta.wani marayan ƙara fattu ta sanya ,wanda koshi Rashad baiji sautin ƙaranba, dan kuwa muryarta tayi mugun dashewa.ahankali idanunta ke lumshewa yana budewa,gaba ɗaya jini ya bata farar best ɗin dake jikinta.amma bako imani bare tausayi haka Rashad yake ƙoƙarin keta mata haddi, ba tare da ya cire koda wannan skin tite ɗin ba.

Wata irin zabura Rashad yayi sakamakon ƙaran da fattu ta kwalla,wanda yayi daidai da ƙarar  faduwar kofar dakin .

”RASHAD!!!!!!....."

Aka kwallah kiran sunan Rashad Wanda saida Rashad ɗin ya buge kansa ajikin tebur ɗin nan tsabar razana da yayi da wannan kiran sunan nashi da akayi.....

Hmmmmm masu karatu,nima tsabar tsoro bansan sanda wayar hannuna ta fadi kasa ba,mutara zuwa gobe idan na ɗauki wayar .fatana dai wayata bata fashe ba.

Mrs babi ce□□

Share and comment fisabilillah

More comment

More typing.

[8/10, 10:15 AM] +234 813 332 3143: □□□□□□□□

MACIJI NE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

_____"RASHAAADDDD"

Aka kwallah kiran sunan Rashad,Wanda saida ɗakin ya amsa.gaba dayan mutanen da suka shigo ɗakin saida suka tsorata ,saboda yadda amon Muryar ya fito da mugun ƙarfi da sauti mai firgitarwa.

Ahankali fattu da ke neman macewa ta buɗe kunburarrun idanunta  da gyar,ta saukesu akan fuskar hammanta, wata shashshekar kukace ta zo mata ,numfashinta na hawa da sauƙa ,da gyar ta daga hannunta tana mikawa Adeeb ,

Da wani irin mugun sauri Adeeb yayi kanta yana mika mata nashi hannu,saidai kafin ya ƙara so tuni hannun nata ya koma ƙasa sharaff!! Ahankali kuma idanunta suka kulle ,duk wata jijiya dake jikinta tasaki,ataƙaice dai fattu ta sume.

Wani irin ƙara Adeeb ya kwalla mai matukar firgitarwa ,hayaƙi na fita ta bakinsa da hancinsa, hannun fattu ya kama ya riƙe cikin nashi tare da damkewa kamar zai balla hannun nata.

Jikinsa gaba ɗaya rawa yake  kamar ana kaɗa masa gangi,ɗago da kansa yayi afusace ya sauke idanunsa akan Rashad,Wanda tsabar tsoro ya kasa koda matsawa daga kan table ɗin gashi tsirara haihuwar uwarsa.

Da sauri Rashad ya runtse idanunsa,numfashinsa na wani irin hawa da sauka kamar shima zai shide tsabar tsoron ganin yadda idanun Adeeb ya koma,ga wani irin bakin hayaƙi daya fara cika ɗakin,

Wani ƙaran Adeeb ya sake kwalla,wanda yafi na farko sanya tsoro da razani,gaba ɗaya dakin yayi wani irin bakiƙirin ,baka ko ganin hannunka bare na kusa dakai.

Su ammi da amma,nanny tareeƙ ,jakadiya,da Zulaihat wacce zuwan ta kenan,bangaren dan ta sami labari gurin yan s.i.d ɗinta.gaba daya tsoro ,firgici da tsantsar mamakin abinda ke faruwa yasa sun kasa koda motsine agurin ,bare suyi wani abu.

Sun ƙanƙame juna jikinsu yana wani irin bari,nanny Banda sunan Allah ba abinda take ambata"innalillahi wa'inna ilaihir raji'un, meye wannan ke shirin faruwa haka,tareeƙ kana ina bana ganin komai fa " nanny ta faɗa tana ƙanƙame tareek dake kusa da ita.

Shi kansa tareeƙ jikinsa rawa yake ,sam ya kasa magana sai rungume mahaifiyarsa da yayi sosai ajikinsa.

Ƙaran rashad ne ya karaɗe dakin ,cikin wani irin sauti na azaba,wanda kana jinsa kasan wanda ke wannan karan yana cikin azaba da halin ƙunci.

Kuka kawai amma ta sanya ,dan tasan yau kam ɗan ta sai abinda hali yayi,shikenan yau abinda ake shukawa agidan ya dawo kansu.

Ahankali ɗakin ya fara washewa daga tsantsar duhun da yayi ,kusan minti uku suna cikin halin tsoro da razani kafin ,suka fara ganin komai tar-tar .

"Innalillahi wa'inna ilaihir raji'un"shine abinda Dukansu suka haɗa baki wajen faɗa,sakamakon ganin wani narkeken maciji mai girman gaske nannade da Rashad ,Wanda kallo ɗaya zakayiwa Rashad kasan cewa ba alamun numfashi atare dashi.

Kallon kallo ake tsakanin mutanen dake cikin dakin,wanda suka shiga tashin hankali fiye dana farko,dan kuwa ba Adeeb aɗakin sai wannan narkeken macijin,wato dai Adeeb shine ya zama wannan macijin.

Jikin nanny Banda rawa ba abinda yake ,haka ammi da amma,jakadiya da Zulaihat wacce tuni ta jiƙa jikinta da fitsari,tana tsaye ƙanƙame da amma wacce itama ta ƙanƙame Zulaihat ɗin.

Sun kasa magana sai kallon ikon Allah suke.

Macijin nan yana tsaye nannade da Rashad ya fasa kai yana wani irin huci da fesar da wani irin bakin abu daga bakinsa.juyi ya farayi da ƙarfi kafin ya maka rashad ajikin bango,ji kake timmmm!!Rashad ya baje akasan tyles,tuni jini ya fara zubowa daga kansa.hakan bai ishi macijin nan ba ya kara zuwa ya nannade Rashad tare da kara makashi jikin bango.

Ihu suka farayi ganin macijin nan na ƙoƙarin tarwatsa kasusuwan Rashad.

Da gudu jakadiya ta juya tayi waje tana ihu ,ta nufi part ɗin mai martaba,tana faɗuwa tana mikewa,gaba ɗaya bata cikin hayyacinta.

Zulaihat ma silalewa tayi agun ba alamun numfashi atare da ita.

"Wayyo jama'a ku taimaka min ,zai kashemin yarona,wayyo Allah na na shiga uku ku taimaka min"amma ta faɗa cikin ficewar hayyaci,dan tsabar tsoro gadan gadan take nufar cikin dakin gurin da Rashad ke kwance ayashe, aikuwa kafin ta ƙarasa kaiwa inda Rashad ke kwance, saijin wani abu tayi mai kama da bulala ya fyadeta a gadon bayanta,wani ihu amma ta kurma tare da faduwa sakamakon azabar raɗaɗin da taji gadon bayanta ya ɗauka.da rarrafe ta koma inda take tsaye. Jikinta na rawa .

Ammi fa tsoro ya gama kasheta,dan ko tsayuwar kirki ta kasayi, sam batayi tsammanin haka abin yake ba,ashe dai da gaske mutum yana iya komawa wata halittar ta hanyar asiri?lallai yau taga abinda ya fi ƙarfinta , sam bata tsammaci abun haka yake ba, amma dole tayi wani abu dan gudun zargi.dan haka cikin bugawar zuciya da tsananin tsoro ta fara takawa zuwa gurin da Adeeb ke tsaye yana zagaya Rashad yana huci.

"A...a.ddd..ee.e.bbb."ammi ta kira sunansa cikin tsinkewar numfashi, shikuwa baiko kalli inda take ba ,burinsa kawai yaga Rashad yayi motsi ya kara karairaya masa inda bai gama lalacewa ba.

"Ka nutsu Adeeb ɗana,.n...i.cce ammin ...ka, ka ...ka...ji."ta faɗa tana matsawa cikin tsoro da firgici.

Ai kuwa jin takunta da adeeb yayi ,afusace ya juyo tare da kai mata tsafka, cikin sa'a kuwa ya damketa,ihu ta farayi tana neman taimako,"wayyo Allah na taimako jama'a taimako"ammi ta faɗa lokacin da Adeeb ke nannaɗeta kamar buhun goro.saida yagama naɗeta sannan ya fasa kansa saitin fuskar ammi yana huci.tsabar firgici tuni ammi ta sume ,kura mata ido Adeeb yayi kafin ya fara dakinta ahankali ,ta faɗa kan gado.

Gurin fattu ya koma tare da hawa gadon bayanta, nade ta yayi tare da mirgina ta ta juyo rigingine,kallon fuskarta yake wani irin farin Ruwa na zubowa daga idanunsa ,kwanciya yayi akan cikinta yayi lamo yana mai juya kansa ,tare da yin wani irin ƙara  yana bude bakinsa.

Al'amarin yayi matuƙar tsorata dukkan wadanda ke cikin dakin,dan nanny ma tuni ta sume ,amma ce kawai mai ƙarfin hali ,dan tana zaune riƙe da bayanta da tasha bulala.

Tareeƙ kuwa hawayene ke zuba daga idanunsa.yana matukar tausayawa yallabai ɗin nasa.

Ana cikin wannan halin ne,abie ya shigo dakin tare da waziri da  manyan faɗa ,sai Shaikh lateef ,babban malamine dake koyar da ilimin addini sannan masani akan abinda ya shafi jinya da maganinta, ya ƙware sosai wajen magance abun daya shafi sihiri.

Lokacin da jakadiya ta kaiwa abie labarin,shikuma suna tare da su waziri suna ɗan tattauna wata magana mai muhimmanci,shine suka garzayo gaba ɗayansu, ɗan ganin abinda ke faruwa.

Ba ƙaramin kaɗuwa abie yayi ba,lokacin da ya wannan kumurcin macijin amatsayin Adeeb ɗinsa,hawaye ne kawai ke zuba cikin idanunsa, ya ƙurawa Adeeb ɗin ido.tunanni kawai  yake ,waye wanda yayiwa adeeb wannan aika -aikar?me yatsarewa wanda yayi masa haka?ace yaro mai gata dan sarauta kamar Adeeb yana zama maciji?duk yadda Adeeb ya kasance mai tausayi da taimakon al'umma ,amma ashe wasu suna can suna shirya masa mugunta.lallai dole ya tsaya tsayin daka ,wajen bawa yaronsa abin sonsa kariya ta ko wacce siga.yasan ammi na ƙoƙarin wajen yiwa adeeb addu'a ,kuma tana sawa ayi masa kamar yadda take faɗa amma dole shima ya dage ta bangarensa.

Abie ne ya kalli Shaikh lateef,cikin damuwa da zubar hawaye yace "Shaikh kaga Adeeb ga ,kaga halin da yake ciki,menene abinyi ?abie ya faɗa yana mai share kwalla.

Shaikh lateef kuwa wanda tun shigowar su yake kallon Adeeb,kallo na tsinake,sai lokacin yayi ajiyar zuciya kana ya kalli abie,yace" ranka shi daɗe lallai Adeeb yana cikin tsaka mai wuya ,da tuggun maƙiya ,amma In Sha Allah komai yazo ƙarshe,yanzu dai ayi ƙoƙarin diban bayin Allah dake kwance dan akaisu ga likita,sannan sai musan abinda ya kamata muyi"Shaikh lateef ya faɗa yana mai kallon abie.

Nan da nan kuwa aka kwashe su ammi da nanny,Zulaihat ,sai dai ko yaya akayi yunƙirin zuwa inda Rashad ke wance kamar gawa,take macijin nan zaiyo kan mutum afusace.

Ganin haka ya sanya abie cikin ƙarfin hali ya tunkari Adeeb dake fagen fattu yana fasa kai,ya kasa ya tsare,

Ahankali abie ke kallon Adeeb da idanuwansa masu fidda hawaye kafin yace"habeebee kayi hakuri adauke dan uwanda,dan asuba lafiyarsa, koma me yayi maka nine nan,zan ɗaukar maka mataki,bazan taɓa yarda da zalunci ba"Abie ya faɗa cikin sanyin murya yana kallon Adeeb.

Huci kawai Adeeb keyi yana kallon Abie kafin ya maida kansa ga fattu yana kallonta,sannna ya ɗago kai ya kalli abie,

Jinjina kai abie yayi cike da fahimtar Adeeb ɗin yace "na fahimta habeebee,dole zan ramawa yarinyar nan abinda rashad yayi mata,dan kasan ba'a zalumci amasarautata" abie ya faɗa yana mai ƙara sawa kusa da Adeeb ɗin ahankali ya sanya hannunsa yana shafa bayan Adeeb.

Shikuwa Adeeb sai huci yake yana guri da wata iska mai matukar zafi.haka aka samu aka lulluɓawa Rashad Abu ajikinsa kafin kayi waje dashi, amma duk yadda akayi ƙoƙarin ɗauke fattu Adeeb ya hana ,dan hatta mai martaba ,da yayi yunƙurin daukar ta saida Adeeb ya kai masa tsafka.haka suna ji suna gani ba yadda suka iya,sai lulluɓe mata jiki da sukayi itama ,dan kuwa yaƙi barin jikinta ma.

Shaikh lateef ne zaune gaban Adeeb yana karanto wasu addu'oi yana tofa masa,lokaci guda jikin Adeeb yayi laushi, gaba ɗaya baya ko kwakwkwaran motsi,sai huci da yake fiddawa ,ya dora kansa akan ruwan cikin fattu dake lulluɓe,jikinsa sai wani bakin hayaƙi ke fita.

Ci gaba Shaikh lateef yayi da addu'ar sa yana tofawa Adeeb,yayin da su abie ke gefe guda suna kallon ikon , Allah,dan zuwa lokacin murƙususu kawai macijin nan keyi,kafin wannan hayaƙin ya turnuke dakin,baka iya ganin komai tsabar duhu.

Su abie suma addu'a suka fara,lokacin da suka ga wanan hayaƙin,dan Shaikh lateef yace karsuji tsoron komai ,duk abinda zasu gani kawai suyi addu'a.

Can kusan wucewar mintuna biyar suna ta addu'oi ,dakin ya fara haske yana washewa har ya gama washewa tar, kamar ba shine yayi wannan duhun ba.

Adeeb ne durƙushe agaban wannan table ɗin da fattu ke kwance,kansa har lokacin yana kan cikin fattu.

Hamdala Abie da su waziri sukayi,ganin Adeeb ya dawo asalin halittarsa, dan abie yayi matuƙar tsorata, kar ace ahaka Adeeb ɗin zai zauna.

Ahankali Adeeb ke buɗe idanunsa ,da har zuwa lokacin basu gama komawa normal ba.

Kanshi ya daga da gyar yana ɗan yatsine fuska tare da dafe kan,dan ciwo yake masa sosai.

Sai kuma yayi saurin zabura ya mike tsaye "Hulwa" shine abinda ya faɗa cikin daga murya yana waige waige,

" Habeebee ka nutsu kaji ga hulwar taka nan kusa da kai "abie ya faɗa yana mai mikewa shima tare da riko kafadun Adeeb.

Sai lokacin Adeeb ya ga su abie aɗakin,kallon abie yayi kafin ya kalli inda abie ke nuna masa,zaro ido yayi ganin hulwarsa kwance kamar gawa,"Hulwa " Adeeb ya faɗa yana mai girgiza fattu,amma ina Hulwa tayi nisan zango.

Janyota yayi zuwa jikinsa ya rungumeta tare da fashewa da wani irin kuka mai tsanani ciwo da zafi.irin kukan da Adeeb keyi kaɗai zai fahimtar da kai yadda yake jin Hulwa da kuma ciwo acikin ransa.

"Rashad !

Rashad !!

Rashadddd!!!ka tabka babban kurkuren ƙoƙarin tabamin mata,kayi kurkure,idan Hulwa ta mutu"yayi shiru yana mai goge hawayen dake kwatanta cikin idanunsa,kafin ya ɗago idanunsa da suka yi wani irin mugun jaaa,ya kalli Abie sannan yaci gaba"wllh billahi,saina kashe Rashad ,idan har matata ma mutu sanadin sa"Adeeb ya faɗa cikin karfafa murya da nuna gaskiyar abinda yake fadi har cikin ransa.

Kallonsa kowa keyi acikin ɗakin,dan kuwa sun zama speechless,matarsa yake ta kira,kodai yarinyar nan amatsayin matarsa take?ko kuma yana nufin ita zai aura?

Shine abinda yake ta yawo cikin zukatan su Abie.

"Ya kamata akai yarinyar asibiti yanzu,nikuma zanje gida domin yin bincike akan larurar prince ranka shi dade"cewar Shaikh lateef yana mai mikewa tare da shafa kan Adeeb,dan yana tausayawa yaron sosai.

" Haka ne Shaikh bari akaita asibiti yanzun nan " cewar abie yana mai kallon Adeeb dake ƙankame da Hulwa kamar zai maidata cikinsa.

Kafin su ankara tuni Adeeb ya sungumi fattu yayi hanyar barin dakin da ita." Habeebee kayi hakuri akai yarinyar asibiti,kaima fa ba cikakkiyar lafiya gareka ba" cewar abie kenan ,ganin Adeeb na ƙoƙarin ficewa daga ɗakin.

" Ba wanda zai kara tabamin mata abie ,domin itaɗin mallakina ce mata tace ta Sunnah,hakkin kula da ita yana kaina,dan haka bana bukatar taimakon kowa,karka manta ,likitanci bangarenane" yana faɗin haka yayi waje da fattu rungume aƙirjinsa.

Kai tsaye fart ɗinsa ya nufa da fattu ,yana zuwa ya shimfiɗeta akan lafiyayyen gadonsa, kallo yabi jikinta dashi,cikin wani irin zafi da ƙunar zuciya,gaba ɗaya glasses sun maƙale ajikinta ,jini duk ya bata mata jiki.hatta fuskarta baka ganewa.

Gimbiya suhaimat ce tsaye tana bin Adeeb da kallon sabe da yarinya akafadunsa,haka kawai gabanta ke tsananin bugawa,so kawai take taga yarinyar,

Ko menene ya sameta oho?ahankali ta juya taci gaba da tafi zuwa dakin ammi,dan su basu san abinda ke faruwa ba.

Zuciyarta gaba ɗaya taki samun nutsuwa ,ba abinda take son gani sama da wannan yarinyar,gaskiya bazata iya jurewa ba dole taje taga yarinyar,sannan ta san meke damunta?me yasame haka gaba ɗaya jikinta jini...

Masu karatu ku biyoni dan jin gimbiya suhaimat zata je ganin fattu ne ko yaya?

Taku anty mammy

Mrs babi □□

Share and comment fisabilillah.

More comment more typing

[8/11, 1:34 PM] +234 813 332 3143: □□□□□□□□

MACIJI NE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Gimbiya suhaimat ta gama tsara cewa data huta zataje part ɗin Adeeb dan ganin yarinyar nan,

Saidai shigarta part ɗin ammi da yanayin da taga ammin yasa ta saurin,ƙarasawa cikin dakin ,cikin damuwa take faɗin"ukktee meke damunki? Yana ganki akwance? gimbiya suhaimat ta faɗa tana kamo hannun ammi ,wanda ba'a daura mata ruwa ajikinsa ba.

Ahankali ammi wacce tayi nisa cikin tunani ta buɗe idonta tana kallon gimbiya suhaimat,kafin ta sauke ajiyar zuciya tare da lumshe ido ta buɗe" ke dai bari suhaimat,yau naga abinda ban taba gani ba arayuwata,nan ta bata labarin abinda ya faru,saidai ta boye mata asalin labarin fattu,sai cewa tayi wata baiwa ce Rashad ɗin yayiwa fyade,dan ita atunanninta Rashad yayiwa fattu fyaɗen.

Sosai gimbiya suhaimat ta tausayawa yarinyar,sannan tayi Allah wadai da halin Rashad,zuciyarta na tsananin bugawa ,har cikin ranta take jin tausayin yarinya.kuma tayi alwashin ,saitaje taga yarinyar nan kafin ta bar ƙasar.

Rashad kuwa kai tsaye aka wuce dashi,lafiyayyen asibitin dake masarautar,emergency akayi dashi,cikin gaggawa likitoci suka duƙufa akansa dan ceto rayuwarsa.

Dan da dama cikin likitocin , sunyi tunanin hatsari ya samu mai muni.

Karon farko ruwa suka fara ɗauka masa,kafin suka fara bincikarsa,karayama kusan biyar ce ajikinsa, bayan munanan raunuka dake jikin sa,sannan since kansa ya bugu ,dole sai sunyi bincike akwakwalwarsa, dan tabbatar da lafiyarta.

Amma kuka take sosai cike da tarin damuwa da baƙin ciki ,meyasa Rashad zaiyi mata haka?me yasa gaba ɗaya halayyar Rashad ta sauya ne?da ɗan ta mai hankaline da nutsuwa ,sannan yana bin maganarta,amma daga baya ya fandare ya zama gagararre,yanzu ga irin abinda ya jama kansa.karaya har biyar ajikin mutum.Nan dai taci kukanta ta ƙoshi,tana zaune gefen ɗan ta.

Nanny ma ta farfaɗo ,hankalinta amatukar tashe ,tana zaune hawaye na zuba cikin idanunta,yayin da tareeƙ ke rarrashinta cikin kwantar da murya.

"Kayya tareeƙ abinnan na magajin faɗa,ya isheni yaron nan tun yana ƙuruciya yake haɗuwa da tuggun maƙiya,har zuwa girmansa,yaushe ne zai sami salama shima,kadufa wai Adeeb ne ya zama wannan ƙaton macijin,wanda idan awani gurin ka ganshi,sai inda ƙarfi ka ya ƙare wajen ceto rayuwarka.

Yanzu idan haka ta faru dashi awani gurin yunkurin kasheshi fa zasu yi"nanny ta ƙarasa cikin kuka tana fyace majina.

Hannunta tareeƙ ya kara damƙewa cikin nashi,kafin yace " wai ummeee yaushe zasu sanar da gaskiyar da muka jima da sanine?yaushe zamu taimakawa yallaɓai mu haska masa hanya danya gane irin haɗari dake  bibiyarsa arayuwa?na gaji da boye gaskiya ummeee kiyi wani abu"tareeƙ ya faɗa cikin damuwa.

"Tareeƙ baka san masarautar ya take ba,idan baka iya kama ɓarawoba ,to shi zai kama ka,dole mubi komai asannu,akwai lokacin bayyana gaskiya kaji?kayi hakuri"nanny ta faɗa tana mai shafa kan ɗan nata.

Yanzu ya jikin ɗiyata yake ?shikenan yanzu yaron nan ya lalata nata rayuwa?ya karbi budurcinta awulaƙance sannan tana cikin al'ada ?kai ban taba ganin fajiri irin

Rashad ba,Allah ya saka miki ɗiyata"nanny ta faɗa cikin kuka sosai,tana tausayawa fattu.

Tareeƙ ma runtse ido yayi zuciyarsa na masa zafi,dan kuwa yasan ahalin yanzu Adeeb yana can cikin bakin ciki da damuwa,saidai shikam yana ganin kamar Rashad ɗin bai sami damar yiwa fattu fyaɗen ba suka karaso, yana kuma fatan Allah yasa hasashensa yazama gaskiya.

Akan gado Adeeb ya shimfida fattu,wacce ke kwance kamar gawa,bata ko motsi,gaba ɗaya jini ya wanke mata fuska,jikinta ko ina raunine ,dan kuwa ba ƙaramin azaba Rashad ya gana mata ba,lips ɗin ta sun bushe idanunta ya kumbura sosai.

Runtse ido Adeeb yayi lokacin da idanunsa suka sauka kan wuyanta zuwa ƙirjinta ,fasassun kwalabe duk sun soketa, zama yayi abakin gadon,cikin wata irin karaya da zafin zuciya.ji yake kamar yaje ya kama Rashad yayi gutsin-gutsin dashi,

Hannunta ya kama na dama ,ya riƙe cikin nashi,gam-gam .jikinsa sai rawa yake ,yama kasa aikata komai akanta.wai hulwarsace kwance agabansa kamar gawa.

"Why Rashad ?why ?duk matan dake cikin fadar nan sai matata?me yasa zaka aikata haka agareni?Adeeb ya faɗa afili yana mai kaiwa bango naushi, ji yake kamar zuciyarsa zata kama da wuta.

Da sauri ya mike tare da ɗauko first aid box ɗinsa, dan Adeeb cikakken likitane akan fannin lafiya yayi karatunsa .

Farar vest ɗin fattu  data yage kaɗan daga sama ya kama,wacce ta rine da jini, ya cire mata ahankali,nan da nan albarkatun ƙirjinta suka bayyana,cikin faduwar gaba Adeeb ya kawar da kansa ga barin kallonsu,zuciyarsa na ci gaba da bugawa. haka ma ya zare wannan dogon wando dake jikinta ya ajiye gefe,ya rage daga ita sai pant Wanda shima gaba ɗaya yayi stairs saboda yadda jini ya ɓalle mata ,tsabar yadda ta shiga ruɗu da razani.

Hannun Adeeb karkarwa yake ya kasa aikata komai,dan haka cikin sauri ya janyo ƙaton bargonsa ya lulluɓe fattu dashi,iya saman ƙirjinta zuwa kanta ya bari abuɗe.

Sosai ya tausayawa fattu lokacin da yake cire mata kwalaben nan,dan kuwa taji ciwo da yawa,ko yaya ya taba gurin da kwalbar take saita zabura kamar zata farfaɗo.

Haka dai ya gama cire mata kwalaben nan,tas yayi mata dressing ɗin duk inda ya kamata, ya sami ruwan zafi da towel ya goge mata jikinta .sai dai kuma ba wani kayan da pant da kuma pad ɗin dazai canja mata.

Dan haka rigarsa ya ɗauko fara ƙal ,doguwar ya zura mata, kafin ya dauko mata kayanta,dan kuwa yana tunanin ta dawo nan part ɗinsa da zama kenan.  Ƙarin Ruwa ya sanya mata ,kafin ya nufi ƙofa, kai tsaye ya kulle ƙofar ya fita zuciyarsa kamar wuta haka yake jinsa,ya nufi part ɗin nanny.

"Tareeƙ na roƙeka kada kace zaka sanar da magajin faɗa komai ahalin yanzu,dan kuwa bamu da kwararan hujjoji akan hakan ,ka bari nan da lokaci kankanin shida kansa zai gano komai,zamu nuna masa hanya ta yadda zai fahimci abubuwa da dama" nanny ta faɗa tana rike da hannun tareeeƙ.

Umme wllh zuciyata zafi take,Aduk lokacin dana ga yallaɓai cikin wani halin,yana zagaye da maƙiya ,amma bai sani ba,shi yana zaune dasu zuciya ɗaya ....

"Su waye maƙiyan nawa?sannan wace gaskiyar ce ake boyemin?"

Suka tsinkayo Muryar Adeeb yana faɗin haka  cikin sautin da ba wasa acikinsa.

Da sauri suka juyo gaba ɗayansu, dan basu tsammanci ganin Adeeb ɗin awannan lokacin ba.

"Magajin faɗa yaushe ka shigo?ya jikin naka?ina ɗiyata take ?"nanny ta faɗa cikin inda-inda da son n kawar da zancen.

Ƙura mata ido Adeeb yayi cike da tuhuma ,gaba ɗaya ta daburce.da alama akwai abunda take boyewa ita da tareeƙ .kallonsa ya dawo dashi kan tareeƙ wanda kansa ke ƙasa ,shi yaji dadin jinsu da Adeeb yayi,fatansa ɗaya ayi komai yau akare.

"Tareeƙ, what wrong me kuke ɓoyemin? Dama  akwai Abinda zaka iya boyemin tareeƙ ?na dauke tamkar kanina da muka fito ciki daya,why tareeƙ?" Adeeb ya faɗa yana kallon tareeƙ.

Kallon nanny tareeƙ yayi,yana jin ba dadi cikin ransa,dama yasan watarana hakan zata iya faruwa,shi baiga amfanin biye boyen ba , amma suna haɗa ido da nanny tayi saurin girgiza masa kai,alamun karya ce komai.

"Tareeeƙ,am tolking to you me kuke hidden mini?kada kusa na fara zarginku fa,Please nanny,bayan ammina da abie, ku kadaine mutanen dana yarda dasu arayuwata,ku kaɗai ne waɗanda nake ganin bazasu taba cutar dani ba,karki karyamin zuciya nanny, Please me kuke ɓoyemin?" Adeeb ya faɗa cikin wata kalar murya mai cike da tsoron kar ace nanny da tareeƙ suma suna daga cikin maƙiyansa .

"Ka kwantar da hankalinka magajin faɗa,wllh har abada bazamu taba cutar da rayuwarka ba,saidai mu bata kariya, amma kasani akwai mutanen da kake kallo matsayin maƙiyanka,saidai sam,ba haka abin yake ba. azahiri kake ganinsu matsayin maƙiya,amma abaɗini sune masoyanka na haƙika.

Su kuma wadanda kake kallo matsayin masoya,suke son ganin bayanka, sune waɗanda suke cin dunduniyarka,Adeeb ka kula kazamo mai lura da mutanen da kake tare dasu " nanny ta faɗa tana mai riƙe da hannun Adeeb,fuskarta ɗauke da damuwa.

Kallonta kawai Adeeb keyi,tunda ta fara maganarta  ,me take nufi kenan?su waye ya yarda dasu ,kuma suke cin dunduniyarsa?

Sannan suwaye yake wa kallon maƙiya ,alhalin sune masoyansa na asali?kallon nanny yayi cike da tarin tambayoyi zuciyarsa na harbawa da gudu.

"Nanny ban fahimceki ba,me kike nufi da kalamanki? Please kiyimin bayanin da zan gane"Adeeb ya faɗa yana kallon nanny,idanunsa sun kada sunyi jajur dasu.

Ajiyar zuciya nanny ta sauƙe mai ƙarfin gaske,sannan tace magajin faɗa ,idan baka manta ba,shekaru kusan sha takwas mijina da kuma gimbiya nazli sunyi haɗari

suka mutu,sanadiyyar wuta data kama motar da suke ciki,harda yaranta mata su biyu,nanny ta faɗa tana kallon Adeeb,

Runtse ido Adeeb yayi da mugun ƙarfi,har abada bazai taba mantawa da wannan baƙar rana ba ,ranar data zamo mafi muni arayuwarsa.

Bude idonsa yayi wanda suka cika da kwalla yana kallon nanny kafin cikin rawar murya yace " tabbas nanny bazan taɓa mantawa da wannan rana ba,domin itace rana mafi muni arayuwata" ya faɗa yana mai lumshe idanunsa hawaye suka ziraro sharrrt.

"To kasani wannan haɗarin ba afkuwa yayi ba ,shiryashi akayi" nanny ta faɗa tana mai kallon Adeeb ,

Azabure Adeeb ya bude idanunsa,da suka gama zama jajur dasu,kallon nanny yake cikin kiɗima da ruɗewa" nanny kamar ya ban gane ba,me kike nufi da shiryashi akayi?waye ya shirya?kuma meye dalilin shiryawa?"Adeeb ya faɗa aruɗe.

Kamo hannunsa nanny tayi ta zaunar dashi akan kujera dan kuwa gaba ɗaya jikin sa rawa yake.

"Tareeƙ maza jeka kulle mana ƙofar nan"nanny ta faɗa cikin damuwa.

Ahankali tareeƙ ya nufi ƙofar tare da kullewa, yana jin sanyi aransa,koba komai yau zasu sauke nauyin da yayi musu bake bake acikin zuciya.

" Nanny kiyi saurin sanar dani, domin zuciyata gab,take da tarwatsewa,dan kaɗuwa" Adeeb ya faɗa cikin tsantsar zaƙuwa .

Ajiyar zuciya nanny tayi kafin tace " ina son ka saurari maganata da kunnen basira ,sannan kayi min kyakykyawan fahimta,kasani bazan taɓa cutar da kaiba, kuma duk abinda nayi nayine don tsiratar da rayuwarka" nanny ta faɗa hannunta riƙe dana Adeeb.

"Please nanny go street to the point kina kara sani cikin wasi-wasi" Adeeb ya faɗa cikin muryar damuwa ,jikinsa na rawa ,ba abinda yake son ji sai wanda ya shirya wanann haɗarin.

Mikewa nanny tayi tare da zuwa jikin window ta tsaya ,kallon Adeeb take tare da karantar yanayinsa, kamar yadda shima yake kallonta cike da ƙosawa.

Ahankali ta buɗe baki tace"ba kowa bane ya shirya wannan hadarin face .....

Wayyo masu karatu cajina ya kare ,amma karku damu mu tara anjima,

Nice dai anty mammynku.

Mrs babi□□

Share and comment fisabilillah.

More comment

More typing.

[8/11, 9:28 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□.

MACIJI NE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Tareda matemakiyanta

(Aseeyah ladan)

Page 59 60

_____ bayan

Shekara 35 dasuka wuce Ammi itace uwar gidan sarki tayi shekaru batataba heihuwaba sunnaima taimako harsun gaji gwatsam wata Rana maimartaba yatafi ziyara gun abokinshi sarkin Sudan saiyaga 'yar shi gimbiya nazli yace ma sarkin Sudan yaga iri anandai suka shirya komai aka daura aure kasan cewan suba kananun mutanebane yashirya yataho da amaryanshi misra tinda jakadiya takaima Ammi labari hankalinta bakaramin tashi yayiba to daga nanne Ammi tafara bin malamai da bokaye akan sarki karyakusanci amaryanshi gimbiya nazli saboda bataso tahaihu sedai Inda akasha banban gimbiya nazli macace maiyawan azkar dakatatun Qur'an shiyasa dik abinda tayi bayakamata tom saitafara makirci ahaka har Allah yabata cikin adeeb murna agun sarki ba amagana haka yadinga kyuta harda masu kujeran hajji masarautama cike yake dafarinciki kasan cewan zaasamu magaji kasancewan maimartaba mutunne adali shiyasa mutanan gari da fadawa suke matukar sanshi Ammi tayi bakinciki tankar zata mutu nandana sukashirya yanda zaazibar da cikin itada jakadiya tashirya tatafi gurin boka Dan tsogugi yayi tsafi iyaka Dan cikin yazube amma Abu yacitira nantake yashaidama jakadiya sai anhaifi cikin hankalinta bakaramin tashi yayiba sai yace mata akwai mafita guda daya bayan ta haihu zaasan yanda za ayi dayaron...

tommmm inanaiman afuwanku dayin karanbani

[8/12, 11:35 AM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

_____Ahankali nanny ta ke kallon Adeeb,kafin ta sauke ajiyar zuciya,tunani take ta yadda Adeeb zai karbi wannan magana,ta yaya zata sanar dashi cewar,amminsa itace silar faruwar komai?shin zai amince da abinda zata faɗa masa ko yaya? Wane irin kallo zai musu idan yasan cewa amminsa ce ta kashe sarauniya Nazli da yaranta tare da baban tareeƙ,kuma abakinsu?anya kuwa basu barowa kansu aiki ba?

"Nanny kiyi magana mana kinyi shiru, ki sanar dani wake da hannu akan hadarin nan?"

Da sauri nanny ta dawo daga dogon tunanin data tafi,kallon tareeƙ tayi cike da karayar zuciya ,amma cikin ƙarfafa gwuiwa tareeƙ ya kalli nanny yana mai jinjina kai da nuna alamun ,kwantar da hankali.

Ajiyar zuciya nanny ta sauƙe Tana mai kallon fuskar Adeeb,kafin ta fara magana.

"Magajin fada kamar yadda na faɗa maka,wasu abubuwan muna kallonsu ne ba a yadda suke ba,ka sani abinda zan faɗa maka ba ƙarya ,ba kuma cutarwa.shiru ta ɗanyi tana jinjina maganar kafin taci gaba"ba kowa ya shirya wannan hadarin ba, face Amminka"nanny ta faɗa tana mai kure Adeeb da ido.

Da wani irin slow Adeeb ya mike tsaye bakinsa bude,zuciyarsa na wani irin bugawa kamar guduma, ji yayi kunnensa ya ɗauki wani ƙara ƙuuuuuuuu!!!

Sai yake jin maganar ta nanny Tana rarrabewa,kamar baiji me take faɗi  daidai ba,jikinsa rawa ya kama,ta yadda yana mikewa tsayen yaji kamar zai fadi dan haka da sauri ya koma ya zauna,idanunsa ƙuri,akan fuskar nanny,

Cikin in-ina ya ke cewa"na...nan.,...y mek....Ike ..son....f..a...ɗ..I n..ee." ya faɗa numfashinsa na rarrabewa,ji yake kamar zuciyarsa zata fito tsabar yadda take bugawa.

Da sauri nanny ta ƙaraso kusa da Adeeb ta zauna ,cikin nutsuwa take shafa bayansa tare da kallon fuskarsa cikin tausayawa,dole yaji maganar tazo masa kamar saukar aradu."ka nutsu Adeeb  domin Abinda nake faɗa maka yana buƙatar nutsuwa,tabbas Amminka itace ta shirya wannan hadari,tare da taimakon wani ma aikaci dake cikin gidan nan,mai kula da harkokin motocin gidan"nanny ta faɗa cikin sanyin murya tana jin zafin rashin mijinta da uwar dakinta kamar yau abin ya faru.

Kallonta Adeeb yake cikin wani irin yanayi na mamaki ,al'ajabi,tsoro,ruɗu dakuma firgici,ji yake kamar zuciyarsa zata iya fashewa ako  wane lokaci,wannan wane irin magana nanny keyi?anya kuwa tana cikin hayyacinta?yaushe nanny ta koma maƙiyarsa ta hanyar hade kai da amma?dan su shiga tsakaninsa da amminsa? Dan kuwa yana tabbatar da cewa wannan shirin amma ne,lallai duniya ba tabbas .cikin zuciyarsa yake wannan maganar,kafin a fili ya kalli nanny ,sannan ya kalli tareeƙ,sai kuma yayi murmushi wanda yafi kuka ciwo ,sannan ya miƙe tsaye yana mai sanya hannunsa cikin aljihu,sannan ya fara magana bayan ya juya bayansa yana kallon bango" ban taba tsammanin cewa matar data raineni tun ƙuruciya zata iya hade kai da makiyana,ɗan ganin sun shiga tsakanina da ammina ba ,yau na kara tabbatar da cewa lallai wanda kake kallonsa matsayin masoyi ,to shine makiyinka aboye, amma bantaba tsammanin haka daga gareki ba nanny;Adeeb ya faɗa cikin zazzafar murya yana mai juyowa ,idanunsa sun kada sunyi mugun jaa, kallo ɗaya zaka masa kasan cewa zuciyarsa akaraye take.ci gaba yayi da cewa"nanny why ?why nanny me yasa zaki canja daga yadda na sanki?me yasa zaki so ganina cikin damuwa?na dauke ki tamkar mahaifiyata,duk wani abinda ya dameni ina zuwa gareki dan samun mafita,ammina tana kula dake da duk wani bukatun ki,amma meyasa kika hada kai da maƙiyanta?me yasa kika saida kanki dan bata alaka tsakanin da da mahaifiya? nanny why?tareeƙ me yasa nanny zatayi min haka?Adeeb ya faɗa yana mai riƙe kafadun tareeƙ idanunsa na zubda kwalla ,gaba ɗaya jinsa yake kamar ba shiba, wani sashen na zuciyarsa yana son karbar maganar nanny,saidai sashe mafi rinjaye na zuciyarsa na tunatar dashi wacece ammi agareshi,dan me zai yarda da batun nanny?.

Cikin damuwa da alhini tareeƙ ya kama hannun Adeeb ,cikin murya mai nuna tabbatarwa ,tareeƙ ke fadin, "yallaɓai ka kwantar da hankalinka,kuma kayiwa maganar nanny kyakykyawar fahimta,da sannu zaka gano gaskiyar dake cikin batunta, yallaɓai munsan abubuwa da dama wanda kai baka sansuba,amma da sannu zaka gane da kanka"tareeƙ ya faɗa cikin marairaita yana kallon Adeeb.

Fizge hannunsa Adeeb yayi tare da dafe kansa da yake jinsa kamar zai tarwatse,kafin ya kalli tareeƙ yana mai jinjina kai"well na gane ,na gane tareeƙ kaima kana bin bayan mahaifiyarka ko?da kai aka hada baki,am disappointed tareeƙ" Adeeb  ya faɗa yana girgiza kai cikin karayar zuciya,idanunsa na fitar da hawaye mai tsananin zafi da ƙuna.ahankali ya juya ya nufi ƙofa yana dafe kansa .

Cikin damuwa da zubda kwalla nanny ta miƙe da sauri tana kiran Adeeb" magajin fada karkayi saurin yanke hukunci akan maganata kana bukatar nutsuwa da bincike dan Allah ka yarda dani ɗana, bazan taɓa cutar da kaiba."nanny ta fada cikin zubda hawaye .

Ko waiwayowa Adeeb baiyi ba ya fice daga ɗakin ,cikin sauri, dan ko ganin fuskar nanny baya sonyi ahalin yanzu.zuciyarsa na tafarfasa ,ji yake kansa kamar zai kama da wuta.kai tsaye part ɗin ammi ya nufa ko zai sami salama cikin zuciyarsa.

"Tareeƙ ka gani ko?kaga Abinda nake faɗa maka,Adeeb ya riga ya makance,baya ganin laifin ammi ko kaɗan,yanzu bansan wane kallo zai rinƙa yi mana ba"nanny ta fada cikin kuka.

Kamata tareeƙ yayi ya zaunar da ita akan kujera ,hannunsa ya sanya yana share mata hawayen dake zuba daga idonta,kafin yace " ummee na,ki kwantar da hankalinki,dama shi aikin alheri haka yake,dole saika fuskanci ƙalubale,nasan yallaɓai zaiyi fushinsa na wani lokacin kafin ya sauko,kuma nasan daga yau zai fara bincike akan abinda kika sanar dashi,In Sha Allah muke da nasara ,tunda  akan gaskiya muke"tareek ya faɗa cikin yanayin ƙarfafawa mahaifiyar sa gwuiwa.

"In sha Allah tareeƙ ,Allah ya datar damu"nanny ta fada tana share hawayenta.

Ameen yace ,kafin suka ci gaba da tattaunawa akan matsalar.

Kai tsaye ya shiga part din na ammi,ko kula gaisauwar da hadimanta  keyi baiyi ba,dan zuciyarsa ba abinda take sai tafarfasa,bai taɓa tsammanin haka daga su nanny ba,lallai mutum bashi da tabbas.

Afalo ya ci karo da sarauniya suhaimat,tana zaune da yaranta,suna cin apple da ya'yan itaceya ,gefe guda kuma suna kallo.

Da gudu su zayyad suka taso suka rungume Adeeb suna murnar ganinsa,kansu kawai ya shafa tare da rungumarsu,shima.

Kallonsa sarauniya suhaimat keyi,dan kuwa taga tarin damuwa cikin idanunsa.

"Sannu yarima ,ya jikin naka?dana yarinyar ?"sarauniya suhaimat ta fada cikin yanayi na nuna damuwa .

Lumshe ido Adeeb yayi cikin damuwa da yanayinsa  na rashin son magana yace "da sauƙi"  atakaice .

"Allah ya bata lafiya " ta fada  da yanayi na damuwa.

"Ameen" Adeeb ya faɗa ahankali.

"Ammin naka tana ciki"sarauniya suhaimat ta fada cikin kulawa.

Kai kawai Adeeb ya jinjina mata kafin ya wuce zuwa cikin dakin.

" Bangane ba ?kamar ya nayi sakacin da kwalbar ta fashe,bayan irin kulawa da ita da nake?kasan irin kuɗin dana kashe akan akwatin da aka ƙera na sanya kwalbar ciki?

Shiru tayi ,da alama tana sauraron abinda ake faɗane daga can bangaren.

"Shikenan ,yanzu muna cikin alhini ne na wannan abun daya faru,dan haka kajira nan da kwana biyu,zan nemeka,dan awannan karon aiki nakeso ayimin na ban mamaki,bana kuma son asami matsala " ammi ta faɗa cikin wani yanayi mai nuna ta shirya mugunta mai zafi cikin ranta.

Gaban Adeeb ne yayi wata irin faɗuwa da har saida ya dafe ƙirjinsa,wane akwati ammi ke magana akai?wace kwalbar ce ta fashe?da wa ammi ke waya?waɗan nan sune tambayoyin da Adeeb ke yiwa kansa,saidai bashi da amsar ko daya daga ciki.

Ganin ammin ta gama wayar kuma tana ƙoƙarin juyowa ne ,dan ta ba ƙofa baya,yasa Adeeb saurin saita kansa yayi sallama tare da shiga.

Da sauri aɗan razane ammi ta juyo tana kallon Adeeb ɗin,dan batayi tsammanin ganinsa yanzu ba, saidai da alama baiji me take faɗi ba,itafa wllh tsoronsa ma ta fara ji yanzu,amma saita maze ta saki murmushi,tare da miƙa masa hannu,alamun ya ƙaraso gareta.

Ahankali Adeeb ke takawa har yaje bakin gadon ya zauna,dan jikinsa sam ba kwari,murmushin ƙarfin hali yayiwa ammi yana kallon fuskarta,

"Habeebee ya jikinka? na tsorata sosai da yanayin dana ganka ɗazu"ammi ta faɗa tana mai janyo Adeeb zuwa jikinta.

Sam yau Adeeb ji yayi baya wani jin dadin kwanciya akan cinyarta,Dan saiyajisa kamar akan ƙaya, dan haka da sauri ya tashi daga kwanciyar da yayi,kafin ya dan saki murmushi,yana mai cewa"ƙalau nake ammi,kada ki damu,ya naki jikin?"ya faɗa sam fuskarsa ba walwala.

"Shafa kansa tayi kafin tace naji sauki dana karka damu"ta faɗa tana kallon fuskarsa ,dan kuwa sam ba haka yake mataba,yau kam ba wannan shaukin da yake nuna mata idan suna tare.

Mikewa yayi yana mai faɗin ammi zanje in duba yarinyar can zan dawo anjima" yana faɗin haka yayi waje abinsa.

"Yawwa yarima ,ina son in duba yarinyar nan "sarauniya suhaimat ta fada tana mikewa lokacin da Adeeb ya zo zai wuce.

Shiru yayi yana ɗan nazari,akwai bukatar ta duba ta ,tunda likita ce itama ,kuma fannin mata ta karanta.

Dan haka yace "ok muje ,tana part ɗina"

Ficewa sukayi tare suka nufi part din Adeeb.

Toh masu karatu ,mubi su Adeeb dan duba Hulwa.

Sai mun hade next page.

Mrs babi ce □□

Share and comment fisabilillah.

More comment

More typing.m

[8/13, 12:15 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

_____Ahankali nanny ta ke kallon Adeeb,kafin ta sauke ajiyar zuciya,tunani take ta yadda Adeeb zai karbi wannan magana,ta yaya zata sanar dashi cewar,amminsa itace silar faruwar komai?shin zai amince da abinda zata faɗa masa ko yaya? Wane irin kallo zai musu idan yasan cewa amminsa ce ta kashe sarauniya Nazli da yaranta tare da baban tareƙ,kuma abakinsu?anya kuwa basu barowa kansu aiki ba?

"Nanny kiyi magana mana kinyi shiru, ki sanar dani wake da hannu akan hadarin nan?"

Da sauri nanny ta dawo daga dogon tunanin data tafi,kallon tareƙ tayi cike da karayar zuciya ,amma cikin ƙarfafa gwuiwa tareƙ ya kalli nanny yana mai jinjina kai da nuna alamun ,kwantar da hankali.

Ajiyar zuciya nanny ta sauƙe Tana mai kallon fuskar Adeeb,kafin ta fara magana.

"Magajin fada kamar yadda na faɗa maka,wasu abubuwan muna kallonsu ne ba a yadda suke ba,ka sani abinda zan faɗa maka ba ƙarya ,ba kuma cutarwa.shiru ta ɗanyi tana jinjina maganar kafin taci gaba"ba kowa ya shirya wannan hadarin ba, face Amminka"nanny ta faɗa tana mai kure Adeeb da ido.

Da wani irin slow Adeeb ya mike tsaye bakinsa bude,zuciyarsa na wani irin bugawa kamar guduma, ji yayi kunnensa ya ɗauki wani ƙara ƙuuuuuuuu!!!

Sai yake jin maganar ta nanny Tana rarrabewa,kamar baiji me take faɗi  daidai ba,jikinsa rawa ya kama,ta yadda yana mikewa tsayen yaji kamar zai fadi dan haka da sauri ya koma ya zauna,idanunsa ƙuri,akan fuskar nanny,

Cikin in-ina ya ke cewa"na...nan.,...y mek....Ike ..son....f..a...ɗ..I n..ee." ya faɗa numfashinsa na rarrabewa,ji yake kamar zuciyarsa zata fito tsabar yadda take bugawa.

Da sauri nanny ta ƙaraso kusa da Adeeb ta zauna ,cikin nutsuwa take shafa bayansa tare da kallon fuskarsa cikin tausayawa,dole yaji maganar tazo masa kamar saukar aradu."ka nutsu Adeeb  domin Abinda nake faɗa maka yana buƙatar nutsuwa,tabbas Amminka itace ta shirya wannan hadari,tare da taimakon wani ma aikaci dake cikin gidan nan,mai kula da harkokin motocin gidan"nanny ta faɗa cikin sanyin murya tana jin zafin rashin mijinta da uwar dakinta kamar yau abin ya faru.

Kallonta Adeeb yake cikin wani irin yanayi na mamaki ,al'ajabi,tsoro,ruɗu dakuma firgici,ji yake kamar zuciyarsa zata iya fashewa ako  wane lokaci,wannan wane irin magana nanny keyi?anya kuwa tana cikin hayyacinta?yaushe nanny ta koma maƙiyarsa ta hanyar hade kai da amma?dan su shiga tsakaninsa da amminsa? Dan kuwa yana tabbatar da cewa wannan shirin amma ne,lallai duniya ba tabbas .cikin zuciyarsa yake wannan maganar,kafin a fili ya kalli nanny ,sannan ya kalli tareeƙ,sai kuma yayi murmushi wanda yafi kuka ciwo ,sannan ya miƙe tsaye yana mai sanya hannunsa cikin aljihu,sannan ya fara magana bayan ya juya bayansa yana kallon bango" ban taba tsammanin cewa matar data raineni tun ƙuruciya zata iya hade kai da makiyana,ɗan ganin sun shiga tsakanina da ammina ba ,yau na kara tabbatar da cewa lallai wanda kake kallonsa matsayin masoyi ,to shine makiyinka aboye, amma bantaba tsammanin haka daga gareki ba nanny;Adeeb ya faɗa cikin zazzafar murya yana mai juyowa ,idanunsa sun kada sunyi mugun jaa, kallo ɗaya zaka masa kasan cewa zuciyarsa akaraye take.ci gaba yayi da cewa"nanny why ?why nanny me yasa zaki canja daga yadda na sanki?me yasa zaki so ganina cikin damuwa?na dauke ki tamkar mahaifiyata,duk wani abinda ya dameni ina zuwa gareki dan samun mafita,ammina tana kula dake da duk wani bukatun ki,amma meyasa kika hada kai da maƙiyanta?me yasa kika saida kanki dan bata alaka tsakanin da da mahaifiya? nanny why?tareeƙ me yasa nanny zatayi min haka?Adeeb ya faɗa yana mai riƙe kafadun tareeƙ idanunsa na zubda kwalla ,gaba ɗaya jinsa yake kamar ba shiba, wani sashen na zuciyarsa yana son karbar maganar nanny,saidai sashe mafi rinjaye na zuciyarsa na tunatar dashi wacece ammi agareshi,dan me zai yarda da batun nanny?.

Cikin damuwa da alhini tareeƙ ya kama hannun Adeeb ,cikin murya mai nuna tabbatarwa ,tareeƙ ke fadin, "yallaɓai ka kwantar da hankalinka,kuma kayiwa maganar nanny kyakykyawar fahimta,da sannu zaka gano gaskiyar dake cikin batunta, yallaɓai munsan abubuwa da dama wanda kai baka sansuba,amma da sannu zaka gane da kanka"tareeƙ ya faɗa cikin marairaita yana kallon Adeeb.

Fizge hannunsa Adeeb yayi tare da dafe kansa da yake jinsa kamar zai tarwatse,kafin ya kalli tareeƙ yana mai jinjina kai"well na gane ,na gane tareeƙ kaima kana bin bayan mahaifiyarka ko?da kai aka hada baki,am disappointed

tareeƙ" Adeeb  ya faɗa yana girgiza kai cikin karayar zuciya,idanunsa na fitar da hawaye mai tsananin zafi da ƙuna.ahankali ya juya ya nufi ƙofa yana dafe kansa .

Cikin damuwa da zubda kwalla nanny ta miƙe da sauri tana kiran Adeeb" magajin fada karkayi saurin yanke hukunci akan maganata kana bukatar nutsuwa da bincike dan Allah ka yarda dani ɗana, bazan taɓa cutar da kaiba."nanny ta fada cikin zubda hawaye .

Ko waiwayowa Adeeb baiyi ba ya fice daga ɗakin ,cikin sauri, dan ko ganin fuskar nanny baya sonyi ahalin yanzu.zuciyarsa na tafarfasa ,ji yake kansa kamar zai kama da wuta.kai tsaye part ɗin ammi ya nufa ko zai sami salama cikin zuciyarsa.

"Tareeƙ ka gani ko?kaga Abinda nake faɗa maka,Adeeb ya riga ya makance,baya ganin laifin ammi ko kaɗan,yanzu bansan wane kallo zai rinƙa yi mana ba"nanny ta fada cikin kuka.

Kamata tareeƙ yayi ya zaunar da ita akan kujera ,hannunsa ya sanya yana share mata hawayen dake zuba daga idonta,kafin yace " ummee na,ki kwantar da hankalinki,dama shi aikin alheri haka yake,dole saika fuskanci ƙalubale,nasan yallaɓai zaiyi fushinsa na wani lokacin kafin ya sauko,kuma nasan daga yau zai fara bincike akan abinda kika sanar dashi,In Sha Allah muke da nasara ,tunda  akan gaskiya muke"tareek ya faɗa cikin yanayin ƙarfafawa mahaifiyar sa gwuiwa.

"In sha Allah tareeƙ ,Allah ya datar damu"nanny ta fada tana share hawayenta.

Ameen yace ,kafin suka ci gaba da tattaunawa akan matsalar.

Kai tsaye ya shiga part din na ammi,ko kula gaisauwar da hadimanta  keyi baiyi ba,dan zuciyarsa ba abinda take sai tafarfasa,bai taɓa tsammanin haka daga su nanny ba,lallai mutum bashi da tabbas.

Afalo ya ci karo da sarauniya suhaimat,tana zaune da yaranta,suna cin apple da ya'yan itaceya ,gefe guda kuma suna kallo.

Da gudu su zayyad suka taso suka rungume Adeeb suna murnar ganinsa,kansu kawai ya shafa tare da rungumarsu,shima.

Kallonsa sarauniya suhaimat keyi,dan kuwa taga tarin damuwa cikin idanunsa.

"Sannu yarima ,ya jikin naka?dana yarinyar ?"sarauniya suhaimat ta fada cikin yanayi na nuna damuwa .

Lumshe ido Adeeb yayi cikin damuwa da yanayinsa  na rashin son magana yace "da sauƙi"  atakaice .

"Allah ya bata lafiya " ta fada  da yanayi na damuwa.

"Ameen" Adeeb ya faɗa ahankali.

"Ammin naka tana ciki"sarauniya suhaimat ta fada cikin kulawa.

Kai kawai Adeeb ya jinjina mata kafin ya wuce zuwa cikin dakin.

" Bangane ba ?kamar ya nayi sakacin da kwalbar ta fashe,bayan irin kulawa da ita da nake?kasan irin kuɗin dana kashe akan akwatin da aka ƙera na sanya kwalbar ciki?

Shiru tayi ,da alama tana sauraron abinda ake faɗane daga can bangaren.

"Shikenan ,yanzu muna cikin alhini ne na wannan abun daya faru,dan haka kajira nan da kwana biyu,zan nemeka,dan awannan karon aiki nakeso ayimin na ban mamaki,bana kuma son asami matsala " ammi ta faɗa cikin wani yanayi mai nuna ta shirya mugunta mai zafi cikin ranta.

Gaban Adeeb ne yayi wata irin faɗuwa da har saida ya dafe ƙirjinsa,wane akwati ammi ke magana akai?wace kwalbar ce ta fashe?da wa ammi ke waya?waɗan nan sune tambayoyin da Adeeb ke yiwa kansa,saidai bashi da amsar ko daya daga ciki.

Ganin ammin ta gama wayar kuma tana ƙoƙarin juyowa ne ,dan ta ba ƙofa baya,yasa Adeeb saurin saita kansa yayi sallama tare da shiga.

Da sauri aɗan razane ammi ta juyo tana kallon Adeeb ɗin,dan batayi tsammanin ganinsa yanzu ba, saidai da alama baiji me take faɗi ba,itafa wllh tsoronsa ma ta fara ji yanzu,amma saita maze ta saki murmushi,tare da miƙa masa hannu,alamun ya ƙaraso gareta.

Ahankali Adeeb ke takawa har yaje bakin gadon ya zauna,dan jikinsa sam ba kwari,murmushin ƙarfin hali yayiwa ammi yana kallon fuskarta,

"Habeebee ya jikinka? na tsorata sosai da yanayin dana ganka ɗazu"ammi ta faɗa tana mai janyo Adeeb zuwa jikinta.

Sam yau Adeeb ji yayi baya wani jin dadin kwanciya akan cinyarta,Dan saiyajisa kamar akan ƙaya, dan haka da sauri ya tashi daga kwanciyar da yayi,kafin ya dan saki murmushi,yana mai cewa"ƙalau nake ammi,kada ki damu,ya naki jikin?"ya faɗa sam fuskarsa ba walwala.

"Shafa kansa tayi kafin tace naji sauki dana karka damu"ta faɗa tana kallon fuskarsa ,dan kuwa sam ba haka yake mataba,yau kam ba wannan shaukin da yake nuna mata idan suna tare.

Mikewa yayi yana mai faɗin ammi zanje in duba yarinyar can zan dawo anjima" yana faɗin haka yayi waje abinsa.

"Yawwa yarima ,ina son in duba yarinyar nan "sarauniya suhaimat ta fada tana mikewa lokacin da Adeeb ya zo zai wuce.

Shiru yayi yana ɗan nazari,akwai bukatar ta duba ta ,tunda likita ce itama ,kuma fannin mata ta karanta.

Dan haka yace "ok muje ,tana part ɗina"

Ficewa sukayi tare suka nufi part din Adeeb.

Toh masu karatu ,mubi su Adeeb dan duba Hulwa.

Sai mun hade next page.

Mrs babi ce □□

Share and comment fisabilillah.

More comment

More typing.m

[8/13, 8:03 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

_____Ficewa sukayi daga part ɗin ammi zuwa na Adeeb, haka kawai gaban sarauniya Nazli ke faduwa,sam ta kasa gane kan wannan faɗuwar gaban nata,saidai kawai ta alaƙa ta hakan da tunanin halin da zata ga yarinyar data sanya tausayi ta cikin zuciyarta.

Su zayyad ma biyo ta sukayi,dan sunce suma son gannin marar lafiyar ,kuma zasuyi wasa agurin uncle Adeeb ɗin.

Suna zuwa Adeeb ya dannan lambobin securityn daya sanya lokacin da zai fice,nan take ƙofar ta bude suka shiga.

"Tana cikin daki" Adeeb ya faɗa yana kallon sarauniya suhaimat wacce ke tsaye cikin faduwar gaba.

Kallonsa tayi cikin tausayawa, tare da jinjina kai .

sam zuciyarsa  Adeeb da jikinsa basa masa daɗi, yana cikin matsananciyar damuwa ,abubuwa sunyi masa yawan da har yana rasa me Yakamata yayi.

" Ku zauna anan maza kafin na fito kunji" ta faɗa tana shafa kan yaran nata,kafin tabi bayan Adeeb zuwa cikin dakin.

Tana kwance kamar yadda ya barta,ruwan daya ɗaura mata ya kusan karewa.

Jiki asanyaye sarauniya suhaimat ta karasa bakin gadon da fattu ke kwance .sosai bugun zuciyar sarauniya suhaimat ya tsananta.

Zama tayi tare da ƙurawa fattu idanu,lokaci guda taji wata masifaffiyar kaunar yarinyar tana ratsa dukkan sannan jikinta,ji take kamar bata taɓa son abu makamancin yadda take jin son yarinyar na shiga lungu da sako na jikinta ba.

Hannun fattu ta kamo tare da riƙewa gam-gam cikin nata,wani sanyi taji yana ratsata  lokacin data kama hannun fattun,batare da saninta ba kawai ta rungume hannun fattu aƙirjinta ,tare da runtse idonta.wani irin shauƙi takeji yana shiga jikinta irin na ƙaunar dake tsakanin ɗa da uwa.haƙika takamu da matsananciyar kaunar yarinyar lokaci guda.

Kallon fuskar fattu take bata ko ƙifta idanunta,Adeeb na tsaye agefe guda yana kallonta ,mamakin yadda yaga fuskarta ta nuna so da kaunar fattu yake,koda yake haka Allah ke al'amarinsa.ganin ta kasa cewa komai kawai tana rungume da hannun fattu ta kura mata ido yasa shi sauke ajiyar zuciya yana mai faɗin"anty lafiya kuwa naga kinyi shiru "ya faɗa yana mai kallon fuskar sarauniya suhaimat.

Sai lokacin tadanyi firgigit ta ɗago kai tana kallon Adeeb,ajiyar zuciya ta sauke mai ƙarfi kafin tace "wllh Prince haka kawai naji ina kaunar yarinyar har cikin raina ,sosai nake jin tausayinta, yanzu ka dan bamu guri inason na dubawa"ta fada ta na mai shafa kan fattu.

Kallon fattu Adeeb yayi cike da tausayawa,zuciyarsa na masa wani irin ɗaci ,kafin ya sauke ajiyar zuciya kana yayi falo gurin su zayyad da yazeed.

Sosai sarauniya suhaimat taji mugun daɗi lokacin data gane fattu period ma take,kuma babu alamun Rashad yayi mata wani abu,hamdala tayi ga Allah tana jin zuciyarta wasai, murmushi kwance kan fuskarta take kallon fattu,wacce ta fara dan motsi tana yamutsa fuska.

Hannunta sarauniya suhaimat ta kara riƙewa da kyau tana mai faɗin"princess buɗe idonki ki ,kalleni kinji" tana faɗin haka tana ɗan buga kumatun fattu.

Ahankali fattu ke buɗe idanunta da suka yi wani irin jaaaa kamar jini ya taru a cikinsu,har ta bude idon fess,tare da  kafe silin da ido,bata ko ƙiftawa.da alama tana son tuno wani abune, shiru sarauniya suhaimat tayi tana bin idanun fattu da kallo.

Kusan minti ɗaya fattu tana kallon silin ,kafin ta zabura tare da kwalla kara tana kokarin tashi,da sauri sarauniya suhaimat ta cire mata karin ruwan dan dama ya kare .

"Wayyo Allah na ,wayyo hammana kazo ka ceceni,zai lalamin rayuwa,wayyo baffana,wayyo innata kizo ,dan Allah ka bari wllh niba yar iska bace karkamin bana so banaso wayyoooooo!!!" Abinda fattu ke faɗa kenan tana fizge -fizge ,dan gani take kamar lokacin Rashad ke ƙoƙarin yi mata fyade,janyota sarauniya suhaimat tayi da sauri ta rungumeta tsam-tsam ajikinta ,cikin mugun tausayinta,tana faɗin"ki nutsu princess ba kowa buɗe idonki ki gani,nice ba Rashad bane ya tafi kiyi shiru ya

isa"abinda take faɗi kenan tana shafa kan fattu ,wacce ilahirin jikinta ke rawa ,ta rufe idanunta ƙam -ƙam taƙi budewa.

Da hanzari Adeeb ya ƙaraso cikin dakinz su zayyad ma bishi sukayi da gudu ,jin ihu da fattu ta kwalla,har neman faduwa  Adeeb yake tsabar sauri,yana zuwa ya zauna abakin gadon tare da kamo hannun fattu ,da sauri ta fizge hannunta tana mai sakin ƙara ,"ahhhhhh,wayyo ni kasakeni banaso ,wayyo hammana kana ina? wayyo Hamma kazo ka taimakeni" fattu ta faɗa tana kokarin zamewa daga jikin sarauniya suhaimat.

Cike da damuwa Adeeb ya ƙara kamo hannunta ya rike cikin nashi ,duk yadda take ta ƙoƙarin kwace hannun nata,amma yaƙi saki,

"Hulwa ki nutsu kinji ,nine hammanki,buɗe ido ki kalleni ,ba Rashad bane nine Hamma" Adeeb ya faɗa cikin sanyin murya yana mai shafa kan fattu.

Jin muryarsa da fattu tayi yasata saurin buɗe  kunburarrrun idantuna ,ta sauke akan fuskar Adeeb,ɗan kafeshi tayi da ido,gabanta na faɗuwa kamar zai fado kasa.

"Nine ,hammanki ne Hulwa kalleni ki gani ,nine Hamma Adeeb " ya faɗa yana ɗan matso da fuskarsa saitin Tata.

Ahankali tace "hammana"

"Na'am Hulwa is me "Adeeb ya faɗa yana mika mata hannu.

Da sauri ta fada ƙirjinsa tare da fashewa da wani irin kuka,mai matukar ban tausayi,kukane irin na wanda ke cikin tashin hankali kuma ya sami mai taimakonsa.

"Hamma ina kaje ka barni?wannan mai kama da kai ɗinne yazo zaiyi min fyade,Hamma dan baki yarda shine yayi ta dukana,ya fasamin baki,ya bugamin kaina ajikin katanga,Hamma bana sonshi,bana son ganinsa ,dan Allah Hamma ka fitar dani daga gidan nan bana so"fattu ta faɗa cikin matsanancin kuka muryarta har wani yankewa take kamar numfashinta zai dauke.

Kamm ƙamm,Adeeb ya rungumeta ajikinsa,yana jin wani irin zafi akirjinsa, mugun tausayinta ne yake zaga dukkan wata kofa dake jikinsa,haushin kansa ma yake ji,wai me yasa ma ya tafi gurin taron ya barta anan?me yasa bai tafi tare da itaba?

Ahankali yake shafa kanta,yana mai faɗin"am sorry Hulwa,kiyi haƙuri laifinane,dana tafi na barki,na miki alkawarin ba wanda zai sake ƙoda miki kallon banza ne bare hakan ta kara kasancewa,ki yafemin hulwata ,an sorry "ya faɗa yana kara ruƙunkumeta ajikinsa,wasu hawaye Masu zafi suna zirarowa daga idanunsa.

Zuru su zayyad sukayi suna kallon fattu,dan yazeed ma tuni ya fara kuka ,dan shi yana da mugun tausayi.

Sarauniya suhaimat na zaune ta kura musu ido,cikin tausayi take zubda kwalla itama,ji take kamar yarta akayiwa wannan zalumcin ,Allah Sarki Adeeb ya cika dan halak dan ga dukkan alamu yana kula da yarinyar nan,duk da kasancewarta ma aikaciya agidansu,kuma tabbas taga zallar kaunar yarinyar cikin idanun Adeeb.

Sun jima cikin wannan yanayin,har saida Adeeb ya tabbatar Hulwa ta sami nutsuwa ta hanyar daidaiton da yaji bugun zuciyarta yayi,sannan ya rabata da jikinsa.

"Sannu princess hulwar Adeeb"sarauniya suhaimat ta fada ,fuskarta ɗauke da murmushi.

Sai lokacin fattu ta juya tana kallonta .rassa!rassa!!rassa!!! gaban fattu ya yanke ya fadi,ƙurrr ,ta kure sarauniya suhaimat da ido,lokaci guda taji ƙaunar matar na ratsata fiye da yadda tayi tunani,duk kunya irin ta fattu,da bata yarda kuyi ta haɗa ido da ita,amma yau kam ta kafe sarauniya suhaimat da ido bata ko ƙiftawa.

Murmushi sarauniya suhaimat take sakarwa fattu,kafin tace" baki sanni ba ko?

Ta fada cikin yanayi na murmushi.

Kamar wata doluwa haka fattu ta daga kai idonta akan fuskar sarauniya suhaimat.

"Daga yau nice innarki ,danaji kina faɗi kinji "ta faɗa tana mai shafa kan fattu.

Ahankali fattu ta matsa kusa da ita tare da ɗora kanta akan cinyar sarauniya suhaimat tana mai faɗin "innata"ahankali tare da lumshe idonta.

Kallonsu kawai Adeeb keyi,zuciyarsa na darsa masa abubuwa da dama,wannan wane irin shakuwace ta lokaci ɗaya?gaba ɗayansu sun kamu da  kaunar juna daga haduwar farko,anya ba wani al'amarine mai ƙarfi atsakinsu ba ?.

Hammmmm mudaije zuwa.

"Sannu  anty "zayyad ya faɗa cikin tausayawa.

Ahankali fattu ta ɗago kai tana kallon yaran masu tsananin kama,

Lokaci guda yaran suka shiga ranta.

Masha Allah kyawawa dasu.

Jinjina kai tayi tana kallonsu cike da kauna.

"Maza kuje falo ko anty zatayi wanka" cewar suhaimat.

Kama hannunsu Adeeb yayi suka fice zuwa falon.

Saida Sarauniya suhaimat ta taimakawa fattu tayi wanka ta gyara mata jikinta sosai,ta bata abinci taci ta sha magunguna sannan ta kwanta barci .kafin ta bar ɗakin akan zata kara dawowa ta duba ta.har ta kai bakin ƙofa fattu ta ce"innata" da sauri sarauniya suhaimat ta juyo ,dan har cikin ranta taji sunan ya shigeta.

"Zaki dawo "fattu ta faɗa tana kallonta .

Jinjina kai tayi tana mai yiwa fattu murmushi tace "tabbas zan dawo yɑata"murmushi fattu tayi  cikin karfin hali tare da rufe idanunta.ba ɓata lokaci  barci yayi gaba da ita.dan kuwa harda maganin barci acikin wanda ta sha.

Koda sarauniya suhaimat ta koma bangaren ammi,zaune ta tarar da ammin ta buga uban tagumi,duk sallamar da take sam ammin bata jiba,dan tayi nisa cikin duniyar tunani,saida ta tabata kafin ta san da zuwanta gurin.

"Suhaimat ina kikaje ?na duba baki afalon?

Ammi ta faɗa da kokarin kawar da samuwar dake kan fuskarta.

Zama suhaimat tayi susa da ammi tace ,wllh yarinyar nan da abin nan ya faru da ita naje na gani,dan kuwa sosai lamarinta ya tsayamin araina ji nake kamar inada wata alaƙa da yarinyar" suhaimat ta fada tana mai lumshe idonta.

Azabure ammi ta kalli sarauniya suhaimat tana mai dafe ƙirji"na shiga ukuna ,suhaimat gurin yarinyar kikaje?me kika gani?da wa kikaga tana miki kama? ammi ta faɗa cikin rudewa da tashin hankali,dan bata taba tsammanin suhaimat zataje gurin fattu ba.

Kallon mamaki suhaimat ɗin ke bin ammi dashi ,kafin tace  "uktee ,yanaga kin rude haka?daga jin cewar naje gurinta?kuma dawa kike tsammanin zanga tana kamar?ta fada cikin mamaki tana kallon ammi,da sai lokacin ta fahimci tayi baran -barama kuma tana son bada kanta.

Cikin sauri ta saita kanta,kafin tace "ai nayi mamakin yadda kika damu da

baiwane,har kikaje dan ganinta"ammi ta faɗa cikin basarwa.

Murmushin suhaimat tayi kafin tace "wllh yadda nake jin yarinyar nan cikin raina ,ko su zayyad bana jinsu haka"ta faɗa cike da shauki akan fuskarta.

Wani shegen kallon ammi ta jefa mata ,tana mai faɗin ,aikuwa saidai kiyi ta jin wannan shaukin cikin ranki,amma keda yaɗarki har abada,bazan ƙara bari ki ganta ba,dan kuwa  kashe shegiya zanyi kowa ya huta.ammi ta fada cikin ranta.

Amma afili saitayi murmushi tana faɗin,"ke dai suhaimat kina nan da son jama'a har yanzu,sukuwa mutane ba abin yarda bane ,Gara ki kula"

Jinjina kai suhaimat tayi kafin tace "ai idan har kana abu tsakaninka da Allah ,to tabbas Allah zai zama gatanka, kuma bazai taba ba maƙiya Sa'a akanka ba,kuma kinsan shi sharri dan aikene,idan ka cutar da wani to kana zaune zakaga sakayyar Allah"cewar sarauniya suhaimat kenan cikin murmushi take bayaninta.

Kallonta ammi keyi,cike da sanyin jiki,sai take ganin kamar magana suhaimat ke faɗa mata afakaice,amma ai tasan suhaimat bata san komai game da halayyar ta ba ,bare tayi mata shagube.dan haka ta Badar da maganar sukaci gaba da hira.

"Ranka ya dade ,hakika al'amarin Adeeb babban abune,wanda Allah shine kadai zai iya kareshi,domin kuwa sihirin da akaiwa yaron nan,badan ƙarfin addu'ar dake tare dashiba, to tabbas mutuwa zaiyi,domin kuwa sihirin anyi shine badan ya rayu ba,saidai akasheshi. Dan haka ba abinda zamuyi face addu'a domin Allah ya kareshi da duk wani mai nemansa da sharri" Shaikh lateef ya faɗa ,yana mai kallon mai martaba ,

Shiru abie yayi cike da tsantsar mamakin waye yayiwa ɗansa wannan aika aikar,kallon ƙaninsa waziri yayi cikin damuwa yace "ɗan uwana kanaji? Kana jin abinda Shaikh ke faɗi, me Adeeb ya tsarewa jama'a ?yaro mai hakuri,hankali da hangen nesa,ba ruwansa da kowa bai tsarewa kowa komai ba,amma ana neman ganin bayansa,Allah ka karemin ɗana ,ka raba shi da sharrin makiya,yanzu Shaikh menene abinyi.

?"abie ya faɗa cikin damuwa yana jin kamar ya zubda hawaye.

Jinjina kai Shaikh lateef yayi yana Jan carbinsa dake maƙale adan yatsansa.

"Ranka ya dade ba abinda zamuyi masa daya wuce addu'oi,sannan zan hada masa maganin karya sihiri wanda zai sha yayi wanka dashi,amma fa kasancewar samutum akoda yaushe abune  mai matukar wahala,dan kuwa Aduk lokacin da ya shiga yanayi na ɓacin rai mai tsanani to tabbas akwai yuwuwar komawarsa macijin " Shaikh ya faɗa yana mai kallon abie.

Wazirine ya sauke ajiyar zuciya yana kallon Shaikh cikin damuwa kafin yace "yanzu ba wata  hanya da Ya kamata abi,Dan arabashi da wannan iftila'in?ta yaya za'ace mutum yana komawa wata halittar? Shaikh aduba dai "waziri ya faɗa yana kallon Shaikh.

Murmushi Shaikh yayi yana mai girgiza kai,kafin yace ,tabbas da 'ace akwai hanyar da zanbi dan ganin na raba yaron nan da wannan al'amarin ,to danabi ,kamar yadda na faɗa muku, anyi amfani da mugayen aljanu waɗanda suka samo macizan da ba irinsu afadin duniyar nan,kafin aka hada lakanin da akayi masa sihirin dashi, dan haka addu'a itace kadai mafitarmu"

Ajiyar zuciya abie ya sauke ,zuciyarsa kamar zata fashe tsabar damuwa da ɓacin rai,sosai yake jin tausayin Adeeb,waye wanda ke son ganin bayan Adeeb? Me ya tsarewa mutane haka?

Dole ya tsaya sosai ya kula da rayuwar dansa ,ta hanyar bashi kariya ta kowace sigar.

"Shikenan Shaikh Allah ya shige mana gaba ,ya bamu Sa'a akan abinda muke nema"cewar abie yana mai lumshe idonsa lokaci guda damuwarsa ta baya ta dawo masa ,yana tuna abinda ya faru shekarun baya,sam baya son abu makamancin abinda ya faru a baya ya sake faruwa.

"Yanzu  ranka shi dade,ina son aturomin yarima zuwa anjima dan akwai abubuwan da zamu tattauna dashi"Shaikh lateef ya faɗa yana mai mikewa dan barin dakin.

Bayan fitarsa waziri ya kalli abie wanda yayi shiru fuskarsa gaba ɗaya ta sauya ,ta koma kalar damuwa sosai,

"Ranka ya dade ka kwantar da hankalinka,In Sha Allahu komai yazo ƙarshe,ba abinda zai sake samun yarima"waziri ya faɗa cikin kwantar da murya aƙokarinsa na kwantarwa da abie hankali.

"Allah yasa waziri,amma abin yana damuna ,kasan yadda nake son Adeeb ,bana son abinda zai tabashi komai ƙanƙantarsa,domin shine magajina"

"Ba komai ranka ya dade mubar komai hannun allah."cewar waziri.

Jinjina kai abie yayi kafin yace ,sai kuma wannan matsalar ta Rashad,Dole in ɗauki mataki mai ƙarfi akansa,jira nake kawai ya sami lafiya"

"Haka ne yaya dole ahukunta Rashad ,Dan yana don bata mana  suna" cewar waziri cikin damuwa.nan dai sukaci gaba da tattaunawa akan matsalar.

Rashad yana nan har yanzu kwance kamar gawa ,ko motsi bayayi, gaba ɗaya kamanninsa sun sauya ,abin tausayi,kullum amma cikin kuka take tana tausayawa halin da ɗan nata ke ciki,

Gimbiya Zulaihat ma tun daga wannan ranar bata kuma ganin Adeeb ba,dan tsoronsa take ji sosai,amma har lokacin tana nan akan bakanta na son aurensa.

Adeeb kuwa yana dakin da fattu ke kwance tana barci,kallonta yake cike da tausayi,gefe guda kuma wayar da ammi tayi gaba ɗaya ta tsaye masa arai,ga maganar da nanny ta fada masa,shi gaba ɗaya ma ya shiga ruɗu baisan me Yakamata yayi ba,yanzu gurin wa zai je neman shawara?waye zai sanarwa da damuwarsa?yanzu tsoron mutanen fadar nan yake ,dan kuwa cike take da mutane marasa amana da gaskiya.

Ahankali ya shafa gefen fuskar fattu tare da sumbatar goshin ta kafin ya mike tare da ficewa daga ɗakin.

Kai tsaye amma ta fito daga part ɗin Rashad bayan ta gama kukanta ta koshi,tunani tayi kan cewar ya kamata akawo karshen wannan al'amarin dake dukunkune cikin fadar nan,dan haka tana da bukatar magana da  nanny Dole taje tayi magana da ita yanzu .

Dan haka can ta nufa ,cikin sa'a ta tarar da nanny zaune afalo, kallo ɗaya zakayi mata kasan tana cikin damuwa da alhini.tana ganin amma ta mike tana mata maraba cikin girmamawa.

Zama amma tayi tare da kallon nanny tace"zauna nanny inason muyi magana dake . "ta fada tana mai kallon nanny ,wacce itama kallonta take.zama nanny tayi jikinta asanyaye kafin tace "wace magana kike son yi dani ranki ya dade?inaga da kin aiko ankirani nazo gurinki dan gudun zargi ,idan aka ganki anan"nanny ta fada cikin damuwa.

"Ajiyar zuciya amma tayi kafin tace ,ya kamata mu daina boye-boye nanny akan abinda muka san menene gaskiyarsa,ki duba halin da ɗana yake ciki ?kuma duk

akan wannan makirar matar ,nasan cewa kome ya faru shirinta ne,meyasa zamu zauna mu zuba mata ido tana aikata abinda taga dama?dan haka dole mu kawo ƙarshen zalunci ta"amma ta faɗa cikin ɓacin rai da damuwa.

Ajiyar zuciya nanny ta sauke mai ƙarfi kafin tace "ranki ya dade wannan abun fa abune mai matukar hadari ,dakuma tarin ƙalubale,domin nayiwa magajin fada maganar hadarin sarauniya Nazli, na sanar dashi wanda ke da hannu akan hadarin, amma sam bai yarda dani ba yayi fushi mai tsanani.tunda ya fita bai sake dawowa ba.dan haka ina ganin mudan jinkirta zuwa wani lokaci,har wannan abinda ya faru yayi sanyi"

Jinjina kai amma tayi cike da gamsu,tace "wannan gaskiya ne ,dan kuwa nasan mai martaba ma jira yake Rashad ya farfaɗo ,kafin ya yanke hukunci akan abinda ya aikata .Allah shine kawai zai fitar damu " ta fada kwalla na cika idonta.

"Kiyi haƙuri ranki ya dade ,komai yayi farko, yana da karshe ina sha Allah muke da nasara"cewar nanny cike da damuwa akan fuskarta.

"Shikenan nanny Bari na koma can gurin Rashad din"Amma ta faɗa tana mikewa.

Biyota nanny tayi tana mata sallama ,har farfajiyar gidan suka fito nanny na kara kwantarwa da amma hankali.

Daidai lokacin kuma Adeeb ya fito daga part ɗinsa ,idonsa ne ya sauka akan nanny tsaye tare da amma.

Kallonsu yayi cike da tsantsar mamaki,da kara tabbatar da zarginsa akansu.

Suma kallonsa suke cikin yanayi na damuwa da rashin jin dadin ganinsu da yayi .

Tafiya amma tayi daga gurin ,ganin irin kallon da Adeeb ke mata.

Nanny kuwa jikinta ne yayi sanyi sosai.da hanzari ta nufi gurin da Adeeb ke tsaye.....

Hmmmmm masu karatu muhaɗe next page .

Takuce anty mammy

Mrs babi□□

Share and comment fisabilillah.

More comment

More typing.

[8/15, 11:33 AM] Deexou 2: □□□□□□□

MACIJI NE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

_____ nanny tanufa Adeep gabanta yana faɗuwa tunana kala kala ya darso a zuciyarta wani irin kallo Adeep yake jifanta dashi yana mamakin yaushe nanny tazama ha lalle mutum ba abin yarda bane ..

Hahhhaaa ankasa kunne ana jiran anty mammy ko ? Nima ita nake jira wayyo anty mammy kizo kimana macijine

[8/15, 2:09 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

_____Jikin nanny ne yayi sanyi sosai,ganin Adeeb atsaye,kuma ya gansu tare da amma,tasan yanzu kam kome zata faɗa masa ,bazai taba yarda da ita ba.ahankali take takawa zuwa gareshi,gaba ɗaya jikinta ba kwari,

Shikuwa Adeeb yana tsaye ya kafeta da Mayun idanunsa ,masu sanya mutum yaji shi cikin tsoro da fargaba.

Nanny Tana karasowa tace "magajin fada ,fushi kake dani ko"?

Ta fada cikin sanyi murya  da mutuwar jiki.

Lumshe ido Adeeb yayi ,zuciyarsa na masa zafi yana mamakin abinda nanny tayi masa,ace wai nanny ta hada kai da maƙiyarsa tana tayata ƙoƙarin cutar dashi,matar daya ɗauka matsayin uwa ?mutum kenan.

"Ko kaɗan nanny bana fushi dake,kawai ina godiya ga Allah ne ,daya nunamin gaskiya ,na gane irin mutanen da nake tare dasu,na daukeki tamkar mahaifiyata nanny,Amma bansan nayi babban kuskuren yin hakan ba,dan Allah kiyi haƙuri"ya faɗa yana mai haɗe hannayensa guri ɗaya alamun neman afuwa.

Sosai nanny kejin ciwo cikin ranta ,damuwa da taraddadi sun cika mata zuciya,dama tayi wannan tunanin,tasan idan har Adeeb ya gansu  tare da amma ,to shikenan,kuma kome zata faɗa masa bazai yarda da ita ba,amma Allah shine shaida bata da nufin cutar da Adeeb ko kaɗan.

"Magajin fada wllh abinda kake zargi ba haka bane ,kada ganina tare da amma yasa maka kokwanto akaina, wllh nima Ina jinka tamkar tareeƙ bazan taɓa cutar dakaiba magajin fada.

Nanny ta faɗa cike da damuwa aranta.

Girgiza kai kawai Adeeb yayi tare da barin gurin,zuciyarsa kamar zata fashe tsabar damuwa .

Kallonsa kawai nanny keyi,tana fatan Allah yasa ya gane gaskiya cikin sauri kafin komai ya daɗa lalacewa.

Ba kowa cikin falon ammi,sai ƙamshi dake tashi ta ko'ina ,dan ammi akwai son kamshi,kai tsaye ya nufi dakin kwananta, nocking yayi amma shiru,hakan yasa shi shiga cikin dakin kai tsaye.saidai nan ma ba kowa cikin dakin.

Harya juya  zai fice ,sai kuma zuciyarsa ta raya masa ya duba wanann akwatin da yaji ammi na  magana akanta.

Dan haka juyowa yayi yana karewa dakin kallo.

Ahankali yake duba dakin dan neman wannan akwatin,amma yayi iyakar dubansa bai ganta ba.

Harya hakura sai kuma ya hango wata akwati mai kyau da ɗaukar ido,yasan akwatin Dan acikinta ammi ke ajiye kwalakwalanta ,dan haka sai yayi tunanin ba komai cikinta,  har ya juya  da nufin barin dakin,sai kuma zuciyarsa ta kwadaitu da son duba akwatin .

Dan haka ahankali ya zauna tare da ɗauko akwatin, danna lanbobin bude akwatin yayi,dan kuwa tuni yasansu, aikuwa saiga akwati ta bude,gwalagwalai ne acikinta iya ganin ka ,masu kyau da ɗaukar hankali,kallo ɗaya zaka musu kasan an zubar da maƙudan kudade wajen mallakar sarkokin.

Dubawa yayi tayi amma baiga  komai aciki ba,sai wani dan karamin akwati mai kyau da ya gani,kallon akwatin yake da mamakin meye acikinsa aka wareshi ?lallai yana son ganin abinda ke ciki.dan haka hannu Ya mika tare da ɗauko akwatin ya bude.

Mamaki ,al'ajabi ruɗu da kuma faduwar gaba sune suka ziyarci zuciyar Adeeb,sakamakon ganin sarƙar nan ta Hulwa data bace ,cikin wannan akwatin,

Me yakawo sarkar Hulwa cikin kayan ammi?har akayi mata adana ta musamman? me hakan ke nufi,shidai yasan ammi tana da sarkokin da suka ninka kudin wannan bare yayi tunanin ta daukene dan bata da mai tsada kamar wannan ,to me hakan ke nufi kenan?innalillahi meke faruwa ne acikin gidan nan?kodai akwai Abinda ammin nashi ke kullawa da gaske ? Wayyo ina zaisa kansa ?dawa ya kamata ya yarda ne cikin fadar nan? Dauko sarƙar yayi cikin sauri ya maida komai inda yake sannan yayi saurin barin dakin na ammi ya koma part dinsa. Zuciyarsa na zafi kamar zata kama da wuta .

Lokacin daya koma part din nasa fattu ta farka,tana zaune tana kuka,tsoro takeji,har lokacin barin ma dataga ita kadaice cikin dakin,ina Hamma ya tafi ya barta?karfa wannan Rashad din ya dawo mata? Gashi wannan innar ma bata dawo ba,wannan tunanin yasata ƙanƙame jikinta tana kuka.

Adeeb kuwa cikin wani irin yanayi na sarewar zuciya ya shigo cikin dakin,abubuwa sunyi masa yawa cikin zuciyarsa,jinsa yake kamar bashiba, kansa banda ciwo ba abinda yake ,wai meke shirin faruwa da rayuwarsa ne ?me hakan ke nufi ?me amminsa ke nufi da ɗauke sarƙar Hulwa?

Kukan hulwar da yaji Yone yasani saurin ƙarasawa cikin dakin.

Tana jin motsi sa ta zabura atsorace tana mai kallon ƙofar dakin.ganin Adeeb ne ya shigo yasata saurin yunkurawa ta mike da gyar tana kuka tare da kallonsa.

Da saurinsa ya ƙaraso inda take ,yana zuwa ya kamo hannunta tare da shafa gefen fuskarta yace "menene kike kuka?inane yake miki ciwo ?ya faɗa cikin mugun sanyin murya ,wanda har saida fattu ta ɗago kanta ta kalleshi,

Idanunsa sunyi jajur sosai jijiyoyin kansa sun fito rudurudu,fuskarsa tayi jajur ,kana gani kasan yana cikin damuwa da tashin hankali.

Cikin kuka fattu ta faɗa ƙirjinsa ta rungumeshi, tana faɗin "tsoro nakeji Hamma ,ko ina ganin ƙaninka nake yana min gizo Hamma" ta fada cikin kuka tana ƙanƙame Adeeb.

Cike da tarin damuwar da baisan menene mafitarta ba shima ya ƙanƙame fattun ajikinsa yana mai lumshe ido da sauke ajiyar zuciya mai ƙarfi,

Ahankali yake faɗin"kiyi haƙuri Hulwa , dagani harke muna cikin damuwa, Hulwa komai bayamin dadi na kasa gane dawa ya kamata in amince cikin fadar nan,Hulwa kowa na fadar nan so yake yaga bayana bansan me na tsare musu ba" Adeeb ya faɗa cikin murya mai tattare da karaya da sarewa.

Shiru fattu tayi tana sauraron abinda yake fadi,ita fa sam bata fahimci inda zancen sa ya nufa ba,ahankali tace "Hamma ,su waye ke son kamin bayanka"?

"Shiru yayi yana mai kara rungume fattu ajikinsa,dan sosai yake jin nutsuwa na samunsa sakamakon rungumeta da yayi,zuciyarsa tana yi masa sanyi .shafa gashin kanta kawai yake bai ce komai ba.

Kusan minti biyar suna rungume da juna ,kafin Adeeb yayi karfin halin zareta daga jikinsa ya zaunar da ita abakin gado,kallonta yake ,har zuwa lokacin idanunta basu koma yadda suke ba,akwai kumburi da kuma dan jaa kadan acikinsu.

Hannunta ya kamo cikin nashi ya rike gam-gam yana kallonta.ji yake kamar ita kadai ta rage masa wacce zai fadawa damuwarsa,saidai fattu yarinyace,idan ma ya faɗa mata damuwarsa bazata fahimci me yake nufiba.

Kallonsa fattu tayi itama,tabbas akwai Abinda ke damun hamman nata,ko menene oho."Hamma meke danunka?baka da lafiya ne ?ta fada cikin muryar marasa lafiya ,wadanda suka sha kuka.

Ahankali ya koma kusa da ita ya zauna ,kallonta yayi yace "Hulwa abinda ke damuna yana da yawa,ina cikin wata sarkakiya wacce Allah ne kawai zai fitar dani,bani da wanda zan fadawa damuwata ahalin yanzu,bana son sanar da abie na komai,dan gudun ɓacin ransa,saboda tsoron kar ciwonsa ya tashi,kiyi ta min addu'a kinji hulwatee" Adeeb ya faɗa yana mai riƙe habar fattu tare da zuba mata gajiyayyun idanunsa.

Cike da tausayawa fattu ke kallon Adeeb,kafin itama ta sanya hannunta akan fuskarsa tana shafa gefen fuskar tashi, kamar yadda yake mata .sannan tace "Hamma zanyi ta maka addu'a Allah ya yaye maka damuwarka, kuma kaima kayi ta addu'a Allah maji rokon bawansa ne ,Allah ya bawa abie lafiya Hamma,amma me

zai hana ka sanar da innarka itama ta tayaka addu'a" fattu ta faɗa bayan ta cire hannunta daga kan fuskar Adeeb.

Wata sassanyar ajiyar zuciya Adeeb ya sauke lokacin da fattu ke shafa gefen fuskarsa ,ahankali ya lumshe idanunsa yana jin wani irin sanyi yana Ratsa zuciyarsa.

Ahankali ya bude idonsa lokacin da yaji ta cire hannunta daga kan fuskarsa.kafin yace "Hulwa ammina tana daga cikin mutanen da nake son boyewa damuwata ,ahalin yanzu bazan iya sanar da ita komai daya danganci lamarinaba,ke dai kiyi ta min addu'a kinji"ya faɗa cikin murya mai cike da ban tausayi.

Sosai fattu kejin tausayin hamman nata yana Ratsa zuciyarta.ahankali ta ɗora kanta gafen kafadunsa tare da rungumoshi ta gefe.tayi shiru cike da tunanin meke damun hamman nata.

Ahankali shima ya dora kansa akan nata kan yana jinsa tamkar marayan da bai da kowa.

"Hamma wannan innar bazata dawo ba ko?" Ta fada ahankali idanunta alumshe.

Shima idonsa alumshe yake yana shafa kan fattu ,yace "kina so ganinta ne?

"Daga kai tayi alamun eh sannan tace " eh Hamma ina son ganinta ,ina kaunar ta har cikin raina ,kuma tace daga yau itace inna ta"

Ajiyar zuciya Adeeb yayi kafin yace " Hulwa  ita kadai kike kauna ? Ni baki kaunata? ya faɗa ba tare da yasan ya fadi hakan ba .saida ya faɗa sannan ya fahimce me yace .

"A'a  Hamma ina ƙaunarka sosai mana,ina sonka,kaidin kamar baffana kake ,bani da kowa saikai, Hamma bana son wani abu ya tab aka ma" ta fada tana ɗago kai tare da kallon Adeeb.

Cikin wani irin farin ciki da jin dadi Adeeb ke kallon fattu,zuciyarsa cike da  jin dadi yace "da gaske kike Hulwa?" Ya faɗa cikin murmushi yana kallonta.

Jinjina kai tayi itama cikin murmushi tana kallonsa.

Ahankali ya janyota jikinsa ya rungumeta  gamm yana mai lumshe ido , sosai yake jin wani irin. Daɗi da Nutsuwa cikin zuciyarsa.

"Kina son ɓata min shiri ko ?,kisani wllh idan kikayi wani kuskuren dana rasa damata,kema zaki karbi naki hukuncin ,kin sanni kinsan halina,kuma kinsan abinda zan iya aikatawa ,dan haka ki kula da kanki,komai yana ƙoƙarin lalacewa saboda sakacinki,to bazan laminci wannan abinda kike yiba.wllh zan aikaki gurin da duk wanda zai zamenin matsala nake aikawa.akan wannan karagar zan iya batar da kowa"

Wani mutum ne daya lulluɓe ilahirin fuskarsa ke fadin wannan maganar cikin ɓacin rai  yana kallon ammi,wacce ke tsaye cikin tsantsar tsoro ,jikinta sai rawa yake cikin tashin hankali tace "dan Allah kayi hakuri ,wllh ina yin iyakar ƙoƙarina akan wannan abun ,kuma aƘwai shirin da nake yi ,karka damu ka kara hakuri "ta fada cikin rawar murya,tana kallon mutumin da baka ganin komai bace kwayar idanunsa.

Cikin fushi mutumin ya damƙi wuyan ammi ya hadata da jikin bango yana faɗin"bana son jin komai  daga bakin ki kawai ki aikata abinda nace miki ,ki tabbatar ya bar duniyar nan nanda lokaci kankani,zan kawo miki abinda zaki saka mishi acikin abinci,zai mutu kuma ba wanda zai zargi wani abu,idan kuma aka samu kuskure .yayi shiru tare da sakin wuyan ammi wacce ke kakari tana kokarin shekawa.

Tari sosai ammi keyi,lokacin da mutumin ya saki wuyanta sannan yayi tafiyarsa cikin sauri yana ƙara gyara rufin fuskarsa.

Saida ammi ta samu nutsuwa kafin ta bar gurin ,kai tsaye dakinta ta nufa ,gaba ɗaya awahale take,

Bakin gado ta zauna cike da damuwa tana tunani,can dai ta dauko akwatin sarkokinta,abin yayi matuƙar tsorata ta lokacin datayi arba da akwatin sarƙar fattu ba komai acikinta.

Wani dan gajeren ihu ta kwalla cikin tashin hankali,tana dube dube cikin akwatin ,waye ya daukemin sarƙar nan?na shiga ukuna wayyo ni ammi .da sauri suhaimat ta shigo dakin ammi ,dan kuwa taji ihun da ammin ta kwalla."uktee lafiya ?naji kina ihu?suhaimat ta fada cikin damuwa tana rike ammi.

"Ba komai suhaimat na Dan bugene "ammi ta fada cikin tashin hankali.

Kallonta suhaimat keyi cikin rashin yarda da abinda ya fada,amma koma dai menene tunda taki faɗa shikenan .

"To mukam muna ta shiri anjima jirginmu zai tashi .zanje in Kara duba yarinyar can "suhaimat ta fada tana kallon ammi.

"Karkije suhaimat ,karkije,na roƙeki,ki rufamin asiri karkije "ammi ta fada cikin tashin hankali tana kama hannun suhaimat.dan tana tsoron kar ace sarƙar ta koma gurin fattu ne kuma suhaimat ta gani ta gane yarta.

Cike da mamaki suhaimat ke kallon ammi,anya kuwa kalau take?ji yadda ta wani rikice daga cewa zani ganin yarinyar can.

Kai gaskiya akwai wani abu aƙasa.

Cikin hade fuska suhaimat tace "uktee ki fadamin menene dalilinki  da baki son na haɗu da yarinyar can?me kike kullawa akanta ?menene hajjarki ? suhaimat ta fada cikin haɗe rai tana kure ammi da ido.

Zato ido ammi tayi tana kallon suhaimat ,kafin cikin in Ina ta fara magana "su...haim..at .....

Hmmmmm muje zuwa masu karatu.

Mrs babi ce□□

Share and comment fisabilillah.

More comment

More typing.

[8/16, 9:32 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

_____"Ki sanar dani dalilin da yasa  baki son zuwana gurin yarinyar nan?

Me alaƙarki da ita ?ko ince me ta tsaremiki uktee?

Sarauniya suhaimat ta fada cikin haɗe fuska ,dan tasan kadan daga aikin ammi ta hanata zuwa gurin fattu.

Zaro ido ammi tayi tana mai kallon suhaimat ,dan sai lokacin ta fahimci tana kokarin bada kanta,cikin in-ina ta fara magana "su...hai..mat,wane dalilin ne zaisa kuwa in hanaki zuwa gurinta?kawai ina gudun ace ko wata munaƙisar muka ƙulla yasa kike ta zarya,kinsan tunda wannan abun ya faru to komai ma laifi zai zama , amma bayan wannan bani da wani dalili"ammi ta fada tana kafe suhaimat da idanu.

Murmushi suhaimat tayi ,kafin tace "Indai dan wannan ne karki damu ,ai kowa yasan Ni likitar matace,kuma ba laifi bane idan naje duba marar lafiya,kuma ma mace"suhaimat ta fada cikin yanayi na rashin damuwa.kafin ta juya ta bar ɗakin.

Harara ammi ta biya da ita ,kamar idanunta zasu fado ,haushin suhaimat takeji fiye da tunanin mai tunani,wllh badan tana tsoron faruwar wani abu ba ,data gama da suhaimat ,dan itace silar shigar ta ko wace irin damuwa.amma ba komai muje zuwa sannu sannu bata hana zuwa,saidai dade ba'ajeba.

koda sarauniya suhaimat ta koma bangaren Adeeb, kwance ta tarar da fattu adaki, idanunta alumshe kamar mai barci,yayinda Adeeb ke falo yana amsa waya.

Bayan sun gaisa yake sanar da ita fattun tana cikin daki, dan sosai yake jin dadin yadda take kula masa da fattu.

Tana shiga fattu ta buɗe idonta,da sauri sakamakon jin muryarta,dan dama tana kwancen nan, tunaninta  Sarauniya suhaimat kawai take.

Da murna ta tashi zaune tana murmushi,tare da kallon suhaimat,

Itama cikin farin ciki ta karasa gareta ta zauna.

Ahankali fattu tace "inna nayi tunanin bazaki dawoba,ina ta tunaninki araina"ta fada fuskarta ɗauke da annuri.

Shafa fuskar fattu tayi kafin tace "yɨata kenan ,tunda nace zan dawo ,ai dole na na dawo naga kaykykyawar fuskar nan taki,ya jikin naki"suhaimat ta fada cikin murmushi.

"Da sauki "cewar fattu.

"Masha Allah,haka ake so ki kula da shan magungunanki kinji"cewar sarauniya suhaimat.

Jinjina kai fattu tayi kafin tace "ina yan biyu "

Murmushi suhaimat tayi kafin tace "suna can suna shiryawa ,Basu san nazo nan ba da kin gansu sun biyoni, dan sun damu dake sosai" ta fada cikin murmushi.

Fattuna murmushin tayi, tana wasa da yɨan yatsunta.

Sun jima suna hira da fattu,duk da tana  ɗan jin kunyar sarauniya suhaimat din,amma zakayi mamakin yadda ya sake suke ta hira ,harda dariya .

Anan ne take sanar da ita cewar yau zasu tafi garinsu.

Lokaci guda fattu ta shagwabe fuska kamar zatayi kuka,

"Ayya inna meyasa zaki tafi?dan Allah ki zauna anan,bana son ki tafi "fattu ta faɗa tana mai kallon sarauniya suhaimat.

Ahankali suhaimat ta kamo hannun fattu ta rike cikin nata tana ɗan murmushi,duk da itama sam batason rabuwa da Fattun,amma dan ta kwantar mata da hankali sai tayi murmushi tace"karki damu my princess ai zan rinka zuwa ina ganinki,kuma

wataran zance yarima ya kawomin ke muyi hutu,ko bazaki zoba"?ta fada tana kallon fattu.

"Zanzo mana inna dama bana son zama agidan nan tsoron wannan mai kama da hamman nawa nake"ta fada cikin yanayi na damuwa, idanunta har ya kawo kwalla.

Cikin damuwa itama suhaimat ta tallafi kumatun fattu,tana mai cewa"ki kwantar da hankalinki yʻata, ba abinda zai miki kinji,ki daina tsoronsa,yanzu haka yana can akwance cikin halin mutuwa da rayuwa,kuma hammanki yana tare da ke"ta fada cikin salon kwantar da hankali.

Jinjina kai fattu tayi tana mai kallon suhaimat ɗin.

Murmushi suhaimat tayi tana mai kallon wayarta dake ringing ,lokaci ta duba taga harta kara minti biyar akan time ɗin da zasu tafi,dan ma private jet ne.kuma mijinta bai sami halartar gurin ba saboda wani meeting da suke mai muhimmanci.

"To yʻata zan tafi saina ƙara dawowa zan dawo mutafi tare dake ,kinji"suhaimat ta fada tana jin ba dadi cikin ranta,ji take kamar zata rabu da abu mafi muhimmanci arayuwarta.

Ahankali fattu ta daga mata kai, idanunta na zubda kwalla,sam bata son suhaimat ta tafi,"Allah ya tsareku,ya kaiku lafiya inna ,saikin dawo"fattu ta faɗa tana ɗan kwantar da kanta jikin suhaimat.

Rungumeta suhaimat tayi cikin alhinin rabuwa da ita .Adeeb ne ya shigo dakin da sallamarsa,da alama wanka yayi dan ya cire kayan dazu ya sanya riga da wando blue  and white yayi matuƙar kyau sosai,sai ƙamshinsa yake kamar kullum.

Kallonsu yayi yadda ko wanne ke zubda kwalla ,lallai lamarin Allah abin kallone,dubi yadda lokaci ɗaya shakuwa ta shiga tsakanin bayin Allahn nan?kamar sunsan juna.murmushi yayi yana kallon suhaimat kafin yace "anty suhaimat har yanzu kina nan da tausayi da  kuma  saurin kuka " ya faɗa yana kallonta.shikam tun sanin da yayi mata haka bakinta yake ,akwai tausayi da son mutane bata da kyamar dan adam.

Share hawayen idanunta tayi kafin tace "prince wllh da zaka bani yarinyar nan dana tafi da ita can Ghana munyi zaman mu ,dan Allah ya doramin kaunarta cikin raina sosai" ta fada tana shafa kan fattu.

"In baki ita ku tafi?Ni kuma inyi yaya,haka kawai ,ki tafimin da mata?inaaa"Adeeb ya faɗa cikin zuciyarsa.amma zahiri saiyace "karki damu watarana zata zo "

"Allah yasa da gaske kake,yanzu dai kayi mana hoto dan tarihi"sarauniya suhaimat ta fada tana mai janyo fattu jikinta.

Luuuf!! fattu tayi ajikin suhaimat tana mai jin wani irin sanyi acikin zuciyarta.hotuna Adeeb yayi musu kusan kala biyar awayarsa, hakama yayi musu awayar Sarauniya suhaimat ɗin.

Da gyar suka rabu da juna cikin kewa da kaunar juna, fattu sai kuka take ta rungume Adeeb lokacin da suhaimat ta tafi rarrashinta yayi tayi da gyar ya samu tayi barci.

Ammi kuwa sosai taji dadin tafiyar suhaimat,dan hankalinta sam bai kwanta ba ,gani take kamar zata iya gano wani abu game da fattu

Yanzu damuwarta daya shine yadda ,zata bullowa lamarin Adeeb.

Rashad ya farfaɗo ,saidai gaba ɗaya ankasa gane  kansa ,dan kullum haka zaka ganshi shiru baya magana saidai kallo,abin yana matukar damun amma,haka zatayi ta kuka tana kallonsa,saidai kawai kaga hawaye yana bin fuskar Rashad din,ya rame sosai,dan baya wani cin abinci,ga karaya ajikinsa ta ko ina likitoci suna ta binciken kwakwalwarsa dan suna tunanin tanan ya sami  matsala.saidai muce Allah ya bashi lafiya.

Sam yanzu Adeeb baya  kula tareeƙ ,haka zai zo yayi ta bashi haƙuri amma Adeeb bazai ce masa ko ci kankaba.duk da yadda yayi kewar tareeƙ ɗin cikin zuciyarsa.

Abin yana yiwa tareek ciwo ,haka zai je gurin nanny yayi ta kuka ,saidai tabashi hakuri.

Alhamdullah jikin fattu ya warke sosai,dan duk tabon ciwukanta ma babu,sosai shakuwa ta kara shiga tsakaninta da Adeeb,dan kuwa ya dawo da ita bangaren sa gaba ɗaya ,ya siyo mata sabbin kayan sawa ,da duk wani abu datake bukata.

Yayin da gefe guda yake ci gaba da bincikensa akan al'amarin su Nazli da kuma sarƙar nan ta fattu,akan ammi ,saidai har yanzu ya kasa samun wata kwakwkwarar hujja da zai kama ammi da ita .dan haka ya kara yarda cewar hadin bakine na amma da nanny ,suke son hadashi da ammi.

Bangaren rashad kuwa ,abin ba'acewa komai,dan har yanzu yana nan jiya iyau, baya uhhhm bare uhm -uhm .magani ta ko ina yi masa ake ,mai martaba da kansa abin yana damunsa,.

Haka ma Adeeb yana jin ciwon abinda yayiwa ɗan uwan nashi,saidai koma menene shiyajawa kansa.kuma hakan bai hana shi neman masa magani ba .

Shaikh lateef ya bawa Adeeb magungunan da zai rinka amfani dashi,kuma yana amfani dasu yadda ya kamata.zamu iya cewa yanzu abubuwa sun dan lafa agidan.

Yanzu haka fattu ana mata lesson kullum ,zakuyi mamakin yadda fattu ta iya Yaren larabci sosai,tana ji kuma tana iya mayarwa, dan fattu akwai ƙwaƙwalwa,shikansa mai mata lesson yana mamakin hazaka irin ta fattu.

Adeeb kullum yana kara nuna mata abubuwan da bata game ba.tayi kyau sosai ta goge idan ka ganta bazaka taba cewa itace ba.

Kullum saisunyi waya da sarauniya suhaimat,sun shaku da juna sosai.

Gimbiya Zulaihat ma tana nan tana nata shirin,dan yanzu kam tana ganin fattu na neman zama wata abar alfahari agidan,dan ta kereta ta ko ina,Shegiyar yarinya kyau kamar yar aljanu.

Wannan kenan.

Ammice zaune ƙaton falonta tana waya,dawowarta kenan daga gurin mai martaba,tana masa maganar ya dace ace zuwa yanzu Adeeb yayi aure ,dan shekaru na tafi kuma shine magajin fada.

Dan haka abie yace ta zaba masa matar da zai aura ,tunda itace amminsa ,kuma yasan Adeeb bazaiki zabin ammin nashi ba.tun da dai shi ba kula yan mata yake ba.

Cikin farin ciki kuwa ammi ta dawo ɗakinta ta kira kawarta.

"Kawata ,albishirinki?

Ammi ta fada cikin ɗoki.

Bansan me akace mata ba ta dayan bangaren naji dai taci gaba da cewa"ai mai martaba ya bani damar zabawa Adeeb matar da zai aura,kuma ba kowa na zaba masaba face yar wajenki,maryam.kinga mun sami hanya cikin ruwan sanyi,da zamu cika burinmu akansa" ta fada cikin doki tana murmushi.

Shiru na ɗan wani lokaci kafin taci gaba"ki rabu dashi, kawai ,nasan barazana ce yake min,amma kinsan bazan taɓa yarda Zulaihat ta auri Adeeb ba,dan kuwa ubanta zatayi wa aiki ba muba,

Batun yarinyar da yazo da ita kuwa,na boye duk wata hanya danasan zai gane suwaye iyayenta na asali,kuma nasanya boka ya hana uwarta zuwa gasar nan ma gaba daya , Kinga har abada bazasu taba haduwa da junaba.

Abu na gaba da zamuyi shine ,da zarar anyi auren nan,zamu sa ta kashe dan banza kowa ma ya huta, zan san yadda zanyi in shawo kan wancan mugun ya yarda ayi auren saimu kashe Adeeb din"

Shiru ammi tayi tare da sauraron abinda ake fadi aɗaya bangaren.

Kafin taci gaba"wllh ƙawata Ni kaina yarinyar nan na tsaneta ,bana don ganinta,Aduk lokacin dana ganta fuskar uwarta nake gani ,kuma ina tunano abinda ya faru abaya,dan haka itama kawar da ita zanyi kowa ya huta ,duk dana ɗauke sarƙar nan Tata,amma na nemeta na rasa ,kuma banganta awuyan yarinyar ba,dan haka ina tunanin bata koma gareta ba,ƙila dai nice na sauya mata gurin ajiya na manta"

Shiru ammi ta sake yi ,kafin tace shikenan sai kinzo ma karasa maganar.

Jikin fattu banda rawa da bari ba abinda yake ,zuciyarta sai neman tarwatsewa take , innalillahi wa'inna ilaihir raji'un!!wanann wace irin masifa ce haka,yanzu ammi tasan su waye iyayena dama ?kenan kashe Hamma zasuyi?me hakan ke nufi? kenan ammi ba itace mahaifiyar Adeeb ba?dan kuwa tasan ba ta yadda za'ayi uwa

tayi yunkurin  kashe ɗan ta,  wai meke faruwa ne?wannan ɗin wane irin badakala ce kuma?

Tsabar rawar da jikinta yakeyi bata san lokacin data buge wani flower vase dake ajiye agefenta ba ,ya fadi kasa ,jikake toshshs!! Ya fashe .

Cikin tsoro da tazana fattu ,tayi sauri buya ajikin ƙofa tare da runtse idanunta.

Ammi kuwa da sauri ta taso Dan ganin waye yayi mata labe ,har yaji sirri ta.

Da mugun ƙarfi aka fizgi fattu akayi waje da ita ,buɗe baki fattu tayi da nufin kurma ihu,taji an toshe mata bakinta.....

Waye ya dauke fattu?

Me zai faru nan gaba?

Muje zuwa anty mammy ce

Mrs babi□□

Share and comment fisabilillah.

More comment

More typing.

[8/17, 8:53 AM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Da sauri ammi ta taso cikin tashin hankali da fargaba,dan kuwa tabbas tasan wani yaji me take cewa.

Fattu kuwa tsabar ruɗewa da shiga tashin hankali tama rasa ina zata dosa,tsoro ya cika mata zuciya ganin ammi ta nufo inda take ,saidai cikin wannan yanayin ne taji an fizgeta da mugun ƙarfi anyi waje da ita.nan take tsoronta ya kara rubanya.buda baki tayi da nufin kurma ihu ,dan atunaninta masu kashe tan ne suka kamata.saidai gam!aka rufe mata baki,bata yadda zatayi ihu.kuma cikin wani irin sauri mai kama da gudu akayi waje da ita,ta wata hanya da bata nan ta shigo ba.

Ammi kuwa tayi iyakar dubanta ,amma bata ga kowa ba,kuma tabbas tasan anshigo cikin dakin nan,to waye?dan duk ta kora yan aiki can farfajiyar gidan dan tasami damar yin wayarta.

Ko dai Adeeb ne?kai bashi bane ,dan kuwa Adeeb baya zuwa gareta ba tare da yayi sallama ba.toko nanny ce ?kai idan nanny ce zan iya cimma ta kafin ta gudu,wai waye wannan yake son shiga rayuwata ne?waye yake son bakuntar lahira kwana kusa?na rantse da Allah idan na gano ko waye saina hukuntashi, hukunci mai tsanani.yanzu dole mu sake sabon tsari dan wannan kam ya rika ya lalace"ammi ta fada cikin zafin zuciya da kunar rai.

Tana nan tsaye Zulaihat ta shigo dakin ba ko sallama,kawai ammi sai ganin mutum tayi bukut ya shigo cikin falon.guri ta nema ta zauna tare da ƙurawa ammi ido.

Harara ammi ta Banka mata tana tunanin koma dai Zulaihat ɗin ce ta shigo dazu da tasan Zulaihat ba hankali gareta ba?

"Ke Zulaihat kece kika shigomin daki dazu kina Min labe?"ammi ta fada cikin haɗe fuska.

Wani shegen kallon Zulaihat ke jifan ammi dashi,kafin ta fara magana "lallai ma ammi har kina tunanin akwai wanda zan zauna inayiwa labe?to me zan labe naji,bayan duk wani tuggun da ake ƙullawa ina sane dashi,me kuma za'a boyemin ? kinsan Ni bana munafurci kai tsaye nake Abunda naga dama "Zulaihat ta faɗa cikin rashin kunya tana wani juya ido.

Kallonta ammi tayi cikin tsantsar ɓacin rai da tsanar halayen ta na rashin kunya kafin tace " yanzu kina Min wannan gatsalin kike son na aura miki Dana?to wllh gara ki nutsu Dan bazan yarda ki auri Adeeb da wannan shegen halin naki ba,domin shirme zakiyi tayi mana,idan mun saki aiki"ammi ta fada cikin faɗa -fada.

Wata irin dariya Zulaihat tayi tana kallon ammi kafin tace "Kinga ammi ki daina min tsawa keba uwata bace,ko iyayena lallaɓani suke ,kuma da kike cewa zan bata muku aiki,ku atunaninku idan anyi auren biye muku zanyi in cutar da abin sona,? wllh garama ku nutsu daga ke har daddy na Dan kuwa rungumar mijina zanyi musha soyayya ,kuma duk wanda yayi yunkurin cutar da shi ,wllh saina kashe mutum,kinsan nima na iya dabancin"Zulaihat ta faɗa cikin gadara tana kallon ammi ido cikin ido.

Baki buɗe ammi ke kallon Zulaihat,lallai yarinyar nan ta wuce yadda suke tunani,Gara ta lallabata,karta jika mata aiki,dan haka cikin dan murmushin yake ammi tace "kai yʼata dadina dake baki san wasa ba,yanzu saiki maida abu gaske,ki kwantar da hankalinki,kinsan nima bazan taɓa bari a cutar min da Adeeb ba, dama nayi tunanin bakinsu ɗaya da mahaifi ki,shiyasa na fadi hakan"ammi ta fada cikin murmushin yaƙe tana hararar Zulaihat ƙasa ƙasa.

"Ato Gara dai mutum ya kula wllh ,dan zan iya komai akan abinda nake so"Zulaihat ta faɗa tana mai gyara zamanta zuwa kwanciya,tare da lumshe idonta kamar zatayi barci.

"Zanyi makaganinki daga ke har uban Maki shegiya"ammi ta fada cikin zuciyarta,tana shigewa daki,cike da tunanin mafita.

Ba'a dire fattu  a ko ina ba, sai cikin wani daki mai dan duhu, wanda kana iya ganin mutum ,amma bazakaga fuskarsa kai tsaye ba.

Koda aka direta sam ba'asakar mata baki ba.

Fattu kuwa banda rawa ba abinda jikinta keyi,sai ƙoƙarin cire hannun mutumin take daga bakinta, ammata kasa .

Cikin nutsuwa da kwantar da hankali ya fara magana "ki nutsu ,niba cutar dake zanyi ba,koda na bude miki baki to karkayi ihu "

Cikin hanzari fattu ke jinjina kanta idonta yayi zuru zuru ,burinta kawai tajita free.

Ahankali ya dannan makunnar dake gefensa,nan take dakin yayi haske ta yadda kana iya ganin komai.

Da sauri fattu ta daga idanunta tana kallon mutumin,

"Hamma tareeƙ"ta fada cikin rawar murya,"ka bani tsoro Hamma tareeƙ,meke faruwa cikin gidan nan,wacece ammi ?meye alaƙarta da hammana?fattu ta faɗa cikin muryar kuka tana kallon tareeƙ.

Shima kallonta yake zuciyarsa na masa zafi ,yayi fatan ace Adeeb da kansa yaji wannan maganar ba wani ne yaji ba.

"Ki kwantar da hankali ki fateema,da sannu zaki fahimci komai "

Ya fada tare da ɗauko wayarsa yayi kira.

"Ummee kuzo ina nan cikin dakin baya"haka kawai ya faɗa ya kashe wayar.

Kallonsa fattu keyi jikinta har lokacin rawa yake ,tana cikin shock da zallar mamaki,kujera tareƙ ya nuna mata tare da cewa"ki zauna anan fateema " jiki ba kwari fattu tabi bango ta zauna aƙasa ba tare da ta hau kan kujerar da tareƙ ke nuna mata ba.zallar mamakin ammi da al'ajabi ta ke ɗawainiya da fattu,yanzu duk zaman da sukayi dama  ammi tasan asalin iyayenta?kuma ita ta sace sarƙarta wacce take matsayin shaidar da zata sadata da iyayenta na asali?amma menene ribar ammi nayin hakan?wane amfani zata samu?lallai dole ta sanar da Hamma wannan maganar .

Bude kofar da akayi ke ya katsar mata da tunaninta ,da sauri cikin tsoro ta kalli bakin ƙofar,nanny ce ta shigo ita da amma.

Da sauri fattu ta mike cikin rawar jiki ta ƙanƙame nanny tare da sakin kuka mai ciwo da radadi," nanny wai zasu kashe min hammana ,kuma nima zata kasheni ,sannan tace tasan asalin iyayena ,amma bazata bari muhadu dasuba.nanny wacece ammi ? meye alaƙarta da hammana,anya kuwa itace ta haifeshi ?fattu ta faɗa tana mai dago kanta tare da kallon nanny.

Cike da tausayin fattu nanny ta riketa ajikinta Tana mai shafa bayanta ,alamun rarrashi,kafin tace "ki kwantar da hankalinki ɗiyata,ba abinda zai sameku da yardar Allah,kuma yau zan sanar dake alakar dake tsakanin Adeeb da amminsa" cewar nanny Tana me zaunar da fattu akan kujera.

Amma kuwa tana tsaye ta kafe fattu da idanu,tabbas hasashenta ya tabbata ,dan kuwa ba tun yau take zargin cewa  fattu yar sarauniya suhaimat bace,dan kuwa tasha ganin irin sarƙar wuyan Fattu atare da iyalin suhaimat,bayan nan sai kayi duba na tsanake zaka gano tsantsar kamar dake tsakanin fattu da suhaimat ɗin.aikuwa insha Allahu yau ba sai gobe ba zata sanar da fattu wacece ammi.

Cikin kuka fattu ke kallon nanny kafin tace "Dan Allah nanny ki sanar dani ala'akar dake tsakanin hammana da kuma ammi,ko zuciyarta zata sami salama,ji nake kamar zan mutu,banson wani abu ya sami hammana nanny Ina kaunar hammana fiye da yadda nake son kaina idan wani abu ya sameshi wllh mutuwa zanyi"fattu ta faɗa cikin kuka mai ban tausayi.

Hawaye nanny ta goge tana mai kallon fattu kafin tace "In Sha Allahu ba abinda zai sami magajin fada ki kwantar da hankalinki ɗiyata.

Hannun fattu amma ta kamo cikin sanyin murya tace "kiyi shiru ,ki kuma kwantar da hankalinki,dan yau zaki san abubuwan da  baki sani ba abaya,dan haka ki adana hawaye ki zai miki amfani nan gaba "cewar amma tana kallon fattu cikin tausayawa.

Share hawayen kuwa fattu tayi tare da kafe nanny da ido,zuciyarta na bugawa kamar ana. Kada ganga.

Ahankali nanny ta fara magana"ammi ba itace asalin wacce ta haifi Adeeb ba,amma itace wacce ta rike shi bayan ta kashe mahaifiyarsa."

Dararararmmmm gaban fattu ya bada sautin karar da saida ta kusan faduwa tana daga zaune.

Ai Ni kaina saida na tsorata na jefar da wayar nan dan tsoron jin abinda nanny zata faɗa .

Muje zuwa masoyan fattu da Adeeb .

Sai mun haɗe anjima in Sha Allahu.

Anty mammy ce

Mrs babi □□

[8/16, 9:32 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____"Ki sanar dani dalilin da yasa  baki son zuwana gurin yarinyar nan?

Me alaƙarki da ita ?ko ince me ta tsaremiki uktee?

Sarauniya suhaimat ta fada cikin haɗe fuska ,dan tasan kadan daga aikin ammi ta hanata zuwa gurin fattu.

Zaro ido ammi tayi tana mai kallon suhaimat ,dan sai lokacin ta fahimci tana kokarin bada kanta,cikin in-ina ta fara magana "su...hai..mat,wane dalilin ne zaisa kuwa in hanaki zuwa gurinta?kawai ina gudun ace ko wata munaƙisar muka ƙulla yasa kike ta zarya,kinsan tunda wannan abun ya faru to komai ma laifi zai zama , amma bayan wannan bani da wani dalili"ammi ta fada tana kafe suhaimat da idanu.

Murmushi suhaimat tayi ,kafin tace "Indai dan wannan ne karki damu ,ai kowa yasan Ni likitar matace,kuma ba laifi bane idan naje duba marar lafiya,kuma ma mace"suhaimat ta fada cikin yanayi na rashin damuwa.kafin ta juya ta bar ɗakin.

Harara ammi ta biya da ita ,kamar idanunta zasu fado ,haushin suhaimat takeji fiye da tunanin mai tunani,wllh badan tana tsoron faruwar wani abu ba ,data gama da suhaimat ,dan itace silar shigar ta ko wace irin damuwa.amma ba komai muje zuwa sannu sannu bata hana zuwa,saidai dade ba'ajeba.

koda sarauniya suhaimat ta koma bangaren Adeeb, kwance ta tarar da fattu adaki, idanunta alumshe kamar mai barci,yayinda Adeeb ke falo yana amsa waya.

Bayan sun gaisa yake sanar da ita fattun tana cikin daki, dan sosai yake jin dadin yadda take kula masa da fattu.

Tana shiga fattu ta buɗe idonta,da sauri sakamakon jin muryarta,dan dama tana kwancen nan, tunaninta  Sarauniya suhaimat kawai take.

Da murna ta tashi zaune tana murmushi,tare da kallon suhaimat,

Itama cikin farin ciki ta karasa gareta ta zauna.

Ahankali fattu tace "inna nayi tunanin bazaki dawoba,ina ta tunaninki araina"ta fada fuskarta ɗauke da annuri.

Shafa fuskar fattu tayi kafin tace "yʻata kenan ,tunda nace zan dawo ,ai dole na na dawo naga kaykykyawar fuskar nan taki,ya jikin naki"suhaimat ta fada cikin murmushi.

"Da sauki "cewar fattu.

"Masha Allah,haka ake so ki kula da shan magungunanki kinji"cewar sarauniya suhaimat.

Jinjina kai fattu tayi kafin tace "ina yan biyu "

Murmushi suhaimat tayi kafin tace "suna can suna shiryawa ,Basu san nazo nan ba da kin gansu sun biyoni, dan sun damu dake sosai" ta fada cikin murmushi.

Fattuna murmushin tayi, tana wasa da yʻan yatsunta.

Sun jima suna hira da fattu,duk da tana ɗan jin kunyar sarauniya suhaimat din,amma zakayi mamakin yadda ya sake suke ta hira ,harda dariya .

Anan ne take sanar da ita cewar yau zasu tafi garinsu.

Lokaci guda fattu ta shagwabe fuska kamar zatayi kuka,

"Ayya inna meyasa zaki tafi?dan Allah ki zauna anan,bana son ki tafi "fattu ta faɗa tana mai kallon sarauniya suhaimat.

Ahankali suhaimat ta kamo hannun fattu ta rike cikin nata tana ɗan murmushi,duk da itama sam batason rabuwa da Fattun,amma dan ta kwantar mata da hankali sai tayi murmushi tace"karki damu my princess ai zan rinka zuwa ina ganinki,kuma wataran zance yarima ya kawomin ke muyi hutu,ko bazaki zoba"?ta fada tana kallon fattu.

"Zanzo mana inna dama bana son zama agidan nan tsoron wannan mai kama da hamman nawa nake"ta fada cikin yanayi na damuwa, idanunta har ya kawo kwalla.

Cikin damuwa itama suhaimat ta tallafi kumatun fattu,tana mai cewa"ki kwantar da hankalinki yʻata, ba abinda zai miki kinji,ki daina tsoronsa,yanzu haka yana can akwance cikin halin mutuwa da rayuwa,kuma hammanki yana tare da ke"ta fada cikin salon kwantar da hankali.

Jinjina kai fattu tayi tana mai kallon suhaimat ɗin.

Murmushi suhaimat tayi tana mai kallon wayarta dake ringing ,lokaci ta duba taga harta kara minti biyar akan time ɗin da zasu tafi,dan ma private jet ne.kuma mijinta bai sami halartar gurin ba saboda wani meeting da suke mai muhimmanci.

"To yʼata zan tafi saina ƙara dawowa zan dawo mutafi tare dake ,kinji"suhaimat ta fada tana jin ba dadi cikin ranta,ji take kamar zata rabu da abu mafi muhimmanci arayuwarta.

Ahankali fattu ta daga mata kai, idanunta na zubda kwalla,sam bata son suhaimat ta tafi,"Allah ya tsareku,ya kaiku lafiya inna ,saikin dawo"fattu ta faɗa tana ɗan kwantar da kanta jikin suhaimat.

Rungumeta suhaimat tayi cikin alhinin rabuwa da ita .Adeeb ne ya shigo dakin da sallamarsa,da alama wanka yayi dan ya cire kayan dazu ya sanya riga da wando blue  and white yayi matuƙar kyau sosai,sai ƙamshinsa yake kamar kullum.

Kallonsu yayi yadda ko wanne ke zubda kwalla ,lallai lamarin Allah abin kallone,dubi yadda lokaci ɗaya shakuwa ta shiga tsakanin bayin Allahn nan?kamar sunsan juna.murmushi yayi yana kallon suhaimat kafin yace "anty suhaimat har yanzu kina nan da tausayi da  kuma  saurin kuka " ya faɗa yana kallonta.shikam tun sanin da yayi mata haka bakinta yake ,akwai tausayi da son mutane bata da kyamar dan adam.

Share hawayen idanunta tayi kafin tace "prince wllh da zaka bani yarinyar nan dana tafi da ita can Ghana munyi zaman mu ,dan Allah ya doramin kaunarta cikin raina sosai" ta fada tana shafa kan fattu.

"In baki ita ku tafi?Ni kuma inyi yaya,haka kawai ,ki tafimin da mata?inaaa"Adeeb ya faɗa cikin zuciyarsa.amma zahiri saiyace "karki damu watarana zata zo "

"Allah yasa da gaske kake,yanzu dai kayi mana hoto dan tarihi"sarauniya suhaimat ta fada tana mai janyo fattu jikinta.

Luuuf!! fattu tayi ajikin suhaimat tana mai jin wani irin sanyi acikin zuciyarta.hotuna Adeeb yayi musu kusan kala biyar awayarsa, hakama yayi musu awayar Sarauniya suhaimat ɗin.

Da gyar suka rabu da juna cikin kewa da kaunar juna, fattu sai kuka take ta rungume Adeeb lokacin da suhaimat ta tafi rarrashinta yayi tayi da gyar ya samu tayi barci.

Ammi kuwa sosai taji dadin tafiyar suhaimat,dan hankalinta sam bai kwanta ba ,gani take kamar zata iya gano wani abu game da fattu

Yanzu damuwarta daya shine yadda ,zata bullowa lamarin Adeeb.

Rashad ya farfaɗo ,saidai gaba ɗaya ankasa gane  kansa ,dan kullum haka zaka ganshi shiru baya magana saidai kallo,abin yana matukar damun amma,haka zatayi ta kuka tana kallonsa,saidai kawai kaga hawaye yana bin fuskar Rashad din,ya rame sosai,dan baya wani cin abinci,ga karaya ajikinsa ta ko ina likitoci suna ta binciken kwakwalwarsa dan suna tunanin tanan ya sami  matsala.saidai muce Allah ya bashi lafiya.

Sam yanzu Adeeb baya  kula tareeƙ ,haka zai zo yayi ta bashi haƙuri amma Adeeb bazai ce masa ko ci kankaba.duk da yadda yayi kewar tareeƙ ɗin cikin zuciyarsa.

Abin yana yiwa tareek ciwo ,haka zai je gurin nanny yayi ta kuka ,saidai tabashi hakuri.

Alhamdullah jikin fattu ya warke sosai,dan duk tabon ciwukanta ma babu,sosai shakuwa ta kara shiga tsakaninta da Adeeb,dan kuwa ya dawo da ita bangaren sa gaba ɗaya ,ya siyo mata sabbin kayan sawa ,da duk wani abu datake bukata.

Yayin da gefe guda yake ci gaba da bincikensa akan al'amarin su Nazli da kuma sarƙar nan ta fattu,akan ammi ,saidai har yanzu ya kasa samun wata kwakwkwarar hujja da zai kama ammi da ita .dan haka ya kara yarda cewar hadin bakine na amma da nanny ,suke son hadashi da ammi.

"Wayyo mai martaba na tuna kayimin rai ka daina dukana wayyo Allah kumatuna"

Kafin ta gama rufe baki kawai taji duka ta ko ina,fuskanta abie keyi kamar ya sami kayan wanki,tun tana ihu tana neman taimako harta kasa daga koda Dan yatsantane,jini ta baki ta hanci.da gyar Adeeb ya janye abie,kuka sosai abie keyi,tanadin"kin cuceni,kin zalunceni,Allah ya isa tsakanina dake,kuma na sakeki saki daidai har uku,sannan saikin girbi abinda kika shuka,muguwa makirar mace,kuma maza maza ki sanar dani dalilin ki na batar da wannan yarinyar daga ahalinta"

Abie ya faɗa cikin rawar murya yana kamo hannun fattu ya matso da ita kusa da ammi ,wacce ke kwance cikin mugun yanayi,ko motsin kirki batayi,gaba ɗaya jikinta ya saki,da gyar take fidda numfashi,

Idonta daya ya kumbura suntum,bakinta ma ya aune, kamamaninta duk sun sauya. Banda kuka ba abinda fattu keyi,gana daya atsorace take jikinta rawa kawai yake tana kallon ammi.

Cikin tsawa abie yace "bazakiyi magana ba,saina karasaki"ya fada yana kai mata kafa,

Wani wahalallen ƙara ammi ta sanya,cikin azaba tana ɗan bude idon ta daya"zanyi bayani, zanyi bayani dan Allah kuyi min rai,tabbas wannan yar gidan suhaimat ce,kuma nice na batar da ita tun tana karama"

Ƙarar faduwar abu da sukaji ne yasashi saurin juyawa ɗan ganin ko menene,ba kowa bace face suhaimat da mijinta,wanda tareeƙ ya shigo dasu yanzun,kuma maganar ammi ta sauka akan kunnensu.....

Masu karatu muje zuwa,

Gada ammi kwance cikin mugun yanayi,wane fata ,zakuyi mata.

Ina mai nannadaddiyar fuska ne?

Muje zuwa, takuce anty mammy

Mrs babi□□

Share and comment fisabilillah.

More comment

More typing.

[8/29, 8:57 AM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE □□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Waziri kuwa,daskarewa yayi agurin,tsabar shiga ruɗu da yayi,sakamakon jin abinda tareeƙ ke faɗa.

Ihu ya sanya tare da faduwa agurin yana birgima da kuka.shikenan ya rasa yarsa, Zulaihat ta tafi ta barshi,ita kadaice yɾar da ya mallaka a duniya,yanzu gashi sakamakon mugun nufinsa ya rasata.kuka yake sosai cike da tarin nadama da dana sani.

Gaba daya sun ji mutuwar Zulaihat,cike da alhini suka dunguma har waziri,saidai yana karkashin kulawar dakaru,saboda karyayi yunkurin aikata wani abu.

Haka akayiwa Zulaihat wanka,tare da sallar gawarta aka kaita gidanta na gaskiya.sai muce Allah ya yafe mata kurakuranta.

,Kai tsaye daga gurin makoki,kurkuku aka wuce da waziri.

Sukuma suka dawo falon Sultan suka zauna.anan Adeeb ke sanar dasu Queen Suhaimat cewar akwai wanda ya rike fattu,ma'ana wanda ya tsinceta tun tana karama,kuma shine ya raineta harta girma.

Sannan shine mutumin da suka taimakeshi tare da Fattun.dan haka idan ansami nutsuwa yana  son  zasu tafi da fattu domin dubo halin da yake ciki.

Sultan Habeeb ne yayi gyaran murya kafin yace "ai wannan tafiya damu ya kamata ayi ta,dolene muje musaka masa da abinda yayi mana,dan kuwa ya cancanci yabo da kyautatawa agaremu"

Sultan ya faɗa cike da jinjinawa bawan Allah daya kula masa da ɗiyarsa.

Shiru falon yayi nadan lokaci kafin Adeeb yayi gyaran murya,yana mai kallon kowa cike jinjina maganar da yake son fadi.

Baisan ya zasu dauki maganar ba.ko zasu yarda da batun aurensa dake kan fattu? duba da yanayin shekarunta.

Dan haka cikin nutsuwa ya fara magana"Abie,uncle  da sauran mutanen dake cikin dakin nan,akwai Abinda nake son sanar daku,amma bansan ta yaya zaku fahimci maganar tawaba, saidai nayi hakan ne bada wata manufa ba,saidan kare hakkin addinina.yayi shiru yana da kallon yanayin fuskokinsu,kafin ya maida kallonsa ga fattu,wacce ke jikin mahaifiyarta,ta ɗora kanta akafadun innarta,jikinta yayi mugun sanyi,dan sosai taji mutuwar Zulaihat,dan adam ba abakin komai yake ba,yanzu duba fa dazun nan Zulaihat tana raye,amma yanzu har an kaita makwancinta.Allah kasa mudace.

Haɗa ido sukayi da Adeeb wanda yake kallonta cike da kauna,yana fatan Allah yasa iyayensu su yarda da batun auren dake tsakaninsa da fattu,dan bazai iya rayuwa ahalin yanzu batare da fattu ba.

Fattu ta zama jinin jikinsa,ta zame masa,mahadin  rayuwa,kuma farin cikinsa.

"Muna jinka dana, ka fadi abinda ke cikin ranka karka damu,zamu zama masu fahimtar ka"Sultan Habeeb ya faɗa yana mai dafa kafadun Adeeb,dan yana kusa dashi ne.

Jinjina kai Adeeb yayi kafin yaci gaba da faɗin"lokacin da zamu taho kasar nan da Fatima,nayi tunanin haramcin yin tafiya da yarinya mace,wacce ba muharramarka ba,dan haka,nayi shawara da tareeƙ akan cewar,zan auri Fatima in taho da ita amatsayin matata,kuma zata ci gaba da zama matsayin matar tawa,har zuwa lokacin da iyayen ta zasu bayyana.sai In sawwake mata ta koma garesu,lokacin da aka daura auren itama kanta bata sani ba,sannan tareeƙ shine wanda ya zama waliyyinta,shina bawa sadakinta,kafin aka daura mana aure.yayi dan shiru kansa akasa  kafin yaci gaba"awancan lokacin nayi aurenne da nufin idan iyayen Fatima suka bayyana zan sawwake mata,saidai kuma ahalin da ake ciki yanzu,bazan iya rabuwa da Fatima ba,ina rokon alfarmar ku barmu, mu rayu tare muci gaba da zama matsayin ma'aurata,domin ina sonta"Adeeb ya kai karshen zancen sa cike da faduwar gaba,yana fatan Allah yasa su amince da batunsa.

Ajiyar zuciya suka sauke dukansu, hakika wannan batun yayi matuƙar daɗaɗa musu rai,domin Adeeb mutum ne wanda duk wasu iyaye zasuyi fatan ya kasance mijin ga yarsu,dan haka ta bangaren su Queen Suhaimat kam,ba wata matsala,dan kallon juna sukayi ita da mijinta cike da jin dadi,suna murmushi.

Abie ma abun yayi masa daɗi,saidai dole abawa yarinyar da iyayenta dama,idan sun amince da batun auren shikenan,sannan itama yarinyar sai sunji ta bakinta idan ta amince shikenan.

Amma ma taji daɗin maganar Adeeb sosai,domin ta jima tana fatan ace,inama Adeeb  zai auri fattu,dan ta yaba da hankali da kuma nutsuwar fattu,saidai awancan lokacin ba damar fadin abinda ke cikin ranta.

Abie ne yayi murmushi cike da jin daɗi,kafin ya kalli Sultan Habeeb,ya fara magana"Sultan kaji abinda ɗan nata ya faɗa ko,ina fatan dai zuciyarka tana irin tunani da fatan da nakeyi, dan haka ina jiran jin ta bakinka,kaida mai dakinka"

Murmushi uncle Habeeb yayi kafin yace "ai ranka shi dade,wannan abun yayi min daɗi fiye da yadda kake tsammani,dan haka mudai ba abinda zamuce, sai Allah ya

haɗa kansu,ya basu zaman lafiya, sannan ya karesu daga dukkan sharrin abin ki"ya kai zancen sa fuskarsa ɗauke da murmushi.

Wani irin sanyin daɗi ne ya ratsa zuciyar Adeeb, Alhamdullah shikenan iyayen fattu ma sun amince da aurensu, shikenan bashi da wata matsala.

Kallonshi ya kai ga fattu,amma bai sami damar hada ido da itaba,dan kanta na duke,murmushi yayi wato  fattu irin  matan nan ne masu,kunyar ,hmmm zama ta ware ne ,dan shikam wllh zagewa zaiyi ya koyar da ita salon soyayya kala -kala,dan shi mutum ne mai son soyayya daga matarsa.

Hamdala abie yayi kafin yace "tunda yanzu mu Dukansu mun amince da wannan auren,yana da kyau muji ta bakin yarinyar,dan kar'ashiga hakkinta,tunda bada saninta akayi auren ba.dan haka Yʻata karki cuci kanki,ki sanar dani shin kin amince da wannan auren ko kuwa?"abie ya faɗa yana mai kallon fattu,da fatan Allah yasa itama tace ta amince.

Fattu kuwa kunyar duniya ta gama cika mata ciki,ji take kamar ƙasa ta tsage  ta shige ciki,yanzu ta yaya zata amsa muce cewar tana son Hamma?tab !wllh bazata iyaba.

Gaba ɗaya dakin yayi shiru,amsar fattu kawai ake jira,saidai ba alamun fattu zatace wani abu.

Kʻuri !!Adeeb ya kure fattu da ido,karfa Hulwa ta ki amincewa da aurensa?kai baya wannan tunanin, domin yasan Hulwa na sonsa sosai bazata taba kin zama dashi ba.dan haka kallonta yake danjin mezatace.

Ganin fattu ta kasa magana sai kara sunkuyar da kanta take,yasa ammi dafa kafadunta cikin murmushi tace "karki ji tsoro yata,ba wanda zaiyi miki dole,amsarki kawai ake bukata"nan ma dai shiru fattu tayi bata ce komai ba.kunya take ji sosai.

Ajiyar zuciya abie yayi kafin yace "to alamu dai sun nuna Fatima bata amince da wannan auren ba,dan haka habeebee dole kayi hakuri ka sawwake mata"abie ya faɗa yana kallon fattu dan ganin yanayinta.

Aikuwa da sauri ta ɗago kai tana zaro ido waje,cikin muryarta mai kama da shagwaba tace "a'a Abie nifa bance bana sonshi ba,dan Allah karkasa ya sakeni,na amince Nima Ina sonshi"fattu ta faɗa cike da kuruciyarta, idonta akan Adeeb.

Gaba daya saida ta basu dariya,dan dai kawai suna cikin alhinin rashin Zulaihat ne, ya hana su darawa.amma saida suka murmusa.

Ajiyar zuciya Adeeb yayi yana mai kafeta da ido,sosai yake jin tana kara shiga cikin zuciyarsa.

Koda su Sultan zasu koma Ghana,sun bukaci tafiya da fattu, domin ta gana da yan uwanta,sannan ta dan saba dasu,amma ba jimawa zatayi ba tunda da aurenta.

Adeeb ji yayi kamar ya kwalla ihu, dan yasan zai sha wahala zama ba tare da fattu ba,amma ba yadda ya iya dole ya amince,akan idan komai yayi daidai, zaizo sai su wuce Nigeria wajen baffa.

Queen suhaimat kuwa tayi hakanne,dan tana son ta gyara yarta sosai,yadda zata kara martaba agurin Adeeb.

Cikin yanayi na gajiyar jiki da zuciya,ga tarin kewar fattu da Adeeb ya fara tun yanzu,ya mike tare da cewa"Anty bari muje dan ta shirya kayanta"ya faɗa yana kallon fattu,fuska amarairaice.

Kallonsa fattu ma keyi,cike da tausayinsa,dakuma kewarsa,amma dole tabi iyayenta,dan kuwa tana bukatar jin duminsu ajikinta,sannan tana son ta san yan uwanta.

Queen suhaimat ce ta kalli fattu tace "Zara kije ki shirya kayanki maza "ta fada tana shafa kan diyar Tata cike da so da ƙauna.

Mikewa fattu tayi,cike da kunya,tabi bayan Adeeb dan tuni yayi gaba.

Tana fita ta ganshi ya jingina bayansa da jikin bango,idanunsa alumshe.tana zuwa ta tsaya akusa dashi,tare da sanya hannu ta rike hannunsa.ahanakli ya buɗe idonsa tare da saukewa akan kyakykyawar fuskarta.baice komai ba ya rike hannun nata suka nufi part dinsa.

Suna shiga ya janyota jikinsa ya rungume tsam.ahankali yake sauke ajiyar zuciya,idanunsa alumshe.fattu ma lumshe ido tayi cike da jin tsananin so da kaunar Adeeb cikin zuciyarta.

Ahankali ya fara magana"Hulwa komai yazo ƙarshe,Allah ya bayyana mana azzalumai,mun ganesu, yanzu lokacine da nake bukatar kulawar ki  da soyayya,saidai kuma gashi zakiyi nisa dani, alokacin da nake tsananin bukatarki kusa dani,Hulwa zanyi kewarki sosai"Adeeb ya faɗa cike da jin kewar fattu sosai yana kara kankameta ajikinsa.

Cike da tausayi fattu tace"Hamma nima fa zanyi kewarka, amma ai ba dadewa zanyi ba,ina son zama tare da iyayena,dan inji dadin da ake ji idan ana tare da su.amma Hamma zanyi kewarka sosai"itama ta faɗa ahankali tana mai ƙara kwantar da kanta cikin faffadan  kirjinsa.

Sun jima ahaka,rungume da juna,Adeeb yana ta saukewa fattuhadda, wanda har bata san lokacin da ta biye masa ba itama,duk abinda yayi mata, itama shi take masa.basu rabu da juna ba har saida Adeeb ya samu nutsuwa sosai.kafin suka daure suka rabu da jikin juna,sai lokacin fattu ta fahimci ko kaya babu ajikinsu.kunya ce ta kamata,da sauri ta janyo bargo ta rufe jikinta tare da lumshe idonta.

Murmushi Adeeb yayi yana mai gyara mata gashin kanta daya barbaje,kafin yace "Hulwa meye kuma na  rufe ido?nifa bana son wanna kunyar taki,Please ki buɗe ido ki kalleni,kinji?"ya faɗa yana hura mata iska akan idanunta.

Cikin wani irin salon murya mai cike da nishadin soyayya tace "Hamma Ni wllh kunya nakeji,kayi ta gane min jiki"ta faɗa ahankali tana rungumeshi.

Rungumeta shima yayi cike da soyayya kafin yace "hulwata idan ban kalli jikin ba,jikin wa zan kalla?jikinki mallakina ne,shine abinda zan kalla ya debemin kewa dan Allah karki hanani kallon abinda ke sani nutsuwa" ya faɗa cikin salon sa na shagwaba yana ɗan turo baki.

Murmushi fattu tayi tana mai kara cusa kanta akirjinsa,cike da kaunarsa.

Gaba daya sun shagala da nunawa juna soyayya,sun manta da su, Sultan Habib dake jiran fattu,saida wayar Adeeb tayi kara sannan suka farga,kiran Abie ne dan haka cike da kasala ya mika hannu ya daga wayar,

"To Abie gamunan "kawai ya faɗa tare da kallon fattu yace "Hulwa su anty na jiranmu"ya fada kamar zaiyi kuka.

Da sauri fattu ta mike tana zaro ido,wllh sam ta ma manta da batun tafiya Ghana,gaba ɗaya Hamma ya mantar da ita komai da soyayyarsa.

Shagwabe fuska tayi tana mai faɗin"Hamma kaga kasa na manta da su inna suna jirana ko?"ta fada tana nufar toilet da sauri tana tafe tana bubbuga kafa,ciki da tabara.

Lumshe ido Adeeb yayi yana mai faɗin "wayyo hulwata,zaki kasheni da salonki"kafin ya bita toilet din,wanka sukayi tare sannan suka fito,da kansa ya shirya fattu,kafin ya haɗa mata kayan da yasan zata bukata,sannan suka fito.

Haka Adeeb da Hulwa suka rabu cike da kewar juna,Adeeb ji yake kamar yayi kuka.

Tunda fattu ta tafi Ghana,kullum sai su wuni suna waya da Adeeb,sosai yake nuna mata yadda yayi kewarta,ita kuwa tausayinsa duk ya gama kamata,ba abinda yake son ji da gani sama dashi.saidai tayi tararrashinsa,tun tana kunyar fada masa kalamai harta zo ta daina,take zagewa tana nuna masa soyayya.

Ba irin gatan da fattu bata ganiba,agurin iyaye da danginta,kowa sonta yake,yana riritata,gyara kuwa tunda suka zo innarta ke fama,an tsuma fattu sosai,ta yadda da kanta wataran take jin tana bukatar Adeeb akusa da ita.

Tayi kyau jikinta ya kara gogewa,kallo ɗaya zaka mata kasan tana cikin jin dadi da annashuwa,komai yaji ajikinta.

Satinta biyu a ghana Adeeb ya kasa daurewa ya shirya kayansa yace ya tafi Ghana.

Amagarkama kuwa,lamarin ammi ya gwabe sosai,dan kuwa zuwa yanzu bai zama lallai ka gane ta ba,wasu abubuwa take tamkar na mahaukata,tayi ta  ihu kenan tana faɗin irin abubuwan da ta aikata,ƙafarta ɗaya ta lalace sakamakon ciwon da taji,banda wasu irin kuraje da suke fito mata masu tsananin karni da doyi.haka zatayi ta ihu tana yagunin jikinta.duk wanda yazo inda take,da gyar yake iya tserewa dan kuwa hauka take sosai,tana dukan mutane.hakan yasa aka kulle gurinta,saidai atura mata abinci ta kasan kofa.

Waziri kuwa,an yanke masa hukumcin daurin shekaru arba'in agidan yari, yayi nadama sosai kullum cikin kuka yake da neman gafara.

Rashad kuwa zuwa yanzu jiki alhamdullah,dan sosai yaji sauki walwalarsa ta dawo, Amma ma hankalinta ya kwanta sosai take kula da abie,abin sai godiyar Allah.

Ranar da Adeeb ya sanar da zuwansa Ghana,ba ƙaramin farin ciki fattu tayi ba,murna sosai takeyi har saida innarta ta fahimta,shiri akayi mata na musamman,cikin shiga irin ta ya'yan sarakuna, tayi matukar kyau kamar kasace ta ka gudu,sai ƙamshi take zubawa,gashi tadanyi kina kwanin sha'awa.

Wani kayataccen daki aka sauki Adeeb,ko ina yayi fes sai ƙamshi ke tashi,an jere masa kayan ciye- ciye,amma ko ruwa ya kasa sha,burinsa kawai yayi tozali da hulwarsa.

Wani sihirtaccen kamshine ya bugi hancinsa,wanda ya sanya shi saurin ɗago kai,cikin hanzari ya mike tsaye tare da kafe fattu da lumsassun idanunsa,wadanda ke cike da tarin gajiya da bukatar fattun tare da kewarta.

Murmushi take sakar masa cike da shaukin ganinsa.tana takawa kamar wata tarwada.

Cikin wani irin salo da zaƙuwa Adeeb ya bude mata hannayensa,alamun ta taho gareshi,da sauri ta ƙaraso tare da fadawa jikinsa,shikuma ya mayar da hannunsa ya rungumeta tsammm.

Muje zuwa masu karatu.

Mrs babi ce□□

Share and comment fisabilillah.

More comment

More typing.

[8/30, 3:14 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book

_____Ko a cikin jirgi fattu na kusa da baffanta,wanda yayi tsuru cike da tsoron jirgin,dan kuwa wannan shine karon farko daya hau jirgi.amma haka fattu ke kwantar masa da hankali har suka ƙarasa Ghana.

Part guda aka warewa baffa wanda ke dauke da duk wani kayan more rayuwa.baffa ya cika da farin cikin ganin irin rayuwar jin dadin da fattunsa keyi.abinci kala kala aka ajiye masa,har yama rasa wanda zaici.haka fattu keta zuba masa abincin tana tura masa.

Saida ya huta sosai nutsuwarta ta dawo jikinsa, sannan aka taru apart din da aka saukeshi, har Sultan Habib.godiya suka farayiwa baffa,bisa irin taimakon da yayiwa rayuwar yarsu,sannan suka ce suna bukatar yayi zamansa anan gurinsu,tunda bashi da kowa acan Nigeria.

Kuka kawai baffa keyi na gani yadda bayin Allah nan ke karramashi, suna son ya kasance tare dasu,amma wadanda ya taso cikinsu,haka suka koreshi korar kare bayan sun karbe masa dukiya.

Fattu ce ta dan turo baki tana kallon innarta da mahaifinta,kafin tace "Ni gaskiya ban yarda baffana ya zauna anan ba,tare zamu tafi dashi can gida,bana son yayi nesa dani,kuma shima yafi son zama kusa da fattunsa ko baffa"fattu ta faɗa cikin salon shagwabarta.

Murmushi baffa yayi,yace kwarai kuwa fattun baffa,duk inda kike to Nima Ina can koda kuwa cikin dokar dajine"baffa ya faɗa cikin murmushi.

Dariya sukayi suma,kafin mahaifin fattu yace "wato dai zara kin kwace mana baffanki ko?"ya faɗa da murmushi akan fuskarsa.

Dariya fattu tayi kafin tace "Allah ba haka bane daddy nayi kewar baffana,kuma nima inason in kula dashi,kamar yadda ya kula da rayuwata abaya"

Jinjina kai sukayi gaba ɗaya,suna ayyana irin kaunar dake tsakanin fattu da baffanta.

Kafin su bar kasar Ghana saida mahaifin fattu ya mallaka wa baffa kanfaninsa na ƙera takalma da jakunkuna,ya maida sunan sa akan takardun kamfanin,sannan ya bashi gida,wanda idan yazo zai rinka sauka aciki sannan ya damkawa fattu takardun gida dana kamfanin,harda mukullin sabuwar mota yar yayi.

Kuka sosai baffa yayi yana godiya,fattu ma tayi matukar murna sosai.adeeb kam godiya yayiwa Sultan habeeb,haka innar fattuma ba'a barta abaya ba,dinkuna ta sanya aka yiwa baffa,na gani na faɗa, masu kyau da tsada.sosai baffa ke yaba karamcin iyayen fattu,ba abinda zaice saidai Allah ya saka musu da aljanna.

Washe gari kuwa jirginsu ya daga zuwa Misra,fattu harda kukan rabuwa da yan uwanta,haka innarta ta cika ta da kayan gyara kala kala.

Wani ƙayataccen bangare su fattu suka sauka,wanda bayan tafiyarta Ghana ,Adeeb sanya aka kera musu.tsyawa fadar irin tsaruwar da bangaren yayi abune mai matukar wahala.kallo daya zakayiwa gurin kasan an kashe kudade makudai.

Baffama bangare guda aka ware masa inda zai zauna.haka yasha kyaututtukan gurin iyalan Adeeb,sannan shima Adeeb ya ba baffa kanfaninsa na motoci,baffa neman zaucewa yayi da irin wannan kyautukan da ake ta bashi.

Sosai ake girmama baffa cikin fadar,dan kowa yasan shidin waye.

Cikin lokaci kalilan baffa ya wanke yayi fes dashi,masha Allah kyakykyawan bafillatani,yayi kiba ya koma Alhaji sosai.ba jimawa suka shirya shida Adeeb da fattu dasu nanny sukaje suka sauke farali.

Sun dawo da kwana uku aka shirya gagarumin taron nadin Adeeb matsayin sarki.sannan ranar za'a gudanar da bikinsu shida fattu.

Anyi taro na ban mamaki wanda saida ya girgiza duniya,taron daya hada sarakunan hasashe daban daban,daga turawa,larabawa zuwa hausawa,ba kalar mutanen da babu agurin.

Taro yayi taro,an nada Adeeb matsayin sarkin misra,SULTAN ADEEB MUHAMMAD ASHRAF.

haka aka kammala taro ya tashi lafiya,kuma ranar Adeeb ya mallaka fattu dankareriyar mota mai shegen tsada da kyau,sannan ya mallaka mata kamfaninsa wanda ake hada mayukan shafawa na mata da kayan kwalliya.

Murna dai agurin fattu ba'a cewa komai.

Sati biyu da nada Adeeb matsayin Sarki,fattu ta kama laulayi, wayyo kuzo kuga murna gurin bayin Allah nan,haka nanny ta zage tana kula da fattu,ita da amma,suna bata gata da kulawa sosai,haka uban gayya,dan har kuka yayi lokacin

da labarin cikin fattu ya sameshi.kuma yayi mata alƙawarin idan ta haihu ta zabi inda take son zuwa yin karatu.

Cikin fattu nada wata biyar aka yi auren tareeƙ da wata yar uwarsa,rana daya aka daura auren dana Rashad,anyi biki na kece raini,su fattu sune akan komai na biki, zakuyi mamaki yadda fattu ta zama babbar mace,tayi mugun kyau har ta gaji,suna nunawa juna soyayya mai tsafta ita da Adeeb,yayin da suke rainon cikinsu cike da so da kauna.saidai fattu tana da girman ciki,dan yanzu haka inka ganta zaki tunanin cikin yakai wajen watanni bakwai, dan girmansa.

Komai yana tafiya daidai arayuwarsu fattu,basu da wata matsala yanzu,domin suna cikin aminci da kulawar yan uwa,sarauniya suhaimat da Sultan habeeb,sunyi matukar murna da samun cikin fattu,addu'oi kuwa,ba irin wanda fattu bata samu,domin takanas ake biyawamutane makka,dan suke suyi mata addu'a.

Lokacin da cikin fattu ya cika wata tara,ko tashi bata iyayi da kanta,saidai idan Adeeb ya tasheta idan tana zaune ko kwance,amma kasancewarta mai hakuri da kawaici,haka take daurewa tana nuna bata jin wahalar ciki,shikuwa Adeeb tausaya mata yake sosai.

Wata rana da safe suna barci nakuda ta kama fattu,aikuwa,nan da nan likitoci kwarraru,wadanda ke mata awo suka rufu akanta,cikin hikimar ubangiji,fattu ta haifi yaranta takwaye, mace dana miji masu matuƙar kama da Adeeb, kyakykyawa na ban mamaki.

Irin murnar da ahalin nan suka nuna abin ba'a cewa komai,ta ko ina zuwa ake ganin jarirai,ranar suna aka sanya musu sunan baffa dana Nazli,Abubakar,amma ana kiransu da Ameer da ameera.

Fattu ta sami alkairi sosai haihuwar yaran nan.dan motoci ma sun sami sama da guda sha biyar,banda gidaje da tsabar kudi.sai muce Allah ya raya twince.

Bayan suna da sati biyu aka daura auren baffa da nanny,bisa ga amincewarsu,bayan fattu tayi shawara dasu,ba nuna ja suka amince,dan dama sun kamu da son juna.

Ammi kullum abu sai kara lalacewa yake,hauka take tun ƙarfi,gaba ɗaya ta gama kwarzane jikinta,tananan kamar wata horuwa, tayi ta ihu tana yakushun jikinta.(ai

dama ammi hausawa sunce idan zaka gina ramin mugunta ka gina daidai da kai,hakkin rayukan da kika kashema kadai sun isheki)

Waziri ma yana gidan yari,saidai shikam yayi ladama,ya koma ga Allah,kullum yana istugfari.

Yaran fattu sun taso cikin kulawa da soyayya,idan kun gansu gurin fattu,to nono kawai zata basu,dan tuni ta fara karatunta ,tace anan gida zatayi karatu,bazata je ko ina ta bar mijinta ba.

Abin sai son barka,rayuwa tayi musu daɗi,suna zaune cikin kwanciyar hankali,fattu ta buɗe gidajen marayu ajahohin Nigeria sosai,ta taimakawa yan kauyen su,tayi musu makaranta, ga ruwa ya wadata,ta tallafawa mabukata, gaba ɗaya sunyi nadama abinda suka yiwa fattu da baffanta,dan lokacin da baffa yaje basu ganeshi ba,haka gwogwgo hansai tayi ta kuwa wai ya maidata  dakinta,dariya kawai yayi tare da bata makudan kudade kafin ya bar kasar.

Amare da angwanye ma suna zaune cikin aminck da soyayya,yayinda ko waccensu ke dauke da yaron ciki,saidai muce Allah ya raba lafiya.

Fattu ce zaune akan kujera tana bawa ameer nono,yayinda Adeeb ke gefenta riƙe da ameera,kallonta yeke cike da ƙauna da sha'awa,yadda take shayar da yaron cikin nutsuwa.

Ajiyar zuciya yayi tare da faɗin "Alhamdullah ,Allah na gode maka kacikani da ni'imarka ta ko ina ,ka bani mace mai hankali da nutsuwa,sannan ka hadamin kan ahalina,ka bani yara kyakykyawa har biyu a lokaci daya,Allah Nagode maka"Adeeb ya faɗa cike da kushu'i yana  mai jin dadi cikin ransa.

Murmushi fattu tayi tare da kamo hannunsa tayi kissing, sannan ta Dora kanta akan kafadunsa, tace "Ina sonka mijina kaine farin cikina,kuma rayuwata,Allah ya raya mana yaranmu bisa hanya madaidaiciya"

"Ameen Hulwa ana ahubbikteeer Hulwa anti sururi"ya faɗa yana mai kara rungumeta ita da yaran ajikinsa.

Tammat bi hamdillah.anan na kawo karshen wanna littafi Mai suna MACIJI NE.

Jinjina gareka mijina,na gode da gudunmawarka gareni,Allah ya bamu zaman lafiya,ya raya mana zuri'a.

Much love.

Godiya ta musamman gareki,maman nafi,na gode sosai da gudun mawarki akan wannan littafi.

Gaisuwa gareku macijine fans inq kaunarku.

Jinjina ga elegant online writers,Allah ya hade kanmu.

Ina godiya gareku yan uwana,da addu'ar ku gareni □□□

Allah ya sa mu amfana da darasin dake cikinsa,muyi watsi da sharrin dake cikinsa.

Allah ka yafe mana kuraruranmu,kasanya imaninmu ya nunku fiye da nada.

Godiya agareku masoyansa ,da kukayi ta bibiyar wannan littafi,tun daga farko har karshe,Allah ya hadamu gidan aljanna.

Sai mun haɗe daku cikin sabon littafina

RAINON DAWA.

Ga mai bukata,zai fita kudinsa kamar haka.

Normal group 300₦

Special group 500₦

Manyan mata masu bukata ta private,kuma ga naku1000₦

Zaku biya ta wannan acc. Din.

Saratu Kabir

U.b.a

2215749011.

Evidence of payment

08148360851

Saina jiku masoya.

Show me You love,

Kuyi payment na wannan littafin.□□□

Kada kusake baku labari.

Saina jikiku.

Takuce har kullum anty mammy.

Mrs babi□□

[8/30, 3:14 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Cikin wani irin salo wanda ke nuna tsantsar farin ciki da zaƙuwa,Adeeb ya bude hannayensa,alamun fattu ta taho gareshi.

Da sauri fattu ta ƙaraso gareshi,cikin takunta mai jan hankali,tare da fadawa jikinsa tana murmushi.

Maida hannunsa yayi ya kulle tare da rungume fattu tsamm,ajikinsa.

Atare suka sauke ajiyar zuciya,wacce ke nuna tsantsar kewar juna da sukayi.

Banda ajiyar zuciya ba abinda Adeeb ke saukewa,kamar wanda yayi wasan tsere.

Ahankali cikin murya mai tattare da shauki yace "I miss You so much  Hulwa"ya faɗa yana kare matseta akirjinsa,kamar zai maidata cikinsa.

Kusan minti biyar suka dauka ahaka,kafin Adeeb yayi karfin halin ɗago da fattu daga jikinsa yana kallon kyakykyawar fuskarta.gani yake kamar ba fattunsa ba,kamar wanda aka sauya masa ita,tayi kyau matuka,ta kara gogewa kai kace acikin ƙanƙara tare rayuwa.

Fattu ma kallonsa take cike da jin zazzafar kaunarsa na ratsa jini da tsokarta,dan gani tayi yayi mata kyau sosai,ya ɗanyi kiba kaɗan ya kara fari,ga sajen da ya kara ajiye wa yayi matuƙar ƙawata fuskarsa.

Ahankali ta kai hannunta tare da shafa gefen fuskarsa,lumshe ido yayi yana mai jin sanyi cikin ransa.cike da son nunawa Adeeb yadda tayi kewarsa ta kai bakinta kan nashi,ta fara kissing dinsa,kawai sai jin bakin fattu yayi cikin nashi.

Ai kamar mayen karfe haka Adeeb ya karbe lips din fattu ya fara sha kamar ya sami lollipop.

Tun abun yana karami har yazama babba,dan sun kasa rabuwa da juna,ganin suna neman faduwa ne yasa su zubewa akan lafiyayyar kujerar dake kusa dasu.adeeb bai bar wannan dama ba ,saida ya kara angoncewa, sosai ya shiga ruɗu da gigita,ɗan jin fattu yayi kamar bai taba ma saninta matsayin ya mace ba,sosai ya nishadantu da ni'imarta,ya rikice mata sosai haka yayi ta sunbatu yana hawaye.albarka kuwa fattu ta shata ba adadi da kyaututtuka kala kala.

Saida suka sami nutsuwa kafin Adeeb ya samu yaci abinci.anan dakin sukayi wanka tare,gaba ɗaya Adeeb ya kara kwarewa fattu,ko yaya tayi motsi hankalinsa na kanta,wani irin so yake mata marar misaltuwa.fattu duk da taji zafi amma haka ta daure bata nunawa Adeeb raki ba.nan suka shantake suna nunawa juna so da kauna,dama tuni Adeeb ya mika gaisuwa ga Sultan Habib da innar fattu.

Dan haka salla ma acikin dakin nan yakeyinta. Fattu kuwa ranar ta yabawa aya zaƙinta,dan ta tabbatar da cewar Adeeb yayi kewarta,kuma shidin jarumi ne na gaske.

Washe gari suka tashi daga Ghana zuwa Nigeria,da tareeƙ akayi tafiyar,dan dama tare suka zo da Adeeb,shiya sauka a masauki na daban.

Kai tsaye a Jos suka sauka,kafin suka nufi kauyen su fattu cikin dalla dallan motocinsu.

fattu da Adeeb cikin mota daya suke,yana rungume da ita ajikinsa,motar su ce agaba,ko kaɗan fattu bata manta hanyar kauyen nasu ba,dan haka tana lura da inda suke nufa.

Sai motar Sultan Habib shida innar fattu dasu zayyad.

Kauyen yana nan inda fattu ta sanshi, ba abinda ya sauya.gidansu ta fara hangowa,cike da doki take nunawa Adeeb gidan"Hamma ga gidanmu can,yanzu zanga baffana,Hamma bazan iya kwatanta irin farin cikin da nake ciki ba"fattu ta faɗa tana rike hannun Adeeb cike da murna idanunta ya cika da kwalla.

Murmushi yayi,dan shima saiya tsinci kansa cikin farin ciki, ganin yadda Hulwarsa ke farin ciki.

"Nima ina farin ciki Hulwa zataga baffanta,saidai anya kuwa zai gane ki?Adeeb ya faɗa yana kallonta da murmushi.

Cikin doki da dariya fattu tace "wllh zai ganeni,ko me nazama na tabbata baffana zai ganeni kuma zaka gani"ta fada daidai lokacin da sukayi facking akofar gidansu fattu.

Da hanzari fattu ta buɗe kofar motar ta fito,bata ko tsaya sauraron Adeeb ba,burinta kawai tayi tozali da baffa.da sallama ta shiga cikin gidan tana rarraba ido dan ganin ta inda zataga baffanta.

Ba kowa cikin tsakar gidan,gaba ɗaya gidan yayi datti,ko ina kazantace cikinsa.jin sallama yasa gwogwgo hansai fitowa daga cikin dakinta,tana ta soshe soshen kwarkwata.

"Waye yau agidan nan nawa?rabon da naji wani yazo gidan nan,harna manta,kodai Hau.....maganar gwogwgo hansai ta makale sakamakon ganin wata balarabiyar yarinya da tayi tsaye fuskarta ɗauke da murmushi.

Cikin rawar jiki gwogwgo hansai ta fara fadin"maraba lalle baiwar Allah,daga ina?wa kike nema kodai gidan mai gari kike nema?"gwogwgo hansai ta fada cikin rawar jiki tana kallon fattu.

Dariya fattu tayi tana kallon gwogwgo Hansai,duk ta rame tayi baki sosai gashi ta tsufa,kallo ɗaya zakayi mata kasan tana cikin wahalar rayuwa.

"Gwogwgo,baki ganeni ba ?nice fa,nice fattun baffa"fattu ta faɗa tana kama hannun gwogwgo Hansai ba tare da gyama ba.

Galala gwogwgo tayi tana kallon fattu,cike da ƙaryata abinda fattun ta fada,saidai kuma wa yasan fattun awani guri?bare yazo yayi mata wasa.cikin rawar murya tace "fa....t.t.tu,kece haka ?kece kika zama kamar balarabi?ina kika je kika zama mai kudi haka?ta fada tana shashshafa fattu.

Dariya fattu tayi kafin tace" nice gwogwgo tare muke da iyayena fa da hammana,suna waje bari nace su shigo,wai ina baffana ne tunda na shigo nake nemansa"fattu ta faɗa cike da doki tana nufar waje.

Lokacin da ta fita atsaye ta tarar da itayenta da Adeeb,mutanen garin sun zagayesu suna kallonsu da shafa motar da suka fito daga ciki.

Bata damu da mutanen gurinba tacewa su Adeeb su shigo.

Murna take sosai kamar wacce akayiwa bushara da gidan aljanna.

Gwogwgo Hansai jiki na rawa ta shimfida musu wata rubabbiyar tabarmar kaba.ko kaɗan basu nuna mata gyamaba suka zauna.

Bayan gaishe gaishene, gwogwgo tayi ta kuka tana bawa fattu hakuri,itadai fattu burinta daya taji ina baffanta yake.

Nan gwogwgo Hansai ta sanar da ita duk abinda ya faru da baffa,ranar da suka bar garin.

Kuka sosai fattu ta sanya,tana jin wani irin kunci cikin zuciyarta,ina zata ga baffa? mutumin daya tallafi rayuwarta ,ya bata kulawa,wayyo Allah.haka fattu tayi ta kuka,ajikin Adeeb yana rarrashinta.

Gwogwgo Hansai cikin nadama take faɗin"bayan tafiyar malam,gaba ɗaya lamari ya lalace garin nan,kowa abinda yake so shi yakeyi,haka inaji ina gani,yarana mata sukayi cikin shege,yanzu haka bansan duniyar da suka shiga ba,shima namijin tuni ya zama rikakken barawo,yayiwa yar mutane fyade shine ya gudu,ya bar rugar nan.mai gari yana nan ya zama gurgu,jauro kuwa abarsa ta lalace har yanzu bata da amfani,haka haroji yana na da fuska kamar ta dodo,saidai yaje Bara cikin gari,dan Allah fattu ki yafe mana ,nasan hakkinkine ke bibiyarmu"gwogwgo Hansai ta fada cikin kuka.

Haushin ta sosai Adeeb yakeji,dan yasan kadan daga cikin mugayen halayenta.

Tashi sukayi domin barin rugar,dan bawani amfanin zamansu,tunda wanda suka zo gurinsa baya nan.

Kudi mai yawa sultan habib ya bawa gwogwgo hansai,sai murna take tana godiya,haka ya tabawa mutanen kauyen ma kafin suka bar garin.

Kuka sosai fattu keyi ajikin Adeeb,ta shiga damuwa mai tarin yawa,haka yayi ta rarrashinta,har suka iso cikin garin jos.

Wata babbar motace tayi faci akan tsakiyar kwalta,hakan ya haddasa go slow agurin,suna tsaye cikin mota,masu bara sai zuwa suke suna Bara.

Wani dattijone cikin shiga ta almajirai,kallo ɗaya zakayi masa kasan yana shan wahala yazo jikin motar su fattu yana Bara,kasancewar gilas din motar irin mai duhun nan ne,yasa na waje baya ganin na ciki.

Fattu ce tayi firgigit tatashi daga jikin Adeeb tana kallon tsohon dake barar.

Wani dan ihu ta sanya tana mai ƙoƙarin buɗe kofar motar.kira take

"Hamma baffana,baffana"tana faɗa cikin rawar jiki tana kokarin buɗe motar.

Da sauri shima Adeeb ya kai kallonsa inda fattun ke nuna masa.

Tabbas baffa ne kuwa.gana ɗaya fattu ta rikice tana kici kici buɗe kofar Amma tsabar farin ciki tama kasa,budewar sai kira take"baffana,baffana"

Hannunta Adeeb ya riko yace "ki nutsu hulwa,karkije kiki ciwo kinji bari muje gurin baffan"ya faɗa yana bude kofar motar.

Da sauri fattu ta fito daga cikin motar ta nufi gurin mutumin da yayi dan gaba dan zuwa wajen wata motar ya sami sadaka.

Da sauri ta kamo hannunsa tana faɗin "baffana kaine,haka ?"cikin azama baffa ya juyo sakamakon jin Muryar da akullum saiyayi kukan rashin ta,kuma duk kuɗin da yake samu na bara tarawa yake,dan yayi ta zaga garuruwa yana neman fattu,yasan watarana zasu hadu.

Jifa yayi da dan buhun dake hannunsa,wanda yake tara kudin barartasa ciki.

"Fattu,kece"baffa ya faɗa cike da shauki.

Kuka fattu keyi tana kallon baffa,kafin ta rungumeshi ajikinta tana kuka.shima baffa kuka yake cike da godewa Allah,yau gashi ga fattunsa,shikenan burinsa ya cika.

Sultan habib,da innar fatyu ma,fitowa sukayi,dan kobasu tambaya ba,sunsan wanna shine baffan fattunsu.

Adeeb kansa saida yaji kwalla ta cika masa ido,dan tausayin tsohon da yadda ya koma.

Horn din da motoci ke musu ne ya dawo dasu cikin hayyacinsu,dan tuni an janye motar data haddasa go slow ɗin,dan haka cikin hanzari suka shige mota dan ba mutane hanya.

Motar su fattu baffa ya shiga,su Sultan ma suka koma cikin tasu ,sannan suka bar gurin.

Kai tsaye gidan da suka sauka suka koma,dan yau suke don komawa Ghana,

Fattu sai murna take daga ga baffanta.

Wanka kawai suka bari baffa yayi,aka bashi wasu kayan ya sanya,kafin suka daga sai Ghana....

Masu karatu bari muyi musu rakiya zuwa ghanar muma.

Ina kuke

Masoya anty mammy?

Albishirinku,ina mai farin cikin sanar daku,sabon littafina mai suna RAINON DAWA,yana nan akan hanya,da zarar mun kammala MACIJINE,hmmmm

Daga jin sunan kinsan ba magana.

Karku bari abaku labari.

Ga mai bukata ,zai iya biyan kudinsa tun yanzu,domin nan da kwana uku zaku fara samun wannan kayataccen labarin na RAINON DAWA.

akan fashi mai sauki,

Normal group 300

Special group 500

Sannan akwai manyan mata dake son atura musu private to kuma ga naku farashi,1000

Dan haka saina jiku,

Acc. No.

Saratu kabir

A.u.b

2215749011

Saiku nuna shadar biya ta wannan no.

08148360851

Saina jiku,masoya.

Show ne your love akan novel ɗi Nan,

😍😍😍□□□□

Mrs babi ce□□[8/30, 3:14 PM] ^^Hawwarh___jiddarh□: □□□□□□□□

MACIJI NE□□□

Na mammy kabeer

(Anty mammy)

Elegant online writers□□

Free book



_____Ko a cikin jirgi fattu na kusa da baffanta,wanda yayi tsuru cike da tsoron jirgin,dan kuwa wannan shine karon farko daya hau jirgi.amma haka fattu ke kwantar masa da hankali har suka ƙarasa Ghana.

Part guda aka warewa baffa wanda ke dauke da duk wani kayan more rayuwa.baffa ya cika da farin cikin ganin irin rayuwar jin dadin da fattunsa keyi.abinci kala kala aka ajiye masa,har yama rasa wanda zaici.haka fattu keta zuba masa abincin tana tura masa.

Saida ya huta sosai nutsuwarta ta dawo jikinsa, sannan aka taru apart din da aka saukeshi, har Sultan Habib.godiya suka farayiwa baffa,bisa irin taimakon da yayiwa rayuwar yarsu,sannan suka ce suna bukatar yayi zamansa anan gurinsu,tunda bashi da kowa acan Nigeria.

Kuka kawai baffa keyi na gani yadda bayin Allah nan ke karramashi, suna son ya kasance tare dasu,amma wadanda ya taso cikinsu,haka suka koreshi korar kare bayan sun karbe masa dukiya.

Fattu ce ta dan turo baki tana kallon innarta da mahaifinta,kafin tace "Ni gaskiya ban yarda baffana ya zauna anan ba,tare zamu tafi dashi can gida,bana son yayi nesa dani,kuma shima yafi son zama kusa da fattunsa ko baffa"fattu ta faɗa cikin salon shagwabarta.

Murmushi baffa yayi,yace kwarai kuwa fattun baffa,duk inda kike to Nima Ina can koda kuwa cikin dokar dajine"baffa ya faɗa cikin murmushi.

Dariya sukayi suma,kafin mahaifin fattu yace "wato dai zara kin kwace mana baffanki ko?"ya faɗa da murmushi akan fuskarsa.

Dariya fattu tayi kafin tace "Allah ba haka bane daddy nayi kewar baffana,kuma nima inason in kula dashi,kamar yadda ya kula da rayuwata abaya"

Jinjina kai sukayi gaba ɗaya,suna ayyana irin kaunar dake tsakanin fattu da baffanta.

Kafin su bar kasar Ghana saida mahaifin fattu ya mallaka wa baffa kanfaninsa na ƙera takalma da jakunkuna,ya maida sunan sa akan  takardun kamfanin,sannan ya bashi gida,wanda idan yazo zai rinka sauka aciki sannan ya damkawa fattu takardun gida dana kamfanin,harda mukullin sabuwar mota yar yayi.

Kuka sosai baffa yayi yana godiya,fattu ma tayi matukar murna sosai.adeeb kam godiya yayiwa Sultan habeeb,haka innar fattuma ba'a barta abaya ba,dinkuna ta sanya aka yiwa baffa,na gani na faɗa, masu kyau da tsada.sosai baffa ke yaba karamcin iyayen fattu,ba abinda zaice saidai Allah ya saka musu da aljanna.

Washe gari kuwa jirginsu ya daga zuwa Misra,fattu harda kukan rabuwa da yan uwanta,haka innarta ta cika ta da kayan gyara kala kala.

Wani ƙayataccen bangare su fattu suka sauka,wanda bayan tafiyarta Ghana ,Adeeb sanya aka kera musu.tsyawa fadar irin tsaruwar da bangaren yayi abune mai matukar wahala.kallo daya zakayiwa gurin kasan an kashe kudade makudai.

Baffama bangare guda aka ware masa inda zai zauna.haka yasha kyaututtukan gurin iyalan Adeeb,sannan shima Adeeb ya ba baffa kanfaninsa na motoci,baffa neman zaucewa yayi da irin wannan kyautukan da ake ta bashi.

Sosai ake girmama baffa cikin fadar,dan kowa yasan shidin waye.

Cikin lokaci kalilan baffa ya wanke yayi fes dashi,masha Allah kyakykyawan bafillatani,yayi kiba ya koma Alhaji sosai.ba jimawa suka shirya shida Adeeb da fattu dasu nanny sukaje suka sauke farali.

Sun dawo da kwana uku aka shirya gagarumin taron nadin Adeeb matsayin sarki.sannan ranar za'a gudanar da bikinsu shida fattu.

Anyi taro na ban mamaki wanda saida ya girgiza duniya,taron daya hada sarakunan hasashe daban daban,daga turawa,larabawa zuwa hausawa,ba kalar mutanen da babu agurin.

Taro yayi taro,an nada Adeeb matsayin sarkin misra,SULTAN ADEEB MUHAMMAD ASHRAF.

haka aka kammala taro ya tashi lafiya,kuma ranar Adeeb ya mallaka fattu dankareriyar mota mai shegen tsada da kyau,sannan ya mallaka mata kamfaninsa wanda ake hada mayukan shafawa na mata da kayan kwalliya.

Murna dai agurin fattu ba'a cewa komai.

Sati biyu da nada Adeeb matsayin Sarki,fattu ta kama laulayi, wayyo kuzo kuga murna gurin bayin Allah nan,haka nanny ta zage tana kula da fattu,ita da amma,suna bata gata da kulawa sosai,haka uban gayya,dan har kuka yayi lokacin da labarin cikin fattu ya sameshi.kuma yayi mata alƙawarin idan ta haihu ta zabi inda take son zuwa yin karatu.

Cikin fattu nada wata biyar aka yi auren tareeƙ da wata yar uwarsa,rana daya aka daura auren dana Rashad,anyi biki na kece raini,su fattu sune akan komai na biki, zakuyi mamaki yadda fattu ta zama babbar mace,tayi mugun kyau har ta gaji,suna nunawa juna soyayya mai tsafta ita da Adeeb,yayin da suke rainon cikinsu cike da so da kauna.saidai fattu tana da girman ciki,dan yanzu haka inka ganta zaki tunanin cikin yakai wajen watanni bakwai, dan girmansa.

Komai yana tafiya daidai arayuwarsu fattu,basu da wata matsala yanzu,domin suna cikin aminci da kulawar yan uwa,sarauniya suhaimat da Sultan habeeb,sunyi matukar murna da samun cikin fattu,addu'oi kuwa,ba  irin wanda fattu bata samu,domin takanas ake biyawamutane makka,dan suke suyi mata addu'a.

Lokacin da cikin fattu ya cika wata tara,ko tashi bata iyayi da kanta,saidai idan Adeeb ya tasheta idan tana zaune ko kwance,amma kasancewarta mai hakuri da kawaici,haka take daurewa tana nuna bata jin wahalar ciki,shikuwa Adeeb tausaya mata yake sosai.

Wata rana da safe suna barci nakuda ta kama fattu,aikuwa,nan da nan likitoci kwarraru,wadanda ke mata awo suka rufu akanta,cikin hikimar ubangiji,fattu ta haifi yaranta takwaye, mace dana miji masu matuƙar kama da Adeeb, kyakykyawa na ban mamaki.

Irin murnar da ahalin nan suka nuna abin ba'a cewa komai,ta ko ina zuwa ake ganin jarirai,ranar suna aka sanya musu  sunan baffa dana Nazli,Abubakar,amma ana kiransu da Ameer da ameera.

Fattu ta sami alkairi sosai haihuwar yaran nan.dan motoci ma sun sami sama da guda sha biyar,banda gidaje da tsabar kudi.sai muce Allah ya  raya twince.

Bayan suna da sati biyu aka daura auren baffa da nanny,bisa ga amincewarsu,bayan fattu tayi shawara dasu,ba nuna ja suka amince,dan dama sun kamu  da son juna.

Ammi kullum abu sai kara lalacewa yake,hauka take tun ƙarfi,gaba ɗaya ta gama kwarzane jikinta,tananan kamar wata horuwa, tayi ta ihu tana yakushun jikinta.(ai dama ammi hausawa sunce idan zaka gina ramin mugunta ka gina daidai da kai,hakkin rayukan da kika kashema kadai sun isheki)

Waziri ma yana gidan yari,saidai shikam yayi ladama,ya koma ga Allah,kullum yana istugfari.

Yaran fattu sun taso cikin kulawa da soyayya,idan kun gansu gurin fattu,to nono kawai zata basu,dan tuni ta fara karatunta ,tace anan gida zatayi karatu,bazata je ko ina ta bar mijinta ba.

Abin sai son barka,rayuwa tayi musu daɗi,suna zaune cikin kwanciyar hankali,fattu ta buɗe gidajen marayu ajahohin Nigeria sosai,ta taimakawa yan kauyen su,tayi

musu makaranta, ga ruwa ya wadata,ta tallafawa mabukata, gaba ɗaya sunyi nadama abinda suka yiwa fattu da baffanta,dan lokacin da baffa yaje basu ganeshi ba,haka gwogwgo hansai tayi ta kuwa wai ya maidata  dakinta,dariya kawai yayi tare da bata makudan kudade kafin ya bar kasar.

Amare da angwanye ma suna zaune cikin aminck da soyayya,yayinda ko waccensu ke dauke da yaron ciki,saidai muce Allah ya raba lafiya.

Fattu ce zaune akan kujera tana bawa ameer nono,yayinda Adeeb ke gefenta riƙe da ameera,kallonta yeke cike da ƙauna da sha'awa,yadda take shayar da yaron cikin nutsuwa.

Ajiyar zuciya yayi tare da faɗin "Alhamdullah ,Allah na gode maka kacikani da ni'imarka ta ko ina ,ka bani mace mai hankali da nutsuwa,sannan ka hadamin kan ahalina,ka bani yara kyakykyawa har biyu a lokaci daya,Allah Nagode maka"Adeeb ya faɗa cike da kushu'i yana  mai jin dadi cikin ransa.

Murmushi fattu tayi tare da kamo hannunsa tayi kissing, sannan ta Dora kanta akan kafadunsa, tace "Ina sonka mijina kaine farin cikina,kuma rayuwata,Allah ya raya mana yaranmu bisa hanya madaidaiciya"

"Ameen Hulwa ana ahubbikteeer Hulwa anti sururi"ya faɗa yana mai kara rungumeta ita da yaran ajikinsa.

Tammat bi hamdillah.anan na kawo karshen wanna littafi Mai suna MACIJI NE.

Jinjina gareka mijina,na gode da gudunmawarka gareni,Allah ya bamu zaman lafiya,ya raya mana zuri'a.

Much love.

Godiya ta musamman gareki,maman nafi,na gode sosai da gudun mawarki akan wannan littafi.

Gaisuwa gareku macijine fans inq kaunarku.

Jinjina ga elegant online writers,Allah ya hade kanmu.

Ina godiya gareku yan uwana,da addu'ar ku gareni □□□

Allah ya sa mu amfana da darasin dake cikinsa,muyi watsi da sharrin dake cikinsa.

Allah ka yafe mana kuraruranmu,kasanya imaninmu ya nunku fiye da nada.

Godiya agareku masoyansa ,da kukayi ta bibiyar wannan littafi,tun daga farko har karshe,Allah ya hadamu gidan aljanna.

Sai mun haɗe daku cikin sabon littafina

RAINON DAWA.

Ga mai bukata,zai fita kudinsa kamar haka.

Normal group 300₦

Special group 500₦

Manyan mata masu bukata ta private,kuma ga naku1000₦

Zaku biya ta wannan acc. Din.

Saratu Kabir

U.b.a

2215749011.

Evidence of payment

08148360851

Saina jiku masoya.

Show me You love,

Kuyi payment na wannan littafin.□□□

Kada kusake baku labari.

Saina jikiku.

Takuce har kullum anty mammy.

Mrs babi